# PIVOTAL TEACHER TRAINING PROGRAMME (PTTP)

# FOR UNIVERSAL BASIC EDUCATION (UBE)

## COURSE BOOK

## ON

# HAUSA LANGUAGE


NATIONAL TEACHERS' INSTITUTE



JUNE 2013

# FOREWORD

The National Teachers' Institute was established by the Decree No. 7 of 1978 to organize programmes for training, developing, upgrading and certification of teachers at all levels. In pursuance of this mandate, the NTI has trained and or upgraded over two million teachers at various levels (PTTP, NCE, ADE, and PGDE) through Open and Distance Learning (ODL) since its inception.

Following Federal government's introduction of the Universal Basic Education (UBE), And the mandate for the Institute to train teachers to meet the nation's urgent need for a large number of qualified teachers through Pivotal Teacher Training Programme (PTTP), the Institute produced course books in Education, English language, Mathematics, Integrated Science, Social Studies, Physical and Health Education, Hausa, Igbo, Yoruba, Christian Religious Studies, Islamic Religious Studies, Home Economics, and Agricultural Science in 2000. Since then, thousands of teachers have benefitted from this broad-based laudable programme and a growing number of states are demanding for it.

In the light of the above, and the need to include more up-to-date developments in pedagogy, the Institute deemed it necessary to revise the course books as well as make them reader-friendly and much less cumbersome. These 2013 second editions are also closely tailored to the latest NCE curriculum. Most of the authors are very seasoned teacher educators from the university faculties of education and colleges of education. The course books combine meaty substance in subject matter and effective current teaching methods.

Without any breach of modesty, we believe that our PTTP trainees will benefit immensely from these course books. All those who have contributed, in one way or the other, deserve special commendation for this effort.

***Dr. Aminu Ladan Sherehu***

**Director General & Chief Executive**

**Table of Contents**

**Pages**


| | | |
|---|---|---|
| **FOREWORD** | | **i** |
| **FASALI NA 1: INSHA'I** | | **1** |
| KASHI NA 1: | {A'IDOJIN RUBUTU | 1 |
| KASHI NA 2: | ALAMOMIN KYAUTATA RUBUTU | 3 |
| KASHI NA 3: | MA'ANAR INSHA'I | 6 |
| KASHI NA 4: | INSHA'I (LABARI, SIFFANTAWA, MUHAWARA, WASI{A) | 9 |
| KASHI NA 5: | SHIFTA DA INSHA'I | 11 |
| KASHI NA 6: | RUBUTUN JAWABI MAI LINZAMI | 13 |
| **FASALI NA 2: FURUCI DA GININ KALMA** | | **13** |
| KASHI NA 1: | BA{A{E | 13 |
| KASHI NA 2: | WASULLAN HAUSA | 17 |
| KASHI NA 3: | MA'ANAR KALMA | 19 |
| KASHI NA 4: | RABE RABEN KALMOMI | 22 |
| KASHI NA 5: | GA\|AR KALMA A HAUSA | 26 |
| KASHI NA 6: | SAIWA DA [AFE-[AFENTA | 29 |
| KASHI NA 7: | [AFA GOSHI | 33 |
| KASH1 NA 8: | [AFA - CIKI | 36 |
| KASHI NA 9: | [AFA {EYA | 39 |
| **FASALI NA 3: NAHAWU DA AMFANI DA SHI** | | **43** |
| KASHI NA 1: | JUMLAR HAUSA | 43 |
| KASHI NA 2: | SASHEN SUNA DA RABE-RABENSA | 46 |
| KASHI NA 3: | SASHEN AIKATAU | 48 |
| KASHI NA 4: | JUMLOLI MASU HARSHEN DAMO | 50 |
| KASHI NA 5: | RARRABA SUNAYE, TSAMO SUNAYE DA GANO SASSAN JUMLA | 52 |
| KASHI NA 6: | NAZARIN GININ KALMA | 56 |
| KASHI NA 7: | IRE-IREN ADON HARSHE | 59 |
| KASHI NA 8: | AMFANI DA ADON HARSHE | 62 |
| **FASALI NA 5: ADABIN GARGAJIYA** | | **65** |
| KASHI NA 1: | AMFANIN ADABIN BAKA GA AL'UMMA | 65 |
| KASHI NA 2: | NAZARIN TATSUNIYA DA ZUBEN LABARI | 68 |
| KASHI NA 3: | MA'ANAR KACICI-KACICI DA RABE-RABENSA | 70 |
| KASHI NA 4: | KARIN MAGANA | 74 |
| KASHI NA 5: | MANUFOFI DA MUHIMMANCIN WA{AR BAKA GA HAUSAWA | 76 |
| KASHI NA 6: | SALON MAGANA | 78 |
| KASHI NA 7: | RABE-RABEN MAKA[AN HAUSA | 80 |
| KASHI NA 8: | NAU'O'IN WA{O{IN MAKA[AN HAUSA | 82 |
| KASHI NA 9: | DARUSSAN DA WA{O{IN MAKA[AN HAUSA KE KOYARWA | 85 |
| KASHI NA 10: | BITA | 88 |
| **FASALI NA 6: ADABIN ZAMANI** | | **90** |
| KASHI NA 2: | RABE-RABEN RUBUTACCEN ADABI | 90 |
| KASHI NA 3: | {WA{{WARAN NAZARIN LITTAFIN WASAN KWAIKWAYO NA (*UWAR GULMA*) | 93 |
| KASHI NA 4 : | FITAR DA JIGON WA{A DA BAYANINTA | 96 |
| KASHI NA 5: | {WA{{WARAN NAZARIN LITTAFIN ZUBE | 98 |
| KASHI NA 6: | FITAR DA JIGON LITTAFIN ZUBE TARE DA BAYANIN SALON SARRAFA HARSHE | 100 |
| KASHI NA 7: | NAZARIN RUBUTATTUN WA{O{I | 102 |
| KASHI NA 8: | {WA{{WARAN NAZARIN WA{A | 104 |
| KASHI NA 9: | NAZARIN LITTAFIN WASAN KWAIKWAYO | 107 |

KASHI NA 10: BITA - - - - - - - 109

**FASALI NA 7: ZAMAN HAUSAWA - - - - - 110**
KASHI NA 1: TSARIN FASALIN IYALI GABATARWA - - - 110
KASHI NA 2: RUKUNAN IYALI DA MATSAYINSU - - - 112
KASHI NA 3: TSARIN SARAUTA - - - - - 114
KASHI NA 4: RA'AYIN BAHAUSHE A KAN ISKOKI - - - 116
KASHI NA 5: AL`ADUN HAUSAWA - - - - - 118
KASHI NA 6: RUKUNAN SHEKARUN YARA DA MATASA DA MANYA DA DATTAWA - - - - - - 120
KASHI NA 7: SIFFOFI DA MATSAYIN KOWANE RUKUNI GA AL`UMMA 122

**FASALI NA 8: DABARUN KOYAR DA RUBUTU DA KARATU - 124**
KASHI NA 1: DABARUN KOYAR DA RUBUTU DA KARATU - - 124
KASHI NA 2: KOYAR DA HARUFFAN HAUSA (Wasulla) GABATARWA - 125
KASHI NA 3: KOYAR DA RUBUTU DA FAYYACE MANYA DA {ANANAN HARUFFA - - - - - - - 127
KASHI NA 4: KOYAR DA AWON FAHIMTA - - - - 129
KASHI NA 5: KOYAR DA KARATU A LITTAFI - - - - 131
KASHI NA 6: KOYAR DA KARATUN SAURI - - - - 134
KASHI NA 7: BITA - - - - - - - 137
KASHI NA 8: DABARUN KOYAR DA HAUSA TARE DA KAYAN AIKI - 139
KASHI NA 9: AUNA FAHIMTA - - - - - - 141
KASHI NA 10: KOYON MAGANA DA KARATU - - - - 143
KASHI NA 11: KOYAR DA BA DA LABARI DA KACICI-KACICI - - 147
KASHI NA 12: RARRABA KALMOMI AJI-AJI TA HANYAR AMFANI DA KATUTTUKA - - - - - - 150

FASALI NA 9: AIKIN FASSARA - - - - - - 153
KASHI NA 1: AIKIN FASSARA - - - - - - 153
KASHI NA 2: KOYAR DA YADDA [ALIBAI ZA SU GABATAR DA JAWABI A RUBUCE DA KA - - - - - - 156
KASHI NA 3: KOYAR DA SHIFTA DA JAWABI DA TAKAITAWA TA HANYAR SAURAREN ZANCE A KASET - - - 158
KASHI NA 5: BITA - - - - - - - - 163

FASALI NA 10: DABARUN KOYAR DA ADABI DA [ABI`U - - 165
KASHI NA 1: HANYOYIN KOYARWA - - - - - 165
KASHI NA 2: LABARU DA AKE DANGANTAWA DA FATALWA - - 168
KASHI NA 3: HIKIMOMIN SANA'OIN GARGAJIYA A ALUMMAR HAUSAWA 170
KASHI NA 4: MU{AMAI DA AYYUKANSU - - - - 172
KASHI NA 5: BAYAR DA MISALAI NA ADABI DA RABE-RABENSA DA RUKUNANSA - - - - - - 175
KASHI NA 6: JAGORA ZUWA GA LITTATTAFAN DUBAWA A KAN KOWANE FANNI - - - - - - 177
KASHI NA 7: KACICI - KACICI DA HIKIMOMIN DA KE CIKINSA - - 179
KASHI NA 8: MATSAYIN CAMFE-CAMFE GA ALU'MMAR HAUSAWA - 181
KASHI NA 9: JIGOGIN LITTAFAN ZUBE DA MUHIMMANCINSU A TARBIYYA 183
KASHI NA 10: BITA - - - - - - - - 185

**FASALI NA 11: DABARUN KOYAR DA HARSHE - - - - 187**
KASHI NA 1: DABARUN KOYAR DA HARSHE - - - - 187

**AMSOSHIN AYYUKA - - - - - - - 189**

**ACKNOWLEDGEMENTS - - - - - - - 219**

**FASALI NA 1: INSHA'I**

**KASHI NA 1: {A'IDOJIN RUBUTU**

**GABATARWA**
A wannan kashi, za a gabatar da }a'idojin rubutun Hausa. Rubutu a kowane harshe ba haka nan ake yin sa ba kara zube. Rubutu yana da }a'idoji ko dokoki kuma tilas ne a kiyaye su domin abin da aka rubuta ya karantu. A wannan kashi za a gabatar da jadawalin haruffa da dokokin raba kalmoni da ha]a su cikin rubutu.

**MANUFA**
Manufar wannan darasi na }a'idojin rubutu ita ce, a koyar da ]alibi wa]annan abubuwa:
a. sanin dukan haruffan Hausa;
b. gane bambancin ba}a}e da wasulla.

**MATAKAN NAZARI**
1. Wannan fannin yana bu}atar karanta littattafai iri-iri na Hausa don tabbatar da cewa an gane yadda ake ha]a kalmomi da raba su, da kuma gane ba}a}e da wasulla.
2. Za ka yi dukan ayyukan da aka ce a yi a wannan kashi.
3. Dukkan amsoshin tambayoyi na }arshen littafi.

**SABABBIN KALMOMI**
[alibi zai san ma'anar wa]annan sababbin kalmoni kamar yadda ake amfani da su a fannin nazarin }a'idojin rubutu. Kalmomin su ne: **ba}i**; **abjadi**, **tagwan wasali**.

**HARUFFAN HAUSA**
Za mu fara wannan darasi da yin bayani game da haruffan da Hausa take da su. "Harafi suna ne da ya ha]e ba}a}e da wasulla baki ]aya. Wato ke nan kowane ba}i harafi ne; haka kuma kowane wasali harafi ne. Hausa tana da harufa 33. Ga jadawalin haruffan:

**Ba}a}e:** b, ~, c, d,], f, fy, g, gw, gy, h, j, k, ky, }, }w, }y, l, m, n, s, sh, t, ts, w, y, 'y, z.
**Wasulla:** a, i, u, e, o, ai, au, ui.

Wa]annan haruffa su ne ka]ai ake amfani da su wajen rubuta duk wata kalma ta Hausa. Akwai haruffan da ake rubuta su ta hanyar, yin amfani da ba}a}e guda biyu. Wa]annan haruffa su ne: fy, gw, gy, kw, }w, ky, sh, da ts. Haka kuma akwai haruffan da ake rubuta su hanyar yin amfani da wasulla biyu. Wa]annan haruffan su ne: ai, au, da ui. Ana kiransu "tagwayen wasulla".

**AIKI I**
Fitar da haruffa biyar wa]an]a suka }unshi ba}a}e biyu.

**DOKOKIN RABA KALMOMI DA HA[A SU**
Akwai dokokin rubutu wa]anda suke nuni ga yddda za a ha]a wa]ansu kalmomi ko a raba su. Kafin mu ambaci wata doka ta ha]a kalmomi ko raba su, wajibi ne a san cewa akwai kalma iri biyu. Iri ta farko, ita ce, cikakkiyar kalma wadda ake rubuta ta ita ka]ai. Misalan cikakkiyar kalrna su ne: wata, gida, doki, sama. Irin kalma, ta biyu ita ce gurguwar kalma wadda ba ta iya tsayuwa ita ka]ai sai ta jingina da wata gurguwar kalmar ko cikakkiyar kalma. Misalan gurguwar kalma su ne, -n, -r, na, kan, ya, ta, su, da sauransu. To, }a`ida ta farko ta raba kalmomin Hausa ita ce duk cikakkiyar kalma ana rubuta ta ita ka]ai, misali: abinci, gida, makaranta, Musa, [an`azumi, Babangida. {a'ida ta biyu ita ce yawancin kalmomin -ne, -ce, -fa, -ma, -ko, -]in, da sauransu ba sa jinginuwa da kowa. A lura da cewa duk kalmar da aka ja layi a }ar}ashinta gurguwar kalma ce.
Baya ga wa]annan manyan }a`idojin rubutu guda biyu, akwai kuma }a`idar kyautata rubutu wadda ya kamata a lura da ita wajen rubutu. Ga misalai:

| | Daidaitaccen Rubutu | Rubutu Maras kyau |
|---|---|---|
| a. | Haifa wa | Haifawa |
| b. | Ko`ina | Koina |
| c. | Ko yaushe | Koyaushe |
| d. | Za a | Zaa |

Akwai kuma dokar dá ta shafi yadda ake rubuta haruffan nan masu ba}a}e biyu. I]an irin wa]annan haruffa suka ru~anya kansu cikin kalma guda, kuma suna biye da juna, to ana rubuta su kamar yadda aka yi a wa]annan misalai:

| | Daidaitaccen Rubutu | Rubutu Maras Kyau |
|---|---|---|
| a. | Gwaggwamutsa | Gwagwgwamutsa |
| b. | Kyakkyawa | Kyakykyawa |
| c. | Matsattse | Matsatstse |

**AIKI II**

Yi amfani da }a'idar rubutun Hausa ta raba kalmomi ka nuna daidaita ko rashin daidaitar wa]annan ( ka yi amfani da alamar don nuna daidaita ko rashin daidaita).

| Kalma | Daidaita | Rashin Daidaita |
|---|---|---|
| Abin da<br>Kwakwkwaba<br>Yakamata | | |

**TA{AITAWA**

A wannan kashi ka koyi wa]annan abubuwa:

- Yawan haruffa a harshen Hausa
- Haruffa su ne ba}a}e da wasulla.
- Wasu daga cikin }a'idojin rubutun Hausa.

**AIKIN GIDA**

1. Mene ne ma'anar harafi?
2. Haruffa nawa ne a Hausa?
3. Zana jadawalin dukkan haruffan Hausa amma ka ware ba}a}e da wasulla daban - daban.
4. Kawo dokoki biyu da ka sani na }a'idojin rubutun Hausa.
5. Fa]i irin }a'idar rubutun Hausa wadda ta ce **za a** daidai ce amma **za'a** ba daidai ba.

**MANAZARTA**

Institute of Education. (1979.) *Karatu Da Rubutu A Harshen Hausa.* Thomas Nelson (Nigeria) Ltd.

Skinner, N. (1977) *A Grammar of Hausa: For Nigerian Secondary Schools and Colleges.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Zarruk, R.M. et al. (1979). *Shimfidar Ilimin Harsuna: Furuci.* Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University.

## KASHI NA 2: ALAMOMIN KYAUTATA RUBUTU

### GABATARWA

Wannan kashi zai yi bayani kan alamomin da ake amfani da su don kyautata rubutu. Ana yin amfani da irin wa]annan alamomi kan kowane irin rubutu. Duk rubutun da aka yi ba wa]annan alamomi, to ma'anarsa ba ta fita sosai. Saboda haka alamomi ne da aka saba amfani da su a rubutun yau da kullum don ma'ana ta fita sosai.

### MANUFA

Manufar wannan kashi ita ce, ya koyar da alamomin rubutu ta hanyar sanin sunayensu da kamanninsu da kuma wuraren da ake amfani da su. A }arshen wannan kashi, za ka fahimci alamomin rubutu da kyau da yadda za a yi amfani da kowanensu da gane su a cikin jumla da kuma iya amfani da su.

### MATAKAN NAZARI

1. Ka gane alamomin rubutu da sunayensu.
2. Ka san yadda za a yi amfani da dukkanin alamomin rubutu.
3. Gane alamomin rubutu a cikin jumla da iya yin amfani da su.

**Dukkan amsoshin tambayoyi na }arshen littafi**

### ALAMOMIN RUBUTU DA YADDA AKE AMFANI DA SU

**Aya (.)**

Ana amfani da aya a }arshen kalma, ko jumla, ko a inda duk aka samu cikar magana. Wato, aya, alama ce ta tsayawa. Wani lokaci don a ja numfashi kafin a ci ga~a. An fi yin amfani da aya ta wannan fuska. Ana ci gaba da rubutu da babban ba}i bayan an yi amfani da aya. Misali:

1. Abdu ya tafi makaranta.
2. Binta ta fita.
3. Ku zo.
4. Zauna.

**Waƙafi (,)**

Ana yin amfani da wa}afi don dakatawa ka]an kafin a ci gaba da rubutu ko karatu. Ana ci gaba da rubutu da }aramin ba}i bayan an yi alamar wa}afi. Misali:

1. Abdu yana da gida a Katsina, kafin a kai gi]an sarki.
2. Abdu ya ci wake da shinkafa, ya manta bai sha ruwa ba.
3. 1]an malami ya zo aji, ]aliban za su yi shiru.

A lura cewa yin amfani da wa}afi yana nuna cewa akwai sauran magana.

**Waƙafi Mai Ruwa (;)**

Ana yin amfani da wannan alama don a raba wa]ansu sassa na jumla, musamman jumla mai tsawo, misali:

(i) Wani lokaci akan yi amfani da simintin ga~a ]ayannsa; wani lokaci kuma, akan yi amfani da rabinsa.
(ii) Abdu ya ba wani riga; wani kuma ya ba shi hula.

**Ruwa-Biyu (:)**

Ana yin amfani da ruwa-biyu yayin da mai rubutu ya bukaci ya zuba wasu misalai ko jera wasu abubuwa. Misali:

i. Ga yadda ake yin aikin: da farko a samu yashi da duwatsu da kuma siminti. Misali: ana son mai karatu ya iya rubutu.

A }asar Hausa ana yin bukukuwa kamar: bukin sallah }arama da na babba da bukin kalankuwa da bukin aure da bukin suna da sauransu.

**Alamar Tambaya (?)**

Ana yin amfani da wannan alama i]an ana bukatar neman wani bayani ko amsa kan wani batu ko wata magana. Alamar tambaya tana zuwa a }arshen jumla ko kalma mai nuni ga tambaya. Misali:

i. Ina za ka ?
ii. Shin Abdu ya tafi?
iii Kana gani na?
iv. Me Abdu yake yi?

**AIKI I**

1. Me ake nufi da wa}afi? Kawo misalin jumla ]aya mai ]auke da wa}afi.
2. Kawo sunayen alamomin rubutu guda uku tare da nuna kamanninsu.

**Alamar Motsin Rai (!)**

Ana yin amfani da alamar,motsin rai yayin da ake cikin halin razana ko ~acin rai ko murna ko tsoro ko hali na wuya. Ana rubuta alamar motsin rai a }arshen jumla ko kalma kuma babban ba}i ke biye da alamar. Ga misali:

i. Wayyo Allah! Zai kama ni.
ii. Kash ! Ashe gobe za a ]aura aurenka ?
iii. lye!
iv. Ba magana!

**Baka Biyu [ ( ) ]**

Ana yin amfani da baka biyu i]an ana son a nuna muhimmancin wasu kalmomi ko don karin bayani ko fayyace ma'ana. Akan saka wa]annan kalmomi a cikin baka biyu. Misali:

i. Kurar da ta kori karen nan (wanda har ya yi zawayi), ta dawo dazu.
ii. Mutumin nan (mai cin-zanzana a fuska) ya zama shuga~an yan kasuwa.

Yin amfani da wannan alama kan sa jimla armashi, to amma fa ba ta zama dole ba.

**Alamomin Zancen Wani (‘’)**

Ana yin amfani da waccannan alamomi i]an ana son a kebe maganar wani. Alama ta farko ana rubuta ta daga hannun hagu; ita ake kira bude zance. Alama ta biyu kuma daga hannun dama ita ake kira rufe zance. Misali:

1. Sai Bala ya ce, ‘Abdu da Musa sun yi tafiya makon da ya wuce’ Lallai ne a rubuta alamar aya a }arshen maganar.

**Karan –ori** (-)

Ana amfani da karan – ]ori a tsakanin kalma da kalma ko kalmomi, su kasance kalma [AYA, mai ma'ana [AYA. Misali:

1. Tallace - Tallace
2. Gaya - wa - jini - na - wuce
3. Ji-ta-ji-ta.

**Zarce (....)**

Wannan ayoyi ne (wato ]ugo) guda huccu ko fiyc don a nuna cewa an katse ko an bar wata kalma ko jimla wadda rubuta ta ba dole ba. Misali:

An yi wani maketacin zaki wanda ya shimfi]a mulki a wani Kasurgumin... Don ba}in mulkin wannan zaki ko fita farauta ba ya yi, sai ya kame a gida, .... Don tsoron sharrinsa da suke ji'.

(An ]auko wannan misali daga littafin: *An Introduction to Hausa Grammar.* 1976: Shafi na 96 - 97)

2. I]an abin alheri ya samu, akan je a yi wa wanda ya samu din tayin murna. I]an kuma na ba}in ciki ne ya samu, wato a taya shi ba}in cikin'.

(An ]auko wannan milsalin daga littafin: *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don {ananan Makarantun Sakandare Littafi Na Uku.* 1990. Shafi na 5).

**AIKIN GIDA**

1. Fa]i bambanci tsakanin wa}afi da kuma aya.
2. Kawo misalai na amfanin karan-]ori a cikin jimla.
3. Kawo misalai biyu na amfanin ayar motsin rai.
4. Me ya bambanta aya da kuma ayar tambaya?

**MANAZARTA**

Institute of Education A.B.U., Zaria. (1979) *Karatu Da Rubutu* A Harshen Hausa. Ikeja: Thomas Nelson.

Yunusa, Y. et al. (1987) *Rubutun Wasi}a* Kano: Uniprinters.

**KASHI NA 3: MA'ANAR INSHA'I**

**GABATARWA**
A wannan kashi za mu duba ire - iren rubutu na Hausa. Rubutu na da muhimmanci domin isar da sako. Don haka dole a bi }a'idoji domin 'samun nasarar isar da sakon daidai . Domin fahimta, za a duba ire-iren rubutu hu]u. Su ne rubutun muhawara da na labari da siffantawa da kuma rubutun wasi}a.

**MANUFA:**
Ma}asudin wannan darasi shi ne koya wa ]alibai ire-iren wa]annan hanyoyi na rubutu domin su tantance yadda za su rubuta kowannesu.

**MATAKAN NAZARI**
(a) Za ka dubi mahimmancin insha`i ga al'umma. Wannan zai ba ka damar sanin yadda za ka isar da sa}o ta hanyar rubutun da ya dace.
(b) Duk abin da aka yi bayaninsa to wajibi ne a san shi.

**SABABBIN KALMOMI**
[alibai kan samu wahala i]an akwai kalmomin da ba su sani ba. Domin samun sau}i ya kamata su san wa]annan kalmomi: **sharhi**; **jan hankali**; **fa]akarwa**; **yabo**; **ilmantarwa**; **siga**.

**MATANI**
Insha'i - shi ne siffanta rubutu da kwatanta abubuwa ko yanayinsu ko yadda suke gu]ana kamar yadda yake a littafi mai suna Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa (1990). Wannan insha'i ya kasu kashi kashi. Akwai insha'i na muhawara; akwai na labari, akwai na siffanta abu; akwai kuma na rubutun wasika.

Insha'i na muhawara shi ne wanda mutum zai rubuta sharhi kan wani abu ko ya yabe shi ko kuma ya soke shi. Misali, ana iya muhawara kan ababe ko abubuwa da dama,wato ko mulki, ko yanayin tattalin arziki, ko siyasa ko ilmi da dai sauransu. Ta irin wannan hanya muturn kan tattauna abu wato ya nuna kyannsa ko rashin kyannsa. Wajen tattauna ~angaren da ya za~a zai kawo misalai na nuna amfanin abu idan yana goyon bayansa ko kuma ya nuna ta fuskar da ba ya da amfani. Mai rubutu kan kula da muhimmancin ko mene ne yake goyon baya. Idan kuma ba ya goyon bayan abu zai samu dalilai masu }arfi domin duk wanda ya karanta ya gamsu da ra'ayinsa.

Muhawara ba ta kammala sai da dalilai masu }arfi. Wa]annan dalilai su za su zama makaman ya}insa domin ya jawo hankalin mai karantawa ya yarda da shi, wato ya amince da duk dalilan da ya kawo. Saboda haka dole ya yi amfani da fasaha da kuma tunani domin amfani da kalmomi da suka dace kuma masu sau}in fahimta da fito da ma'ana. Irin wannan rubutu na bukatar dogewa kan dalilai masu }arfi. Wato, tabbatar da cewa wa]annan dalilai sun dace kuma kowa na iya amincewa da su. Misali, idan kana rubutawa kan ci gaban }asa, dalilai irin su samun masu ilmi a kasa na da mahimmanci. Haka kuma ana iya duban ci gaban }asa ta fuskoki da yawa kamar su }ere-}ere da ilmin kimiyya da ilmin tattalin arzi}i da sauransu.

Adabi, wato abin da ya shafi al'ada na iya zama abin mahawara. Idan mai rubutun ya yi nazarin al'adun wasu al'umma da nufin gano wasu muhimman abubuwa, yana iya fahimtar idan suna da amfani ko babu. Ta wannan fuska yana tattauna wa]annan muhimman abubuwa da ya gano. Misali, wa}o}i suna da muhimmanci wajen fa]akarwa. Haka idan wasan kwaikwayo ne, shi ma yana da muhimmaci wajen ilmantarwa ko fa]akarwa. Duk abin da mai rubutu ya ]auka ta fannin adabi yana iya rubuta muhawara ya nuna muhimmanci ko kuma rashinsa, Misali, irin sutura ko abinci ko wasanni ko bukukuwa. Duk wanda mai rubutu ya ]auka yana iya yabo ko kuma sukan abin, yana mai duba yanayi da kuma tsarinsa.

**LABARI**
yana nufin abin da wani ya zo ya fa]a ma wani ko wasu, ko kuma ya rubuta da nufin isar da sa}o ga wasu al'umma ko wani mutum. Labari na nufin fa]ar wani abu da ya riga ya faru. Saboda: haka mai rubutu zai fa]i abin da ya gani idan gani ]in ya yi ko abin da ya karanta idan karantawa ya yi, ko kuma abin da ya ji

idan ji ya yi da ya ji, kuma. mutum yana iya }ir}iro labari don garga]i ko nisha]i ko waninsu.

Labari wani hanya ne na isar da sa}o da fa]akarwa idan an rubuta shi domin haka. Ya na iya kuma zama wata hanya ta ilmantarwa. Misali, rubuta labari domin fahimtar wani muhimmin abu kamar jaruntaka ko ha}uri ko }wazo da sauran abubuwan yabo. Haka akwai labarai masu sosa rai, wato kamar tausayi, ko kuma labari na rashi da ha}uri na wadata da taimako. Wannan ya nuna cewa ana iya rubuta labari iri-iri domin wata manufa. Ana iya rubuta labarin kan aure domin a jawo hankalin matasa su yi. Ko kuma a rubutu kan sida ko cutar }anjamau domin al’umma su fa]aka da irin illarsa.

**AIKI I**

1. Kwatanta rubutun muhawara da na labari

**SIFFANTAWA**

Siffantawa ita ce bayyana sigar abu, mutum ko dabba ko wata halitta. Haka ana samun siffar wani abu da ]an Adam ya }ir}iro ko ya mallaka. Misali, siffar namiji da ta mace, ko ta zaki da giwa, ko ta mota da babur da dai sauransu. Duk abin da ake iya gani da }wayar ido ana iya rubuta siffarsa. Siffa ita ke bambanta wani abu daga wani. Ko da a tsarin rayuwa ta yau da kullum, ana iya samun bambancin siffa. Misali, rayuwar Musulunci da wadda ba ta Musulunci ba, kamar ta arne ko Bamaguje. Musulmi yana sallah, yana Azumi, ko ya je Hajji yana ba da Zakka, kuma ya yi imani da Allah da Manzanni da Al}ur’ani da sauransu. Shi kuma arne ko Bamaguje ba ruwansa da duk wa]annan. Saboda haka komai na da siffa ko dai mai kyau ko mara kyau. Wannan kuwa ana iya fahimtarsa ne kawai ta hanyar al’adun mutane.

Wato ke nan, siffa wata hanya ce da ]an Adam ke gano bambanci da kamanni. Don haka siffa wata hanya ce ta ilmantarwa ga ]alibi wadda zai fahimci wani yanayi ko kamanni . Wato idan babu bambance - bambance ta siffa mutum bai gane mahaifi, ko uwa, ko iya ko }ani ko wa da sauran yann’uwansa. Haka mutum bai gane abin da ya mallaka ko gida ko mota ko doki ko jaki da sauransu. Don haka ana amfani da siffantawa wajen rubuta kamanni domin ]alibi ya fahimci mahimmancin sani ko kuma gane banbanci tsakanin abubuwa.

**WASI{A**

Wasi}a wata hanya ce ta isar da sa}o ga wani ko wata ko kuma wasu al’umma. Rubutun wasika na da }a’idoji haka kuma wasi}a iri-iri ce. Akwai wasi}ar abota ko kusanci,
Wato wasi}a ga aboki ko ]an uwa. Akwai kuma wasi}a ta musamman, wato wadda ake rubutawa kamfani ko kuma wani mutum wanda ya girme ka ko kuma yana da matsayi mai muhimmanci cikin al’umma. Wa]annan wasi}u guda biyu suna, taimakawa a rayuwar ]an Adam. Misali, ana rubuta wasi}a a sanar da wani sa}o ba tare das u mutanen biyu sun ga junansu ba.

Wasi}a zuwa ga aboki ko abokiya na da nata tsari kamar haka:

1. rubuta adireshi daga sama a hannun dama.
2. rubuta kwanan wata daga }arshen adireshin.
3. farawa da gaisuwa.
4. tattauna mahimman abubuwa na sako.
5. }arewa da 'wasalam' da kuma rubuta sunan farko ka]ai.

Wannan shi ne tsarin wasi}a zuwa ga aboki ko kuma sa’a wato mutumin da kuke shekaru ]aya.
Ita kuwa wasi}a zuwa wani babban mutum ko mai ri}e da wani mu}ami babba tsarinta daban. Ga irin nata tsarin:

1. rubuta adireshin kamfani a sama hannun dama
2. rubuta kwanan wata daga }arshen adireshin
3. rubuta mi}amin shugaban wuri a hannun hagu
4. rubuta adireshin kamfani a kasan (3)
5. rubuta shugaba na a }arkashin (4)
6. rubuta taken ko ma}asudin rubuta takardar a tsakiya, }ar}ashin (5) kuma aja layi }ar}ashi
7. bayanin dalilin rubuta takarda kai tsaye

8. rufewa da fatan neman sa’a ga abin da aka nema
9. rubuta ‘ka huta kafiya' kuma a rubuta suna cikakke, sannan a saka hannu.

**AIKI II**

1. Rubutun siffantawa da na wasika sun bambanta. Yi bayani kan bambancin.

**AIKIN GIDA**

1) Fa]i matsayin insha’i a adabin Hausa,
2) Mece ce muhawara?
3) Wace hanya ce, bayan wasi}a, ake iya isar da sa}o?
4) Ko ana iya siffanta jaki ta hanyar rubutu?
5) Kawo muhimman sigogin wasikar aboki.

**TA{AITAWA**

A wannan kashi ka koyi wa]annan abubuwa:

- Insha'i: Ire-iren rubutunsa sun ha]a da
- Muhawara;
- Labari;
- Siffantawa;
- Wasi}a.

**MANAZARTA**

Daura, B. Isa, Y., and Madauci, I. (1968) *Hausa Customs.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company.

Zarruk, R.M. et al. (1990) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.* Iba]an: University Press Limited.

**KASHI NA 4: INSHA`I (LABARI, SIFFANTAWA, MUHAWARA,WASI{A)**

**GABATARWA.**

Inshai iri-iri ne: Saboda haka kowane akwai hanyar da ake bi a rubuta shi: salonsu da ire-iren kalmomi da ake amfani da su sun sha bamban ko da kuwa duk manufarsu ]aya. Akwai insha'in da za a ri}a ba mai karatu hoton labarin ta hanyar Siffanta abubuwa da labarin ya kunsa }uru -}uru. Mai karatu zai ji kamar ya san abubuwan da ake fa]a domin zai ji kamar ya gan su. Wani nau'in kuwa salon gardama yake ]auka. Wani kuwa ra'ayi ne za a kawo a kuma dage a dinga kawo hujjoji da }abli' da ba'adi domin a kare wannan ra'ayi. A nan ba a yin suka da kushe ra'ayin da ba a so. Sai dai maijawabi zai zayyana nasa bayanin. A insha'in labari kuwa, zance ne kawai za a labarta. Mai karatu zai ji bayani ne a kan wani abu da ya faru ba tare da dole an siffantar masa da wani abu ba, ko an yi muhawara ko kuma dagewa kan kawo wasu hujjoji. A nan dai ita ce a bayar da labari . Babu wasu }yale-}yale, hoto-hoto ko gardama. Salon insha'i na karshe shi ne salon rubuta wasika. Ita kanta wasika kuwa suna ta tara amma hanyar rubuta ta ya bambanta. Iri iri ce.

**MANUFA**

A lokacin da ]alibi ya karanta wannan fasali, ya kamata a ce.

i) Zai iya yin bayani a kan nauo'in insha'i da ake da su;
ii) Ya fahimci salon da ake bi a rubuta kowane ]aya daga cikin nauo'in insha'in;
iii) Zai iya rubuta ire-iren insha'in nan.

**MATAKAN NAZARI**

i) Ka karanta labarin a tsanake.
ii) Ka gane nau'in labarin da kuma bin salon da aka yi amfani da shi:
iii) Ka amsa tambayoyin da aka yi, a kuma kwatanta amsoshi da wa]anda aka kawo a }arshen fasalin**.**

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Malalen | - wuri mai fa]i |
| tasar | - dumfara |
| mai laushi | - mai taushi |
| kalaci | - karin kumallo |
| soraye | - benaye |
| dakali | - ]an tudun zama |
| wasaki | - guga |
| zabari | - lalaben guga a rijiya |
| asako | - kiwo |
| hantsi | - farkon fitar rana |
| burtali | - hanyar shanu |
| hole | - more |

**MAIKULKI**

Maikulki wani gari ne mai ban sha'awa wanda ke shimfi]e a malalen wuri mai jigawa. Ga kuma tu]anni matskaita masu tsatse sun kusan yi masa zobe.

Idan aka tasar wa garin sai 'a ji wani irin }anshi da iska mai laushi na tashi da an hangi garin sai a zaci wata, yar }aramar aljannar duniya ce, idan da farko- farkon rana ne sai a ji ta~are sun kacame ana ta dake-dake har da lugude a cikin gidajen. In farkon marece ne kuma sai a ji }ul}ule da }anshi na tashi ana tanadin kalacin marece kuma ana hangen wutar makarantun allo a kowace unguwa ta garin da dare.

Akwai bishiyoyi kuma masu ban sha'awa a cikin garin. Galibin bishiyoyin da itatuwana suka masu soraye da kalankuwa kuma an shafe su tsaf da zarta da makuba. An yi wa kowane gida dakali don hutawa. An ranga]a alkuki a soron }war gida don ]ora fitilar kasko ko }arfe. Akwai kuma wasu gidaje na jinka masu zauruka da ]akuna da ku]an]an da buka da rumfa. An kawo gumaguman itace mulmulallu an raba su da zauruka don hutawar jama'a. Ga kuma rumbuna a ciki da wajen gidaje.

Akwai rijiyoyi a wuraren da suka dace cikin gidaje da wajensu. Mutanen gari su tura ana ]ibar ruwa da

guga ko wasaki ko zabari ana zubawa a cikin tuluna da kasake ana jida ana kai gidaje. A rijiyoyin waje kuwa ana ba dabbobi ruwa cikin akala.

Da safe kuwa sai iska mai da]i ta dinga buga itatuwa suna rausayawa. Da hantsi ya yi sai a yi asako na dabbobi suna fita suna taruwa a hurumi inda asako zai kora bisashen su bi burtali zuwa gun kiwo. Idan lokacin damina ne kuwa, sai samari su yi ta tafiya wurin noma da shuka. Bayan hantsi ya dubi ludayi sai mata tsofaffi ko yara su rinka kai lomi gonaki. Kowace mace tana sauri don gudun kar a yi mata, ]orawa makashiya, ga tantabaru da kaji  da zabbi sun fito suna shawagi suna holewa, su kai nan su kai can. Idan rani ne sai mutane su yi ta kai taki gona da jidar }asa don gini. Duk mutane a lokacin aiki da lokacin hutu suna cikin aminci da raha sai nisha]i. Kowa na sha'anin gabansa don gu]anar da sha'anin rayuwarsa na yau da kullum.

Idan La'asar ta yi sanya -sanya kuma sai dabbobi su dawo daga kiwo. Kuma tsuntsaye kamar su balbelu da kasshere}ai da sauransu su dawo su yi ta 'rera wa}a mai da]i kan bishiyoyi. Dare na yi kuwa sai a hura wutar makarantar allo a kowace unguwa. Bayan an tashi makaranta sai yara su yi du~u~u suna na-hole. suna ta wasanni iri-iri. Daren kasuwa da na salla kuma sai a ji ana ki]e-ki]e da bushe-bushe har talatainin dare, Muhimman wuraren garin kuma su ne masallacin Juma'a wanda ke kusa da gidan sarautar garin . Sai kuma marina wadda ke can gabas da gari. Ga kuma kasuwa mai rumfa hululu a yamma da gari. Kuma akwai "yardole mai ci kullum inda mutane ke taruwa suna hira da raha wasu kuma suna sai da abubuwa kamar goro da agashe da langa~u da kilishi da mashe da tubani da ]anwake da ]anshanana da {osai da waina da mabun}usa }asa da kayann marmari iri-iri.

A takaice dai mutanen garin Maikulki maza da mata da gidajensu duka a tsabtace suke. Kowa yana da tasa sana'a don haka ake yi wa garin kirari da cewa: " Maikulki; ]an gari mai ni`ima. Maikulki mai kulaken da]i. Garin Lukumanu mai dame zambar goma har a ji zambar goma".

Duk wannan bayani da aka yi a takaice ne, don haka ana ba mai karatu shawara ya tafi ya ganar wa idonsa garin Maikulki. Saboda:"gani ya kori ji"

**AIKI**

1) Yaya tsarin gidajen garin Maikulki yake?
2) Wane aiki ake yi da hantsi a garin nan?
3) Me ake nufi da hantsi ya dubi ludayi?
4) Wa]anne wurare ne muhimmai a garin Maikulki?

**TA{AITAWA**

Maikulki gari ne dake cikin malale yana cike da ni'ima da yalwa, kuma mutanen garin na zaune a cikin kwanciyar hankali da annashuwa. Kowa yana da aikin yi a garin har ma ana yi wa garin kirari da cewa "…..kulaken da]i"

1. Wane irin insha' i ne wannan? Kawo hujjojinka.
2. Kawo dalili biyu da ke nuna cewa akwai wadata a garin nan.
3. Mene ne addinin mutanen garin?.
4. Wane suna za ka ba labarin?

**MANAZARTA**

Alhassan, & Musa U.I. et al (1989) et al. New Nigerian Newspapers Kaduna, Kaduna.
Kirk- Greene, A.H.M. & Yahaya, A.A. et al., London: University of London Press Ltd.

**KASHI NA 5: SHIFTA DA INSHA`I**

**GABATARWA**

Me ake nufi da shifta? Kuma me ya ha]a ta da insha'i? Wannan tambaya ce mai ma'ana.

Idan ba an duba su ba a tsanake ana iya cewa ba su da wata ala}a, alhali kuwa ba haka ba ne. Suna da ]angantaka. Shifta na nufin rubuta wani jawabi ko zance wanda wani. Ya rika fa]a da baki. Tana yiwuwa mai fa]ar karantawa yake yi, ko tunanin shi ne yake

}ir}iro shi da kansa. insha' i kamar yadda aka riga aka gani wani salo ne na rubutã wani sharhi ko bayani. Dukkansu dai hanyoyi ne da ake rubuta wani abu. A wajen yin rubutu kuwa tilas a bi }a'idojin rubutu. A nan ne ake da ala}a tsakanin shifta da insha'i. A wannan fasalin za mu ri}a kai gwauro mu kai mari. Mu bugi jaki, kuma mu bugi taiki.

**MANUFA**

Idan ]alibi ya gama wannan fasali ana sa ran.

i) Ya san yadda zai rubuta duk wani jawabi da za a karanta ko shaida mashi.
ii) Ya san yadda zai rubuta insha'i musamman samfurin Labartawa.
iii) Ya san yadda zai sarrafa }a'i dojin rubutu a wajen yayin da yake rubutu.

**MATAKAN NAZARI**

(i) A karanta jawabin nan a tsanake domin a fahimce shi da kyau.
(ii) Ayi tunani a kan salon rubutun da dacewarsa da (nauin) insha'in.
(iii) A duba dangantakar labari da sunansa

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Guntu | - gajere |
| Kazigi' | - Matsiyaci |
| Jim cida | - Jiran ruwa |
| Kwangeren | - kwamasgi |
| Busasshe | - }e}asasshe |
| Bakan | - jira |
| {ato | - wulli |
| [unguma | - suka tafi |
| Sowa | - ihu |
| Arne | - kafiri |
| yann galla | - hawaye |
| Na mai bara | - ha}uri |
| }iri da muzu | - firi falo |
| Baki da hanci | - daf da daf |
| Lifidda | - abin da aka sa wa doki |
| Jibge | - aje. |

**GUNTUN GATARINKA YA Fl SARI KA BA NI**

A wani }auye can a }asar |ena, wanda ke tsakanin Takikiri da Tamuzumuzu,wai shi Tangaram. To a nan ne aka yi wasu samari su biyu, Shamudora da Shakatafi, uban Shamudora wani gawurtaccen attajiri ne uwarsa ma ba baya ba, amma uban Shakatafi wani kazgin manomi ne, jira cida, ]an farauta, kwangeren kwamasgi, busasshe. Ko da yaushe yana kafa kunne ya yi bakan, domin ya ji }arar }ahon farauta, ya ridi sunguminsa ya kira karensa mai suna Babare, don su dunguma zuwa daji wurin kama karya, inda za a dinga yi musa kirari ana cewa, "Kwan]angwam na masu gari, arne mai tattalin sababi". Kuma uwar ta Shakatafi saboda tsiya ta yi mata kanta in ta fita sai ka ji yara suna cewa, "Bindindirwa ciriski bindin kin bi rariya wuta ta kama". Suna ta yi mata sowa.

Wata rana da Shakatafi ya ji haka, bai san lokacin da `yan galla suka tararo masa daga }ar}ashin }wayukan idanunsa ba suna ratata. Da ya gama shafe hawaye, sai uwar ta kira shi, ta rurumar da shi ta ba

shi na mai bara. Allah baran ashe nan duk wani irin mugun tukuburi yake ji, sai ya soma gunaguni har yana cewa; "Uban kowa mawadaci, uwar kowa abin sha'awa, amma ni iyayena tamkar tunku da mujiya"! Uwar ta ce masa duk da haka ya yi ha}uri.

A kwana a tashi, sai ya }ulla abotaka da Shamudora, abin ~alas-~alas har ya tare gidansu, su ci su sha su ]aura tare, ya zama kamar ]an gidan. Ya }i iyayensa }iri da muzu, suna ji suna gani, sai ka ce ba su suka haife shi ba, ga su kuma baki da hanci. Abin ka da duniya sai ran nan wata irin masassara ta rufe shi, ya kumbure sasul kamar taikin cukurfa, aka yi ta magani, amma ina! Bayan abin ya ci ruwan lifidda sa'annan aka kira wata bokanya, da ta je ta kunna kai inda saurayin yake, ta yi }urmuzugun }oki ta fa]a wurin, ai nan take ta fito a gigice tana cewa ita kam ba za ta iya maganin sa ba, domin wannan ciwo irin wanda ake ]auka da sauri ne, kuma mai wuyar magani ne.
Da jin haka sai attajirin ya hori barwansa da su fitar da shi daga gidansa su kai shi gidansu, sai aka kwakkwashe shi aka tallaba shi haka nan a }yamace, aka kai wa iyayensa aka jibge musu rakwakkwa~ai. Su kuma suka ci gaba da neman masa taimako, suna tattalinsa da nuna tausayinsa, uwa kuka uba kuka. Allah kuma ya taimake su ya sami warkewa sarai, ya yi sumul, ya zama lafiya lau }alau, ya mai da jiki tubarkalla. Ya yi hankali, ya ]angana da inda Allah ya aje shi.
Wa ne mutum! Lallai guntun gatarinka ya fi sari ka ba ni.

**AIKI I**

1) Ra]a wa labarin nan wani suna.
2) Me ake nufi da ya ri]i sunguminsa?
3) Me ake nufi da abin ka da duniya?
4) Me ka gane da "attajirin ya hori barwansa"?

**AIKIN GIDA**

1. Ashe dai “hannunka ba ya ru~ewa ka yanke ka yar.”
2. Ta yaya wannan karin - magana ya yi daidai da labarin nan.
3. Me za ka ce a kan sunayen da suka fito a labarin nan?

**TA{AITAWA**

A kauyen Tangaram an yi wani yaro da ya guji iyayensa saboda Allah bai ba su samu ba. Amma da ya shiga fitina attajirin da ya like ma ya yi watsi da shi, sai ga shi ya koma gidansu, ya hakura ya zauna da su haka nan.

**MANAZARTA**

Alhassan, H. and Musa, U.I, (1989) et al, New Nigerian Newspapers, Kaduna.

**KASHI NA 6: RUBUTUN JAWABI MAI LINZAMI**

**GABATARWA**
A darasin da ya gabata an yi bayani kan insha'i da rabe-rabensa. A wannan kashi, za mu duba rubutun jawabi mai linzami

**MANUFA**
Manufarmu a nan ita ce koyar maka yadda za ka fahimci rubutun jawabi mai linzami domin ka gane shi duk inda ka gan shi.

**MATAKAN NAZARI**
(a) Za ka yi nazarin salon rubutu mai linzami domin fahimtar bambancinsa da sauran salo na rubutu.
(b) Ya kamata ka san wasu hanyoyin rubutu ko salo don tantance su da rubutu mai linzami.

**SABABBIN KALMOMI**
Sanin sababbin kalmomi na cikin bun}asar harshe. Saboda haka akwai bukatar sanin wa]annan kalmomi: **sa}o; shugaba; walwala**; **yanci; tsari**; **salo**; **doge; hujjoji; shirme; watayawa**.

**RUBUTUN JAWABI MAI LINZAMI**
Jawabi dai na nufin magana ko rubutu wanda ya }unshi bayani kan wani abu. Wato kamar sa}o ne na mayar da martani ga wata magana wadda aka riga aka yi. Saboda haka wata magana ce ko kuma wani rubutu ]angane da ra'ayi na wani mutum, game da wata harka. An fi yin amfani da kalmar ‘jawabi’ wajen maganar shugabanni, wato manyan mutane a cikin al'umma. Misali, jawabin mai martaba Sarkin Musulmi da sauran ire-irensu.
Jawabi mai linzami shi ne wata hanya ta rubutu mai hana walwala. Ita wannan hanya akan nemi a }ayyade wa mai rubutu yawan kalmomin da zai yi amfani da su. Wato babu `yanci na walwala ga shi mai rubutu. Ana iya cewa an sa wa mutum linzami domin a jawo shi ga kawai abin da ake so. Linzami dai mun san wani abu ne na fata dogo mai tsawo wanda ake sa wa doki a baki domin a sarrafa shi.
Idan muka dubi rubutu ta wannan hanya za mu ga cewa bukata ita ce a yi rubutu kan wani tsari da ake so a wani lokaci mai yawa }ayyadadde.

**AIKI I**
1. Me ake nufi da rubutun jawabi mai linzami?

Rubutu iri - iri ne. Wato akwai hanyoyi na rubutu. Ba wai rubutu ba kawai har magana tana da salo. Akwai salon rubuta wasi}a ga aboki, akwai salon rubutawa ga babban mutum ko kamfani. Haka kuma akwai salon rubutu na musu (muhawara) wanda mai rubutu zai doge kan wani abu ya nuna ta yadda ya fi wani da hujjoji irin nasa. Bayan wannan, akwai kuma rubutu mai siffantawa. Wato, mai rubutu zai fa]i yadda wani abu yake ko gida ko gari ko abin hawa, ko wata mace da sauransu. Sannan akwai kuma rubutu na kara zube, wato, labari kai tsaye na wani abu ko wani mutum, da dai sauransu. Duk wa]annan wa]ansu salo ne na rubuta labari ko kawo abu a rubuce ta wata hanya don isar da sa}o.
Duk wa]annan salo sun bambanta da rubutu mai linzami. Shi wannan rubutu a kan samu wasu }a'idoji da mutum dole ya bi don haka, idan aka ce layi ]ari dole ya tsaya nan layi ]ari ko kuma a ce a rubuta labarin jirgin sama. Duk wanda ya rubuta labarin jirgin }asa ko jirgin ruwa ya yi shirme. Wannan ya nuna cewa dole mutum ya tsaya inda a aka ce ya tsaya. Bayan doka ko }a'ida, rubutu mai linzami na iya zama kowanne daga wa]anda aka fa]i a sama. Dalili kuwa shi ne kowanne ka ]auka ka ]afa masa linzami shi ke nan ka mayar da shi mai linzami. Hanyar yin haka ita ce misali, idan aka ce, a rubuta muhawara ana iya cewa ka nuna yarda kawai ko kuma ka }i yarda. Wannan linzami ne aka li}a wa rubutun muhawara ya zama mai linzami.
Haka idan na siffantawa ne ana iya cewa ka soki siffar ko ka yabe ta. Wannan shi ma ya zama linzami. Idan kuma rubutu na kara zube ne, wato labari ana iya cewa ka nuna yarda ko rashin yarda da abubuwan cikin labarin. Saboda haka linzami wani takunkumi ne da ake ]afawa wajen ba da umarni na yadda ake so rubutu ya kasance. Muhimmancinsa shi ne idan ka bi abin da aka ce, ka huta. Rashin muhimmancinsa shi ne takura mai rubutu da hana shi watayawa ko takura ta ~angaren kalmomi idan an ba da }a'idar ko

nawa ake so.Wani muhimmanci kuma shi ne sanin abin da ake so ba sai ka wahalar da kanka ba wajen rubutu mai yawa. Wani muhimmancin kuma shi ne al'umma na da walwalar hanyoyi idan ka duba ire-iren hanyoyin ko salon rubutu. Ana iya cewa rubutu mai linzami na da rauni idan aka kalle shi ta fuskar hana mai rubutu ya yi amfani da nashi tunani sai wanda aka ce masa. Wato akwai linzami ga tunanin marubuci.
Idan muka yi nazarin wa]annan abubuwa game da rubutu mai linzami muna fahimtar cewa akwai amfani ko muhimmanci ta wani ~angare, sannan akwai rashin amfani ko muhimmanci kuma ta wani ~angare.

**AIKI II**

1. Ta wace hanya za a iya la}a wa insha'in muhawara linzami?

**AIKIN GIDA**

1 Mene ne jawabi?
2 Wace hanya jawabi ke samun linzami?
3 Shin jawabi mai linzami na da amfani?
4 Wace kalma ce za ta yi amfani tsakanin 'walwala' da ' takura' wajen fassara jawabi mai linzami?

**TA{AITAWA**

A wannan kashi ka koyi abubuwa kamar haka:

- Rubutun jawabi mai linzami,
- La}a wa insha'i na muhawara linzami.
- La}a wa labari linzami;
- La}a wa insha'i na siffantawa linzami

**MANAZARTA**

Zarruk, R. M. et al. (1990) University Press Ltd.

**FASALI NA 2: FURUCI DA GININ KALMA**

**KASHI NA 1: BA{A{E**

**GABATARWA**

Harshe ko magana babbar baiwa ce da Allah ya yi wa ]an Adam. Hasali ma, ai harshe ne babban abin da ya bambanta mutum da sauran halittu, domin ta hanyar harshe ne ]an Adam ya fi sauran halittu ilmi da hikimar rayuwa.

Babu tantama, hatta wanda bai je makaranta ba ya san da zaman jerin haruffa, domin kuwa ma har 'yar wa}a ake yi ana cewa:

'Komai girman ]an boko,

ba zai wuce e bi si di ba'.

Wato ma'ana, ko me mutum ya zama sanadiyyar makaranta to da e bi si di, wato abjadin bokon ya fara, ke nan komai ]aki ya samu albarkacin }ofa ne.

**MANUFA**

Ana fatar yayin da ka nazarci wannan kashi ka:

(1) gane cewa furuci tubalin farko ne na dukkan zance;

(2) fahimci cewa a harshen Hausa, sautukan sun kasu nau'i biyu, ba}a}e da wasulla;

(3) bambance tsakanin nauo'in ba}a}en Hausa.

**MATAKAN NAZARI**

A bi wannan kashi a sannu, ban da garaje, a bi shi mataki – mataki, a yi }o}arin la'akari da karkasuwar ba}a}e da wasulla, kana a yi }o}arin amsa tambayoyin da aka bayar dalla-dalla don kuwa wannan kashi ne harsashin ginin dukkan sauran kasusuwan da suka shafi nahawu.

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| **Nahawu:** | Fannin nazarin kalmomi da jumloli da fasalin tsarin zance. |
| **Cunkoso:** | Wato tarin abu da yawa. |
| **Gwauro:** | Abu }wara guda tilo. |
| **Goyon ba}a}e:** | Ha]uwar ba}a}e fiye da biyu su tayar da furucin ba}i guda. |

**MATANI**

Shi dai harshe, wato a magance ko a rubuce, cunkoso ne ko ha]akar sautuka kan ta da kalma. Ita kuma kalma idan ta ha]u da wasu kalmomi `yan uwanta sai su tayar da jumla. Su kuma jumloli su ke tayar da zance.

Su kuwa sautukan nan da suka kasance tubalan ginin kalma sun kasu zuwa nau'i biyu: ba}a}e da kuma wasulla. Domin haka a harshen Hausa kamar a wasu harsuna ana ha]a ba}a}e ne da wasulla domin a samar da kalma.

**BA{A{E**

Duk da cewa ba a iya cewa wa]anne suka ]ara muhimmanci tsakanin ba}a}e da wasulla. Ba}a}e sun gota yawan wasulla. Domin masana sun yi ittifa}i cewa akwai ba}a}e guda talatin da ]aya a Hausa. Bugu da }ari kuma an karkasa ba}a}en nan zuwa nau'i biyu: gwauraye ko sau}a}a da kuma masu goyo.

**Gwaurayen Ba}a}e**

Gwaurayen ba}a}e su ne ba}a}en da suke }wara ]ai-]ai ko falen ]aya. Wa]anda walau a magance ko a rubuce za a iske ]ai-]ai suke su ne: b, ɓ, f, m, n, t, d, ɗ, k, }, g, s, z, r, l, h, c, j, w, t, y, da kuma ba}in hamza wato, shi kuwa ba}in hamza ya fi wakana yayin furucin wasali.

**AIKI I**

Kawo adadin gwaurayen ba}a}e ka kuma fa]i dalilin da ya sa ake kiran su gwauraye.

**Ba}a}e masu goyo**

Ba}a}e masu goyo kuwa su ne ba}a}e da aka yi musu }arin wasu ba}a}e su ha]u su zama ba}i guda mai furuci guda. Ga su:

Gy, fy, ky, }y, gw, kw, }w, da kuma ‘y, ~, ], }, ts

**AIKI II**

Kawo adadin ba}a}en Hausa, ka kuma jero su.

**AKIN GIDA**

(1) Gida nawa za ka iya karkasa ba}a}e?
(2) Me ya bambanta na'uoin ba}a}en?
(3) Kawo kalmomi 5 masu nuna ba}a}e masu goyo.
(4) Fa]i adadin ba}a}en da ke cikin wannan jumla ka kuma ja musu:

“Rashin sani ya ]arar ma rashin tsaba, barna ko da to gyada ce”

**TA}AITAWA**

Kamar dai yadda aka bayyana a baya, harshen Hausa tamkar wasu harsuna, ba}a}e da wasulla wato sautuka kan cu]anya da juna su haifar da kalmomin da ake magana da su. Da]in da]awa mun gane cewa su ba}a}e guda talatin da ]aya ne kana kuma sun kasu zuwa manyan rassa biyu wato gwauraye da masu goyo.

**MANAZARATA**

Gala]anci.l M.K.N (1976) *An Introduction to Hausa Grammar. Iba]an* - Nigeria.
Bagari, D. M. (1986). Bayanin Hausa. Imprimerie Elmaarif Al-jadida, Moroc
Ibrahim, Y. Y. et al. (1992). Darussan Hausa. Iba]an: University Press Limited.
Jinju. M.H. (1981) *Rayayyen Nahawun Hausa* N.N.P.C. Zaria
Zaria A.B.(982): *Nahawun Hausa. Lagos Thomas Nelson.*
Zarruk, R.M. (1980) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa. Iba]an University* Press, limited.

**KASHI NA 2: WASULLAN HAUSA**

**GABATARWA**

Kamar yadda Hausawa ne ke cewa hannu ]aya ba ya ]aukar jinka, to haka lamarin yake tsakanin ba}i da wasali, sai sun ha]u sannan a samu kalma.
Hasali dai, ba}i da wasali ]anjuma ne da ]anjummai. To, yannzu za a yi bayani ne a kan wasali**.**

**MANUFA**

Ana burin a }arshen wannan kashi ka:

(1) gane cewa wasali nau'i ne na furuci;
(2) gane cewa a Hausa zance bai faye ma'ana ba sai da wasali;
(3) bambance tsakanin nau'o'in wasullan Hausa.

**MATAKAN NAZARI**

Kafin a fa]a wannan kashi da ke bayani a kan wasulla ya kyautu a yi bitar kashin da ya gabata a kan ba}i domin ]anjuma ne da ]anjummai.

**SABABBIN KALMOMI**

Gwauron wasali- wasali }wara guda
Tagwai/Auren wasali - wasulla biyu masu zaman kansu da kan cu]anya da juna su tayar da furuci.

**MATANA**

Idan dai ana biye da wannan kashi tiryann-tiryann, an ambata tun can wajen gabatarwa cewa wasulla su ne abokan burmin ba}a}e domin cu]anyarsu da juna ne ke tayar da kalma.
Masana sun bayyana cewa, akwai wasulla guda goma-sha-biyu. Daga cikin wannan adadi akwai gwauraye da masu aure.

**Gwaurayen wasulla -** Wasulla ne da suke falen ]aya - ]aya wato, guda-guda. Bugu da }ari malamai sun kasa gwaurayen zuwa nau'i biyu; gajeru da dogaye

**Gajeru** : akwai gajerun-wasulla guda biyar, su ne:

| | | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|---|
| 1. | /a/ | Misali | kafa | daka | kafaa | dakaa |
| 2. | /i/ | Misali | ciki | ki]i | cikii | cikii |
| 3. | /o/ | Misali | goro | toto | gooro | ungo |
| 4. | /u/ | Misali | gudu | hu]u | uku | muuduu |
| 5 | /e/ | Misali | gefe | refe | geefee | waje |

**Dogaye -** Suma gwaurayen wasulla ne amma babban abin da ya bambanta su da gajeru shi ne su wajen furta su akan ]an tsawaita wasalin, shi ne ma ya sa ake ce musu dogaye wato masu tsawo. Ga su:

| | | | |
|---|---|---|---|
| 1. | /aa/ | Kaazaa | maataa |
| 2. | /ii/ | tiitii | kiifi |
| 3. | /oo/ | kookoo doogoo | |
| 4. | /uu/ | huuhuu tuuruu | |
| 5. | /ee/ | keekee | sheefe |

**AIKI I**

Yi bayanin gwaurayen wasulla.

**TAGWAN WASULLA/WASULLA MASU AURE**

Wasula masu aure su ne nau'i na biyu na wasullan Hausa. Ana kiran su da wannan suna saboda mabambantan wasula gwauraye guda ne kan ha]u su fitar da wannan furuci. Su ne:

(1) /au/ - auree, audugaa, kau]aa, dau]aa, garau

(2)  /ai/  -  aikii, taikii, fai-fai
(3)  /ui/  -  guiwa, kui~ii

Sai wani abin lura da dogayen wasulla gwauraye shi ne, duk da cewa a furuci wasulla biyu ne a wajen rubutu na yau da kullum wasali guda ake rubutawa.

**AIKI II**

Yi bayanin tagwan wasali auren wasulla.

**AIKIN GIDA**

(1) Kawo adadin wasullan Hausa ka kuma jero su.
(2) Me ya bambanta gwaurayen wasulla da tagwaye ko masu goyo.
(3) Kawo kalmomi 5 masu ]auke da auren wasulla.
(4) Kawo kalmoni 5 masu gwauron wasulla dogaye.

**TA{AITAWA**

A wannan kashi an yi }o}arin a bayyana cewa ne akwai wasulla guda goma sha biyu a Hausa. Da]in da]awa sun kasu zuwa manyan rassa biyu: gwauraye da tagwaye ko masu aure. Kana kuma gwauraye sun sake kasuwa zuwa nau'i biyu dogaye da gajeru guda biyar- biyar tun da dama su masu aure }wara uku ne kurum – wato /ai/ da /au/ da /ui/.

**MANAZARTA**

Abubakar, A (1991) A *Further Work of Hausa Plurals* an unpublished paper presented at a Seminar. Frankfurt, Germany.

Abrahams, R. C. (1947) *Dictionary* of *Hansa Language,* London U. D.

Gala]anci; M K: M. (1976) *An introduction to Hausa Grammar. Iba]an: University Press Ltd.*

Skinner, N. (1977) *A Grammar of Hausa for Schools.* Zaria NNPC Ltd.

Zaruk, R. N. (1979). *Shimfi]ar Ilimin Harsuna.* Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University, Zaria.

**KASHI NA 3: MA'ANAR KALMA**

**GABATARWA**

A kashin da ya gabata an bayyana cewa sautuka, wato ba}a}e da wasalla su ne kan taru su yi cu]anya da juna su haifar da kalmomi, ita kuma kalma idan ta yawaita takan gina jumla, yayin da jumloli kuma kan samar da zance ko kalami.

Ashe ke nan, idan ka ]ebe sautuka wato ba}a}e da wasulla babu abin da ya kama }afar kalma a wajen muhimmanci ta fuskar magana ko zance ko kuma rubutu.

**MANUFA**

Babbar manufar wannan kashi ita ce a fahimci:

(1) Mece ce kalma;

(2) Matsayin kalma a fasalin zance;

(3) Abubuwan da ke tantancewa tsakanin nau'o'in kalmomi a Hausa ta fuskar tsari.

**MATAKIN NAZARI**

Wannan kashi ma mataki-mataki aka tsara shi, a sabili da haka, ka tabbata ka fahimci kowane mataki kafin ka ci gaba, duk da cewa kowane daga cikin abubuwan da ake bayani a kai zaman kansa yake yi, dukkansu suna da ala}a ta }ut da }ut.

**SABABBIN KALMOMI**

**Suna** Ma'anar suna a nahawu ta ]ara ta yau da kullum. Suna na yau da kullum suna ne a Nahawu wato wanda ya yi wani aiki ko aka yi aiki ya fa]a masa.

**Aikatau** Ita ma kalma ce ta Nahawu da ke bayanin duk aikin da suna ya yi. Haka nan, za a iske cikakken bayanin wa]annan kalmomi da sauran ire-irensu kamar-sifa, bayanau da tsigilau, a kasusuwa na gaba.

**MA'ANAR KALMA**

Ita kalma kamar yadda Yahaya (1992:17) ya bayyana ta, lafazi ce mai dun}ulalliyar ma'ana da ake nunawa a rarrabe su wajen rubutu.

Domin haka, ana iya cewa kalma ha]akar sautuka ce, wato ba}a}e da wasulla, domin su tayar da curin zance guda mai cikakkiyar ma'ana, shin a magance ne ko a rubuce. Misali kamar a ha]a /g/ da /o/ da /r/ da /i/ da /b/ da /a/, a gina kalmar goriba wato 'ya`yan itace da ake gwagura/gwguya/gurgura da ha}ora ana ci.

A Hausa, nau'o'in kalmomi suna da ]imbin yawa sai dai manya daga cikinsu sun ha]a da suna, da aikatau da sifa da bayanau da wakilin suna da tsigilau da sauransu.

**AIKI I**

Mece ce kalma?

Akwai abubuwa uku masu matu}ar muhimmanci wajen tantance kalma a harshen Hausa walau a magance ko a rubuce. Wa]annan abubuwa uku kuwa su ne:

a - Tsawon wasali

b - Tsarin ga~a

c - Karin sauti

**TSAWON WASALI**

Kamar yadda ya gabata a kashi na farko a cikin wasullan Hausa, akwai masu gajeren wasali baya ga auren wasulla. Tsawon wasali kan rarrabe tsakanin makamantan kalmomi a Hausa, domin kuwa ana iya samun kalmomi 2 masu harufa ko sautuka iri guda wa]anda da taimakon fayyace tsawon wasali sai a bambance tsakaninsu.

**MISALI**

saa}aa/sa}aa, tsaarii/tsarii; ciikoo/cikoo; taasoo/tasoo ko tsakanin

ba}ii - launi mai duhu, kishiyar fari

baa}i - wato wa]anda suka bar gida suka zo wani sabon wuri

**Ko tsakanin:**

fari - launi mai haske, kishiyar ba}i

da faarii - wato soma yin wani abu farko ke nan.

B. Tsarin ga~a ma kan taimtaka wajen na}altar kalma da kuma fisshe ta cikin 'yan uwanta. Idan an ce ga~a ana nufin falle-fallen ba}a}e da wasula da suka ha]u suka gina kalma, misali, kalmar goriba idan aka furta ta za a iske da /go/ da /ri/ da /ba/ suka gina ta wato ba}i da wasali (b+w) da haka wannan kalma ga~a 3 take da su.

A Hausa, ana iya samun kalmomi masu ga~a ]aya, misali: zo, yi, bi, wa, kai, can su, da sauransu

Ana kuma iya samun masu ga~a biyu misali:

| | | |
|---|---|---|
| gida | wato | gi + da |
| gona | | go + na |
| auki | | au + ki |
| aji | | a + ji |

Ana iya samun masu ga~a uku-uku, misali:

| | |
|---|---|
| rikita wato | ri+ki+ta |
| mugunta | mu + gun+ ta |
| talaka | ta + la + ka |
| tsuntsaye | tsun + tsa + ye |
| agogo | a + go + go |

Ana iya samun masu ga~a 4:

| | | |
|---|---|---|
| samaniya | wato | sa + ma + ni + ya |
| ]awainiya, | | ]a + wai + ni + ya |
| kakkalma]a | | kak + kal + ma + ]a |
| dabaibaye | | da + bai + ba + ye |

Akan samu masu ga~a biyar ko da yake ba su faye yawa ba, misali:

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| shu | wa | ga ban | tar | |
| 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| mu | }ad | da | san | tar |

Hakanan kuma, idan an lura tsarin ga~o~in kan sha bamban: akwai masu

| | |
|---|---|
| (BW) | Ba}i da wasali misali bi |
| (BWB) | Ba}i da wasali da ba}i misali yar. |
| (BWW) | Ba}i wasali wasali, misali jaa da fuu da yii |
| (WB) | Wasali ba}i, misali ar, an |
| (W) | Wasali, misali a |

Don haka, idan muka duba kusan dukkan ga~o~in kalmomin Hausa za mu tarar ba su gota wa]annan tsari ba wato: W da WB da BW da BWW da BWB.

C. Kamar yadda tsawon wasali kan iya bambanta tsakanin kalmomi biyu wajen 'furta su, haka shi ma karin sauti yakan bambata furucin kalmomin da suka yi kama da juna a rubuce. Karin sauti kuwa shi ne hawa da saukar da murya kan kowace ga~a da aka furta. A Hausa muna da karin sauti nau'i.3:

(a) karin sama da ake alamta shi haka

(b) karin kasa da ake alamta shi haka

(c) kari mai fa]uwa wato

misali: ja bara

tafasa maraba

mashin sadaki

**AIKI II**

Wa]anne abubuwa ne ke da muhimmanci wajen gane kalma?

**AIKIN GIDA**

**(1)** Kawo kalmomi masu kama da juna guda 5 da yanayin wasali ke bambanta su.
**(2)** Kawo kalmomi guda 10 ka nuna yawa da tsarin ga~ar kowacce daga cikinsu.
**(3)** Kawo kalmomi guda 5 ka nuna yanayin karin sautinsu.
**(4)** Gwada tsawon wasali da tsarin ga~ar kalmomi guda biyar masu kama da juna.

**TA{AITAWA**

Ita kalma, wato curin zance guda mai ma'ana tana da muhimmanci sosai a wajen nazarin harshe. Bugu da }ari kalma ta kasu zuwa kasusuwa da dama a fagen nazarin harshe. misali akwai suna da 'aikatau da bayanau. Haka nan kuma abubuwa uku na da tasiri wajeri nazarin kalma wato tsawon ga~a da tsawon wasali da kuma karin sauti. A fagen wasali mun gane cewa a Hausa akwai wasula nau'i 12. guda 5 gajeru. guda biyar dogaye, guda 3 kuma masu aure.
Kalmomin Hausa ba su faye wuce ga~a 5 ba, akan samu masu ga~a ]aya. Ita kuwa ga~a imma dai ta kasance ba}i ko wasali guda ko kuma BW ko BWB ko BWW
Mun kuma fahimci cewa karin sauti kan bambance tsakanin kalmomi masu kamanni guda a Hausa. Karin sauti kuma ya kasu nau'I uku( 3) da na sama da na }asa da kuma mai fa]uwa.

**MANAZARTA**

Bagari, D.M (1986) *Bayanin Hausa* Imprimerie El rnaarif Aljadida -Maroc
Ibrahim, Y Y et. al (1992) *Darussan Hausa. Iba]an* UPL
Jinju**,** M.H. (1981) *Rayayyen Nahawun Hausa* . Zaria: NNPC Ltd.
Institute of Education ABU (1979) *Karatu da Rubutu a Harshen Hausa. Zaria:* Nelson

**KASHI NA 4: RABE RABEN KALMOMI**

**GABATARWA**

A kashin da ya gabata mun fara bayani ]angane da kalma, mun dai ji ma'anarta kana mun fahimci cewa tsawon wasali da tsarin ga~a da kuma karin sauti duk suna da gagarumar gudumuwa ta fagen nazarin kalma. Bugu da }ari mun ]an gutsura cewa tun da kalmomi ke, ha]uwa su tayar da jumloli, kuma su tayar da zance ashe: ke nan kalmomin za su kasance, nau'inau'i daidai da aikin da kowannensu ke, ginuwa a cikin jumla. A don haka, a wannan kashi-zamu yi }o}arin rarrabewa tsakanin nau`o`in kalmomin Hansa.

**MANUFA**

Muna fata yayin da ka nazarci wannan kashi, ya zamana ka na}alci:

(1) nau'o'in kalmomi a Hausa;
(2) bambance-bambance da ke tsakanin kalmomi;
(3) matsayi tare da aikin da suke gu]anarwa cikin zance:

**MATAKAN NAZARI**

(1) A fahimci gabatarwar wannan aiki sosai.
(2) A rika yi ana waiwayar kashin da ya gabata.
(3) A kuma lura da la}abin da ake kiran nau'o'in kalma da su sun sha bamban da yadda aka san su a yau da kullum.

**SABABBIN KALMOMI**

Nahawu — Fanni ne na nazarin matsayin kalmomi da jimloli da ma zance a bisa tsarin da masu harshe suke furtawa.
Allanbaran — Sam-sam ko faufau
Bigire — Wuri ko mazauni ko muhalli
Galibi — Sau da yawa
Sunan yannka - Sunan da ake kiran abu guda da shi ba lallai sunan littafi ba da aka saba da shi ko sunan yannka na yau da kullum.
Aikatau — A nan ba ]aya take da }wadugo na neman ku]i ba kamar dako.

**MATANI**

Kalmomi sun bambanta ta fuska dabam-dabam daidai da manufarsu ko aikin da suke aiwatarwa a cikin zance. A domin haka ne masana nahawu suka karkasa su zuwa rukuni rukuni da dama gwargwadon aikinsu da mafarinsu da muhimmancinsu.

Shi dai galibi duk wani zance, imma dai a ce wani ne ya yi wani abu ko zai yi ko yake yin abun nan, ko kuma abu kaza ne ya faru ko zai faru, ko yake faruwa a wani wuri ko kuma abu kaza mai kama kaza ne ya wakana ko zai wakana ko yake wakana a wuri kaza da siga kaza, ko a lokaci kaza.

Ma'ana, akan tarar akwai wanda ya yi wani abu, ko wanda aka yi wa wani abu da kuma 'abinda aka yi. Wani lokaci a ambaci yanayi ko siffar wanda ya yi abin da yanayin ya yi koma wanda ya yi wa.

Sabili da wa]annan bambance-bambance ne masana suka karkasa kalmomi zuwa rukuni-rukuni. kamar haka:

A Suna
B. Aikatau
C. Bayanau.
D. Sifa

Wa]annan ka]an ne kurum daga cikin rukunan kalmomi, sai dai sauran ba su faye muhimmanci kamar wa]annan ba.

**(A)** **Suna** - Kusan a iya cewa suna ya fi daraja a bisa sauran rukunan kalma domin kuwa duk abin da za a ambato a ce ya yi wani abu ko an yi masa wani abu ko kuma an yi wani abu da shi ko, domin shi.ko a kan shi, to suna ne. Suna ka iya zama sunan wani abu mai rai ko maras rai da wanda ake gani da wanda ba a gani (Yahaya:1992,1). A sabili da haka ne, masana suka raba suna zuwa rabe-rabe da dama. Ga misalai:

Na yannka - wato suna da ake kiran abu guda da shi. Misali Indo, Kande, Tani**,** Zariya, Kano,

Jigawa, Zamfara, Daura, Nijeriya, Amurka, Ingila, Saudiyya da sauransu.
Suna gama-gari -suna ne da ba lallai na abu guda ba domin kamar yadda sunanasa ya nuna za a iske shi a ko'ina ma, kuma sunan da yakan amsa ke nan, misali mutum , dabba ciyawa, goro, littafi, kujera, allo, alli da sauransu.
Suna tattarau - watau sunan da ke bayyana tsarin abubuwa da yawa a wuri guda misali }ungiya, garke, tawaga, duntsi, mudu, rukuni da sauransu.
Suna gagara-}irga- wato nau'in suna da ba a iya }irga shi saboda yawansa ko yanayinsa misali: ruwa, madara, gishiri, zuma da sauransu.
A don haka idan aka furta zance aka ce: Abdu ya sha ruwa jiya a ru]e, zamu iske Abdu ne ya yi aiki, wato shan ruwa. Domin haka da Abdu da ruwa duk sunaye ne.

(B) **AIKATAU** kalmar aikatau a nan tana nufin aikin da suna ya yi a cikin zance. Idan muka dubi misalinmu na Abdu ya sha ruwa jiya a ru]e, za mu tarar da ba a ~oye kalmar sha take ba a zancen. A don haka kalmar 'sha' ita ce kalmar aikatau a wannan jumla tun da ta bayyana aikin da suna (Abdu) ya yi ma suna (ruwa) wato ya sha .
Ga wasu misalai:

Abdu ya ci tuwo
Indo ta **<u>Kulle</u>** kofa.
Ruwa ya **<u>doki</u>** zakara
Kare ya **<u>kama</u>** zaki

A wa]annan misalai dukan kalmomin da aka ja ma layi domin fayyace aikin da sunayen da aka ambata ne suka yi. A fagen nazari aikatau, akan yi la'akari da abubuwa uku:

(1) Tsarin ga~a - wato yaya ga~ar aikatau ta ke gu]ana? Misali
Masu ga~a (1) yi, bi, shi , Sule ya bi Musa
1 2 1 2 1 2
Masu ga~a (2) ka/ma bu/ga ta/sa 1ro ya buga }ofa
1 2 3 1
Masu ga~a (3) ru/guhai,kam/fa/cii,bulibuilolanita/yar
1 2 3
bir/kike' Kulu ta kamfaci tuwo
1 2 3 4: 1 2 3 4 1 2 3 4
Masu ga~a (4) ri/kir/ki/ta Shi/rilrin/tar/' ttit/tuniku/do
1 2 3 4
Shi/ri/ri/ce Tani ta rikirkita
Masu ga~a (5) 1 2 3 4 5 1 2 3 4. 5
mu/ka/ddasantar Shu/wa/ga/ban/tar
Gwamna ya mu}addasantar da mu wurinsa sai dai kuma galibi akan la'akari da karin sautin kowacega~a wannan fanni.

(2) So kar~a da {i – kar~a: Baya ga waccan hanya ta nazarin ga~a da karin sautin aikatau, haka nan akan nazarci aikatau ta fasalin yardarsa ko rashin yardarsa da wata kalma ta zo bayansa.
Abin nufi a nan, su aikatau idan sun zo a zance za a fara suna ko wani abu daban ya biyo bayansu, misali:
Abdu ya <u>ci</u> tuwo
Kande ta <u>kulle</u> }ofa
Ruwa ya <u>doki</u> zakara
Kare ya <u>kama</u> zaki

A wa]annan misalai na sama, duk aikatau ]in da aka ja wa layi so-kar~au ne domin sun amince kalmonin suna wato tuwo da kura da zakara da zaki sun biyo bayansu su kuwa aikatau {i-kar~au faufau ba su amince ma wata kalma musamman suna ta taho bayansu kullum aikin kan komai ga mai aikin ne .

Bala ya bugu
Kande ta ta~u
Ige ta sauka

Mamman ya gaji

A wa]annan misalai za mu tarar suna ba ta biyo bayan aikatau da aka ja wa layi ba a maimakon haka aikin kan koma ga suna ne da ya yi aikin wato, Bala, Kande, Ige da Mamman.

(3) Nazarin wasalin {arshen kalmar aikatau a nan akan yi la'akari ne da harafi, wato wasalin }arshe ko ba}i da aikatau ya }are da shi.

Masana sun lura cewa aikatau ]in Hausa kan }are da wasali shida ne da kuma ba}i ]aya wato kamar haka:

-a Misali `buga', `yannka', `hana', `raka'

"Iro ya buga ganga".

"Kande ta tu}a tuwo".

-aa Misali tafasa, ruguzaa, rikitaa. Hindu ta ki]imaa shi. Kiyari ya karyaa ni. Laarai ta tafasaa shi.

Abin lura a nan shi ne wannan wasali kan zo ne a aikatau ]in da wakilin suna ya zo bayan shi.

e- Misali shige, buge, haye, cike, rikice, shantake.

Idi ya buge kurciya. Lanti ta cike rami. Kwaini ta wuce Lami.

i- tafi, guji, saki, an ragargaji, duddumbuli, Garba ya duddumbuli ruwa, Inno ta ragargaji kaji. Rabi ta }i aure

u- kakkammalu, gamu, ha]u, mammarka]u faru

Bala ya ha]u

Aiki ya gamu

Rigima ta faru

Abin lura da aikatau masu }arewa da wannan siga shi ne dukkansu aikatau ne kar~au.

o- so, ciko, zunguro, rankayo, sayo,biyo

Kande ta so Alu

Bilki ta **sayo nama.**

Gwamnati ta **bugo** ku]i.

ar- (di) kifar, amayar, mu}addasantar

Almajiri ya **kifar** da tuwo.

]alibi ya **kifar** da magani.

Malami ya **sanar** da

Su aiktitau masu }arewa da wannan siga za a iske (da) na shiga tsakaninsu da suna ko wanda aiki ya fa]a wa.

c-**Sifa:** Sifa ma na da muhimmanci a wajen nazarin kalmomin Hausa, domin kuwa ko da yaushe suna }ara fayyace sunan da ya yi aiki ne ko kuma mutanen da aiki ya fa]a mawa.

Misali. Yaro **}arami** ya sayi hula **fara.** A nan }arami sifa cc da ke }arin bayanin suna tilo kamar yadda kalmar **fara** ke da]a fayyace hula. Domin haka da fara da }arami duk kalmomi ne da ke bayyana sifa.

Masana irin su Jinju (IM) Bagari ( 1986). da Yahaya (1992) duk sun tofa albarkacin bakinsu a ]angane da sifa. Sai dai Yahaya (1992:4, ya raba sifa zuwa gida 3)

1. Sassau}a
2. Aiwato
3. Nanatau

Sassau}ar sifa ta hada da ba}i, fari, ja, }arami, babba, dogo, doguwa, dattijo da sauransu, misali. yarinya daguwa ta kama kaza. A nan daguwa da ba}a duk –sau}a}an sifa ne.

Aiwato: Ma}aryaci, mazambaciya, malalata, mayaudara, mamugunta, kamamme nunanniya, lafiyayyu.

Misali: mutum **ma}aryaci** ya kori gari.

Mangwaro **nunanne** ya faskari dillali.

Nanatau: buhu -buhu, iri-iri, kwando-kwando, dami-dami.

Misali: Maikano ya sayi sutura iri-irin.

Kande ta sari hatsi buhu-buhu.

**D. Bayanau**

Su bayanau aikinsu shi ne bayanin aiki wato kamar yadda sifa ke }ara bayyanni ga suna haka su ma bayanau ke }ara bayyanni ga aikatau.

**Misali:** Bala ya tafi jiya. Jiya bayanau ce da ke }arin bayani ga lokacin da aiki (tafiya) ya faru. A sabili da ha}a ne shaihunnai irinsu Zarruk (1988) da Bagari (1986) da Yahaya (1992) suka yi ittifaki cewa akwai bayanau nau'i-nau'i misali, masu bayyana lokaci da masu bayyana bigire (wuri) da masu bayyana yanayi kai har da masu bayyanne }ima.

Misali, bayanau na lokaci – ]azu jiya, gobe, bara, ba]i da sauransu. Mari ta tafi aji **]azu**

Fati ta shiga makaranta **bara.**

Masu bayyana bigire - can, nan

Misali: Kabiru ya fita ta **can**

Saro ta shiga ta **nan**

Masu bayyana yanayi - da sauri, a hankali, a guje, a ru]e da sauransu.

Misali: Hamza ya koma da sauri, zulai ta ruga a guje. Masu bayyana }ima - }warai, ainun, sosai, matuka.

Misali: Kaji sun soyu sosai.

Rogo ya dafu matuka.

**AIKI I**

(1) Kawo rabe raben kalmomi da ka sani.

(2) Bambanta tsakanin 2 daga cikin su.

**AIKIN GIDA**

(1) kawo nau'o'in suna tare da misalai.

(2) a. Kawo misalan aikatau so-kar~a guda 3.

b. Kawo misalan aikatau }i-kar~au guda 2.

(3) Kawo jimla mai kalmomin bayanau guda 3 -

(4) Kawo jimloh 2 masu sifa.

**TA{AITAWA**

A wannan kashi an yi }o}arin a bayyana karkasuwar kalmomi dai dai da irin amfaninsu ko aikin da suke yi a cikin jimla ko }unshin zance. An nuna cewa suna da aikatau da sifa, da bayanau na daga cikin mafiya muhimmanci.

Suna shi ne galibi kan aikata wani abu a zance ko kuma a aikata a kansa. Wato dai ko sunan mutum ko dabba ko wani abu.

Aikatau kuwa shi ke nuna aikin da ake ba da labarin an yi ko za a yi ko ake yi.

Sifa kuwa ko da yaushe tana }arin bayani ne game da suna, domin ta fayyace yanayinsa da sigarsa.

Bayanau kuma kan }arin haske ne ga yanayi ko wuri ko lokacin da aiki ya gu]ana.

**MANAZARTA**


Bagari, D.M. (1986) *Bayanin Hausa linperimerie el tnaarif* al Jadida Rabat Maroc

Jinju M.H (1981) *Rayayyen Nahawtt Hausa* NNPC Zaria Nigeria

Yahaya, I.Y et al (1992) *Darussan Hausa* UPL Iba]an Nigeria

Zaarruk M.R et al (1980) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa* UPL IbadahNijeriya

**KASHI NA 5: GA|AR KALMA A HAUSA**

**GABATARWA**
Kamar yadda yake a Zarruk da sauransu (1987), ga~a ya ce gunduwar ba}i da wasali a cikin kalma. Za ka ga cewa ga~ar kalma tana iya kasancewa ba}i da wasali kawai. Wani lokaci kuma ga~ar kalma za ta }unshi ba}i biyu da wasali a tsakaninsu.

**MANUFA**
Manufar wannan kashi ita ce a yi kyakkyawar gabatarwa a kan tsarin ga~a a }arshe, Hausa**.** An so a }arshen wannan darasi ya zama ka san abin da ake nufi da ga~ar kalma za ka iya bayani a kan ta cikin sassau}ar Hausa. Ana so kuma ka san ire-iren ga~ar Hausa da yadda za a yi bayaninta ga ]aliban Hausa yara.

**MATAKAN NAZARI**
Na farko ana so a wannan nazari ka fahimci cewa, ba ma'ana ake nazari ba. Ba kalma ake nazari ba. Wani tubali ne na kalma ake nazari amma domin ma'anarsa ba sai don }irarsa ba.

A nan ana so ka yi la'akari da cewa a Hausa akwai kalmomi gajeru, akwai kuma matsakaita, akwai kuma masu tsawo da kuma masu tsawo ainun. Yi }o}ari ka tattara ire-iren kalmomin da kake ganin za su shiga wa]annan rukunoni na rabe-rabe. Wannan nazari yana bu}atar natsuwa. Kamin haka kuma ya kamata a ce kana da masaniya a kan sautukan Hausa, ba}a}e da wasulla kar ka manta da hamza a matsayin ba}i. Ya kamata ka san ire-iren wasulla kamar gajeren wasali da dogon wasali da auren wasali. Don sai ka koma ka sake bitar wannan sassan.

**MATANI**
Kamar yadda ka gani a baya ga~a ita ce gunduwar ba}i da wasali a cikin kalma. Ka ga kuma an ce ana iya samun ba}i biyu da wasali a tsakaninsu su zama ga~a. Wato dai abin nufi a nan shi ne ka fahimci cewa a ga~a za ka sami a}alla ba}i ]aya da wasali. Ga surorin ga~a a Hausa:
(1) mai ba}i da wasali ka, ke, ki, ko, ku, ga, ge, gi, go, gu, la, le, li. lo.
(2) mai ba}i biyu da wasali a tsakiya kan, ken, kin, kon, kun, gan, gen, jin, gon. gun, san, sen, sin, son, sun, lan, len, lin, lon. lun.

**AIKI I**
1. [auki ga~a ]aya-]aya daga kashi na farko da kashi na biyu ka gina kalmomi masu ma'ana da su.
2. Wa]anne ga~o~i ne za su iya maimaita kansu su ha]a kalma?

Yaya za ka shaida ga~ar kalma a Hausa? Wannan abu ne mai sau}i. Ka ]auki kalma ]aya mai gunduwa uku ko hu]u ka yi }o}arin furta ta sannu a tsanaki wato dai-dai. Idan ka tuna ~angare na farko sai ka numfasa tukun ka fa]i na biyu. Wato haka dai zuwa har ka kai }arshen kalma. Idan ka yi haka to lallai ke nan ka daddatsa kalmomi zuwa ga~o~in da suka yi su**.** Bari mu gwada da wasu 'yan kalmomi a nan. Ga su:
a) katankatanaa
b) taakutuhaa
c) ta~argazaa
d) tantakwashii
e) kwatankwacii
f) baubaawaa
g) maisuwaa

A tsarin ga~a-ga~a wato za mu furta wa]annan kalmoni kamar haka:
a) ka-tan-ka-ta-naa
b) taa-ku-tu-haa
c) ta-bar-ga-zaa
d) tan-ta-kwa-shii
e) kwa-ttan-kwa-cii

f) bau-baa-waa
g) mai-su-waa

**AIKI II**

1. Wa]anne kalmomin Hausa da ka sani suke da tsarin ba}i da wasali.
2. Wa]anne kalmomi suke da tsarin ba}i biyu da wasali a tsakaninsu?

Ga~o~i a kalma sun karkasu gida-gida inda suke hamayya da juna. Na farko akwai ga~a bu]a]]iya, akwai kuma ga~a **rufaffiya**. Bu]a]]iyar ga~a ita ce wadda ta }unshi ba}i da wasali. Rufaffiyar ga~a ita cc wadda ta kunshi ba}i da wasali da kuma ba}i har wa yau.

Bu]a]]iyar ga~a a takaice takan }are ne da wasali. Wasalin da takan }are da shi ya kasu gida uku. Akwai mai }arewa da:

1. gajeren wasali
2. dogon wasali
3. auren wasali

**GA MISALAI**

1. Bu]a]]iyar ga~a mai gajeren wasali.
   katan**kata**naa
   taa**kutu**haa
   **ta**~ar**ga**zaa
   tan**ta**k**wa**shii
   kwatan**kwa**cii
   mai**su**waa

Duk ga~o~in da ake ja wa layi suna da bu]a]]iyar ga~a mai gajeren wasali ne.

2. Bu]a]]iyar ga~a mai dogon wasali.
   katankatan**aa**
   **taa**kutuhaa
   tabarga**zaa**
   tantakwa**shii** kwatankwa**cii**
   baubaaw**aa**
   maisuw**aa**
3. Bu]a]]iyar ga~a mai auren wasali
   Baubaawaa maisuwa

**AIKI III**

Kawo ma' anar wa]annan kalmomi da aka yi ta ba da misalai da
Rufaffiyar ga~a takan }are da ba}i. Manufa ita ce duk ga~ar da ta soma da ba}i kuma ta }are da ba}i ita rufaffiya ce.
Ga misalai.

| | |
|---|---|
| Katankatanaa | tan |
| Ta~argazaa | ~ar |
| Tantakwashii | tan |
| Kwatankwacii | tan |

Bayan bambancin da ke tsakanin bu]a]]iyar ga~a da rufaffiyar, akwai kuma bambanci tsakanin ga~a **sakayau** da ga~a **nannauya**

**GA|A SAKAYAU**

Ita ga~a sakayau ita ce mai ba}i da gajeren wasali kawai, ba ragi ba }ari. Shi ke nan ya bayanin ga~a sakayau. Abin lura a nan shi ne, duk ga~a sakayau bu]a]]iya ce. Ka duba baya ka ga misalan bu]a]]iyar ga~a. Ga wasu misalan ga~a sakayau: katatankatanaa, ta~argazaa, tantak washii, kwatankwacii

**GA|A NANNAUYA**
Ga~a nannauya ta ha]a da ire-iren bu]a]]iyar ga~a da kuma rufaffiya. A takaice dai ita nannauyar ga~a kan biyo ma karewa da wasali da mai }arewa da ba}i.
Mai }arewa da wasali tana }arewa da dogon wasali.
**Ga misalai**
Katankatanaa (dogon wasali)
Ta~argazaa
Kwatankwacii
Baubaawaa auren wasali
Maisuwaa

Ga~a nannauya mai }arewa da ba}i ita kuma ita ce wato mai ba}i biyu da wasali a tsakaninsu. Ga misalai: Katankatanaa ta fi ta~angazaa

Misalan nan ya kamata a kula da ]abi'un ga~o~i. Ga~a bu]a]]iya ana iya mata }arin ba}i sai ta komo rufaffiya. Saboda a na iya mata }ari shi ya sa ake kiranta bu]a]]iya.
Misali. Ka —> kab, kas, kar kan, kal

Ita kuma rufaffiyar ga~a ba a iya }ara mata ba}i. Idan aka yi haka to an fita fasalin harshen Hausa. Shi ya sa ake ce mata rufaffiya. Amma idan aka }ara mata wasali akan samu ga~o~i biyu bu]a]]u.
Misalin karin wasali kar —> kara (ka-ra); kul —> kula (ku-la)

**AIKIN GIDA**
1. Kafin mutum ya iya nazarin ga~a sosai, me da me ya kamata ya fahimta sosai?
2. Ga~a iri nawa ce ]angane da wasalin }arshe?
3. Idan ga~a ta }are da ba}i wace iri ce ke nan?
4. A Hausa ga~a na farawa da wasali kuwa?

**TA{AITAWA**
Ga~a ta kasu gida biyu: akwai bu]a]]iya akwai rufaffiya. Bu]a]]iyar ga~a iri biyu ce**:** akwai gajeriya, akwai kuma doguwa. Doguwar ga~a ta kasu gida biyu: akwai mai dogon wasali, akwai kuma mai auren wasali.

Har wa yau za a iya cewa ga~a ta kasu gida biyu: akwai sakayau akwai kuma nannauya. Gajeriyar ga~a ita ce kawai sakayau. Da doguwar ga~a da rufaffiyar ga~a dukansu sun fado rukunin nannauya.

**MANAZARTA**
Sani Mu’azu A.Z. (1989) *Ilimin Tsarin Sauti.* Kano, Triumph Publishing Co.
Zarruk R. M. et al (1997) *Sabuwar Hanyar Nazarin* Hausa Vol II

**KASHI NA 6: SAIWA DA [AFE-[AFENTA**

**GABATARWA**
A kashi na farko an yi bayani a game da kalma. Tun daga ga~o~i da ke ha]uwa su gina kalma har zuwa ma'anar kalma. Haka kuma, an yi maka bayani a kan azuzuwan kalma har zuwa amfanin raba kalma a cikin rubutu da karatu.

A wannan kashin kuma za mu yi nazari ne har wa yau akan kalma. Amma wani ~angare nata daban. Daga cikin abin da za mu yi nazari a kai akwai saiwar kalma da kuma takaitaccen bayani game da ]afi.

Don haka akwai ala}a matuka tsakanin kashi na farko da wannan kashi. Ka }ara bitar darasin da ya gabata.

**MANUFA**
A }arshen wannan kashi, ana sa ran ka iya:
1. Fa]in ma'anar saiwa;
2. Fa]in ma'anar ]afi;
3. Ba da misalan tushen kalmomi;
4. gina kalma daga tushenta;
5. rarrabe saiwar kalma da sauran abubuwa da ake li}a mata.

**MATAKAN NAZARI**
1, Ka yi bitar kashin da ya gabata saboda ]angantakarsu.
2. A cikin wannan kashi akwai misalai masu tarna}i don haka ka natsu sosai.
3. A duk lokacin da aka kawo misalai, to kai ma ka yi tunanin irin wa]annan misalai.
4. Ka tabbata ka yi dukkan aikin da aka bayar.

**SABABBIN KALMOMI**
**Saiwa -** tushe/asali
**[afe-]afe-** li}e-li}e
Tarna}I - wuya
Jirkita - sauya

A kashin da ya gabata in ka lura, an ce ba}a}e da wasulla su ke ha]uwa su zama ga~a. Ga~o~i kuma ke ha]uwa su zama kalma. A cikin kowace kalma akwai tushenta wadda aka yiwa }ari ta ba da ma'ana. Saiwa na iya yiwuwa ta zama cikakkiyar kalma. Idan an yi wa saiwa }ari sai ta zama wata kalma mai cikakkiyar ma'ana.
Ibrahim ya tafi **fada**
Na ga wani **bafade**
Ibrahim zai je **fadanci**
A kalmomin da aka ja layi a }ar}ashinsu, saiwar tushen kalma ita ce fad. sai aka }ara - ba da kuma -nci. Da fada da fa]anci da bafade ba ma'anar su ]aya ba.

**Wani Misali**
Talauci, talauta, talauci, matalauci, matalauta. Saiwar wa]annan Kalmomi ita ce talak. Har ila yau a wani misali kamar haka:
Tushen kalma - **Yar**, za a sami
**Yaro**
**Yarinya,**
**Yara**
**Yaranta**
Bisa bayanan da misalan da suka gabata, za ka fahimci cewa a cikin kalma akwai wani sashe wanda ba ya jirkita. Saboda haka za mu iya cewa, saiwar kalma ita ce sashen kalma wanda ba ya sauyawa.
Yauzu tun da ka san abin da ake nufi da saiwar kalma, to yaya zaka iya rarrabe saiwar kalma? (Daga

littafin Darussan Hausa don manyan makarantun sakandare na su Ibrahirn Yaro Yahya).

## YADDA AKE FITAR DA SAIWAR KALMA

Yadda za ka fitar da saiwar kalma shine, ka shafe wasalin karshe na wannan kalma idan akwai wasalin. In kuma babu wasali a }arshenta, shi ke nan dukkanin ~angaren kalmar shi ne saiwar misali:

| A | B |
|---|---|
| Birjik | dogo |
| Sidif | zame |
| Kirin | salla |
| Biyar | turai |
| Takwas | yaro |

A wannan jadawali, kalmomin rukunin A babu wasulla a }arshensu. Rukunin B sun }are da wasulla, abin da ya rage idan aka shafe wasalin }arshen shine saiwa. Zai zama kamar haka ke nan:

dog
zam
sall
tur
yar

Daga wa]annan tushe za mu iya }ara wasu sashe su zama kalma. Saboda haka za su koma kamar haka:

dogo zame salla turai yaro

| Saiwa | kalmomi | | |
|---|---|---|---|
| Dog | dogo | dogaye | doguwa |
| Zam | zame | zamiye | zamewa |
| Sall | salla | sallan | masallata |
| Tur | turai | turanci | turawa |
| Yar | yaro | yarinya | yara. |

**AIKI I**

1. **Me ake nufi** da saiwar kalma?
2. Yaya ake fitar da saiwar kalma?
3. Saiwar kalma na jirkita kuwa?

## [AFE-[AFEN KALMA

yannzu ka san saiwar kalma, ka san yadda ake fitar da ita. Abin da za mu yi kuma shi ne ~angare na biyu na wannan kashi wato ]afe-]afen kalma.

## [AFI

Kamar yadda sunan ya nuna, ]afi shi ne li}awa a jikin wani abu. Saboda haka ]afi shi **ne li}awa** saiwa wani abu yadda za a gina wannan kalma. A misalinmu na farko, wato fada, bafade da fa]anci mun ce duk suna da saiwa fad. An lika - a da ba da - anci aka sami fada, bafade, fa]anci. Za mu iya fitar da saiwar da kuma ]afi na wannan kalmomi kamar haka:

| Saiwa | [afi |
|---|---|
| fad | fada |
| “ | fa]anci |
| “ | bafade |

Tun da aka fahimci ]afi da kuma yadda ake li}a shi a jikin saiwa, yannzu za mu shiga ire-ken dafi da aikin da suke yi a cikin kalma.

**IRE-IREN [AFI DA AIKINSU A CIKIN KALMA**

1. **[afi** na nuna mai yin aiki kamar haka: ma –

| Saiwar tushe | Aiki | Mai yi aki |
|---|---|---|
| Dunk | dunki | madinki |
| Gin | gini | magini |
| Nom | noma | manomi |
| Tuk | tuki | mayaudari |
| Yaud | yaudara | |

2. [afi na nuna asali kamar haka: Ba -

| **Saiwa** | **Asali** |
|---|---|
| Turai | bature |
| Kano | Bakano |

3. [afi na nuna sana'a ko dabi'a - anci

| **Saiwa** | **Sana'a** |
|---|---|
| Duk | dukanci |
| Fad | fa]anci |

4. [afi na nuna abin da ake yin aiki da shi kamar haka:

| **Saiwa** | **Aiki** | **Kayann aiki** |
|---|---|---|
| Gog | goga | magogi |
| Lik | lika | maliki |
| Jingin | jingina | majingini |

**5.** Yana nuna wurin yin aiki misali, ma

| **Saiwa** | **Aiki** | **Wurin yin aiki** |
|---|---|---|
| Nom | noma | manoma |
| Bug | buga | mabuga |
| Dink | dinki | madinka |
| Aikat a | ikata | ma'aikata |

Bayan wa]annan misalai da ka gani, akwai wasu ire-iren ]afi amma sai a kashi na gaba za a yi nazari a kansu. (Daga littafin Rayayyen Nahawun Hausa na Muhammad H. Jinju).

**TA{AITAWA**

A cikin wannan kashi ka koyi:

- saiwa ko tushen kalma;
- yadda ake fitar da saiwar kalma;
- yadda za ka rarrabe saiwa da sauran sashen kalma;
- ]afi da yadda yake li}uwa a jikin kalma;
- ire-iren ayyukan dafi a jikin kalma.

**AIKIN GIDA**

Cike guraben da aka bari da abin da ya dace.

| | **Saiwa** | **Aiki** | **Mai yin aiki/Hanya aiki** |
|---|---|---|---|
| 1. | damfar | ma]anfari | - |
| 2. | ratay | rataya | - |
| 3. | - | - | ma' akaci |
| 4. | - | cuta | - |
| 5. | - | buda | - |
| 6. | Dub | duba | - |
| 7. | Hud | - | - |

| | | | |
|---|---|---|---|
| 8. | - | - | majema |
| 9. | Suy | - | masova |
| 10. | - | zagaye | mazagaya |

**MANAZARTA**

Gala]anci, M.K.M.(1976): *An Introduction to Hausa Grammar,* Longman.

Junju, Muhammadu Hanbali, (1981). *Rayayyen Nahawun Hausa,* Zaria: Northern Nigeria Publishing company.

Ibrahim Yaro Yahaya et al, (1992) *Darussan Hausa don Manyan Makarantun Sakandare* Iba]an: University Press PK.

**KASHI NA 07: [AFA GOSHI**

**GABATARWA**

A kashin da ya gabata, mun yi nazari ne kan saiwar kalma. Kuma an ce maka saiwar kalma ita ce sashen kalmar da ba ta sauyawa ko jirkita ta kowane, hali. Kuma duk wani abu da aka li}a mata ko ]afa mata domin samun ma' ana a cikin wannan kalmar ko kuma domin sauyawar ma' ana ya zama }ari. Zan }ara tuna maka kuma cewar mun yi magana a kan salon da ake bi ake gane saiwa daga jikin kalma. Kuma mun yi nazari a kan abin da ake cewa ]afi da kuma yadda yake li}uwa a jikin kalma.
A }arshen bayani akwai kuma misalai da na ba ka a kashin da ya gabata. Na ce maka akwai wasu ire-iren ]afi amma sai a wannan kashi za mu yi nazari akai.
Saboda haka, a cikin wannan kashi za mu yi nazari ne a kan ]aya daga cikin ire-iren ]afin da ake da shi. Wannan shi ne ]afa-goshi.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi za ka koyi:
1. ma'anar ]afa-goshi;
2. yadda ake sanin ]afa-goshi a cikin kalma;
3. yadda ]afa-goshi ke sauya ma'anar kalma;
4. yadda ]afa-goshi ke li}uwa a jikin saiwa su zama kalma ]aya;
5. azuzzuwan ]afa-goshi;
6. bambanta ]afa-goshi da sauran ]afe-]afe.

**MATAKAN NAZARI**

1. Ka yi }o}arin fahimtar ma'anar ]afi da kuma saiwar kalma,
2. Ka bi matakan da aka bi wajen gano yadda ]afa-goshi yake.
3. Ka yi }o}arin kawo misalai na kanka na kalmomi masu ]afi sannan ka za~e kalmomi masu ]afa-goshi.
4. Ka yi }o}arin bambance saiwar kalma daga nan za ka iya gane cewa wannan ]afi da ke jikin saiwa ]afa-goshi ne ko a'a.
5. Bayan aiki da aka bayar ka }ir}iri wasu misalan sannan ka ba abokin karatunka ya duba maka.

**SABABBIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| Saiwa | - | tushe ko kuma asali na abu |
| Sauyawa | - | jirkitawa ko canzawa |
| [afa | - | li}a |
| [afe-]afe | - | li}e – li}e |

**[AFA-GOSHI**

Kamar yadda sunan ya nuna, idan ka shafa kan ka tun daga farkon kai har zuwa }arshe, za ka iya raba kan zuwa gida uku. Gida na farko za ka ce min shi ne goshi, na biyu kuma ma]iga, wato tsakiyar ka ke nan, sannan gida na uku kuma }eya. Kamar yadda ka ce farkon kai shi ne goshi domin shi aka fara gabatarwa kafin wani ~angare ko sashi na kai. To haka nan ma a wannan kashi an kira shi da sunan ]afa-goshi ne domin shi ne abin da ake li}a wa saiwar kalma a farko a gina kalmar. Farkon kalma a nan, wato shi ne goshinta. Misali:

| | | |
|---|---|---|
| bagobiri | bakatsine | |
| mawa}i | ma]inki | |
| mafurta | mashiga | |
| masana | makoma | da sauransu. |

A cikin wa]annan misalai za ka iya gane ]afa-goshi a farkon saiwar kalma. Don haka ba ri mu yi }o}arin gano saiwar kalmomin. Biyo ni a hankali.

| **Saiwa** | **]afa-goshi** |
|---|---|
| Gobir | **Ba**gobiri |
| Katsina | **Ba**katsine |
| Wa}a | **Ma**waki |

| | |
|---|---|
| [inki | **Ma**]inki |
| Shig | **Ma**shigi |
| San | **Ma**sana |

To ka lura da cewar a cikin kalmonin nan kafin saiwar an }ara wani abu. Yi }o}arin gano su kafin ka ga yadda na yi nawa.
Ina fata ka gama.
To duba ka ga yadda na yi, ka kwatanta da naka.

| | |
|---|---|
| Akwai | ba a bagobiri |
| | ba a bakatsine |
| | ma a mawa}i |
| | ma a madiniki |
| | ma a mashigi |
| | ma a masana |

Wa]annan misalai su za su yi maka jagora a dalilin da aka samu abin da aka li}a a farkon saiwar kalma ]afa -goshi.

**AIKI I**

Ciro abin da aka ]afa a farkon saiwar wa]annan kalmomin.

| | | | | | |
|---|---|---|---|---|---|
| 1. | Babafullatani | 2. | Bazazzagi | 3. | Bakano |
| 4. | Bature | 5. | Macuci | 6. | Ma'aikaci |
| 7. | Mahori | 8. | Matashi9. | Mazaganta | |
| 10. | Makewaya. | | | | |

Yannzu tun da na gane cewa duk abin da aka ]afa a farkon saiwar kalma ana ce mai ]afa -goshi, to za mu shiga abu na ga~a.

**IRE-IREN [AFA-GOSHI DA ABIN DA SUKE NUNAWA**

1, Ɗafa- goshi na nuna asali, misali:

| **Kalma mai ]afa goshi** | **Asali** |
|---|---|
| Bazazzagi | Zazzau |
| Bakatsine | Katsina |
| Bazamfare | Zamfara |
| Bature | Turai |
| Balarabe | Arab |
| Banufiya | Nufe |
| Bafade | Fada |

A nan, an yi amfani da ]afa-goshi wajen nuna asalin wa]annan kalmomi.

**2.** Ɗafa goshi na nuna sana'a misali:

| **Sana'a** | **saiwa** | **(]afa - goshi)** |
|---|---|---|
| bafade | fad | ba |
| baduku | duk | ba |
| mawanki | wanuk | ma |

A nan kuma ]afa goshi ya yi amfani wajen fitar da sana'a

3. [afa-goshi na taimakawa wajen nuna mai yin aiki, misali:

| **Saiwa** | **Aiki** | **Mai yin aiki** | **(]afa-goshi)** |
|---|---|---|---|
| Aikat | aikata | ma'aikaci | ma |
| Nom | noma | manomi | ma |
| yauda | yaudara | mayaudari | ma |
| damfar | damfara | madamfari | ma |
| Cut | cuta | macuci | ma |

4. [afa-goshi ná nuna abin da ake yin aiki da shi (kayann aiki) misali:

| Saiwa | Aiki | Kayann aiki | ]afa-goshi |
|---|---|---|---|
| Dub | duba | madubi | ma |
| Gog | goga | magogi | ma |
| Bud | buda | mabu]i | ma |
| Burg | burga | maburgi | ma |

5. ]afa-goshi na nna wurin yin aiki, misali:

| Saiwa | Aiki | Kayann aiki | ]afa-goshi |
|---|---|---|---|
| Aikat | aikata | ma'aikata | ma |
| Soy | soya | masoya | ma |
| Bug | buga | mabuga | ma |
| buy | buya | ma~uya | ma |
| Jem | jema | majema | ma |
| Kom | koma | makoma | ma |
| Hor | hora | mahora | ma |

In ka lura an kara wa]annan ]afa-goshi suka nuna wurin yin aiki.

**AIKI**

1. Kawo misalan ]afa-goshi a jikin saiwa mai nuna sana'a guda 10.
2. Kawo misalan ]afa-goshi mai nuna wurin aiki guda 10.

**AIKIN GIDA**

1. Mene ne ]afa-goshi?
2. Ta yaya za ka gane ]afa-goshi a jikin saiwa?
3. Kawo misalan kalmomi masu ]auke da ]afa-goshi guda ashirin ka warware su ]angane da abin da suke nunawa

**TA{AITAWA**

- A cikin wannan kashin ka koyi:
- ma'anar ]afa-goshi;
- yadda ake gane ]afa-goshi a jikin saiwar kalma;
- ire - iren ]afa-goshi;
- abin da ]afa-goshi suke nunawa a jikin kalma.

**MANAZARTA**

Junju, Muhammadu Hambali (1981) *Rayayyen Nahawun Hausa*, Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

**KASH1 NA 8: [AFA-CIKI**

**GABATARWA**

A farkon wannan fasali mun fara nazari ne a kan kalma. Kuma muka ce kalma lafazi ce - mai dunkulalliyar ma'ana da ake rarrabewa wajen rubutu. Kuma mun yi bayanin ire-iren kalma. Mun ce sun ha]a da su suna da wakilin suna, da sifa da aikatau da sauransu. Mun kuma yi bayanin cewa kalma tana }unshe da abubuwa masu yawa. Akwai saiwar kalma. Mun kuma yi bayani a kan yadda za ka iya gane saiwar kalma. Daga nan kuma mun yi bayani a kan ]afi. Mun fa]i ma'anarsa tare da gamsassun misalai. Sannan kuma muka yi magana a kan ]afa-goshi da yadda yake li}uwa a jikin saiwar kalma. Har yau, mun yi bayani a kan ire-iren ]afa-goshi da kuma yadda yake sauya ma'anar kalma idan ya ]amfaru da saiwar kalma.

Bugu da kari, mun yi nazarin ]afa-keya, mun ga bambancinsa da ]afa-goshi. ]afa-}eya ma mun ga ire-irensa wanda aka kawo a cikin misalai masu yawa.

To, a wannan kashi abin da za a yi bayani duk ha]e suke da sauran kashin da suka gabata. Wannan kashi shi ne cikamakon su. Sai ka biyo ni mu je. Za mu yi nazari ne kan ]afa-ciki.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi za ka san:

1. ma' anar ]afa-ciki;
2. ]angantakar ]afa-ciki da saiwar kalma;
3. ]angatakar ]afa - ciki da ]afa-goshi;
4. ]angantakar ]afa - ciki da ]afa-keya;
5. yadda ]afa-ciki yake li}uwa a jikin saiwa.

**MATAKAN NAZARI**

1. Ka yi bitar kashin da ya yi magana a kan saiwar-kalma.
2. Ka }ara yin bitar ]afa-goshi.
3. Ka }ara yin bitar ]afa-}eya.
4. Yi }o}arin gano dagantakar su.
5. Yi ayyukan da aka bayar a wannan kashin.
6. Ka kawo misalai irin wanda aka ba ka a cikin wannan kashi.
7. Wannan kashin ka san shi ne ]an autansu don haka sai ka yi duk abubuwan da aka ce a yi.

**SABABBIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| [amfaru | - | cikuwa |
| ]angantaka | - | ala}a |
| ]an auta | - | na }arshe |
| cikamako | - | na cikan abu |

Kafin mu shiga cikin bayani a kan ]afa - ciki, bari irin tuna maka wani abu a kan saiwar-kalma da kuma ]afi.

Saiwar kalma na ce maka ita ce sashen kalma wadda ba a sauyawa. Wato ita ce asalin tushen wannan kalma. Idan saiwa ta ha]u da wani abu sai a samu kalma mai ma'ana.

Ka }ara tunawa mun ce maka ]afi shi ne li}a wa saiwar kalma wani abu yadda za a gina wannan kalma. Kuma mun ga ire-iren ]afi da aikinsu a cikin kalma.

Kuma mun yi nazari a kan ]afa-goshi da kuma ]afa-keya. To yanzu za mu yi magana a kan ]afa-ciki. Amma kafin nan ga wani ]an aiki na somin ta~i.

**AIKI**

1. Me ake nufi da saiwar kalma?
2. Yaya ake fitar da saiwar kalma?
3. Saiwar kalma na jirkita kuwa?
4. Kawo misalan ]afi.

5. Mene ne bambancin ]afa-goshi da ]afa-keya?

**MA'ANAR [AFA - CIKI**

Kamar yadda sunan ya nuna ]afa-ciki shi ne abin da ake mannawa saiwar kalma a ciki a gina kalmar, misali:

| | |
|---|---|
| murhu | murahu |
| gurgu | guragu |
| aska | asake |
| kurma | kurame |
| birni | birane |

A misali na farko a ]afa-ciki ne. A misali na biyu -a ]afa-ciki ne. Haka nan duk ba}i ko wasalin da aka ja layi a karkarshinsa ]afa-ciki ne. Amma bari in fitar maka da shi dalla-dalla a cikin jadawali domin ka sami sau}in fahimta.

| **Saiwa** | **]afa-ciki** | **Kalma** |
|---|---|---|
| gark | a | garaka |
| murh | a | murahu |
| gurg | a | guragu |
| ask | a | asake |
| kurm | a | kurame |
| birn | a | birane |

**DANGANTAKAR [AFA-CIKI DA SAIWAR KALMA**

Saiwa takan samu ]afi ne a farkon ko kuma a }arshenta. ]afa-ciki ya kan zo ne a cikin saiwa, kuma in an samu ]afa-ciki yana }arawa kalmar ma' ana, misali:

| | | | |
|---|---|---|---|
| Saiwa | Tilo | ]afa-ciki | Jami |
| Murh | murhu | -a | murahu |

A wannan misalin ]afa-ciki ya }ara ma'anar kalmar daga tilo zuwa jam' i.

**TA{AITAWA**

A wannan kashi ka koyi:

- ma'anar ]afa-ciki;
- yadda ake gane ]afa-ciki;
- yadda ake ware ]afa-ciki a jikin saiwa;
- ]angantakar saiwa da ]afa-ciki;
- bambancin ]afa-ciki da sauran ]afe-]afe.

**AIKIN GIDA**

1. Me ka fahimta da ]afa - ciki?
2. Kawo misalan kalmomi masu ]afa-ciki.
3. A ina ]afa-ciki yake fito wa saiwa?
4. (a) A kalma, wane abu ne ba ya sauyawa?
   - A Farkonta.
   - B. [afinta
   - C. Saiwarta
   - D. [afa-keya

   (b) In za a fitar da saiwar kalma sai a
   - A) Shafe ba}in farko.
   - B) Shafe ba}in }arshe.
   - C) Shafe wasalin farko.
   - D) Shafe wasalin }arshe.

(c) ]afa - ciki
  A) Wasali ne.
  B) Ba}i ne.
  C) Wasali da ba}i ne.
  D) Ba}i ne ko wasali.

(d) Mene ne matsayin 'e' a kalmar garewani?
  A) ]afa-goshi ne
  B) ]afa-ciki ne
  C) ]afa-goshi ne
  D) Saiwa.

(e) Mene ne matsayin 'ma' a kalmar ma]inki?
  A) ]afa-goshi ne
  B) ]afa-}eya ne
  C) ]afa-ciki ne
  D) [afi-ne

(f) Fitar da saiwar kalmar `danniya'
  A) dan
  B) dann
  C) danni
  D) da

(g) Fitar da saiwar kalmar `zakanya'
  A) za
  B) zakan
  C) zak
  D) zaki

(h) [afi shi ne
  A) saiwa.
  B) saiwar kalma.
  C) li}uwa a saiwar kalma.
  D) mannuwa a kalma.

(i) Akwai ]afi iri
  A) biyu
  B) ]aya
  C) uku
  D) hu]u

(j) Saiwa sashe ce ta
  A) ]afa-goshi.
  B) kalma.
  C) ]afa-ciki.
  D) ]afa-}eya.

**MANAZARTA**


Jinju, Muhammadu Hambali (1981) *Raray.ven Nahawun Hausa.* Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Ibrahim Yaro Yahya et at (1992) *Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandire.* lbadan: University Press Plc

Zarruk R. M. et at (1987) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Kananan Makarantun Sakandare.* Ibadan: University Press, Plc.

**KASHI NA 9: [AFA {EYA**

**GABATARWA**

A kashin da ya gabata, na ba ka wasu ayyuka daga ciki har da aikin gida. Kuma na ce maka ka kawo jerin misalan kalmomi masu ]auke da ]afa-goshi. Lalle idan ka yi su to wannan kashin ba za ka sami matsalar fahimta ba sosai domin akwai ala}a da wancan.

Na ce ka shafi kanka. Da ka shafa sai ka ce min ya kasu kashi uku. Ka tuna? Ka ce min akwai goshi da tsakiyar ka (ma]iga) sannan da }eya.

To a wannan kashi za mu yi nazari ne a kan abin da ake kira ]afa-}eya.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi, za ka koyi wa]annan abubuwa:

1. fa]in ma'anar ]afa-keya;
2. dalilin da ya sa aka sa wannan suna ]afa - keya;
3. bambanta ]afa-keya da ]afa-goshi;
4. sanin yadda za ka gane ]afa-keya;
5. sanin yadda za ka ware ]afa-}eya daga jikin saiwa;
6. sanin ire-iren ]afa-keya da ayyukansu idan sun ha]u da saiwa;
7. sanin yadda ]afa-keya yake sauya ma'anar kalma.

**MATAKAN NAZARI**

1. Ka }ara kawo misalan kalmomi masu ]afa-goshi.
2. Ka sami abokin karatunka ya duba maka misalan da ka kawo.
3. Ka yi }o}arin bambanta misalan dá aka bayar ]afa-goshi da kuma ]afa-keya.
4. Kar ka manta ka kawo misalai bayan na ba ka nawa.
3. Ka yi ayukan da aka ba ka, sannan ka duba amsoshi a bayan littafi.

**SABABBIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| **Jam'i** | **-** | abubuwa masu yawa wanda ya fi ]aya. |
| **Sauyawa** | **-** | canzawa |
| **{eya** | **-** | }arshen }o}on kai |
| **Alaka** | **-** | ]angantaka |

**[AFA {EYA**

Kamar yadda }eya ta kasance }arshen }o}on kai haka ma wannan ]afa-}eya take. Abin nufi a nan shi ne, an sa wannan sunan ne domin takan zo ne a }arshen saiwar kalma sa~anin abin da ke zuwa a farkon saiwar kalma. Shi ]afa-}eya sai saiwar ta }are tukun sannan a ]anfara a }arshen kuma ya zama kalma mai ma'ana.

Saboda haka, za mu ce ]afa-keya shi ne abin da ake li}a wa saiwar kalma a }arshe a gina kalma. Misalin kalmomi masu ]amfare da ]afa-}eya.

Fa]anci
Dukanci
Godiya
Togiya
]anniya
Wankau

A wa]annan misalai namu (Jai, za mu iya ganin ]afa-}eya alle idan muka yi }o}arin fitar da saiwar kalmomin kamar haka:

| **Saiwa** | **]afa - keya** |
|---|---|
| fad | anci |
| duk | anci |
| god | iya |
| tog | iya |

]ann    iya
wank    au

Idan ka lura za ka ga saiwar daban take da kuma aka ]amfara wa]annan ga saiwar sai su zama kalma mai ma' ana. Kuma in ka }ara lura za ka ga sun zo ne a }arshen saiwar kalma. To, haka ]afa-}eya yake, ko a yaushe, shi ne na }arshen saiwar kalma.
Wani misali kuma;
Mugunta
Farauta
Yarinya
Zakanya
Jaka. (macen jaki)

Ka lura cewar akwai }ari da aka yi a }arshen saiwar kalmomin. Bari ka gani –
A cikin kalmomin an kara;

| | | |
|---|---|---|
| -unta | a | mugunta |
| -awa | a | farawa |
| -inya | a | yarinya |
| -anya | a | zakanya |
| -a | a | jaka |

Wannan }arin da yake ya zo ne a }arshen saiwar kalma don haka ya zama ]afa-}eya ke nan.

**AIKI I**

1. Mece ce ]afa-keya?
2. Mene ne ya bambanta su da ]afa - goshi?
3. Yi }o}arin fitar da ]afa-}eyar da ke wa]annar kalmomin.
   A) Larabci.
   B) Turanci
   C) Gobiranci
   D) Yaro
   E) Yawaita
   F) Gajarta
   G) Gociya
   H) Zamiya

Yannzu tun da ka fahimci ]afa-keya da yadda yake fitowa a kalma, to za mu ci gaba da naziri a kan ire - iren ]afa-}eya da kuma aikin da yake yi.

**IRE IREN [AFA-{EYA DA AYUKANSA**

]afa-}eya ya bambanta, ma'ana akwai irinsu da yawa kuma kowanne da irin gudunmawar da yake bayarwa a jikin kalma. Akwai wanda in an li}a su a jikin saiwa sai su bambanta jinsin namiji amma, wasu kuma sai su bambanta tilo da jam'i. Kai akwai ma wa]anda suke nuna aikin da mutum yake yi domin samun ku]i. Ga misalansu nan.

1. ]afa-}eya mai nuna jinsi - misali;

| **Saiwa** | **Namiji** | **Mace** |
|---|---|---|
| Yar | yar**o** | yari**nya** |
| Tsoh | tsoh**o** | tsoh**uwa** |
| Bak | ba}**i** | ba}**a** |
| Mug | mug**u** | mug**uwa** |
| Far | far**i** | far**a** |
| Baraw | ~araw**o** | ~ara**uniya** |
| Gajer | Gajer**e** | Gajer**iya** |

Abin da ka ga an ja layi a }asa shi ne ]afa-}eya kuma ai ka ga duk tushensu ]aya amma ]afa-keya ya mai da wani namiji wata kuma mace.

2. [afa-keya na nuna harshe ko al'adar mutum ko kuma sunan }abila, misali.

| Saiwa | Ɗafa keya mai nuna }abila ko harshe |
|---|---|
| Katsina | Katsinanci |
| Gobir | Gobiranci |
| Tur | Turanci |
| Arab | Larabci |
| Fulat | Fulatanci |
| Nuf | Nufanci |

3. [afa - }eya na nuna halin mutum. Idan kalmar suna ne in aka }ara ]afa-}eya sai ya nuna hali na mutum. -

| Saiwa | Halin mutum |
|---|---|
| Mug | Mugunta |
| Rag | Ragwanci |
| Rikit | Rikitacce |
| Firgit | Firgitacce |

4. [afa - }eya na nuna sakayyar aiki. Wato abu da ka yi wa wani shi ma ya yi maka irinsa. Misali, kana son matarka, ita kuma tana son ka. Tsakaninku akwai soyayya. In kuna }in juna tsakaninku akwai }iyayya. Ga wasu misalai.

| Saiwa | Ɗafa-}eya mai nuna sakayya |
|---|---|
| Cu] | Cu]anya (hulda) |
| Sak | Sakayya |
| Nun | Nunayya (nuna juna) |

5. Ana amfani da ]afa-}eya domin nuna aikin da ake yi domin samun ku]i,

| Saiwa | Ɗafa-}eya mai nuna aiki |
|---|---|
| Wank | Wankau |
| [ink | [inkau |

6. [afa-keya na nuna aikin da mutum biyu ko mutane fiye da biyu ke yi wa juna, misali.

| Saiwa | [afa-}eya mai nuna aiki |
|---|---|
| Yard | Yarjejeniya |
| Ams | Amsheseniya |

A wannan misalai, in akwai al}awari da kuma yarda tsakanin mutum biyu ko fiye sai a ce yarjejeniya.

7. [afa-keya na nuna sana'a idan an ha]a shi da saiwar kalma, misali:

| Saiwa | Sana'a |
|---|---|
| Fad | Fa]anci |
| Duk | Dukanci |
| Kasuw | Kasuwanci |
| Fatauc | Fatauci |

8. Ɗafa-}eya na nuna jam' i

| Saiwa | Tilo | Jam'i |
|---|---|---|
| {of | {ofa | {ofofi |
| Wat | Wata | Watanni |
| Was | Wasa | Wasanni |
| Kur | Kura | Kuraye |
| Dog | Dogo | Dogaye |
| Rig | Riga | Riguna |
| Zan | Zane | Zannuwa |

Ba}   Ba}i   Ba}a}e

Wa]annan su ne wasu daga cikin aikace aikace da ire-iren ]afa-}eya.

**ALA{AR [AFA-GOSHI DA [AFA – {EYA**

A can baya na ce maka ]afa-goshi koyaushe shi ke fara zuwa a farkon saiwar kalma. [afa -}eya shi ke zuwa ko yaushe a }arshen saiwar kalma.

1. Dukkansu wato ]afa-goshi da ]afa-keya suna li}uwa ne a jikin saiwar kalma.
2. A kan sami saiwa wacce za ta iya ]aukan ]afa-goshi da ]afa-}eya bada ma' ana.
3. Wani lokaci har sai ]afa-goshi da ]afa-keya sun ha]u da saiwar kalma ake samun, kalma mai ma'ana.

**Ga misalai**

| **]afa-goshi** | **Saiwa** | **]afa —}eya** |
|---|---|---|
| Ma | ]ink | i |
| Ma | wa} | i |
| Ba | Gobir | i |
| Ba | Nuf | e |

A wa]annan misalan an samu

Ma]inki

Mawa}i

Bagobiri

Banufe

Ka ga an samu ]afa - goshi da saiwa da ]afa-keya a kalma guda.

**AIKI II**

1. Kawo misalan kalmomi masu ]auke da ]afa-goshi da saiwa da ]afa-}eya
2. Akwai wani alaka tsakanin saiwar kalma da ]afa-}eya?

**AIKIN GIDA**

1. Mene ne ]afa-}eya?
2. Mene ne ]angantakarsu da saiwar kalma?
3. A kan sanni ]afa-}eya a farkon saiwar kalma?
4. Kawo misalan ire-iren ]afa-}eya guda uku.
5. Kawo misalan ayukan da ]afa-}eya ke yi.

**TA{AITAWA**

A cikin wannan kashi ka koyi:

- ma’anar ]afa-}eya;
- dalilin wannan suna ]afa-}eya;
- ire -iren ]afa-}eya;
- sauyawar da ]afa-}eya ke yi ya nuna abubuwa kamar su, jinsi, halin mutum, jam'i da sauransu a cikin jumla:
- alakar da ke tsakanin ]afa-goshi da ]afa-}eya;
- yadda ake iya samun ]afa-goshi. saiwa da ]afa-}eya a cikin kalma ]aya.

**MANAZARTA**


Jinju, Muhanu-nadu Hambali (1981) *Rayayyen Nahawun Hausa*, Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Yahaya, I**.** Y. et at (1992) *Darussan Hausa don Makarantun Sakandire.* Ibaɗan: University Press Plc.

**FASALI NA 3: NAHAWU DA AMFANI DA SHI**

**KASHI NA 1: JUMLAR HAUSA**

**GABATARWA**

Jumla ita ce jera kalmomi a cikin magana mai ma'ana. Akwai jumloli na Hausa iri-iri a bisa dokar nahawu. Kamar yadda jiki yake da ga~o~i, haka ita ma jumlar Hausa take da ga~o~i. Akwai jumla mai zaman kanta da kuma wadda ba ta zaman kanta: Akwai kuma sassau}ar jumla, da har]a]]iya da kuma sar}a}a}}iya: Haka kuma, akwai sashen jumla ]angantau, da sashen jumla bayanau da kuma sashen jumla siffatau.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi, ana sa ran ka fahinci:

a) ma' anar jumlar Hausa;
b) Tsare-tsarenta da nau’o’inta;
c) Ire-iren jumlar Hausa;
d) Gane sassan ]angantau, bayanau da siffatau.

**MATAKAN NAZARI**

a) Mai karatu ya karanta wannan kashi, kana ya fahinci manyan ~angarori na jumla,
b) A fara nazartar sau}a}an jumloli sannan masu sar}a}iya,
c) A nazarci sabbin kalmomi.

**DUKKAN AMSOHIN TAMBAYOYI SU NA A {ARSHEN WANNAN LITTAFI**

**SABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Nahawu | tsarin harshe cikin kalma |
| Harshe | hanyar sadarwa ta adabi |
| Jumla | tsara kalmomi bisa }a’idar harshe |
| Aikatau | aiki |
| Lamiri | wakili |
| Har]a]]iya | gwama abu biyu su zama ]aya |
| Sar}a}}iya | wadda aka cusa cikin wata |
| Ɗangantau | mai ]angantaka |
| Bayanau | mai siffatawa |

**JUMLAR HAUSA**

Idan ana maganar abin da ya shafi nahawu a kowane harshe kamar Hausa, to ana nufin yadda tsarin wannan harshen yake, wato yadda suke ha]uwa da juna cikin tsari mai kyau domin su bayar da ingantattun jumloli masu ma'ana da za su dace da yadda masu harshen ke magana a harkokinsu na yau da kullum.

Saboda haka, jumla a Hausa kalma ce da ake nufin yadda ake. tsara kalmomin Hausa tare da bin }a’ida domin yin magana. Ga misali:

a) Audu ya zo.
b) Ali ya karanta littafi.
c) Kande ta dafa abinci.

**TSARIN JUMLOLIN HAUSA**

Tsarin Jumlolin Hausa abu ne 'mai sau}in fahinta,' wato galibi jumlolin Hausa sukan }unshi ma'aikaci, lamiri, aikatau da kuma kar~au. Wa]annan abubuwa suna da ]angantaka ]angane da rawar da suke takawa a cikin jumla, wato kamar ko fuskar ma'aikaci ko da suna ne, to dole ne ya yi aiki tare da lamiri. Ga misali:

a) Musa ya tafi.
b) Sule ya wanke rigarsa.
c) Idi ya rubuta wasi}a cike da albishir.

**AIKI I**

1. Wa]anne abubuwa ne suke inganta jumloli?
2. Ba da ma'anar wa]annan kalmomi:
   i. Aikatau
   ii. Ma'aikaci
   iii. Kar~au
3. kawo misalan jumloli 3 ingantattu

**IRE-IREN JUMLAR HAUSA**

Akwai ire-iren jumlolin Hausa guda biyu manya; wato mai zaman kanta da kuma maras zaman kanta. Ita ta biyun, ana kiranta da jumlar ]angantaka.

i) Jumla mai zaman kanta tana iya tsayawa ko dogaro da kanta, wato ita ce jumlar da take da ma'ana cikakkiya. Ga misali:
   - Ali ya ci abinci
   - kande ta tafi
   - sani ya zo

ii) Amma maras zaman kanta kokuma jumlar ]angantaka ba ta da ma'ana cikakkiya. Galibi ba za a iya fahimtar ta ba sai tare da wata jumlar wadda }ira babba. Ga misali:
   - Wata ta tafi
   - Wata ta ga littafi
   - Wadda ta ga littafi ta tafi
   - Wani ya zo
   - Wani ya mutu
   - Wanda ya zo ya mutu

Saboda haka jumla dai suna ta tara, wato, akwai jumla mai aikatau da kuma maras aikatau. Haka kuma, jumla na kasancewa sassau}a, har]a]]iya da kuma sar}a}a}}iya. Ga misalan wa]annan jumloli:

i) Sassau}ar jumla
   - Audu ya zo
   - Fati ta tafi kasuwa

ii) Har]a]]iyar jumla
   - sun zo amma sun koma
   - sun ajiye sannan suka ]auka

(iii) Sar}a}}iyar jumla
   - wanda ya zo ya koma
   - yaron da aka aiko ya kawo sa}on

**AIKI NA II**

1. Yi bayanin manyan kasusuwa biyu na jumlar Hausa
2. Rubuta ta}aitaccen bayani kan:
   i. sassau}ar jumla
   ii. har]a]]iyar jumla
   iii. Sar}a}}iyar jumla
3. Kawo misalai 5 na jumla mai zaman kanta

**NAU'OIN JUMLAR HAUSA**

Jumlolin Hausa na da nau'i uku da suka shafi siffantawa, bayyanawa da kuma dangantaka, wato ta yanayin wa]annan ne ake fito da ainihin abin da jumla ta }unsa;

i) dangantau ya shafi dangantaka tsakanin wani abu da wani. A cikin jumlolin da ke biye, kalmomi **wanda**, **da**, su ne kalmomin dangantaka, wato wa]anda suka dangantaka sashe na farko na jumlar da saura.
   Ga misali:
   - **Wanda** ya zo ya koma
   - Agogon **da** ya ~ata an gan shi

- Rigar **da** sani ya ]inka ta siliki ce

ii) Bayanau yana bayyana suna ko aiki a cikin jumla. A cikin jumlolin da ke biye, kalmomin a mota. bakin kogi da ]azu-]azu, su ne bayanau wato masu bayyana suna ko aiki ]angane da yadda aka yi abu wurin da aka yi da kuma abin da aka vi amfani da su wajen yi. Ga misali:

- mutanen da suka zo **]uzu-]azu** sun zazzauna
- Audu ya tafi **bakin kogi**
- ’Yan jarida sun zo **a mota**

iii) Siffatau yana siffanta suna ko aiki a jumla. A cikin jadawalin da ke biye guntu da maguji da lalatacciya su ne ke siffanta ainihin yadda al’amura suke ta yadda za a fahimta. Ga misali:

- Yusuf yana noma da **guntun** gatari
- Yaro **maguji** ya karye
- Motar Audu **lalatacciya** ce

**AIKIN GIDA**

1. Nau'oinjumlolin Hausa nawa ka sani?
2. Me ake nufi da nahawun harshe?
3. Menene jumla? Bayyana tsarin jumlar Hausa
4. Kawo ire-iren jumlar Hausa, sannan ka dauki kashi daya ka yi bayaninsa

**TAKAITAWA**

A WANNAN KASHI, MUN NAZARCI WADANNAN ABUBUWA:

- Ma'anarrahawun harshe
- Matsayin jumla da tsarinta
- Ire-iren jumlar Hausa
- Dangogin jumla na dangantau, bayanau da siffatau

**MANAZARTA**

Ahmed, U. B. (1975) *A School Certificate Hausa Course,* Zaria: NNPC.
Gaaladanci, M.K.M. (1976) *An Introduction to Hausa Grammar: Longman*
Junju, M.N. (1980) *Rayayyen Nahawun Hausa, Zaria:* NNPC.
Mohammed, D. (1970) *Hausa Metalanguage,* Ibadan: University Press.
Zaria, A.B. (1981) *Nahawun Hausa*, Nigeria Thomas Nelson Nigeria

## KASHI NA 2: SASHEN SUNA DA RABE-RABENSA

### GABATA RWA

Sashen suna wani ~angare ne a cikin jumla wanda mai karatu ya kamata ya fahimta. A nan abin nufi idan aka sami cikakkiyar jumlar Hausa, to za ka tarar cewa an raba ta gida biyu. Akwai ~angaren suna da kuma na aiki, saboda haka, a nan za mu yi magana ne a kan ~angaren suna na jumlar Hausa.

### MANUFA

A }arshen wannan kashi, ana sa ran ka fahinci wa]annan abubuwa:

a) ma'anar yankin suna;
b) rabe-raben fasalin yankin suna a jumla;
c) dangantakar yannkin suna da sauran sassan jumla
d) bambancin yankin suna da kuma yankin aiki.

### MATAKAN NAZARI

a) yana da kyau ka karanta wannan kashi cikin natsuwa ka fahinci rabe-rabensa.
b) Ka amsa tambayoyin aiki da kuma na aikin gida
c) Ka kiyaye sassan jumla da irin sigogin da take ]auke da su.

### SABABBIN KALMOMI

Sassa = ~angarori
Tattaru = ha]uwa waje ]aya
Kwagiri = sanda wadda ake dogarawa
fahinta = ganewa
jumla = jeren kalmomi da suka tayar da ma'ana
Nahawu = }aidar harshe
Siffatau = mai siffata suna ko aiki
yankin suna = sashin farko na jumla

### SASHEN SUNA

Idan ka dubi jumlar Hausa to babu shakka za ka ga ta }unshi abubuwa daban daban. Amma dai kowace irin jumlar Hausa idan ka dube ta za ka tarar ta }unshi abubuwa kamar haka:

i) dole ne ta }unshi sassa na nahawu wa]anda aka shirya su suka tayar da jumlar Hausa cikakkiya mai ma'ana.
ii) Sashen nahawun da suka tattaru suka tayar da jumla zai kasance an gina shi ne a kan tsari sannan kowane sashe zai kunshi a kalla kalma daya ko ma fiye da daya.
A nan ga misalan tsararrun jumlolin Hausa masu ma'ana domin a jarraba a duba kowace bangare:
1. Habiba ta sayi gishiri.
2. Farar - }aya ta fi }aron – kalgo.
3. Wane ne ya ]auki kwagiri?
4. Wannan ya ]ara wancan.
5. Marowaci ya ga makwai]aici.
6. Wa]anda suka zo sun koma.
7. Naka ya fi nasa.
8. Tsakar fili ta fi bakin ruwa.
9. Can yamma da bakin kasuwa ta tafi.

### AIKI I

a) Mene ne ya kamata jumlar Hausa ta }unsa?
b) Yaya sashen nahawu zai kasance a cikin jumla?
c) Kawo jumlolin Hausa sau}a}a gudu biyar

**TSARIN YANKIN SUNA**
Kafin a kawo magana a nan, dole a fara kawo jumlar Hausa sannan a yayyannka ta domin mai karatu ya fayyace abin da ake nufi.

Jumla: Yaro ya tafi kasuwa.

To, a nan idan an tashi za a raba wannan jumla ne gida biyu, wato ~angaren aikau da kuma ~angaren lamiri kamar Haka:

Yaro / ya tafi kasuwa (aikau)

A ~angaren aikau za mu fi mai da hankali yannzu, wato "yaro", domin nan ne yankin suna a cikin jumlar.

1) yankin suna (YS) zai iya samun wasu }are }are, misali idan an ce "wani yaro", a nan (YS) ya sami }ari daga baya.

YS ⟶ mafayyaci + SN

2) Haka kuma yankin suna (YS) zai iya sumun }arin sifatau daga gaba kamar haka: (wani) yaro (fari)

YS mafayyaci + SN + sifa

3) Haka nan dai za a iya samun }arin wata kalma a ga~an aikau duk dai a yankin suna kamar haka;

4) (wani) yaro (fari mai dogon kai)

Saboda haka yankin suna zai iya ]aukar wasu kalmomi a gaba da kuma bayan aikau, yannzu ke nan jumlar mu ta farko ]in nan ta dawo kamar haka:
Wani yaro fari mai dogon kai ya tafi kasuwa.

**AIKI NA II**
1) Kawo jumla mai yankin suna. Wadda take da siffatau a ga~a da baya.
2) Me ake nufi da aikau?
3) Ko za a iya samun jumla marar yankin suna?

**AIKIN GIDA**
1) Yaya tsarin jumlar Hausa yake?
2) Mene ne ake samu a yankin suna na jumlar Hausa?
3) Mene ne bambancin lamiri da yankin aiki?
4) Ko yankin suna zai iya ]aukar siffatau?

**TA{AITAWA**
- Jumla tana ]auke da sassa a cikinta;
- yankin suna da yankin aiki;
- Aikau a yankin suna yake;
- suna yakan ]auki siffatau gaba da baya;
- a kwai jumla marar siffatau a yankin suna;

**MANAZARTA**

Ahmed, U. (1975) *A School Certificate Hausa Course.* Zaria: NNPC.
Gala]anchi M.K.M.(1976) An *Introduction to Hausa Grammar.* Longman
Jinju, M.A. (1980) *Rayayyann Nahawun Hausa*
Muhummad D. (1990) *Hausa Metalanguage.* Ibadan: University Press Limited.
Zaria A. B. (1981) *Nahawun Hausa,* Thomas Neslon Nigeria limited

**KASHINA 3: SASHEN AIKATAU**

**GABATARWA**

Idan aka ce aikatau, watakila abin da zai fara zuwa ran mai karatu shi ne aikatau da akan yi na mata wato daka da surfe da sauransu. To a nan, abin da ake nufi da aikaitau, shi ne a cikin jimla ta Hausa ma akwai ~angaren aikatau, bayan da muka yi maganar sashen suna a kashi na biyu da ya gabata. To a nan kuma za mu yi magana ne a kan ~angaren aikatau ]in.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi, ana sa ran za ka fahinci:

a) ma'anar aikatau;
b) yadda sashen aikatau yake a jumla;
c) ]angogin da suka shafi ita aikatau ]in;
d) dangantakar kowane sashe a jumla da aikatau.

**MATAKAN NAZARI**

a) A nan yana da muhinunanci mai karatu ya fahinci cewa yankin aikatau (lamiri) kamar yadda aka yi bayani a kashi na biyu da ya gabata.
b) A karanta matanin wannan kashi sau biyu domin a fahinci manufar kashin sosai da sosai.
c) A nazarci sababbin kalmomi kamar yadda suke a jere a wannan fanni.
d) Ka gwada rubuta jumloli masu yankin aikatau da kanka.

**SABABBIN KALMONI DA TA{AITA SU**

| | | |
|---|---|---|
| Yankin Aikatau | = | (YA) = inda aikatau take a jimla |
| Gurbin aiki | = | (GA) = inda aikatau da kar~a suke |
| Aikatau | = | (A) = aikin da ake yi |
| Kar~au | = | (k) = yankin suna a cikin yankin Aiki |
| Jumla | = | (J) = Jeren kalmoni masu ma'ana |
| sassa | = | ~angare-~angare |
| suna | = | la}abi |
| wakilin suna | = | mai wakiltar aikin da suna yake yi |

**YANKIN AIKI**

A wancan kashi da ya gabata mun yi magana ne a kan yankin suna, a halin yannzu kuma za mu yi magana ne a kan yankin aiki.
A nan yankin aiki ya fa]o ne a }ar}ashin lamiri kamar yadda yake a nahawun gargajiya.

Idan za a iya tunawa a wancan kashi da ya gabata, mun yi magana a kan wata jimla inda muka kawo misalai tare da kawo jimlar kamar haka:

Yaro / ya tafi kasuwa.

A wancan bayani mun kyale bangaren yankin aikatau inda kuma muke a yanzu mun bar wancan bayani. Dangane da daya bangaren.

ya tafi kasuwa

1) wannan yanki ya }unshi abubuwa guda biyu;
   a) akwai lamirin suna "ya"
   b) gundarin aikatau ]in ita ce "tafi"
   c) akwai kuma kar~au wato "kasuwa"
2) |angaren da ya shafi lamiri suna da aikatau nan ne ake kira gurbin aikatau
   Saboda haka za a iya alamta wannan kamar haka:

Gurbin Aikatau (GA) ⟶ (LS) + (A)

**AIKI I**

1) Mene ne aikatau?
2) Me ake nufi da kar~au?
3) Kawo yankin aikatau iri biyar.

**GURBIN AIKATAU**

Wasu misalai na gurbin aikatau sun ha]a har da irin kamar haka.

i) ya dawo
ii) ta koma
iii) sun hana
iv) ya kama
v) an mayar

Saboda haka dole a lura cewa ~angaren da ya shafi yankin suna wato "kasuwa" ke nan idan muka duba

Jumlarmu ta farko, ita ta fado a matsayin (kar~au) ke nan. Abubuwan da za su iya kasance kar~au wadanda yake suna ne kamar haka: gona, gida, littafi bakin kasuwa da dai sauransu. Saboda haka, wadannan duk za su iya kasancewa a matsayin karbau a sashin yankin suna na karkashin yankin aikatau.

Yankin aikatau din gaba ]aya wanda ya }unshi gurbin aikatau da kar~au ana iya suranta su kamar haka:

YA ⟶ GA + YS

Wato, yankin aikatau ya kunshi gurbin aikatau tare da yankin suna inda karbau yake. Su kuma za, iya rubuto misalansu kamar haka:

i) ya hangi wata
ii) ya dara na shehu
iii) sun kama Amarya
iv) ya fi na Hassan
v) ta gaishe da sarki

**AIKI II**

1) me ake nufi da gurbin aikatau?
2) Kawo gurbin aikatau iri biyar
3) Kawo misalan gurbin aikatau a cikin yankin aikatau guda biyar

**AIKIN GIDA**

1) Kawo Jimloli biyar masu aikatau.
2) Kawo bayanin yankin aikatau a cikin jumla.
3) Rubutajumloli hu]u sannan ka tantance gurbin aikatau.
4) Rubuta aikatau guda goma.

**TA{AITAWA**

- Jumla ta kunshi manyan sassa guda biyu.
- A cikin manyan sassan jumla a yanki suna da yankin aikatau.
- Yankin aikatau ya }unshi abubuwa biyu.
- A cikin yankin aikatau akwai gurbin aikatau da kuma aikatau.

**MANAZARTA**


Ahmed, U.S. (1975) *A School Certificate Hausa Course,* Zaria: NNPC.
Galadanchi, M.K.M. (1976) *An Introduction to Hausa Grammar,* Nigeria: Longman.
Jinju, M. H. (1980) *Rayayyen Nahawun Hausa,* Zaria: NNPC.
Muhammad, D (1990) *Hausa Metalanguage,* Ibadan: University Press Limited.
Skinner, N. (1972) *A grammar of Hausa,* Zaria: NNPC.
Zaria, A.B. (1981) *Nahawun Hausa,* Thomas Nelson, Nigeria . Limited

## KASHI NA 4: JUMLOLI MASU HARSHEN DAMO

**GABATARWA**

Harshe tsarin kalmomi ne cikin wata }ira mai ma'ana tare da bin }a'ida domin samar da zance mai ma'ana. To amma duk da haka a wasu lokuta sai a samu cewa ga jumla bisa tsari da }a'ida amma kuma tana da ma'ana fiye da guda ]aya. Hakika ma'ana takan fito a jumla mai harshen damo sai dai takan kasu gida biyu ko fiye da haka. Akan ce harshen damo ne saboda harshensa yana da gwafa, saboda haka duk inda aka ga wannan jumla a fili suke; wani zai ce ga yadda ya fahinci jumla. wani kuma ya ga shi ai ga yadda ya fahimta.

**MANUFA**

A lokacin da za a kawo }arshen nazarin wannan kashin, to kana iya ka:

(a) fahimci ma'ana biyu a jumla ]aya mai harshen damo da dalilan harshen damon.

(b) Ka iya bayani a kan jumla mai harshen damo.

(c) Ka san misalai da dama na jumla mai harshen damo.

(d) Ka fahinci nau'oin ma'ana na jumla.

**MATAKAN NAZARI**

(a) Ka nazarci wannan kashi sannan ka fahinci zubi da tsarin jumlar

(b) Ka san nau'o`i da yadda jumlar take faruwa

(c) Ka yi }o}arin kawo misalan jumlar

**SABABB1N KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Harshen damo | ma'ana fiye da ]aya |
| Ma'anar ~oye | wadda ba ta fito fili ba |
| Ma'anar sarari | wadda ta fito fili |
| Zubi da tsari | ainihin yadda abu yake |
| Siga | yanayin abu |
| Tsokaci | tunani ko nazari kan wani abu |
| Harshe | hanyar sadarwa ta amfani da magana |

**JUMLOLI MASU HARSHEN DAMO**

Iri wannan jumla a Hausa ta }unshi tsarin kalmomi na musamman cikin }ira mai bin }a'idar harshe domin fitar da furuci mai ma'ana da yawa.

Dalilai da dama kan sa a samu ma'ana fiye da ]aya, wato me yake sa a ce tana da harshen damo (Sigarta). Galibi irin wa]annan jumloli suna da ma'ana ta boye da kuma ta sarari. A ma'ana ta sarari, ita ce kan zo zuciyar mutum a lokacin da aka ambace ta ]angane da abin da ya faru a zahiri, wanda shi ne ma'ana. Haka kuma za a iya kallon wannan jumla da wata ma'ana wadda ba ta fito fili ba. Kalmomi ne masu sar}a}iya a wuri guda kan haifar da harshen damon, wato samar da ma'anoni biyu a lokaci ]aya.

**YADDA JUMLA MAI HARSHEN DAMO KE FARUWA**

Idan akwai jumla kamar:

{ananan yara na da wuyar tashi barci, to abin da zai zo zuciya shi ne saboda yanayin yadda kafatanin yara suke ne ya sa ba sa son su tashi daga barci, wato sun fi son su yi ta yi ba tare da an tashe su ba. Ita wannan ma'ana ta sarari ce. Amma kuma ana iya sake kallon jumlar ta wata fuska, wato cewa idaniyann mutane za su tashi yara daga barci suka sha wahala. A wannan ma'ana ta biyu ana iya cewa ta ~oye ce. Saboda haka idan aka yi la' akari da yadda ma' ana biyu ko fiye ke fita daga jumla guda, to sai a ambace ta da mai harshen damo, tamkar dai yadda harshen damon yake idan ya fito misali wannan siga jumololin kan ]auka wajen aukuwa da kuma ba da ma'ana fiye da ]aya.

**MISALAN JUMLOLI MASU HARSHEN DAMO**

Domin }ara fahimtar jumloli masu harshen damo ga wasu misalai da aka warware wa harshen damon kamar haka:

(a) Farautar zaki na da da]in kallo. A ma'ana ta farko, abu ne mai da]in kallo mutane su taru idan ana

yin farautar zaki, musamman saboda matsayin zakin a cikin dabbobi. Haka }ara wata ma' anar na zama cewa a duk lokacin da shi zaki yake farautar abincin da zai ci a daji to abu ne mai da]in kallo.

(b) Kande ta ]afa wa Musa wake. A ma'ana ta farko, Kande ta yi ]an banzan karambani da ta ]ebi waken Musa ta dafa ba tare da saninsa ba.
A ]aya ~angaren kuma ta iya zama kande ce da kanta ta dafa wake saboda Musa a }ashin kanta

(c) Yaran Halima da fati sun makara. Daga wannan jumla, za a fahimci ma'ana ta farko da cewa yaran da suka makara na Halima ne, amma tare da Fati suka makara. Haka kuma ana iya ]auka cewa da Halima da Fati mata ne guda biyu da ke da yara, kuma wa]annan yaran nasu ne suka makara. To ta haka ne ake iya kallon kowace jumla domin fahimtar ma'anarta ta sarari da kuma ta ~oye.

**AIKI I**

1. Wace ce jumlar Hausa mai harshen damo?
2. Kawo misalai 5 na jumla mai harshen damo.
3. Me ya bambanta jumla mai harshen damo da wata daban?
4. Yaya sigar jumla mai harshen damo yake?
5. Rubuta ta}aitaccen bayani kan:
   i. Ma'ana ta sarari.
   ii. Ma'ana ta ~oye.
6. Bayyana yadda jumla mai harshen damo ke farawa.

**AIKIN GIDA**

1. Mene ne matsayin jumla mai harshen damo a nahawun Hansa?
2. Nau'o`in ma'ana nawa ka sani na jumla mai harshen damo?
3. Ta yaya jumla mai harshen damo ke faruwa a Hausa?
4. Rubuta ta}aitaccen bayani kan wa]annan:
   i. Nahawun harshe
   ii. Kalma
   iii. Jumla

**TA{AITAWA**

A wannan kashi, mun nazarci abu buwa da dama da suka ha]a da:

- Ma'anar jumla mai harshen damo da dalilan samuwarta.
- Zubi da tsarin jumla mai harshen damo.
- Nau`o`in ma'ana a jumla mai harshen damo
- Yadda jumla mai harshen damo ke faruwa, da kuma misalai a cikin harshen Hausa.
- Yadda ma' ana kan ]auki siga a jumla, wato, ko dai ma'ana ]aya ko kuma fiye da ]aya.

**MANAZARTA**

Junju, M. H. (1980) *Rayayyen Nahawun Hausa,* Zara: NNPC:
Robinson, C, (1927) *Grammar of the Hausa Language,* 5th edition
Skinner, N. (1977) *A Grammar of Hausa,* Zaria: NNPC.
Taylor, F. W. (1959) *A Practical Hausa Grammar,* London
Zaria, A:B. (1981) *Nahawun Hausa,* Thomas Nelson: Nigeria.

**KASHI NA 5: RARRABA SUNAYE, TSAMO SUNAYE DA GANO SASSAN JUMLA**

**GABATARWA**

Kalmar suna a Hausa tana nufin abin da ake ambaton abu ko kiransa da shi. Kuma da suna ne za a iya bambanta abubuwa. Kowane abu na duniya yana da suna, kama daga mutane da dabbobi da tsuntsaye da }wari da itace da tsirrai da wurare da kayann aiki da har ma da ~oyayyun abubuwa wa]anda ba a ganinsu sai dai a ji ko a ga tasirinsu, misali, zafi da iska da zumunta da soyayya.
Ta fuskar mutane za a ga suna da sunayen yannka, wa]anda ba taro ake yi a ra]a musu su a ranar da yaro ko yarinya ya kai kwana bakwai a duniya ba.

Za ka ji ana kiran mutane da sunaye kamar su Abubakar ko Hadiza ko Sa'adatu ko Muhammadu ko Balkisu. To a nan wa]annan sunayen su ne irin sunayensu na yannka wa]anda aka zana musu kwana bakwai bayan haihuwa. Sannan kuma akwai la}abi ko sunayen la}abi wa]anda su kuma sunaye ne da akan sa wa mutane saboda wani dalili, misali, ranar da aka haife shi, ko lokaci ko yanayi ko jerin mata da mazan da aka haifa kafin haifuwarsu. To wannan ne ya sa kake jin ana kiran Bahaushe da sunaye irin su Talle, Tine/Altine, Jummai, ci-wake/Taroro, Wada,-Tanko, Kande da Gambo da dai sauransu.

Wurare ma suna da sunayen da aka san su da su, kuma ake kiransu da shi. Tabbatattu ko kafaffun wurare Suna da sunayen da akan kira mutane sun san inda ake nufi. kano, Sakkwato, Hadeja, Zariya, Daura, Nijer, Maradi da sauransu.

Haka ma abubuwan cikin gida da daji kai komai na duniya yana da sunan da ake kiransa da shi, wanda da zarar an ambata mutane sun san abin da ake nufi. Kuma abin ko ana ganinsa ko ba a ganinsa an dai tanada masa sunan da za a kira shi da shi. Misali, tukunya, riga, ]aki, ka]anya, zafi, iska, jaki, zaki, tana, maciji, takalmi.

**M A N U F A**

A cikin wannan kashin za ka fahinci abubuwa kamar su: sunaye da rabe-rabensu. Gano sunaye da tsamo su daga cikin matani
Gano sassan jumla

**MATAKIN NAZARI**

Ka kula da inda bayanin da ya zo a gabatarwa, domin samun damar kiyaye abubuwan da ke da muhimmanci ga bayanin sunaye a Hausa.

- Irin bayanan da ke ciki za su ba ka hasken hango batun sunayen Hausa.
- Haka ma za a fahinci rabe-raben sunaye.
- A }arshe kuma za ka fahinci yadda za a gane sashen suna da sashen aiki.

**SABABBIN KALMOMI**

Ana sa ran za ka ci karo da ba}in kalmomi da mai nazari zai nemi ya samu cikakkiyar ma'anarsu. Idan kalmomin da za mu iya tsamowa daga cikin wannan kashin sun ha]a da:

| | |
|---|---|
| Ambato | kira |
| Tasiri | Sakamakon aikin abu |
| Sunan yannka | babban sunan da aka ra]a |
| Sunan la}abi | sunan da aka sa saboda wani dalili. |
| Tabbatattu | Abubuwan da aka gaskata |
| Kafaffu | Abubuwan da aka }afa. |

**RABE-RABEN SUNAYE**

A Nahawun Hausa sunaye sun kasu kashi biyu ne, wato sunayen yannka da suna gamagari; shi sunan yannka mun ce suna ne wanda shi ne aka sa wa yaro ko yarinya bayan haifuwa, wanan har biki ake yi don ra]insa. Ta fuskar mutane ke nan. Baya ga mutane wurare ma a da sunayen yannka wa]anda aka saka musu, kuma da wa]annan sunayen ake kiransu. Saboda kafaffun wurare ne da aka tabbatar da samuwarsu to da zarar an ambaci sunan mutane sun san inda ake nufi. Ka ga kenan za mu iya raba sunayen yannka

zuwa gida biyu kamar haka:

SUNAYEN YANKA

| **Mutane** | **Garuruwa Da {asashe** |
|---|---|
| Abubakar | Daura |
| Muhammadu | Gusau |
| Hamza | Kano |
| Balkisu | Zariya |
| Salamatu | Damagaran |
| Mariya | Nijer |
| Yusufu | Neja |
| Ibrahim | Kaduna |

Baya ga wa]annan irin sunaye da muka kira sunayen yanka, wato ko da na mutane ko kuma na wurare, akwai wasu sunaye a Hausa. Misali, akwai sunayen dabbobin gida irin su tunkiya, doki, akuya da dabbobin daji irin su kura, gwanki, barewa da na ruwa irin su tsari, kada. Akwai tsuntsaye irin su kaza, balbela, jimina da kuma na kwari irin su tsutsa, tururuwa da tana.

Bayan wa]annan abubuwa masu rai akwai mu da abubawa wa]anda ba su da rai wa]anda ake amfani da su a rayuwa. Misali tabarma, fitila, littafi, tsintsiya da sauransu.

Haka ma akwai wasu sunaye na ~oyayyen abubuwa. Misali, sanyi, }iyayya, zumunci da sauransu. Wa]annan abubuwan ba a iya ganinsu. Saboda haka ba a ta~a su ko a sarrafa su akasin fitattun abubuwan da ake amfani kuma ake gani. Sai dai mutum zai iya jin tasirinsu, ko ya shiga halin da zai iya shaidar sakamakon aikinsu a rayuwarsa.

Akwai mu kuma da wasu sunaye da suke da bil'adama da dabbobi da abubuwa misali mutum, dabba, tsaba. Idan aka ce mutum zai iya kasancewa babba ko yaro, namiji ko mace misali. Halima ko Aliyu ko Kande ko Tanko. Dabba kuwa na iya zama bunsuru ko giwa ko jaki. Tsaba na iya zama ta gero ko ku]i ko alkama.


Idan aka tattara sunayen abubuwa masu rai da sunayen ~oyayyun abubuwa da sunnayen fitattun abubuwa da kuma irin sunayen da ke ha]a mutane ko dabbobi ko hutu, to, duk za a kira su sunaye gamagari. Sunaye gamagari sun rabu kashi hu]u:

Sunaye gamagari

Idan muka lura da bayanin da ya gabata, to muna iya ta}aita rabe-raben sunaye zuwa gida biyu manya wato sunan yannka wanda ya }unshi fannoni biyu da kuma sunaye gamagari wanda ya }unshi fannoni hu]u:

Sunaye Gama-gari

| | (1) | | (2) | (3) | (4) |
|---|---|---|---|---|---|
| **Dabbobi** | **Tsuntsaye** | **Da Kwari** | **Fitattun Abubuwa** | **|oyayyun Abubuwa** | **Dabbobi, Bil`adama Abubuwa** |
| Godiya | Talotalo | Tururuwa | Gatari | Soyayya | Mutum |
| Giwa | Cilakowa | Shazumami | Dutse | Mugunta | Bishiya |
| Kada | Shaho | Cinnaka | Labule | Jaruntaka | Ciyawa |
| Saniya | KurciyaKiyashi | Shigifa | Mutunci | Hutu | |
| | | | Muciya Tsaba | | |
| | | | | Dabba | |




**AIKI I**

1. Kawo sunayen yannka na mutane guda biyar da na wurare guda biyar
2. Me ya bambanta suna "Muhammadu" da suna "Awwalu"?
3. Idan aka ce icce ana nufin suna ne gamagari da ya dun}ule itace da yawa. To kawo sunayen icce guda shida da ka sani
4. Kawo sunan la}abi guda hu]u da dalilin da ya sa ake sa su.

**TSAMO SUNAYE DAGA CIKIN MATANI**

A ranar juma'a wani mutum mai suna Labbo, ya taso daga }auye ya shigo birnin Magaji neman abin hannu. Ya yi yawo har Allah ya gajiyar da shi bai samu kome ba, kuma ga yunwa ta kama shi tana neman ta halakar da shi. Sai ya yi kici~is da wani mai sayar da abinci. Ya kutsa kai ya shiga sai ya tarar da Bayerabiya ce mai sayar da abinci kuma ga shi shagon yá cika ma}il da mutane.

Shi ma ya zauna ya ce a kawo masa shinkafa da wake da nama. Ya ci sai da ya }oshi, sai ya gaya wa mai abincin ba ya da ku]in da zai biya ta, amma idan tana da aikin da za ta ba shi ya yi mata a madadin ku]in abincinta, to sai ta ba shi. Sai ta ce ita ba ta da aikin da za a ta ba shi. Sai ya tambaye ta ko ta yi ha}uri ta bar ma Allah, wato ta yafe masa. Har ta yarda ta ce ya tafi, sai ya sa kai ya kama hanya sai ta kira shi ya zo kusa da ita sai ta ce kuma ya tafi. Da ya juya baya zai wuce sai ta ]auki hannuwanta biyu, ta kai masa bugu a baya.

**AIKI II**

1. Tsamo sunan yannka guda biyu daga cikin labarin.
2. Tsamo sunaye gama gari guda goma sha biyar daga cikin labarin.
3. Akwai sunayen gamagari na ~oyayyun abubuwa guda biyu a cikin labarin. Kawo su.

**{ARIN MISALAI A KAN SASSAN JUMLA**

Duk cikakkiyar jumlar Hausa tana kasuwa zuwa gida biyu, wato akwai yankin suna da kuma yankin aiki. yankin na suna shi ne ke ]auke da suna da sauran }arin haske da aka samu game da shi sunan. Shi kuwa yankin aiki shi ne ke ]auke da aikin da ya faru a cikin jumla da ma sauran karin haske game da wannan aikin da aka yi a cikin jumla. Misali, idan muka ce "Wani farin yaro gajere ya kashe,fitilar ]aki".

'Sai a lura daga kalmar "wani "har }arshen kalma "gajere" duk suna ne. Kalmar yaro ita ce Sunanda ake magana kuma sauran kalmomin irin su "wani" da "farin" da "gajere" duk kalmomi ne da ke ba mu haske kan siffar yaro. Na farko dai mun gane namiji ne shi ya sa aka ce "wani" kuma launin fatar jikinsa "fara" ce ko akasin ba}i sannan kuma tsawonsa bai kai mizanin a ce masa dogo ba.

Wani farin yaro gajere ya kashe fitilar ]aki. Sashen da ya soma daga kalmar "ya" shi ne sashen aiki a jumlar domin shi ne ya }unshi aikin. Me yaron ya yi a jumlar? Ya kashe. Me ya kashe? Ko akan wa aikin ya fa]a. Sai mu ce fitila. Idan kuma aka ce wace fitilar ce ya kasha? Sai a ce ta ]aki ce ba ta wani wuri ba. Bari mu kawo wasu jumloli kuma mu raba su zuwa sashen suna da sashen aiki tare da amfani da wannan alamar "/" da ke nuna cewa ga kowane yanki na jumlar kamar haka:

Wani bako/ya kawo shanu jiya.

'Yar karamar yarinya/ta dafa Shinkafa.
Aliyu/ya tafi kasuwa.
Rabin Bello/ta saka sabon tuma}asa.
'Yan bokon zamani/sun fi na da sha}iyanci.
Wani }aton maciji ba}i/ya shiga rijiyar makaranta.
Fati karama/ta ci jarabawa.
Sabon littafin malam/ya fi da]in karatu.
Wata zungureyar mota ba}a wulik/ta shiga tasha.
Shar~e~iyar wu}a/ya yanka wa }afar.
[anmani mai nama/ya auri yarinya mai fura.

**AIKI III**

1. Kawo 'sunayen sassan jumla.
2. Wane }arin haske ne aka samu game da sunan da ke cikin wannan jumlar: Wata doguwar yarinya fara ta wuce.
3. Kawo jumloli biyar tare da raba su da alama.

**AIKIN GIDA**

1. Me ka fahimta da sunan yanka kuma me ya bambanta shi da la}abi? Ka kawo misalai don }awata amsarka.
2. Suna gama-gari ya kasu kashi hu]u. Kawo kowane kashi da misalai biyu nasa.
3. (a) {ir}iro jumioli biyar masu sashen suna kawai.
   (b) {irkiro cikakkun jumloli biyar tare da amfani da wa]annan Sunayen
      (i) Aliyu mai doki.
      (ii) Fatima 'yar mai masa.
      (iii) Miko dogo.
      (iv) Farar akuya gurguwa.
      (v) Mai gar]i.
4. {irkiro gajeren labarin da ya }unshi sunayen yannka biyar

**TA{AITAWA**

Idan ka sa natsuwa sossai za ka lura cewa a }arshen wannan kashin ka fahimci abubuwa kamar haka:

- Sunaye da rabe-rabensu.
- Yadda za a tsamo sunaye daga matani.
- Sassan da ke cikin jumlar Hausa.

**MANAZARTA**


Zarruk, R. M. (1990) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Kananan Mak'arantrai Sakandare,* Ibadan: University Press.

Gala]anci, M. K. M. (1976) *An Introduction to Hausa Grammar* Ibadan: Longman Nig.

Zariya, Ahmadu B. (1981) *Nahawun Hausa,* Ibadan: Thomas Nelson Nig. Ltd.

Ahmed, Vmaru B. (1975) *A School Certificate Hausa course,* Zaria: 'NNPC.

**KASHI NA 6: NAZARIN GININ KALMA**

**GABATARWA**

Idan kana sauraren maganar da wani yake yi, za ka ga tana bayyana abubuwa Wa]annan abubuwa lalle ne zuciyarka ta iya }addara kamanninsu, har ma ta iya ware su kashi -kashi. Irin wa]annan abubuwa za su kasance ko dai idanunka sun ta~a ganin su, ko kuma kunnenka ya ta~a jinsu. Wa]ansu kuma ba a ta~a ganinsu ba ko saduwa da su. {ir}irar su aka yi aka ra]a musu sunaye da wasu halaye. Sunayen wa]annan'abubuwa da ayyukansu da siffofinsu da bayanansu da makamantansu su ne suka zama kalmomi. Kuma su ne ake }o}arin warewa dalla-dalla a ciki rubutu.
A cikin wannan kashi za mu yi nazari ne a kan kalma da ]angoginta

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi, za ka iya:
1. fahintar abubuwan da suka ha]u suka zama kalma;
2. fa]in amfanin raba kalmomi a cikin rubutu;
3. Bambance tsakanin kalma da kalma;
4. fayyace ko mece ce kalma;
5. kawo misalan wasu kalmomi.

**MATAKAN NAZARI**

1. Ka karanta gabatarwar da ke sama domin zai yi maka jagora zuwa bayanan da za su biyo baya.
2. Aikin da ke ciki yana da sau}i, amma duk da haka ka yi su.
3. A duk lokacin da aka kawo maka misalai to kai ma ka yi tunanin wasu misalan makamantansu.

**BAYANI A KAN GA|A**

Kafin a fara yi maka bayani a kan kalma, bari a koma da kai baya a tuna maka ka]an daga cikin sassan kalma. An san ka na}aki ba}a}e da wasullan Hausa. Soboda haka za a yi maka ta}aitaccen bayani a kan ga~a.
Ga~a wani sashe ne na jikin kalma wanda ya }unshi ba}a}e da wasulla. Misali idan kana koyar da wanda bai ji Hausa ba, sai ka ambaci kalmar maganganu. Sai ya ce maka kamar ta yi mai tsawo ka fa]a masa ita a hankali. Za ka }ara maimaita masa ne ta wannan siga kamar haka: ma-gan-ga-nu.
A haka ka yi masa filla-filla ke nan da kalmar wato ka rarrabeta. To gunduwa-gunduwar nan da ka yi ita ake cewa ga~a.
Ga~a iri-iri ce ]angane da abin da ta }unsa. Akwai ga~a kamar haka:
1. BW. misali: ci, ki, sha da sauransu
2. BWB. misali: kan, har, kaf, da sauransu

A cikin kowace kalma mafi }arancin ga~a ita ce mai ]auke da BW kawai, amma babu kasa da wannan kuma ka tuna wasu kalmomi suna ]auke da gabobin da suka gina su kalmomin. Akwai misalai kamar haka:
1. Kalma mai ga~a ]aya, kamar haka: ci, sha, ni, nii, shi, shii,
2. Kalma mai ga~a biyu misali:- gobe, jiya, ]aki, gona, taro
3. kalma mai ga~a uku misali:- Akuya, tafiya, handama, magana, karatu
4. kalma mai ga~a hu]u misali:- tatsuniya, makaranta, matashiya.
5. Kalma mai ga~a biyar misali:- almubazzari.

Tun da ka fahimci haka, yanzu za mu shiga darasin na ga~a wanda zai yi magana a kan kalma.

**MECE CE KALMA?**

Kalma lafazi ce mai dun}ulalliyar ma'ana da ake rarrabewa wajen rubutu misali:- idan na ce,
Ali ya sha koko da safe.
Idan ka }irga su za ka ga ta }unshi kalmomi har guda shida kamar haka:
1. Ali 2. Ya 3. Sha 4. koko 5. Da 6. Safe
Ga wani misali kuma.
Malam ya shigo cikin aji da littafi a hannunsa. Idan ka duba wannan jumlar za ka fahimci

ce wa ta }unshi kalmomi har guda tara kamar haka:
1. malam
2. ya
3. shigo
4. cikin
5. Aji
6 da
7. littafi
8. a
9. hannunsa
Duk abubuwan nan da aka rubuta su a rarrabe, cikin wannan jumla, kalmomi ne.

**IRE-IREN KALMOMI**
Kalma kamar yadda a ka yi maka bayani ba iri ]aya ba ce. Akwai kalmomi masu yawa a Hausa kuma sun bambanta. Akwai suna, wakilin suna, sifa, bayanau, nunau, mafayyaci da sauransu.
yannzu za mu ]auki wasu daga cikin su mu yi nazari kamar haka:

1. **SUNA**

Suna ya }unshi kalmomi da ake amfani da su wajen kiran abu, wato suna kalma ce da ke nuna sunan abu mai rai, ko maras rai, namiji ko mace, wanda ake iya gani da wanda ba a iya gani.

| **Sunan abu mai rai** | **Sunan abu maras rai** |
|---|---|
| Mutum | fitila |
| Agwagwa | tsintsiya |
| Tantabara | kujera |
| Kyankyaso | littafi |

Sunan abin da ba a iya gani kamar: Iska, sanyi, hankali, ba}in-ciki da sauransu. Haka kuma, in ka duba kusa da kai za ka ga mutane, dabbobi, garuruwa, abubuwa, }wari, tsuntsaye, abubuwa marasa motsi duk suna da sunaye. Kuma sunayen wa]annan duka kalmomi ne.
Misali akwai sunaye kamar haka:

| | | |
|---|---|---|
| Abubakar | Zariya | Doki |
| [anlami | Sakkwato | kura |
| Ladidi | Kano | akuya |
| Aishatu | Katsina | }uda |
| Yaro | Tudun-wada | kunama |
| [alibi | Daura | dutse da sauransu. |

2. **WAKILAN SUNA**

Wakilan suna su ne kalmomi da kan fito a madadin suna, wato maimakon a ambaci sunan abu sai a yi amfani da wata kalma a madadin abin. Misali: Idan na ce
(a) Ibrahim ne ya tafi Kaduna.
(b) shi ne ya tafi Kaduna. Ko kuma na ce,
(a) Hauwa ta mare shi.
(b) ita ta mare shi.
kalmar Ibrahim da Hauwa sunaye ne amma sai aka maye gurbinsu da kalmar **shi** da **ita.** Irin wa]annan kalmomi ake cewa wakilan suna. Misalan wasu wakilan suna su ne: ni, mu, kai, ke, ku, shi, ita, su.

**3. AIKATAU**

Aikatau kalma ce da ke ]auke da aiki. A Hausa duk kalmar da za ka iya nuna aiki a cikin jumla wannan aikin yana cikin ta. Misali:

Ibrahim ya **zauna** a kan kujera.
Sahura ta **hura** wata.
[alibi yana **<u>rubutu.</u>**
[anladi ya **<u>rame.</u>**

Kalmomin zauna, hura, rubutu, rame suna nuna aiki ne a cikin wa]annan jumloli kar fa ka manta har yannzu ana magana ne a kan kalmomi.

4. **SIFA**

Sifa kalma ce da ake amfani da ita domin }arin haske a kan suna. Misalai:

| | | |
|---|---|---|
| ba}i | malalaci | iri-iri |
| ba}a}e | mayaudari | kashi-kashi |
| ba}a | malalata | buhu-buhu |
| dogo | mabamata | |
| gajere | mafa]aciya | |

Wa]annan ka]an ke nan daga cikin abin da kalmomi suka kunsa.

**AIKIN GIDA**

1. me ake nufi da kalma?
2. ta yaya ake gane kalma a rubuce?
3. yi ta}aitaccen bayani a kan:
   A) suna
   B) aikatau
   C) sifa
4. Jero misalan ga~o~i sannan ka ha]a su su zama kalmomi

**TA{AITAWA**

A cikin wannan kashi, ka koyi:

- yadda ake shaida ga~a;
- yadda ake daddatsa kalma zuwa ga~a-ga~a;
- ma'anar kalma;
- abin da ake gina kalma da shi;
- azuzuwan kalmomi wa]anda suka ha]a da suna, wakilin suna, sifa;
- muhimmancin raba kalma a cikin karatu da rubutu.

**MANAZAARTA**


Galadanci, M.K.M. (1976) *An Introduction to Hausa Grammar.*

Jinju, M. H. (1981) *Rayayyen N'ahawun Hausa:* Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Ibrahim Yaro Yahaya etal, (1992) *Darussan Hausa don Manyan Makarantun Sakandare.* Ibadan: University Press Plc.

Zarruk, R. M. etal *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa don {ananan Makarantu Sakandare.* Ibadan: University Press Plc.

**KASHI NA 7: IRE-IREN ADON HARSHE**

**GABATARWA**

Kamar yadda tarihi ya nuna, harshe baiwa ne ga mutum wanda mahalicci ya yi wa ]an Adam.
Dangane da tarihi ma, masana sun nuna cewa, ]an Adam na da harshe tun tuni, wato tun yana yawo a cikin daji, ba shi da ko sutura, (Dowse R. eta! 1979)Shi batun harshe kamar yadda aka nuna, yana tare da bil' adama ne tun-tuni, }ila shi ya sa ]an Adam ya na}aki abinsa sosai har yakai yana yi masa ado. Irin wannan adon na harshe, ana samunsa a zantukan yau da kullum. Ana samunsa a wa}o}in baka, da a rubutaccen adabi. A wannan kashin, za a nazarci adon harshe ne a adabi gaba ]aya wato adabin gargajiya da rubutaccen adabi (na zamani).

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi, ana ganin ]alibai za su iya:

1. Sanin abin da ake nufi da adon harshe a dun}ule;
2. Sanin da yawa daga cikin rabe-raben adon harshe;
3. Sanin inda ake amfani da adon harshe;
4. Tsamo adon harshe a cikin adabi ko na gargajiya ko na zamani.

**MATAKAN NAZARI**

1. Za ka nemo wasu daga cikin sassan adabin gargajiya, ka saurare su da kyau ko iya tsamo adon harshen da ke ciki.
2. Ka nemo ire-iren rubutaccen adabi, ka nazarce su da kyau , ka fitar da irin adon harshsen da ke ciki.
3. Ka yi }o}arin yin amfani da adon harshe a lokacin da kake magana da abokinka, ko da a rubuce don ka nuna gwanintarka ta harshen.
4. Ka yi }o}arin fahimtar kalmomin da ba ka gane ba a cikin adon harshen da ka ci karo da shi.

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Ado | yana nufin kwalliya |
| Harshe | zance ko magana |

**ADON HARSHE**

A wajen nazarin adon harshe akan nazarci yadda sha'iri ya nuna gwanintarsa ne a cikin aikinsa na fasaha. Za a kawo misalai daga adabin gargajiya da na zamani:

**KAMANTAWA**

Wannan hanya ce da `yan asalin harshe ke bi domin kwatanta abubuwa biyu wa]anda sun sha bamban tun asali. Akwai kalmomin da ake amfani da su wajen kamantawa, wa]annan kalmomi sun ha]a da kamar da tamkar da awa da sai ka ce da sauransu da yawa, za a iya ganin misalign kamantawa daga wa}ar shago ta ]an anace inda yake cewa:

Mazan jiya sun san |aleri bawan fama;
Balle mazan yau mata;
Haka mika ganin maza kamar `yann mata;

Haka a Wa}ar Kilishi Jikar Dikko, Shata ya ce:

Ni sai zuba wa}a nake,
kama da ta Alfa-Zazi kamar ana tamsiri.

Ga kamantawa a rubutacciyar wa}ar ‘yar gagara ta A}ilu Aliyu:

Dubi idonta kamar yar caca,
kar ka sa mata tsoron sarki.

Haka a wa}ar Kadaura Babbar Inuwa ta Akilu Aliyu ya nuna kamantawa kamar haka:
Shi jahili, kun gan sai, shi ne hoto,
Tamkar baka ba tsirkiyar daurawa.

**AIKI I**

1. Me ka fahimta da adon harshe, kawo misalai guda biyar.
2. Tsamo wata wa}ar baka, ka kawo adon harshsen da ya burge ka guda bakwai.

**MUTUNTAWA**

A nan akan ]auki wani abu ne maras rai sai a ba shi ]abi'a na mutane. Ga misali daga kacici kacicin }ulun-}ulufita:

Na je daji, daji na mini dariya.

Haka a wa}ar Sarkin Kudu ta Sa idu Faru inda ya ce:

Can na ta~a yar tafiya ka]an
sai ni ishe suda na kiwo,
Tana ta wa}ar Sarkin kudu,

**SIFFANTAWA**

A wannan akan kwatanta abubuwa biyu kamar a kamantawa, amma shi wannan ba ya amfani da wasu kalmomin da za su nuna wannan kamantawar. Shi kuma wannan yana da 'yar ru]arwa ka]an.
Ga misali daga zance irin na yau da kullum a lokacin da ake son kwarzanta mutum domin }arfinsa ko kwarjininsa, inda akan ce:

Ai wane zaki ne!

**KAMBAMAR ZULA{E**

Wannan ya kunshi a fa]i wata magana ko a cikin wa}a ko wani nau'i na adabi domin a tsananta abin. Shi dai wannan abin da ake fa]a wa mutum a wani lokaci ma ba zai iya yiwuwa ba, kuma l]an mutum bai fahimci wannan nau'i na adon harshe ba, sai ya yi tsammani }arya ake yi. Ga misali daga zancen yau da kullum:
"Ai saboda yunwa zan iya cinye buhun hatsi. Kamar kuma yadda wani ]an wakar Sabo Saya-saya yake cewa:

Kallo ya koma sama;
samari, kallo ya koma sama;
tun da shaho ya ]au giwa.

**{ARFAFAWA**

Idan ana son }arfafa zance, sai a yi ta maimaita wani abu a cikin zancen, ko kuma dukkansa.
A wa}ar Sarkin Taushin Katsina ta Babbar {asar Shehu [anfodiyo, ya nuna haka:
Ibada tana inda Nijeriya; Karatu yana inda Nijeriya; Biyayya tana inda Nijeriya; Tunani yana inda Nijeriya.

**{ARANGIYA**

A nan akan yi wani salon magana ne ta hanyar yin lugude ko maimaita wani sauti da ke cikin kalmomin da ake magana da su domin a nuna gwanancewa. Akan yi ma wannan salon la}abi da gagara-gwari. Ga misali:

Tun da ta~o take,
Ba ta ta~a ta~a ta~o ba.

Idan aka lura da kyau an yawaita maimaita sautin /~/ kamar kuma yadda Saidu Faru ya yi amfani da irin wannan salon inda yake cewa:

Yaro in ta}amar salon magana kaka yi,
Ce tsare tsara,
Tahi tsantsamin tsantsara,
Ka tsatstsame tsari,
Tsaf ga tsamiya.

**KARIN MAGANA**

Wannan gajeren zance ne a dun}ule wanda ya kunshi ]imbin hikima, saboda muhimmancin karin magana hatta sauran nau'o'in adabi sukan ]auki wasu karin magana kai tsaye ko kuma su yi kwaskwarima domin su isar da sa}onninsu. Ana samun karin magana a zance na yau-da- kullum kamar kuma yadda akan ji ]uriyarsu a sauran nau'o'in adabi. Ga misalign karin magana:

Ban sá a ka ba, in ji barawon tagiya.
In gani a }as, an ce wa kare ana biki a gidansu.

Haka, Shata ya ce a ]aya daga cikin Bakamdamiyarsa:

----duk mai rowa ya yi rowa----
"komin tsiyarsa, ba ya hana mu
shiga Aljanna".

**BA{AR MAGANA**

Wannan wata irin magana ce da ake yi wa mutum domin a muzanta masa rai. A wa}ar ]an'anace ta Shago ya ce:

Bari in fa]a muku,
'Yan dambe masu yawon banza kuna girma
ubanku na rage gona.

**HABAICI**

Ana amfani da habaici domin a yi da mutum a fakaice ba tare da an ambaci sunansa ba. Ga misali daga wa}ar Alhaji [ankwairo ta Shrya Kayann Fa]a, inda ya ce:

"Ga wani ya Kulla wa}atai, Sai a amsa mashi,
ba a }ara mai,
in na }ulla wa}a, a }ara man----"

**AIKI**

1. Me ka fahinta da wa]annan?
   (a) karin magana
   (b) }arfafawa
   (c) mutuntawa

**AIKIN GIDA**

1. Bayyana abin da ka fahimta da wa]annan.
2. Habaici
3. Kamantawa

**TA{AITTAWA**

- An nazarci bayanin adon harshe.
- An san wasu misalai na adon harshe
- An nazarci muhallin da wasu daga cikin adon harshe ke fitowa.

**MANAZARTA**


Ahmed , M. M. eta! (1999) - *Understanding Literature and Criticism.* Zaria: Supreme Printer

Allyn, Akilu (1976) -fasaha *Akiliya.* Zaria, N.N.RC. Ltd.

[ANGAMBO, A, (1984)- *Raben-Raben Adabin Hausa da Muhimmanci ga Rayuwar* Hausawa. Kano: Triumph Publisshers

Dowse, R.E. eta! (1979) - *Political Sociology.* New York: John willey & Sons ltd. Sani, M.Z. (1992) - *Darussan Hausa 1-3.* Ibadan: University Press Pk.

**KASHI NA 8: AMFANI DA ADON HARSHE**

**GA BATARWA**

Wannan kashi zai koyar da kai amfani da adon harshe. Adon harshe wani nau ne na maganganun nazarci kamar karin magana ko habaici. Muna yin amfani da adon harshe a maganganu na yau da kullum da kuma rubuce-rubucen da muke yi, ko muke karantawa. Wani lokaci kakan yi amfani da adon harshe ba tare da ka sani ba.

**MANUFA**

Manufar wannan kashi ita ce, ya koyar da kai amfani da adon harshe. A }arshen wannan kashi za ka fahinci adon harshe da wuraren da ake amfani da adon harshe da yadda za ka gane adon magana a cikin labari ko wa}a.

**MATAKAN NAZARI**

Mataki na farko, ana so ka san ma'anar adon harshe. Mataki na biyu, ka san wuraren da za ka yi amfani da adon harshe tare da yadda za ka gane adon harshe da iya amfani da shi.

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Adon harshe: | Ya }unshi rukunan kalmomi da suke ]auke da ma'anoni daban, wato }ari a kan ma'anoninsu na zahiri. |
| Ma'ana ta zahiri: | Ma'anonin kalmomi na asali: |
| Ma'ana ta ba]ini: | Wato, ma'ana wadda take a ~oye ko ta daban. |
| Ma'anoni: | Abin da kalma take nufi, ko kalmomi suke nufi. |

**MA'ANAR ADON HARSHE**

Adon harshe ya }unshi kalma ko kalmomi da suke ]auke da ma'ana ta daban. A saboda haka, adon harshe na rukunan kalmomi ne masu ]auke da ma'ana ta ba]ini. ]angane da haka, za ka fahimci cewa, kalmomi na adon harshe suna da ma'anoni iri biyu, akwai:

1 ma'ana ta zahiri
2. ma'ana ta ba]ini

**MA'ANA TA ZAHIRI**

A ma'ana ta zahiri ana kallon kalma ko kalmomi ne bisa ma'anar da suke ]auke da ita kai tsaye. Misali:

1. Abdu ya tafi makaranta
2. Binta ta ]afa abinci

Idan ka dubi wa]annan jimloli za ka ga cewa, kowace kalma tana bayyana ma'anarta ta asali. Wato, jimloli kai tsaye suke bayyana kansu, ba sa ]auke da wata ma'ana ta daban. Irin wa]annan jumloli ba sa nuna adon harshe.

**MA'ANA TA BA[INI**

A ma'ana ta ba]ini, ana kallon kalmomi ne bisa ma'anar da suke ]auke da ita ta ~oye ko ta daban, sabanin ma'anonin kalmomi na asali ko zahiri. Ire-iren kalmomi masu ]auke da irin wannan siffa, su ake kira adon harshe.

Wani abu da ya kamata ka yi la'akari da shi ]angane da jimloli da suke ]auke da adon harshe shi ne, suna da ma'anoni guda biyu:

1. ma'ana ta zahiri
2. ma' ana ta ba]ini

**Ga misali:**

**1.** Abdu ya yi **<u>zaben tumun dare.</u>**
**2.** Abdu ya ba shi **]<u>an karen kashi.</u>**
3. Wani **<u>sha-ka-tafin </u>**yaro ya zo.

Idan ka duba misalan da aka nuna 1-3, za ka fahinci cewa duk kalmornin da aka ja musu layi suna da

ma'anoninsu na zahiri, amma idan ka yi amfani da su ta haka, ba za ka fahimci ma'anar da suke ]auke da ita ba. Saboda haka suna ]auke da ma'ana ta boye ko ta ba]ini.

**AIKI I**

1. Bayyana ma'anonin wa]annari adon harshen:
   (a) Za~en tumun dare
   (b) [an karen kashi
   (c) Sha-ka-tafi.

**WURAREN DA AKE AMFANI DA ADON HARSHE**

Ana yin amfani da adon harshe a wurare dabam-daban, wasu daga ciki sun }unshi:

1. Labarai
2. Wa}o}i
3. Tatsuniyoyi
4. Kirari
5. Rubutattun bayanai sa~anin na labarai

***Ga misali:***

(1) In ban da }arya rashin kunya,
a ]akinka **<u>jaki ya zage ka</u>.**
(Wakar Hawainiya ta Tijjani Tukur Yola).
Maza sun **<u>sha kashi,,</u>**
(Littafin Gan]oki: 1968 shafi na 5).

(2) ko an **<u>daka a turmi,</u>** da mu a cikin masu fita,....'
(Gan]oki, shafi na 4)

(3) Abdu ya yi **<u>shuka a idon makwarwa.</u>**

**YADDA ZA A GANE ADON HARSHE**

A nan za ka fahimci yadda za ka gane adon harshe, wanda ka sani da wanda ba ka sani ba.
A mataki na farko , abin da ya kamata ka sani shi ne, ba a yin amfani da adon harshe haka kawai. Ana yin amfani da shi ne don a }ara wa zance armashi ko a jaddada sa}on da ake son isarwa, ko kuma, don a }ara fahimtar da mutum.

***Misali:***

(1) shi ne wanda aka fi nema **<u>ruwa a jallo</u>**

Ka ga a nan an yi amfani da adon harshe da aka ja wa layi don jaddadawa. Idan aka ce:
Shi ne wanda aka fi nema. Ma'ana ta fita.
Babbar hanyar da za ka gane adon harshe ita ce, in har ka ga ka kasa fahimtar ma'anar jumla ta hanyar ma'anonin kalmomin na asali, to lallai akwai maganganun adon harshe a cikin jumlar ko sakin layin.
Hanya ta biyu ita ce, yawancin kalmomin adon harshe suna dun}ulewa ne su ba da ma'ana ]aya, kuma wani abu da wuya ya iya shiga tsakaninsu. Idan kuwa har wata kalma za ta iya shiga tsakanin kalmomin, to ba su kasance adon harshe ba.

***Misali:***

**1.** A bar **<u>kaza cikin gashinta</u>**
**2.** Abdu ya **<u>fasa }wai</u>**

Wa]annan kalmomin da aka ja wa layi, duk kalmar da aka tsarma a tsakiya ko a }arshensu, to za su tashi daga adon harshe.

***Misali:***

1. A bar kaza cikin gashinta (kar ta mutu)
2. Abdu ya fasa (mana) }wai.

**AIKI NA II**

1. Kawo misalan adon harshe guda biyu masu ]auke da kalmomi guda biyu.
2. Kawo misalan adon harshe guda uku masu ]auke da kalmomi guda uku

**AIKIN GIDA**

1. Jumla ko kalmomi masu ma'anoni na musamman, me ake kiran su?
2. kawo misalai guda biyu na adon harshe daga cikin labari.

**TA{AITAWA**

A wannan kashi, ka fahimci cewa adon harshe wasu rukunan kalmomi ne ko kalmomi da suke ]auke da wata ma'ana ta daban. Sa~anin ma'anoninsu na zahiri. Ka fahimci cewa ana gane adon harshe ta hanyar dangantaka ma'anarsa da batun da ake magana. Kuma ka fahimci cewa wasu kalmomi ba sa iya shiga cikin jerin kalmomin adon harshe. Haka kuma anyi amfani da adon harshe don }ara wa zance armashi don jawo hankalin mai sauraro ko kuma don jaddada wata manufa.

**MANAZARTA**


Dikko, I., Maccido, U. (1991) *Kamus na Adon Managar Hausa.* Zaria: N.N.P.C.

Yahaya, I.Y. (1979) *Labarun Gargajiya Na* 2. Ibadan: University Press Limited.

Zarruk R.M., Kafin-Hausa, A.A. da Al-Hassan, B.S.Y. (1986) Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don Kananan Makarantun sakandare Littafi Na [AYA. Ibadan: University Press Limited.

Bello, A.M. (1968) *Gan]oki*. Zaria: N.N.P.C.

## FASALI NA 4: ADABIN GARGAJIYA

### KASHI NA 1: AMFANIN ADABIN BAKA GA AL'UMMA

**GABATARWA**

Wannan kashi zai koyar da amfanin adabin baka ga al'umma. dangane da haka za a fitar da amfanin adabin bakan a dun}ule yadda ]alibi zai fahimci amfanin a fa]a]e. Tuni, da ma, an fahimci ma'anar adabi da kuma rabe-rabensa a cikin Fasalin da ya gabata.

**MANUFA**

Manufar wannan kashi ita ce, ya bayyana maka amfanin adabin baka ga al'umma. A bisa wannan manufa, za ka san ma` anar adabin baki da kuma amfaninsa ga Hausawa.

**MATAKAN NAZARI**

A mataki na farko, ka san ma'anar adabin baka da ire-iren abubuwan da ya }unsa. A mataki na biyu, ka, san amfanin adabin baka. Sannan a mataki na }arshe ka gane dangantakakar adabin baka da rayuwar al'umma. Wato, yadda adabin baka yake bayyana rayuwar al' ummar Hausawa.

**SABABBIN KALMOMI**

Adabi: Adabi yana nufin duk wata fasaha ta alumma wadda aka wanzar da ita da harshe wato cikin kalmomi.

Adabin baka: Na nufin duk fasahar da ta fito ta bakin ]an Adam. Misali: tatsuniya da karin magana da wa}a da kacici da makamantansu.

**MA'ANAR ADABIN BAKA**

Adabin baka wani nau'i ne na adabi da ke }unshe da maganganu ko zantuka na hikima da suka fito daga bakin Hausawa ko Bahaushe. Ire-iren wa]annan zantuka sun kunshi:

- tatsuniya
- labarai
- almara
- wa}e-wa}e
- karin magana
- kirari
- habaici
- kacici-kacici
- kakkarya harshe
- da makamantansu

**AMFANIN ADABIN BAKA GA AL'UMMA**

An kira adabin baka da wannan ne, kuma ya samo asali tun kaka da kakanni. A dalilin haka ne adabin ke da matu}ar amfani ga rayuwar al'ummar Hausawa ta fuskoki kamar haka.

Adabin baka ya zama taska ma'a]anar duk hikimomi da al'adu na al'umma yadda ba za a neme su, a rasa ba. Tun da komai da ka ake kawo shi, ba za a ta~a rasa shi ba.

Adabin baka kan taimaka wajen ilmantar da al'umma, ta hanyar cusa musu kyawawan ]abi`u da suka dace da tsarin zama na Bahaushe. Ana samun hakan ta hanyar tatsuniyoyi da karin magana da wa}o}i da sauransu. Ga wasu misalai daga karin magana:

(1) na gari na kowa, mugu sai mai shi;
(2) bayan wuya sai da]i;
(3) kwa]ayi mabudin wahala.

Adabin baka kan taimaka wajen koya wa yara harshensu da na}altarsa da wasa }wa}walwa. Ana samun haka ta hanyar kacici-kacici da dabarun kakkarya harshe da wasannin yara da makamantansu.

**MISALAI:**

(1) Wasannin yara irin su:
- ]an maliyo-maliyo
- carmandudu
- tama-ya-}i-tama
- tafa-tafa
- lugu-lugu-ta-nuna
- na-jej-je-ni
- `yar kurciya
- da makamantansu.

(2) Wasan kakkarya harshe, kamar:
- Salamu alaikum matar {ona-}ota.
- {ona-}ota yana gida?
- {ona-}ota ya je gona'
- To ke matar {ona-}ota ba ni aron
- }otar {ona-}ota in }ona.
- Haba! ni matar {ona-}ota ban ]auki
- kotar {ona-}ota na }ona ba, sai kai
- bakon Kona -kota zan bai wa }otar
- {ona-}ota ka }ona?

(3) Kacici-kacici
- Abdu: }ulin-}ulifita
- Musa: gauta
- Abdu: Matar }ulifita
- Musa: Yalo
- Abdu: Takande ba }ashi ba
- Musa: Kanwa
- Abdu: Makaranta a dokar daji
- Musa: Gidan tururuwa
- Da makamantansu.

Adabin baka kan sa nisha]i da annashuwa, yana sa jama'a su kasance cikin jin da]i, su ma manta da wasu matsaloli da suke fuskanta. Misali: dubi yadda adabin kan taimaka wa amarya, ya ]ebe mata kewar rabuwarta da iyayenta da zaman ka]aici, har lokacin da mijinta zai dawo. Yara kan taru a gidan su yi ta yin tatsuniya da wasu nau'o'in adabin baka. Tsofaffi mata kuma kan tara yan`yannsu da jikokinsu a gida, suna ba su wasu labaran hikima da tatsuniyoyi, yadda hakan zai zaunar da su a gida, ba za su tafi yawon banza ba. Wato, adabin baka ya zama tankar abokin hira.

Adabin baka kan taimaka wajen yin tarbiyyar yara Misali:
idan aka dubi tatsuniyar *Ruwan Bagaja* za a ga cewa tatsuniyar ]auke take da abubuwa
masu koyar da tarbiyya ga yara da kuma nuna musu muhimmancinta. Kamar yadda Bora ta yarda ta yi komai na aikace-aikacen gida, ba tare da damuwa ba. Haka ma ta koya wa yanrta ladabi da biyayya. Wanda a }arshe wannan tarbiyya da yanr-bora take yi; ta zaman mata hanyar arzikinta. Inda bayan an sa ta, ta wanke }irgi, ta dawo garin a kan doki da `yann rakiya, gidansu ya cika da }anshin turare, da ita da babarta suka sami ]aukaka da jin da]i ga kuma arziki hankalinsu kwance.

Adabin baka kan taimaka wajen ke~ewa da fito da tarihin al'umma. Misali: *Wa}ar `yannci* ta Sarkin Taushin Katsina.

**AIKI**

(1) Me ake nufi da adabin baka?
(2) Kawo amfanin adabin baka guda biyu.

**DANGANTAKAR ADABIN BAKA DA RAYUWAR AL'UMMAR HAUSAWA**.

A wannan mataki za mu ga yadda adabin baka ke ]auke da ha}i}anin rayuwar al`ummar Hausawa. Wato, a nan za a fahimci yadda nau'o'in adabin baka kan fassara ko nuna rayuwar al'ummar Hausawa. Ga wasu

misalai kamar haka:
Karin magana:
(1) Ga mu ga Allah, wai bawan sarki ya rasa doki.
(2) Mai mace ]aya aminin gwauro.
(3) Da zaman banza, gara aikin kishiya.

Ɗangane da karin magana ta farko za mu ga yadda bayi suka ta'alla}a ga sarki da kuma matsayin sarki a }asar Hausa. Baya ga dogaro ga Allah, bayin sarki ba su dogara da kowa ba don biyan bu}atunsu sai sarki.
Karin magana ta biyu kuwa na nuna tsarin rayuwar Bahaushe ne ta auren mace fiye da ]aya.
Karin magana ta uku kuwa na nuna al'adar nan ta matan Hausawa, wato misali matsanancin kishin da ke tsakanin mata a }asar Hausa. Amma duk da wannan kishin, matar Bahaushe ta yarda da fa]in, 'da zaman banza, gara aikin kishiya.

**AIKI II**
(1) Kawo Karin magana guda biyu da suke nuna rayuwar Bahaushe.
(2) Fa]i hanyoyi guda uku da adabin baka kan koyar da yara harshensu.

**AIKIN GIDA**
(1) Kawo nau'o'in maganganun hikima guda uku.
(2) Kawo misalin kakkarya harshe guda ]aya.
(3) Fa]i amfanin adabin baka guda biyu.
(4) Kawo misalan kacici-kacici guda uku.

**TA{AITAWA**
A wannan kashi an fahimici cewa adabin baka wani nau'i ne na adabi da ke }unshe da zantuka na fasaha da suka fito daga bakin Bahaushe. An fahimci ire-iren wa]annan zantuka wa]anda suka }unshi: karin magana da tatsuniya da wa}e-wa}e da kakkarya harshe da labarai da makamantansu.
Haka kuma, an ga arnfanin adabin baka wajen ilmantar da yara harshensu ta hanyar amfani da nau'o'in adabin baka.
Adabin bakan ya zama tamkar taska na al'umma, yadda yake a]ana tarihin al'umma da tsarin zamantakewarta.
A }arshe, an fahimci cewa adabin baka yana da dangantakaka da rayuwar al'umma, da kuma koya wa yara tarbiyya da kyawawan halaye.

**MANAZARTA**

Yahaya, I.Y, Zariya, M.A., Gusau, S.M. and yanr'aduwa, T.M. (1992) *Darussan Hausa Don Manyan Makarantun Sakandare. Littafi na [aya.* Ibadan: University Press Plc

Umar, M.B.(1987) *dangantakakar Adabin Baka Da Al'adun Gargajiya.* Kano: Triumph Publishing Company.

Yahaya, I.Y. (1979) *Labarun Gargajiya.* Ibadan: University Press Limited.

Ɗangambo, A. (1984) *Rabe-Raben Adabi Da Muhummancinsa Ga Rayuwar Bahaushe.* Kano: Triumph Publishing Company.

## KASHI NA 2: NAZARIN TATSUNIYA DA ZUBEN LABARI

**GABATARWA**
Idan wani abu ya faru, ko kuma mutum ya yi wani tunani a cikin zuciyarsa, to idan ya kasance yana son ya sanar da wani wannan abin da ya faru ko kuma abin da ya yi tunani to yana bayar da labari ke nan . Wato shi labari yakan kasance ne a kan wasu abubuwa da suka faru ko aka }ir}iri faruwarsu.
Irin wa]annan labarai wa]anda ake }ir}ira kuma ake aiwatar da su ta baka sun kasu kashi biyu; tatsuniya da zuben labari. Wannan kashi zai yi bayani ne a kan abin da ake ce wa tatsuniya da wanda ake ce wa zuben labari.

**MANUFA**
Manufar wannan kashi ita ce koyar da ]alibi wa]annan abubuwa:

i. tatsuniya da ire–irenta;
ii. zuben labari da ire-irensa;
iii. bambancin tsasuniya da zuben labari;
iv. abubuwan da suka bambanta tatsuniya da zuben labari;
v. abubuwan da zuben labari ya }unsa.

**MATAKAN NAZARI**

1. Abu na farko da za ka yi shi ne ka karanta gabatarwar wannan kashi a cikin tsanaki.
2. Ka lura da cewa tatsuniya na da bambanci da sauran zuben labari.
3. Ka kula sosai da aikin da za a bayar domin shi zai taimaka ya }ara tantance bambancin da ke akwai tsakanin tatsuniya da sauran labaran zube.

**SABABBIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| Mabu]i | = | Jumlar da ake fara tatsuniya da ita |
| Marufi | = | Jumlar da ake }are tatsuniya da ita. |
| Tarihi | = | Labari mai ban mamaki na asalin wani abu |

**TATSUNIYA**
Ita tatsuniya wani labari ne }agagge da Hausawa suka tsara tun kaka da kakanni domin manufa ta musamman. Wannan manufar kuma ita ce koya wa yan`yannsu dabarun zaman duniya.
Tatsuniya ta kasu gida biyu; kacici-kacici da tatsuniya mai labari.

**Kacici-kacici**
Tatsuniyar kacici-kacici ita ce wadda ake shiryawa domin auna fahimtar yara. Ana aiwatar da ita ne ta hanyar sakaya sunan wani abu amma sai a fa]i wata sifa tasa, daga baya a nemi yaro ya gane ko mene ne. Misali; ``Tun daga nesa na ji muryar wana", sai yaro ya amsa ya ce„ " kalangu". Ko kuma a ce, "gari ]aka, yara kwana da yunwa" sai yaro ya ce, "toka". Da dai sauransu.

**TATSUNIYAR LABARI**
Tatsuniyar labari ita ce wadda za a bayar da wani dogon labari ]angane da wata hanya ta rayuwa domin nuna wa yaro wani darasi da labarin zai }unsa. Misali, tatsuniyar *Ta-kitse* ko tatsuniyar *Gizo da Budurwar ]an}o.*
Tatsuniyar ta }unshi wasu sigogi wa]anda su ne suka bambanta ta da sauran zuben labarai. Daga cikin wa]annan sigogin akwai:

i. Farawa da wata jumla ta musamman domin a san tatsuniya ce ake yi. Wannan jumlar kuma ita ce, 'ga-ta-nan-ga-ta-nan ku'. Su kuma masu saurare su ce 'Ta zo mu ji ta'. Daga nan ne mai tatsuniya zai ci gaba.
ii. {arasawa da wata jumla kuma ta musamman. Jumlar ita ce, `}ungurus kan kusu'. Wannan shi ke nuna an }are tatsuniyar.
iii. Taurarin da ake samu a cikin tatsuniyar suna hada mutane da aljannu da dabbobi da bishiyoyi da }wari da kuma wasu halittu da babu su. Misali, Sarki ko Fadawa ko Zaki ko Dila ko 'yan ruwa ko Gizo ko {o}i ko batorami da dai sauransu.

**AIKI**

(a) Tatsuniya iri nawa ce?
(b) Wane lokaci ake aiwatar da tatsuniya?
(c) A ina ake amfani da jumlar "}urungus kan kan kusu" a cikin tatsuniya?

**ZUBEN LABARI**

Zuben labari shi ne labarin da ake bayarwa ba a cikin tsari irin na tatsuniya ba. Shi ma irin wannan labari akwai shi tun kaka da kakanni. Samari da manyan mutane su ke aiwatar da ire-iren wa]annan labarai. Shi ma nasa ire-iren akwai: almara da hikaya da tarihi da tarihihi.

**Almara**

Almara ita ce labari wanda ya }unshi ayyukan mutane kuma ya yi kama da gaskiya. Ana yin almara domin nuna fahimta. Wannan shi ya sa ake samun tambaya a }arshen kowace almara.

**Misalin Almara**

Da mutumin da ruwan sama ya sama, ya dinga bau]e masa har yakai gida bai ji}a ba, da wanda santsi ya kwasa amma kafin ya fa]i ya ]ebo kaba ya sa}a tabarma ya fa]i a kanta. To, daga cikin mutanen nan biyu wa ya fi hikima?
Ka lura sosai ita almara ba kamar tatsuniya take ba domin ita almara tana }arewa da tambaya.

**Hikaya**

Hikaya wani nau'in labari ne da ake aiwatarwa mafi yawa a wuraren zaman malamai musamman lokacin gu]anar da karatu. Ana yin hikaya domin nuna martabar abin da ake yin hikayar a kansa. Misali, hikayar Shehu Usman ]anfodiyo da wani mutum da ya nemi agajinsa cikin lokacin da jirginsa yake tangal-tangal da shi a Kogin Kwara.

**Tarihi**

Shi kuma wannan wani nau'in labari ne da ake bayarwa a kan tarihin samuwar wasu abubuwa kamar garuruwa ko }abila ko wata masarauta, da dai sauransu. A irin wannan labari akan caku]a shi da wasu abubuwan mamaki wa]anda da wuya hankali ya iya kar~ar su. Misalin wannan shi ne irin labarin Bayajida da asalin Hausawa.

**AIKI II**

Fa]i abin da ya bambanta almara da sauran labarai.

**AIKIN GIDA**

(a) Mene ne tatsuniya?
(b) Fa]i ire-iren labarun zube guda biyu.
(c) Fa]i abubuwan da tatsuniya take da su wa]anda sauran labaru ba su da.
(d) A ina ne Botorarni ke fitowa a matsayin tauraro?
(e) Su wa ke yin almara?

**TA{AITAWA**

Tatsuniya da labari dukansu labarai ne da ake bayarwa, amma tatsuniya ta bambanta da sauran labaran ta hanyoyi uku na musamman; wato yadda ake farata da yadda ake kare ta da kuma lokacin aiwatar da ita.
Sauran labarai ba su da wa]annan abubuwa, sai dai ita almara tata alama da ke bambanta ta da sauran labarai ita ce tambayar da kan biyo bayan }are labarin. Hikaya da tarihi kuma wuraren da ake aiwatar da su ne ke bambanta su da sauran labarai.

**MANAZARTA**

Yahaya, I.Y. & Ɗangambo, A. (1986), *Jagoran Nazarin Hausa.* Zaria: NNPC.

## KASHI NA 3: MA'ANAR KACICI-KACICI DA RABE-RABENSA

### GABATARWA

Tatsuniya labari ne wanda tsofaffi suke yi wa yara da fatar baki. Akwai tatsuniya iri biyu wato da tatsuniya kacici-kacici da kuma tatsuniya labari. An fi yin tatsuniya da daddare bayan cin abinci. Yara sukan taru a ]akin ko gidan wata tsohuwa ko amarya mai iya ba da labari.

Ita tatsuniyar kacici-kacici, tatsuniya ce da ake yinta ta hanyar yin tambayoyi kuma ana ba da amsar tambayoyin. Kuma idan wanda aka tamabaya ya kasa ba da amsar, akan same shi ya ba da gari. Wato a ce, "ka ba ni gari"? Shi kuma sai ya ce "na ba ka gari" Sai mai tambayar ya ce "wane gari"? A nan wanda aka tambaya sai ya ambaci sunan wani babban gari da aka sani ya ce shi ya bayar. Ana yin tambayoyin tatsuniyar kacici-kacici ne game da abubuwan da yara suka sani daban-daban na kewaye da su, kamar abubuwan cikin gida da tsirrai da dabbobi da kuma abubuwan ci ko sha da sauransu.

### MANUFA

Manufar tatsuniya kacici-kacici tana da yawa. Ga wasu ka]an daga cikinsu:

1. A koya wa yara dabarun sadarwa da harshen Hausa da kuma hanyoyin sarrafa shi harshen.
2 A koya wa yara sanin al'adun Hausawa da ire-iren su, har ma da yadda su al'adun suke canzawa saboda shigowar ba}in wasu mutane ko al'adu cikin Hausawa.
3. A koya wa yara kaifafa tunaninsu.
4. A koya wa yara yin amfani da hankali da lura wajen warware matsala ko ba da amsar tambaya.
5. A koya wa yara sanin abubuwan da suke gani kewaye da su a gida da waje.

### MATAKAN NAZARI

1. A koya wa yara sanin ma'anar kacici-kacici da rabe-rabensa.
2. A koya wa yara su san amfani kacici-kacici a al'adun Hausawa.
3. A koya wa yara su na}aki tasirin kacici-kacici ga rayuwar yaran Hausawa.

### SABABBIN KALMOMI

| | | |
|---|---|---|
| Takanda: | ma'anarta: | kanwa |
| Suri | " | gidan tururuwa |
| Tufaniya | | murfin }ofa na ciyawa mai }arfi |
| Amata | " | ]orawa |
| [il | " | }an}ani |
| Maiwa | " | sunan gero ne |
| Fito | " | hayar da mutum idan kogi ya cika da ruwa |
| Turbu]e | " | ~acewa a ciki |
| Bajinta | " | gwaninta |

### MATANI

Tatsuniyar kacici-kacici dai ita ce tatsuniyar da ta }unshi tambaya da amsarta**.** Kuma ita tatsuniyar kacici-kacici ta rabu zuwa rabo biyu ne. Wato akwai ta wasan cinke da kuma ta wasa }wa}walwa.

Ita kacici-kacici wato wasan cinke, ita ce wadda ake tambayar yaro, sannan shi kuma ya yi }o}ari ya cinki amsar ya fa]a. Watakila a iya cewa daga irin wannan ne aka samo asalin sunan tatsuniyar wato kacici-kacici ko kuma a wani }aulin ka cinci ka cinci. Domin duk akan kira tatsuniyar da wa]annan sunaye. Haka kuma wasu suna kiranta da sunan tatsuniyar "'Yar gane"- wato wadda za a gano amsarta a fa]a. Ana yin ta da daddare bayan cin abinci.

### GA MISALINTA

Tambaya: {ulun }ulifita?
Amsa: Gauta

Tambaya: Matar {ulifita
Amsa: Yalo

Tambaya: Shirin ba ci ba
Amsa: Baba

Tambaya: Takanda ba }ashi ba
Amsa: Kanwa

Tambaya: Ɗanbaka a bayan suri
Amsa: Farce

Tambaya: A fake a fake ba kya shigo ba ]akin na uwaki ne?
Am sa: Tufaniya

Tambaya: Makaranta a dokar daji
Amsa: Gidan tururuwa

Tarnbaya: Gaya ]aya dama duniya
Aamsa: Farin wata

Tambaya: Tsohuwar gidanmu ta takwarkwashe tana ro}on Allah
Amsa: Rumfa

Tambaya: Yammatan gidanmu kullum za su fita sai sun raba mana goro.
Amsa: Kashin awaki

Tambaya: Kututture uku gagara ]auri
Amsa: {wai

Tambaya: Shanuna dubu-dubu madaurinsu ɗaya
Amsa: Tsintsiya

Tambaya: Iya ta zaga, Baba ya zaga, ba su ha]u ba
Amsa: Kunne

Tambaya: Kogina ya kai ya kawo sai a gefe nake wanka
Amsa: Fate-fate

Tambaya: Na je jeji, jeji na yi mini dariya
Amsa: Auduga

Tambaya: Abu ]il ya sa mai gari kuka
Amsa: Barkono

Tambaya: Kullum ana ba ka, ba ka godiya
Amsa: Ciki

Tambaya: Abu ]il ya saukar da mai gari daga kan doki
Amsa: Fitsari

Tambaya: Tasa guda ta ishi duk duniya amfani.
Amsa: Rana

Tambaya: Daga nesa na jiwo muryar }awata.
Amsa: Ganga

Tambaya: Ja ya fa]o, ja ya ]auka
Amsa: [anfulani da kayann giginya

Tambaya: Daga nesa na ga layun }awata
Amsa: [orawa

**AIKI I**

(i) Fa]i ma'anar kacici-kacici
(ii) Gida nawa kacici-kacici ya rabu?
(iii) Idan mutum ya kasa ba da amsar to yaya ake yi?
(iv) Me kacici-kacici yake koya mana?

**WASA {WA{WALWA**

Wasa }wa}walwa shi ma wani salo ne na kacici-kacici. Sai dai a nan ana yi wa yara tambaya ne ta hanyar gabatar musu da wata matsala mai rikitarwa, sannan a ba su damar yin tunani cikin natsuwa wajen ba da amsar ko warware matsalar.

**Ga misali**

Wata rana wa]ansu mutane su uku, ]an Sarkin Ji da ]an Sarkin Gani da ]an Sarkin {iɗaya suka tafi fatauci tare. [aya daga cikinsu ya yi buhun maiwa, ]aya kuma buhun ri]i shi kuma ]ayan buhun shinkafa, suka ]ora wa jakunansu suka kora su. Suna cikin tafiya sai suka tarar kogi ya kawo, dole sai an yi musu fito.
Suka kira masu fito suka ce a hayar da su da kayannsu da jakunansu. Aka ]ora su dukan su a kan gadon fito aka tu}a su.
Ana cikin hayar da su, da aka zo tsakiyar kogi sai ]an Sarkin Ji ya ce, kai ku tsaya! Na ji }wayar maiwa ]aya ta fa]a kogi?
Sai [an Sarkin Gani ya ce "Haba, gaskiya na hango wani abu kamar }wayar hatsi ya sullu~o daga cikin buhu ya fa]a ruwa zundum!'
Can sai [an Sarkin {idaya ya ce, 'to in dai ta fa]a ku mu }iɗaya hatsin cikin buhun sannan mu ga wanda ya ragu".
Suka haye kogi aka zazzage hatsin kowane buhu. [an Sarkin {idaya ya }idaye buhun shinkafa da na ri]i ya gan su daidai, ya }irga na maiwa sai ya ga ba bu }waya ]aya a ciki.
Sai [an Sarkin Gani ya ce, 'Na gaya muku na ga }waya ]aya ta fada: Amma bari in fa]a cikin kogin in gano inda take in ]auko ta.
Ya shiga ruwa yana tona rairayi, can sai ya hango }wayar maiwa a turbu]e cikin yashi ya ]auko ya fito da ita.
To, yannzu a cikin wa]annan mutane, da wanda ya ji fa]uwar }wayar maiwa cikin ruwa, da wanda ya ga lokacin da ta fa]a ruwa da wanda ya }irge buhunhunan hatsin, wanne ne ya fi nuna bajinta?

**AIKI II**

(i) Ina [an Sarkin Ji da [an Sarkin Gani da [an Sarkin {idaya suka je tare?
(ii) A wane wuri ne suka nuna gwanintarsu?
(iii) Waye ya fara nuna bajinta?

**AIKIN GIDA**

1. Kawo tatsuniya biyar ta kacici-kacici tare da amsoshinsu.
2. Fa]i abubuwan ci ko sha da ake fa]a a cikin kacici-kacici guda biyar.
3. Wa ya fi ba da mamaki a tsakanin [an Sarkin Ji da [an sarkin gani da [an Sarkin {iɗaya?

**TA{AITAWA**

Malami zai ta}aita abin da ya koyar da yara. Misali: An koya wa yara sanin ma'anar kacici-kacici da rabe-rabensa. Kuma an sanar da su amfanisu da kuma kin tasirin da yake da shi ga rayuwar yaran Hausawa tare da fatan yara sun na}alaci abubuwan da suka koya.

**MANAZARTA**

Ibrahim, Y.Y. (1979) *Labarin Gargajiya* 2. Ibaɗan: Oxford University Press Ltd.
Zarruk, R.M. (1979) *Sifiƙofin Aikin Koyarwa* , Ibaɗan: Oxford University Press Ltd.
Zarruk, R.M. e tal (1990) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa,* Ibaɗan: Oxford University Press Ltd.

**KASHI NA 4: KARIN MAGANA**

**GABATARWA**
Hausawa suna da hikimomi na magana ta yadda suke nuna basirarsu da al'adunsu. [aya daga cikin irin wannan hikima ita ce nuna basirar sa}a karin magana a zance.

**MANUFA**
Bayan an koyar da wannan darasi na karin magana, za ku iya:
(1) fayyace ma'anar karin magana;
(2) amfani da karin magana;
(3) na}altar ma'anar farko ta karin magana.
(4) kawo karin magana iri-iri.

**SABABBIN KALMOMI**
Karin magana: ta}aitaccen zance mai }unshe da hikima.

**MATANI**
Karin magana ta }unshi hikima iri biyu. Hausawa sukan kawo karin magana ta sigar yadda suka lura da a wani al’amarin yau da kullum.

**MISALI**
(i) {aramin goro ya fi babban dutse.
(ii) Komai yake cikin ]an tsako, shaho ya sani.
(iii) [an kuka ba ya zama ]an tsamiya.
Na biyu kuma shi ne, karin magana ta }unshi wani ra'ayi na Hausawa wanda sun yarda da shi.

**MISALI**
(i) Cutar da kare ya yi ya tashi, idan ]an akuya ya yi ta sai yannka.
(ii) Da muguwar haihuwa gara kyakkyawar tusa.
(iii) Idan gemun ]an'uwanka ya kama wuta yayyafa wa naka ruwa.
Idan aka lura za a ga cewa duk wa]annan kare-karen maganasuna }unshe da hikimomi da basira irin ta Hausawa.

**AIKI I**
1. Me ake nufi da karin magana?
2. Fito da ma'anar karin maganar da ke cikin wannan labari na tafe.
A zamanin da, an yi wani sarki a }asar gabas mai tausayin talakawa da jin }ai. Mutanensa suna matu}ar jin da]in mulkinsa. Amma duk abin nan ba shi da magaji na }warai. [a ]aya yake da shi wanda kowa ba ya yaba halayensa. Wazirin Sarkin nan kullum ya kan ce 'da muguwar haihuwa gara kyakkyawar tusa'. Ganin haka ne ma shi Wazirin ya ri}a kula da nasa yaron don kar ya lalace don kuwa Hausawa sun ce idan gemun ]an’uwanka ya kama wuta sai ka yayyafa wa naka ruwa.
(3) Me karin magana ke nunawa game da al'adun Hausawa?

**SIGOGIN KARIN MAGANA**
Karin magana tana da sigogi iri-iri. Abubuwan da ake amfani da su a cikin karin magana suna da yawa. Ana amfani da mutum ko dabba ko wani abu marar rai.
Karin magana sun bambanta ]angane da yadda mutane kan yi amfani da su. Akwai wa]anda za ka iya kawo rabi, wani mai sauraro shi kuma ya kawo rabin idan ya so. Misali
(i) Laifi tudu ne (sai ka take naka ka hango na wani).
(ii) Allah mai halitta (ja~a ta ga bakin mijinta).
(iii) Hauka ja! (hular dara ba riga).

Akwai kuma wa]anda dole idan an kawo su a cika su. Misali:
(i) Ba a mugun sarki (sai mugun bafade).

(ii) Daga ganin sarkin fawa (sai miya ta yi za}i).
(iii) Rai dai! (an cire wa fara kai).

Akwai wa]ansu karin maganar wa]anda suka }unshi wani labarin abin da ya faru ga wani kuma sai a sarrafa shi ya dace da wani abu da ya faru ko zai faru a yanzu. Misali:
(i) Gaba ta kai ni (gobarar Titi).
(ii) Allah ya yi min gya]ar Dogo (sama 'ya 'ya, }asa 'ya 'ya)
(iii) Fa]an Goggo a kofa.

**AIKI II**
1. Kawo sigogi uku da ka sani na karin magana.
2. Saka wannan karin maganar a jumlar da ta dace
Da zuwan sarkin fawa sai miya ta yi za}i?
3. Kawo karin magana iri uku ta yadda za ta kasance: ]aya- a kan mutum;
]aya- a kan dabba;
]aya a kan wani abu sandararre.

**AMFANIN KARIN MAGANA**
Karin magana na da amfani wajen biyan wasu ba}atu na rayuwa. Akan kawo karin magana don a kwantar da hankalin wani. Misali:
Maha}urci mawadaci ne.
Rabon kwa]o ba ya hawa sama.
Wasu kare-karen maganar kuma suna nuna ladabi da biyayya. Shi ya sa Hausawa kan ce
- dur}usa wa wada ba gajiyawa ba ce sai ka tashi da tsayinka.
- Girman kai rawanin tsiya.

A wani zubin kuma, karin magana kan nuna ha]in kai da son juna.
- Hannunka ba ya ru~ewa ka yannke ka yar.
- Hannu ]aya ba ya ]aukar boto.

**AIKIN GIDA**
Ana bu}atar ka tsamo karin magana biyar masu koyar da:
a) Ladabi
b) Nuna }in zaman banza
c) Ha]in kai.

**TA{AITAWA**
A cikin wannan babi an ta~o ire-iren karin magana - wato wa]anda suka }unshi al'amari da Hausawa suka lura da shi da kuma wani ra'ayi da suka yarda da shi. An kuma ta~o irin sigogin karin magana. Za ta iya kasancewa doguwar jumla wadda ba dole ba ne kai mai fa]i ka ciko sauran sassanta. Za kuma ta iya zamewa ta }unshi wani labari wanda dole ne sai an san shi kafin a gane karin maganar.
Daga }arshe kuma an kawo ire-iren amfanin karin magana. Akwai masu jaddada zamantakewa da ha]in kai, ko masu }arfafa gwiwa don a yi wani abu, ko masu tarbiyya a kan ladabi da biyayya, da masu hana munafunci da kira a kan zaman salama.

**MANAZARTA**
Zarruk R. M. et.al (1986) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.* Ibadan: Oxford University Press Limited.
Yusuf Yunusa (1977) *Hausa A Dun}ule.* Zaria: NNPC Ltd.
Nigerian Education Research Council (1980) *UPE Textbook of Methodology*, Zaria: Gaskiya Corporation.

## KASHI NA 5: MANUFOFI DA MUHIMMANCIN WA{AR BAKA GA HAUSAWA

### GABATARWA
Mun yi bayani a kan abin da ake ce ma wa}ar baka da kuma rabe-rabenta. A wannan kashi kuwa za mu dubi wa}o}in ne mu yi bayanin muhimmancinsu da manufofinsu ga al'ummar Hausawa. Manufa dai tana nufin mu yi bayanin ko don me Hausawa ke shirya wa}a? Bayan haka kuma sai mu yi bayanin irin muhimmancin da wa}a take da shi ga Hausawa.

### MANUFA
Ana fatar ya kasance ka fahimci manufar wa}ar cikin al'ummar Hausawa da kuma muhimmancinta bayan }are darasin da ke cikin wannan kashi a wannan fasali. A cikin wannan kashi ne ake fatar ka san manufar wa}a da kuma muhimmancinta.

### MATAKAN NAZARI
Ana son ka kula sosai a cikin wannan kashi domin ka tantance manufar kowace wa}a da muhimmancinta. Sai ka lura da cewa akwai ire-iren wa}a daban -daban kuma kowace tana da tata manufa da kuma muhimmanci. Don haka sai ka yi hattara don kada ka hargitsa manufar wata irin wa}a da wata. Ka yi }o}arin gane kowane kashi na wa}a tare da sanin manufarsa da muhammancinsa.

### MANUFOFI DA MUHIMMANCIN WA{AR BAKA GA HAUSAWA
Idan ka lura za ka ga wannan kashi yana magana ne a kan abubuwa biyu, wato manufa da muhimmanci don haka za mu ]auke su ]aya bayan ]aya mu yi bayani. Don haka sai ka lura.

### MANUFAR WA{AR BAKA
Manufofi jam'in manufa ne, wannan kuwa yana nufin ma}asudin abu. Ita wa}a ko da Bahaushe ya tsara ta to akwai abubuwan da yake nufi da tsara ta. Wannan shi ya sa ya tsara ta yara daban, ta mata daban da sauransu. Akwai manufofi ga wa}a gwargwadon yadda aka tsara ta kamar haka:

### WA{O{IN YARA
Su wa]annan wa}o}i wa]anda yara ke yi a ]andali da wa]anda ake samu a cikin tatsuniya suna da manufofi kamar haka:

i. Tabbatar da abin da ake son yaro ya fahimta a cikin tunaninsa. Wannan shi ya sa ake yawan maimaita wa}a ]aya mai ]auke da jigo a cikin tatsuniya.
ii. Jawo hankalin yaro ga abin da ke jiran shi idan ya yi sake ya kuskure abin da yake daidai kamar *wa}ar sha-burburwa* inda ake ambaton kulki da siffofinsa.
iii. Nuna wa iyaye wani abu da ke ci wa yaro tuwo a }warya amma kuma ba ya da ikon yin magana, kamar yadda yake a cikin wa}o}in `yan mata masu nuna kyamar auren tsoho.

### WA{O{IN MATA
Wa}o}in da mata ke yi a lokacin reno da daka da wuraren da~e da sauransu nasu manufofi kamar haka:

Furta wata damuwa da ke cikin zuciyar mace. Ana iya ganin haka a cikin wa}ar da ke cewa;

"Ni, ni ba zan iya ba.
Ni ba zan iya aure gidan yawa ba.
Gidan yawa ga **tsintse da tsintse-tsinte**.

Nuna }auna ga jariri. Misalin wa}ar nan ta "kai yi shunka, ba ni daka da kai goye
Don kada gari ya ~ata ka."

Arashi: haka kuma mata kan yi wa}a domin su yi ma kiyoshinsu gugar zana. Misali kamar wa}ar, "|era mai ]iya an dawo"

### WA{O{IN MAZA
Wa}o}in maza wa]anda ake aiwatarwa tare da ki]a su ma suna da manufofi kamar haka:

i. Fito da martabar wanda ko abin da ake yi wa wa}ar, misali, wa}o}in fada
ii. Bayar da }arfin gwiwa ga wasu masu wani aiki domin su ji da]in gu]anar da aikin, misali, wa}o}in sana'a.

iii. Zuga wani mutum domin ya yi wani aiki na ta'ad]anci, kamar wa}o}in maza.
iv. Bayar da nisha]i, kamar wa}o}in `yan kama da na `yan gambara.

**AIKI I**

(a) Mene ne manufar wa}o}in tatsuniya?
(b) Wace manufa ce mata ke yin wa}o}insu domin ta?

**MUHIMMMANCIN WA{AR BAKA**

Wa}ar baka na da muhimmanci sosai ga Bahaushe da kuma rayuwarsa. Wannan shi ya sa ake iya samun wa}a a cikin kowane ~angare na rayuwar Bahaushe. Daga muhimmancin wa}a ga Bahaushe akwai:

i. koyarwa: Bahaushe na amfani da wa}ar baka domin koyar da 'ya`yansa wasu darussa. Misali, wa}ar da ke cikin tatsuniya," Musan Gayya" inda ake koyar da jin kunya ga `yan matan Hausawa.
ii. A]ana harshe: Bahaushe na amfani da wa}ar baka a matsayin rumbun ajiye harshe. Misali a cikin wa}ar, Narambada ta *Ya Ri}a Ni da Girma* inda yake amfani da kalmomi kamar "bobaka" wadda ke nufin fatun da ke reto a wuyann namiji.
iii. Kafa hujja: Bahaushe na amfani da wa}ar baka domin kafa wata hujja a cikin zance.
Misali, "Kowas sami abinai, yana da dama yai shagalinai".
(Hassan Wayam)
iv. Nisha]i: Wa}ar baka na da muhimmanci ga Bahaushe wajen bayar da nisha]i. Wannan shi ya sa a cikin kowane buki na Bahaushe sai wa}a ta taka rawa.
v. Garga]i: Bahaushe kan yi amfani da wa}a domin yin garga]i. Misali. "Yau sarkin kasarsa Hakimman }asar Isa
Duk da diyann duk da kanne, ku bi shi ku bar kissa Wallahi in gandon ya fi fashe ba kujin dadi" (Narambada: Amadu Bubakar)
vi. Sadarwa: Bahaushe na yin amfani da wa}a }warai ga sha'anin sadarwa. Domin haka ne hukuma da kanta ke amfani da wa}o}in maka]a domin sadarwa idan suna son isar da sa}o ga jama'a.
vii. Wayar da kai: Wa}a na da muhimmanci ga Bahaushe wajen wayar da kan jama'a. Misali, Wa}ar Shata ta, "Allurar riga kafin agana"

**AIKI II**

(a) Ta yaya wa}ar baka ke iya zama rumbun a]ana harshe ga Bahaushe?
(b) Ta yaya hukuma ke amfani da wa}ar baka ga al'ummar Hausawa?

**AIKIN GIDA**

(a) Wa]anne manufofi ne suke da dangantakaka ga wa}ar yara?
(b) Mene ne manufar wa}ar reno?
(c) Wa}o}in fada suna da manufa, fa]i manufar.
(d) Fa]i muhimmanci uku na wa}a ga Bahaushe.

**TA{AITAWA**

Wannan darasi da ya gabata a cikin wannan kashi ya yi magana ne a kan abubuwa guda biyu muhimmai:

i. manufar wa}ar baka ga Bahaushe da
ii. muhimmancin wa}ar baka ga Bahaushe.

**MANAZARTA**

Yahaya, A.B.(1997), *Jigon Nazarin Wa}a.*Kaduna: FISBAS Media Services.

## KASHI NA 6: SALON MAGANA

### GABATARWA

Magana ita ce, furta wani abu domin isar da sa}o. a idon Bahaushe magana ta karkasu daban-daban. Daga cikin magana akwai karin magana da ba'a da ba}ar magana da kirari da habaici da zambo da salon magana da dai sauransu. Wannan kashin za mu mayar da hankali ne kawai kan salon magana. Kamar yadda muka ga bambanci a maganganun Bahaushe, salon magana ma na da rabe-rabensa.

Salon magana, wata sar}a}}iyar magana ce da ake tsarawa domin isar da sa}o da burge masu sauraro. Idan aka ce ana nufin tsarin wani abu na musamman. Magana kuwa na nufin isar da sa}o ta musamman. A tsarin Hausa idan aka ce "salon magana cikin wani salo za~a~~e mai burge mai sauraro mai nuna }warewar mai magana**.**

A tsarin salon magana akwai:

(i) Gagara-Gwari

(ii) Ingiza-Bami

(iii) Ingiza-wawa.

Kowane kashi daga cikin wa]annan kaso wani rukuni ne da kansa. Kada in cika ka da gafara sa ba ka ga }aho ba, ga kashin.

### MANUFA

Manufa a wannan darasi shi ne, ya lurar da mai karatu abubuwwa kamar haka:

(i) ma'anar salon magana da muhallinta;

(ii) kashe-kashen salon magana;

(iii) wuraren da ake amfani da salon magana;

(iv) yadda tsarin salon magana yake;

(v) a karanta salon magana a rubuce.

### MATAKAN NAZARI

Nazarinmu zai bi fasalin daki-daki, ]aya bayan ]aya da bayanai da misalai, don haka:

(i) ka kula sosai da ginin kalmomin salon magana;

(ii) ka lura da yadda jumlolin salon magana suke;

(iii) ka fayyace yadda ma'ana ke fita a̩ciki;

(iv) dinga lura da tsarin sautukan kalmomin.

### SABABBIN KALMOMI

| | |
|---|---|
| Salo: | tsarin gu]anar da abu |
| Bami: | ]an koyo |
| Gwari: | wanda ba Bahaushe ba, Bagware ke nan Sar}a}}iya: wani cikin wani |
| Za~a~~e: | fitacce ko fiyayye ko yardajje. |
| Burge: | abin da ya ba da sha`awa |
| Sa}o: | abin da ake son a isar. |
| Kirari: | kalmomin yabo cikin washi |
| Habaici: | yi da mutum ta kaikace. |
| Zambo : | kushe mutum ta fuskar }age. |
| Ba}ar magana: | magana maras ladabi ta izgili |
| Ba'a: | maganar wasa don raha da ban dariya. |

### GAGARA-GWARI

Wannan rukunin salon magana ya }unshi kalmomi masu sauti iri ]aya. Suna da wuyar fa]a ga kowane mutum da ba a mama ya sha Hausa ba. A ta}aice dai Bagware da ]an mun-iya da su mun-ji-Hausa duk za a bar su a baya. Ga tsarin su kamar haka:

(a) kwa]o a }o}o a kogo a kwance.

(b) ]an }o}o cike da tsaba batsa-batsa.

(c) na zo }o}o, na yini }o}o, ban sha }o}on }o}o ba }o}o }on.

(d) cab cabe kashi tsoka tsoke soke ga fa}o.

(e) da Kalla da abokin Kalla sun tafi kallon kalangu aka kalle abokin Kalla da mari wajen kallon kalangu
(f) da kwa]o da }ato sun yo }oto. Kwa]o ne zai kar~e wa }ato }oto ko }ato ne zai kar~e wa kwa]o }oto.

Ka lura duk kalmomin da ba cikin suna da sautuka masu kusa da na juna. Don haka su ne ake ce musu gagara-Gwari.

**AIKI I**

(i) Don me ake kiran sa gagara-Gwari?
(ii) Kawo misali ]aya na gagara-Gwari.

**INGIZA-BAMI**

Bami ana nufin wanda bai }ware da Hausa ba sosai da sosai watau ]an koyo. Ana nufin idan bami zai fa]i zancen da wuya bai zagi kansa ba. Ingiza-Bami abokin "gagara-Gwari" ne, bambancinsu kawai shi ne, a "gagara-Gwari" ba batsa amma a "Ingiza-Bami" a kan sami batsa.

(a) Na bugi bakin dokin baba da bayan hannu.
(b) Fara-fara ba faraniya, ba}a-ba}a ba faraniya.
(c) Gashin muntan mussab baba zaro-zaro.

**AIKI II**

(i) Me ya bambanta "Gagara-Gwari" da "Ingiza-Bami"?
(ii) Kawo "Ingiza-Bami" ]aya mai ma'ana.
(iii) Me Ingiza-Bami na lambar (b) ke son a ce a yi kure?

**INGIZA-WAWA**

Wannan rukunin wasu `yan gajerun jumloli ne da idan aka za ta sauya a yi batsa. Don haka sam bai yi kusa da gagara-Gwari ba, kuma ya yi kama da Ingiza-bami. Ga dai yann misalansa kamar haka:

(a) Na cika katata tab da ruwa
(b) Rami na gefen rigar Habu
(c) Rii tab cike da ruwa duu.

**AIKIN GIDA**

(i) Rubuta kashe-kashen salon magana.
(ii) Kawo misalin Gagara-Gwari ɗaya.
(iii) Zo da misalin Ingiza-Bami" ]aya.
(iv) Rubuta misalin Ingiza-Wawa ]aya.

**TA{AITAWA**

(i) Mun gano ma'anar salon magana.
(ii) Mun fayyace ma'anar Gagara-Gwari.
(iii) Mun gano manufar Ingiza-Bami
(iv) Mun rarrabe misalan Ingiza-Wawa.

**MANAZARTA**

Ɗangambo. A. (1984) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph Publishers Ltd.
Umar, M.B. (1980) *Adabin Baka don Makarantu.* Zariya: NNPC Ltd.

## KASHI NA 7: RABE-RABEN MAKA[AN HAUSA

**GABATARWA**
Kusan kowace al'umma tana da ire-iren maka]anta da mawa}anta. Al'ummar Hausawa tana da maka]a iri daban-daban. Wannan rabe-rabe ya samu ne sakamakon nau'in ko irin wa}o}in da jigon wa}o}in da dangantakaka da kuma dalilan da suka sa ake yin wa}o}in da ka]e-ka]en da irin mutanen da ake yin wa}o}in dominsu.

**MANUFA**
Ma}asudin wannan matani shi ne bayan an kammala ana so ka iya:
i. bambancewa tsakanin maka]an fada da na jama'a;
ii. ba da misalan sunayen maka]an fada da maka]an jama'a da maka]an sana'a;
iii. tantance maka]an maza daga cikin jerin maka]an Hausa;
iv. bayani kan maka]an sharholiya.

**MATAKAN NAZARI**
1. Da farko zai dace ka yi tunanin ire-iren rnaka]an da ka ta~a gani ko sauraron wa}o}insu ko dai a fili ko kuwa a rediyo ko a garmaho ko a talabijin.
2. Sannan ka karanta wannan kashi cikin natsuwa
3. Ka sake bitar karatun amma wannan karon amma ka ri}a ja wa kalmomin da suka yi maka tsauri layi.
4. Idan ka ga cewar abubuwa sun shige maka duhu ka yi bita ta musamman a kansu.

**SABABBIN KALMOMI**
**Sharholiya** - nisha]i ko abu mara muhimmanci
**{ayatar** - ban sha'awa

**RABE-RABEN MAKA[AN HAUSA**
Ki]a yana nufin wanzar da dadda]an amo daga abubuwan bugawa ko gogawa ko busawa ko kuma na girgizawa. Wa}a kuma magana ce cikin sarrafaffiyar murya wadda ake rangwa]awa bisa wani tsari. Duba Zarruk da abokansa a littafinsu mai suna *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa*, littafi na biyu don karin bayanin.
Maka]a su ne masu yin ki]a kawai ko kuma ki]a ha]e da wa}a Maka]an Hausa sun rarrabu gida-gida kamar haka:

**MAKA[AN FA[A**
Maka]an fada su ne wa]anda ba sa yi wa kowa ki]a sai mai ri}e da wata sarauta musamman mu}amin da ya shafi gargajiya, misali sarki da hakimi da manyan fada da dagaci da sauransu.

Da wuya ka samu cewar maka]in fada ba shi da uban gida. Al'adar sarakunan }asar Hausa ce ta ]aukar nauyin maka]i na cinsa da shansa da tufafinsa don a sha ki]a. To, irin wa]annan maka]a dole sai sun nemi izini daga uban-gidansu domin su yi wa wani ki]a.

Daga cikin shaharrun maka]an sarauta akwai su:
Musa ]an}wairo da Salihu Jan-ki]i da Narambada da Sa'idu Faru da Mamman Sarkin Taushin Katsina.

**MAKA[AN JAMA'A**
Maka]an jama'a kan yi wa kowa ki]a. Wannan ya ha]a da basarake da mai ku]i, talaka ko mai wata sana'a. Duk wanda ya ba su suna iya masa wa}a. Wani lokaci ko ba a ba su sai su yi a bisa ganin dama.
Maka]an jama'a sun ha]a da shahararrun makaa irin su Alhaji Mamman Shata da Amadu Doka da [an-maraya Jos da Mammalo Shata da. Garba Liyo da Babba Mai goge da Garba Sufa da Caji da Muhammadu Ganga-ganga da Hassan Wayam da sauransu.

**AIKI I**
[auki takarda da al}alami ka ja layi ka raba takardar gida biyu. A ~angare guda ka rubuta sunayen maka]an fada. A ~angare na biyu ka rubata sunayen maka]an jama'a.

**MAKA[AN SANA'A**
Akwai sana'o'i iri biyu a Bahaushiyar al'ada. Da farko akwai sana'o' in tattalin arziki da kuma sana'o 'in neman suna masu dangantakaka da jarunta ko hikimomi. Ku san kowace sana'a tana da maka]an ta. A }asar Hausa akwai sana'o'in tattalin arziki irin su noma wanda ake yi wa take da `na du}e tsohon ciniki, kowa ya zo duniya kai ya tarar". Haka kuma akwai sana'ar wanzanci da sana'ar jima da sa}a da rini da kasuwanci d a sauaransu. Akwai kuma sana'o'in }arfi da jarunta. Wa]annan sun ha]a da farauta da tauri da dambe da kokawa da sauransu. Wasu sun ]auki irin wa]annan tamkar sana'a. Amma za mu ware su a matsayin maka]an maza.
Misalan maka]an sana'a su ne [an}urji da Isa [an Makaho da [an Anace. Duba littafin Zarruk da abokansa mai suna *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa* don }arin misalai.

Misalan maka]an maza wato masu yi wa `yan dambe da `yan kokawa da `yan tauri dai su ne: ]an-anace da Kassu Zurmi da Hamisu mai Ganga da lsa ]an makaho.

**MAKA[AN SHARHOLIYA**
Maka]an sharholiya dai su ne masu sa mutane dariya don a yi raha da nisha]i. Saboda irin da]in da mutane ke ji ne kan sa su ba su ]an abin masarufi. Wasu daga cikinsu sun }ware ne wajen ba'a wasu kuwa sun iya sarrafa harshe. Akwai kuma wa]anda suka }ware wajen iya kwaikwayo.
Misalan irin wa]annan maka]a su ne `yan Gambara wa]anda suka }ware wajen ba'a, sai kuma `yan kama gwanaye a wajen kwaikwayo. Akwai kuma maka]an zari.

**AIKI II**
1. Tsakanin `yan kama da `yan Gambara wane rukuni ne ya fi }ayatarwa?

**AIKIN GIDA**
1. Me ake nufi da ki]a?
2. Wa]anne maka]a ne a ganinka ba su da `yancin yi wa kowa ki]a. Don me ka ce su ne?

**TA{AITAWA**
A wannan kashi an karanci rabe-raben maka]an Hausa. An kuma bayyana rukunan mutanen da sukan yi wa ki]a. Haka kuma, akwai misalan sunayen maka]an.

**MANAZARTA**
Zarruk R.M., da Kafin Hausa A.A. da Al-Hassan B.S.Y. (1987) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.* Ibadan: University Press Ltd.
[angambo A. (1984) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Mahumnancinsa Ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Gaskiya Corporation Ltd.

## KASHI NA 8: NAU'O'IN WA{O{IN MAKA[AN HAUSA

### GABATARWA

A kashi na bakwai da ya shu]e mun tattauna a kan rabe-raben maka]an Hausa. Wannan kashi yana }unshe ne da bayani a kan nau'o`in wa}o}in maka]an Hausa. Za mu tattauna kashe-kashen nau'o'in wa}o}in maka]an fada da na jama'a da na sana'a da kuma na maza. Bayan kammala tattaunawar, akwai misalan wa}o}in maka]an domin ]alibi ya karanta.

### MANUFA

Bayan kammala wannan kashi za ka iya:

i) rarrabe wa}o}in maka]an fada da na jama'a;

ii) bayani a kan nau'o'in wa}o}in maka]an maza;

iii) ba da misalan wa}o}in fada da na jama'a da na maza.

### MATAKAN NAZARI

I. Ka karanta wannan kashi daki-daki.

2. Idan ka yi karo da wata kalma wadda ba ka sani ba, to sai ka rubuta ta a takarda

3. Ka yi }o}ari ka amsa dukkan tambayoyin da ke cikin wannan kashi.

4. yana da kyau ka duba amsoshin da ke }arshen wannan littafi amma ka yi wa kanka adaki wato sai ka amsa tambayoyin sannan ka duba.

### SABABBIN KALMOMI

Ji~anci - ]anganci
Alfarma - mu}ami

### NAU'O'IN WA{O{IN MAKA[AN HAUSA

Za a iya rarraba wa}o}in maka]an Hausa zuwa rukunoni kamar guda hu]u. Da farko akwai wa}o}in maka]an fada da na jama'a da na sana'a sai kuma na maza.

### WA{O{IN FADA

A }asar Hausa, Sarakunan gargajiya na da maka]a masu yi musu wa}a. Za a iya cewa al 'ada ce ta sarakuna su ]auki nauyin wani mawa}i na abin da ya ji~anci cinsa da tufafinsa, kai har ma da muhalli don ki]a da wa}a da yake yi musu. Wa}o}in fada sun fi fito da tsofaffin kalmomi da tarihi da kuma siffofi irin na alfarma.

Haka kuma, jigoginsu sun fi karkata ne ga yabo da zuga da zambo.

Wani muhimmin abu ]angane da wa}o}in maka]an fada shi ne amshi. Akan maimata amshi a }arshen kowace ]iya. Amma ba lallai ne a samu cewa }arshen kowace ]iya ake maimaita amshi iri ]aya kacal ba. Haka kuma, ba al'adar irin wa]annan mawa}a ba ce ta su zo da ]iyoyi masu layuka bibbiyu ko biyar-biyar ba.

### AIKI I

Sarakunan gargajiya na }asar Hausa na da ke~a~~un mawa}a na musamman. Kawo misalan irin wa]annan mawa}a a}alla guda biyu tare da irin wa}ar da kowanne ya yi.

### WA{O{IN JAMA'A

{asar Hausa cike ta ke da mawa}an baka gama-gari. Ire-iren wa]annan mawa}a ba su ke~ance wa}arsu ga wani rukunin jama'a. Kuma suna iya zuwa ko'ina domin su yi wa}a. Rukunin wa]annan mawa}a kan je gidajen mutane ko kasuwanni ko mashaya wato wuraren sharholiya don yin wa}o}insu.

### WA{O{IN MAZA

Mazaje masu ayyukan }arfi da jarumai suna da maka]a na musamman. Mazaje irin su `yan dambe da `yan kokawa na da mawa}a na musamman. Haka kuma `yan tauri da `yan farauta suna da nasu mawa}an.

Misalan irin wa]annan mawa}a su ne Mamman [an`anace da Kassu Zurmi da Hamisu Mai Ganga wanda ya yi wa Sabo Wakilin Tauri na Kano da Alhaji Abu [an Kurma Maru Maka]in Baura da dambe da

Musa [angulbi (kokawa) da Garba [anwasa (tauri).

**MISALAN MAWA{A DA IRIN WA{O{INSU: WA{O{O{IN FADA**

Daga cikin irin jerin wa}o}in fada akwai ta Sarkin taushin Katsina Alhaji Mamman wadda ya yiwa Sarkin Zazzau Aminu Kandagarki. Ga ka]an daga cikinta:

"Mamman tsakin tama gagara tamna,
Baja da kai wargi ba,
Tsoronka akai uban zagi,
Hadarin safe mai ba uban wani kashi.

Haka kuma akwai wa}ar Sarki Kano Ado wadda [ankwairo ya yi kamar haka:

aljannar duniya!
[an Abdulkadir, Sarki Ado,
Na tare da kai ya liwanta,
Ruwan wankin dau]a,
Alhaji ruwan wankin dau]a ne

Misalan WA{O{IN JAMA'A. Za mu fara da ta A lhaj i Mamman Shata wanda ya yi wa Amadun Gaya. Amshinta 'shi ne:

"Na gode wa Amadun gaya" Kurkyat-kurkyat in ji zabuwa Ga Amadu mai ba da magani"

Alhaji [an-maraya Jos shi ma wani fitaccen mawa}in jama'a ne. Ga misalan wata wa}ar Ta'aziyya da ya yi.

"Allah na roke ka,
Albarkar manzon Allah
Ka kyautata ma Haladu
Haladu farin tsoho

Misalan wa}o}in maza. Daga ciki akwai ta Hamisu Mai Ganga wadda ya yi wa Sabo Wakilin Tauari kamar haka:

"Ayye! Sabo Wakilin Tauri, dominka suke cin tauri,
Saboda kai suka san sa~ani, Kana suka san kas-kaifi,
Da ba-duhu layar zana Domin ka maza ke cin sagau"

Sai ta [an`anace da ya yi wa Ado [ankure (dambe)

"La' ilaha illallahu,
duniya sakatil mauti,
ya tabara ka cetan,
garin da ban san kowa ba".
Amshinta kan kare da,
"Maza na tsoron karo da Ado [an kure".

**AIKI II**

1. Mawa}an jama'a kan yi wa kowa wa}a. Wane mawa}i ne ka fi jin da]in wa}arsa? Kawo misalin wa}o}insa guda biyu.
2. Mawa}an maza sun }ware wajen wasa jarumai kamar `yan tauri da `yan dambe. Kawo misalan irin wa]annan mawa}a tare da a}alla wa}a ]ai-]ai.

**AIKIN GIDA**

1. Yi }o}arin sauraron wa}o}in jama'a da sarakuna da na maza. Kana iya ke~e lokaci guda don sauraron Rediyo Kaduna a lokutan da suke za~e.
2. Lokacin da kake sauraro, ka ]auki al}alaminka da takarda don rubuta abubuwan da kunnenka ya ji.

**TA{AITAWA**

A wannan kashi an nazarci nau'o'in wa}o}in maka]an Hausa musamman mawa}an fada da mawa}an jama'a da mawa}an sana'a da kuma mawa}an maza. Haka kuma kashin }unshe yake da misalan wa}o}in fada da na jama'a da na maza. Wa}o}in fada sun fi bayyana yabo da zuga da zambo.

Wa}o}in jama'a ma na }unshe da yabo, fa]akarwa da wayar da kai. Wa}o}in maza kuwa sun fi mai da

hankali wajen bayyana jarunta.

**MANAZARTA**

Zarruk R.M. da Kafin Hausa A.K da Al-Hassan B.S.Y. (1987) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa,* Ibadan: University Press Ltd.

]angambo A. (1984) *Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Zaria: Gaskiya Co-poration Ltd.

**KASHI NA 9: DARUSSAN DA WA{O{IN MAKA[AN HAUSA KE KOYARWA**

**GABATARWA**

Wa}o}in maka]an Hausa ba kawai sun tsaya ga nisha]i ko bandariya ne ba, a'a. Akwai darussa managarta da suke koyar wa jama'a.

Daga cikin ire-iren darussan da suke koyarwa akwai wa'azi da a]ana tarihi da nasiha da wayar da kai da koyar da iya sarrafa harshe da sauransu. Saboda haka, kusan a duk matakan matsayi ba rukunin da ba sa son wa}o}in maka]a.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi ana sa ran ka iya:

1) bayyana darussan da suka ]anganci wa'azi da wa}o}in maka]a ke koyarwa;
2) sharhi kan wa}o}in da suke fa]akar da jama'a a kan wani sabon abu;
3) jawabi tare da ba da misalan wa}o}in maka]a da ke a]ana tarihi;
4) fito da }arangiya da ke cikin wa}o}in maka]a.

**MATAKAN NAZARI**

1. Ka karanta wannan matani sosai.
2. Bayan ka kammala karantawa sai ka natsu ka kuma tuna ire-iren wa}o}in maka]an da ka sani.
3. Akwai ayyuka wa]anda za ka yi guda biyu: ]aya a tsakiyar matanin; na biyu kuma a }arshen matanin. Yi }o}arin amsa dukan tambayoyi.
4. Haka kuma, akwai aikin gida da ya kamata ka yi shi. Bayan ka kamala, sai ka duba }arshen wannan littafi domin akwai amsoshin tambayoyin.

**SABABBIN KALMOMI**

{arangiya - salon magana ce da ke nuna gwanancewa a cikin harshe.
Luguden kalmomi - jera kalmomi masu kama da juna
Katutu - abu ya taru da yawa

**DARUSSAN DA WA{O{IN MAKA[AN HAUSA KE KOYARWA**

Wa}o}in maka]a suna da matu}ar muhimmanci ga rayuwar al 'ummar Hausawa. Kusan za a iya cewa a dukkan matakan matsayi fara daga kan sarakuna da hakimai da dagatai da attajirai da malamai da masu sana'o'i da talakawa babu rukunin da ba su son wa}a. Hakan ya faru ne saboda ]umbin darussan da wa}o}in ke koyarwa.

Daga cikin irin darussan da wa}o}in ke koyarwa, akwai wa'azi da nasiha da fa]akarwa ko wayar da kai da a]ana tarihi da sauransu.

Da yake an bayyana ka]an daga cikin irin darussan da wa}o}in ke koyarwa, to, za a ]auki kowane darasi domin gano irin wa}ar da ke }unshe da shi.

**WA'AZI**

A cikin irin wa}o}in maka]an Hausa akwai wa]anda jigonsu wa'azi ne. Misali wa}ar ]an–Maraya Jos ta Aure*:*

"Maigida da uwargida,
In an yi fa]a don Annabi,
Don Allah a bar saurin fita.
Da can kina ko gidan miji,
Rigar sawa sai ya yi,
Zanen ]aurawa sai ya yi,
Su ]an-kwali shi za ya yi,
Maigida kai zan maka gargadi,
Kai ma wannan matarka ce,
Ruwan wanka ita za ta kai,
……………………………
Daga }arshen wa}ar, sai ]an-Maraya ya ce:

"mata ku ri}e aure da kyau,
to maza ku ri}e aure da kyau,
A cikinku maza ma har da ni".

]an-Maraya ya fara da ro}on mata da su daina fita da zarar sa~ani ya shiga tsakaninsu. Kana ya rufe da ro}on mata da maza da su ri}e aure da kyau.

Haka kuma Shata a cikin wata wa}arsa da ya yi yana cewa:
"Don sallah da salatil fatihi
don Allah mata ku yi aure".

**DARUSSA KAN TARIHI**
Wasu wa}o}in maka]an kuma cike suke da darussa kan tarihi da al'adu. [auki misalin wa}ar Alhaji Musa ]ankwairo kan *Al'adun Gargajiya* da yake cewa:
"Kar mu sake mu mance
m bi al'adummu na gargajiya.
sai ka ga ]an Musulmi
ga 'yasshat ya sa ga wuya
ba hulla ga kai nai
aljihu nai babu tasbaha
sai kwalin sigarim
mu bi al'adummu na gargajiya!

Haka kuma Sarkin Taushin Katsina na cewa:
"Duniya ta yi kyau,
arziki ya yi,
tun da mun kar~i mulki,
cikin sa'a.
Ran Asabar [ai Watan Goma rannan
ka ji rannar da ba za mu manta ba"
Wannan wa}a na nuni ga tarihi, wato ranar da aka kar~i mulkin kai a Nijeriya.

**AIKI**
1. A fahintar ka, me wa}ar Musa [ankwairo ta ke koyarwa?
2. Rubata hakkin maigida guda ]aya da kuma hakkin uwargida guda ]aya da ka koya a wa}ar [an-Maraya.

**WAYAR DA KAI**
Wasu wa}o}in maka]an Hausa suna himmatuwa wajen wayar da kan al'umma. Don haka mutane kan fahimci abubuwa da dama sakamakon sauraron da suke yi na wa}o}in.
Misali akwai wa}ar Haruna Oji ta *Sababbin Ku]a]e.*
"Naira da kwabo sabon ku]i
ina maganar sabon ku]i
ka duba jikin naira biyar
jikinta akwai dalar gyada
…………………………..
Ya Allah kai mana arziki
Saboda wula}ancin gaba."

Haruna Oji ya yi }o}arin bayanin ire-iren alamomin da sababbin ku]in ke ]auke da su.
A lokacin da kiliya ta koṃa hanun dama Mamman Shata ya yi wa}a don wayar wa mutane kai.

**KOYAR DA SALON SARRAFA HARSHE.**
Wasu wa}o}in suna koyar da iya sarrafa harshe da kuma }ara fa]a]a fahimtar kare-karen harshe. Misalan

in wa]annan wa}o}in sun ha]a da, wa}ar Sani Sabulu da kuma wa}ar Sa'idu Faru wadda ke ]auke da }arangiya kamar haka:

"Yaro in takamar salon magana ka ka ji,
ce tsare-tsara, tafi tsattsame tsattara,
ka tsantsame tsari tsaf daga tsamiya"

A wannan wa}a }arangiya ta bayyana a fili. Wannan sar}a}}iyar ko luguden kalmomi ne domin nuna }warewa cikin harshen.

**AIKI**

1. Daga cikin wa}ar Sa'idu Faru, tsamo kalmomin da aka yi lugudensu.
2. Ka ta~a jin wannan wa}ar? Idan amsarka 'e' ce, to, wace }arangiya ce ta zo kafin wannan da aka kawo misalin?

**AIKIN GIDA**

1. Wa}o}in maka]a ba komai suke koyawa ba illa sharholiya kurum.
   Shin ka yarda da wannan batun. Tallafi ra'ayinka da bayani gamsasshe tare da misalai.
2. Rike al'adun gargajiya yana da muhimmanci. Yi bayani a kan wannan }aulin tare da kawo misalin wa}a ]aya tak.
3. Me wa}ar Haruna Oji take koyarwa?

**TA{AITAWA**

Wa}o}in maka]an Hausa cike suke da darussa masu amfani ga jama'a. Suna wa'azantarwa da wayar wa mutane kai ]angane da wani sabon abu da kuma a]ana tarihi da koyar da salon sarrafa harshe.

An kawo misalan wa}o}i da dama don fayyace ainihin darussan da suke ]auke da su. Akwai ayyuka da ake bu}atar ka yi bayan ka kammala karanta matanin.

**MANAZARTA**


Umar, M.B. (1987) *dangantakakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya.* Kano: Tofa Commercial Press.

Ɗangambo, A. (1980) Hausa Wa'azi Verse from C.A. 1800 to C.A 1100: A Critical Study of Form, Content and Style" Kuridin digiri na Uku. London: Jamilax London Kundin Bincike.

**KASHI NA 10: BITA**

**GABATARWA**

A cikin wannan fasali, mun karanci adabin gargajiya a cikin al'ummar Hausawa. Kashi na farko ya yi nazarin amfanin adabin baka ga al'umma. Na biyu da na uku sun kula da tatsuniya, zube da kacici-kacici. Kashi na hu]u ya tattauna a kan karin magana, na biyar kuma a kan wa}ar baka. Kashi na shida ya dubi salon magana, na bakwai da na takwas ]ana tara kuma maka]an Hausa.

A nan kuma, za mu yi bitar muhimman batutuwan da wa]annan kasusuwa suka }unsa.

**MANUFA**

Ana fatar idan ka karanta wannan fasali ka iya:

1. Lissafa amfann adabin baka ga al'umma;
2. Bayani a kan tatsuniya da zube da kacici-kacici;
3. Tattaunawa a kan karin magana da wa}ar baka da kuma salon magana;
4. Fayyacewa tsakanin maka]an Hausa da ka]e-ka]ensu.

**MATAKAN NAZARI**

I. Ka dubi a}alla sashen Gabatarwa na dukan kasusuwan da suka gabata, wato kashi na 1 zuwa na 9.
2. Ka karanta wannan kashi dalla-dalla, a hankali kana mai la'akari da abin da ka karanta a kashi na 1 zuwa na 9.
3. Ka yi ¸ }o}arin amsa tambayoyin da za su biyo a cikin ayyukan wannan kashi ba tare da dubo amsoshin daga Sashen Amsoshi ba.
4. Ka maimaita karanta kashin baki [AYA don ka tsamo amsoshin tambayoyin da suka gagare ka a karon farko.
5. Ka karanta amsoshin da ka bayar da na cikin Amsoshi a bayan littafin nan.

**ADABIN BAKA A AL`UMMA**

A kashi na farko ne muka ga bayani a kan ma'anar adabin baka, cewa yana }unshe ne da maganganu na hikima kamar su tatsuniya, labari, almara, wa}e-wa}e, karin magana da kirari, habaici, kacici-kacici da kakkarya harshe.

A nan ne fa muka fahimci cewa adabin baka ne taskar hikimomin al'umma irin Hausawa. Yakan taimaka wajen ilimintar da al'umma ta amfani da hanyoyin da muka lissafta a baya irin su tatsuniya da karin magana. Yakan koya wa yara harshensu ta hanyar kakkarya harshe da kacici-kacici, yakan kuma samar da nisha]i da annashuwa.

Baki ]aya dai adabin baka yakan taimaka wajen tarbiyyar yaranmu har dai wajen su tatsuniya irin ta *Ruwan Bagaja*. Yakan kuma taimaka wajen fito da tarihin al'ummanmu kamar yadda muke samu a wa}e-wa}en irin na su Sarkin Taushin Katsina a *Wa}ar `yannci*.

**AIKI**

Lissafta amfanin adabin baka ga Hausawa tare da misalai.

**TATSUNIYA DA ZUBE DA KACICI-KACICI**

A kashi na 2 mun yi nazari a kan tatsuniya da zube. Tatsuniya dai }agaggen labari ne mai ma'anar kuma yana }unshe da hikima da tarin abin koyo ga yaranmu. Wannan ya bambanta da rubutun zuben labari. Shi kuma ya kasu gida biyu: akwai almara, akwai kuma hikaya. Almara labarin hikima ne mai bu}atar mai sauraro ya gano wanda ya fi hikima cikin daga cikin hikimomin da aka kwatanta a cikin labarin. Ita kuma hikaya kamar hanyar koyarwa ce a makaranta inda ake }o}arin fito da martabar wani abu da aka yi labarin hikayar da shi. Tarihi ma na irin labara ne tun da shi kan hakikanin abin da ya faru ne ake gabatarwa.

Kacici-kacici, tatsuniya ce mai neman wasa }wa}walwa don ta }unshi tambaya ko kuma aike.

**AIKI II**

1. Mene ne bambancin tatsuniya da zube?
2. Mene ne bambancin almara da kacici-kacici?

**KARIN MAGANA DA WA{AR BAKA DA SALON MAGANA**

Mun fahimci cewa karin magana ya kasu kashi biyu. [aya mai kula da al'amarin yau da kullum, ]aya kuma wanda ya }unshi ra'ayin da aka yarda da shi. Mun kuma wajen amfani da karin magana kamar wajen kwantar da hankali `yann `uwa ko nuna ladabi ko ha]in kai.

Mun kuma karanta muhimmancin wa}ar baka saboda yawanci ana tsara wa}o}in ne da manufa. Akwai na yara irin na cikin tatsuniya da ke koya tarbiyya. Akwai na mata irin na renon yara ko wajen da~e ko arashi. Akwai kuma na maza a cikin ki]a misali don fa]anci da zuga da nisha]i kawai.

**SALON MAGANA**

Mun karanta salon magana da nau'o'insu guda uku: Gagara-Gwari da Ingiza-Wawa da kuma Ingiza-Bami.

A nan akan kakkarya harshe ne ko a caku]a kalamomi yadda za su ba wanda ba Bahaushe ba abin da bai san ma'anarsa mai nuni kamar zagi ko ma batsa.

**AIKI III**

Bambanta Kacici-kacici da salon magana tare da misalai

**WA{O{I DA MAKA[AN HAUSA**

Kashi na 7 ]ana 8 ]ana 9 sun kula da rabe-raben maka]an Hausa. Sun duba al'amarin maka]an fada irinsu Musa [an {wairo da Salihu Jan Ki]i da Naramba]a da Sa`idu Fara wa]anda ke wa sarakunanansu na musamman wa}o}i don suna ]aukar nauyin cinsu da shansu da ma sutura da sauran al'amuransu na bukatuwa.

Anyi nazarin maka]an jama'a irin su Mamman Shata da Amadu Doka da [an Maraya, Jos da Garba Liyo. Su kuma wa]annan sukan wa jama'a wa}a ne don ku]i ko iko ko ma }auna kawai. Akwai kuma maka]an sana'a, watau maka]a na musamman da ke wa sana'o`i na musamman wa}a kamar noma da wanzanci da jima da }ira da fawa da jarunta dai kowace in wajen dambe ko farauta ko tauri.

An kuma yi nazari a kan wa}o}in sharholiya irin na raha kamar su gambara da `yann kama. An kuma lisafta darussan irin wa}o}in kamar wa'azi, garga]i, wayar da kai, tarihi da sauransu.

**AIKI IV**

Ba da }arin misalan ire-iren maka]an Hausa bayan wa]anda aka rubuta a sama.

**AIKIN GIDA**

1. Yi ]an gajeren bayani a kan dangantakakar tatsuniya da labara na zube.
2. Kawo misalan wa}o}i da maka]an Hausa da irin darussan da ke cikin wa]ansu daga cikin wa}o}in da ka za~a.

**TA{AITAWA**

Wannan fasali ya yi bitar abin da kashi na 1 zuwa na 9 suka kawo wanda ya ha]a da:

- Ma'ana da amfanin adabin gargajiya;
- bayani tatsuniya da zube da kacici-kacici;
- bayani a kan wa}ar baka da maka]an Hausa.

**MANAZARTA**

Duba Manazartun kashi na 1 zuwa na 9.

## FASALI NA 5: ADABIN ZAMANI

## KASHI NA 2: RABE-RABEN RUBUTACCEN ADABI

### GABATARWA

Rubutaccen adabi shi ne, adabin da ya zo a rubuce kuma shi ne wanda ake kira da adabin zamani. Shi ne adabin da masu ilimi suke rubutawa a cikin littattafai domin jama'a su karanta su kuma amfana da shi. Wannan adabi ya samu ne sanadiyyar cu]anyar Hausawa da Larabawa da addinin Musulunci da kuma zuwan Turawa }asar Hausa. A wannan kashi, za a nazarci muhimman kaso da wannan adabi ya }unsa.

### MANUFA

A }arshen wannan kashi, ana fatan za a iya:

i. Kawo muhimman rabe-rabe uku na rubutaccen adabi;
ii. Kawo misalai uku-uku daga ayyukan rubutaccen adabi

### MATAKAN NAZARI

i. Karanta bayani sosai
   Ka duba jadawalin rubutaccen adabi da rassansa. Ka kalli misalai na ayyukan rubutaccen adabi sosai.


### SABABBIN KALMOMI

| | |
|---|---|
| Wanzuwa: | Samuwa |
| {arni: | Kalma mai nufin shekaru ]ari |
| Jigo: | Kalma mai nufin sa}o ko manufa |

### RUBUTACCEN ADABI

Rubutaccen adabi kamar yadda aka bayyana, adabi ne, wanda zamani ya kawo. Wato tun kafin zuwan Musulunci da Turawa babu rubutaccen adabi sai dai na baka. Rubutaccen adabi shi ne adabin da masu hikima suka rubuta shi a littattafai domin jama'a su karanta su kuma amfana. Shi dai rubutaccen adabi ya kasu zuwa gida uku muhimmai. Ga su:

a. rubutacciyar wa}a
b. rubutaccen zube (labari)
c. rubutaccen wasan kwaikwayo.




### RUBUTACCIYAR WA{A

Rubutattun wakoki sun samo asali ne daga wa}o}in Larabawa. Wa}o}in Hausa na farko an rubuta su ne cikin Hausar Ajami. Haka su wa]annan wa}o}in duka sun wanzu a sakamakon addini. {o}arin yada addinin Musulunci shi ne ya haddasa samar da su, kuma ya taimaka wajen ha~aka rubuta su. Rubutattun wa}o}i sun faro tun daga lokaci mai tsawo. Ana kyautata zaton cewar rubutun wa}o}in Hausa sun faru ne tun bayan da Musulunci ya yi }arfi sosai a }asar Hausa. Rubutattun wa}o}i sun ha~aka sosai a }arni na 19. {arni na 19 lokaci ne da Shehu Usman [an Fodiyo ya yi zamani. Shehu da almajiransa sun wallafa wa}o}i da dama a kan wa'azi na addinin Musulunci.

Akwai nau'o' in wa}o}i iri biyu. Wa}o}in }arni na 19 da na 20. Rubutattun Wa}o}i suna da jigon addini, su kuwa akwai misalai kamar:

i. Tabban Ha}i}an ta Shehu Usman
ii. Yabon Shehu Abdul}adiri ta Shehu Usmanu
iii. Wallahi-Wallahi ta Shehu Usmanu.
iv. Dalilin Samumar Allah ta Isan Kware.

Rubutattun wa}o}in }arni na 20, suna bayani a kan addini da wasu harkokin duniya. A wannan }arni na 20 Turawa suka shigo }asar Hausa. Turawa sun zo da ba}in abubuwa kuma an samu wa}o}i game da su. Ga misalan ka]an daga wa}o}in }arni na 20.

i. Wa}ar {iɗaya ta Akilu Aliyu
ii. Wa}ar Basukur ta Aliyu Namangi
iii. Wa}ar Ha]a kan Afirka ta Abubakar La]an
iv. Wa}ar Bu]e Sitadiyam ta Garba A.B.C.D.

A {arni na 20 aka rubuta wa}o}i da Hausar boko. Wannan tsari ya taimaka wajen samar da wa}o}i masu tarin yawa.

**RUBUTUN ZUBE**

Rubutun zube shi ne rubutun }agaggun labarai. Shi irin wannan rubutu ya bambanta da wa}a da wasan kwaikwayo. {agaggun labarai na cikin littattafai, irin su *Ruwan Bagaja*, da *Magana Jari Ce*, *Gan]oki* da *Iliya [an Mai {arfi* su ake tsarawa da rubutun zube. Rubutun zube ya zo ne bayan zuwan Turawa }asar Hausa. Rubutun zube ya faru ne bayan da aka kafa makarantun boko da yawa. An fara wallafa }agaggun labarai ne domin samar da 1ittattafan karatu ga ]alibai. An fara wa]annan rubuce-rubuce tun wajen shekakar 1930. Hukumar fassara a }ar}ashin wani Bature, R.M. East ce ta fara rubuta labaru. An samu labaru rubutattu na farko don karantawa kamar:

i. Dare dubu da [aya
ii. Labaru Na Da Da Na yannzu

A shekarar 1933 an yi gasar rubuta kagaggun labarai, aka nemi malamai da kowa ya rubuta littafi. Kowane littafi da aka rubuta to labarinsa }agagge ne kuma masu ilimin boko.

`yann Arewa sun rubuta littattafai da dama. Hukumar Talifi ce ta gu]anar da gasar rubuta littafin labari. An za~i littattafai guda biyar:

i. *Ruwan Bagaja* na Abubakar Imam
ii. *Gan]oki* na Bello kagara
iii. *Shaihu Umar* na Abubakar Tafawa |alewa
iv. *Idon Matambayi* na Muhammadu Gwarzo
v. *Jiki Magaji* na John Tafida.

Bayan wannan gasa an ci gaba da samun rubutattun labarai har zuwa yau.

**RUBUTACCEN WASAN KWAIKWAYO**

Rubutaccen wasan kwaikwayo wasa ne da aka rubuta shi a littafi: Ana rubuta shi ne domin ilmantarwa da sanya nisha]i da kuma ]ebe kewa. Akwai rubutattun wasanni a kan fannonin rayuwa dabam-daban. Wasan kwaikwayo rubutacce ya fara samuwa ne a shekarar 1898. An fara rubuta wasa na farko a wannan shekara ne kuma a cikin harshen Jamusanci. Wasan farko shi ne *Turbar {udus.* Wanda ko ya rubuta shi kuwa shi ne Dokta Rudolf Prietze. Daga nan, ya rubuta wasu wasannin kamar haka: *`yann Matan Gaya* (1900), *Turbar Tarabulus* (1902), *Tarihin Rabeh* (1902), *Wasan Boka da Majinyaci* da *Wasan Gizo da {o}i* (19 ). Daga nan ne aka sami wasannin nan masu suna *Six Hausa Plays* na Dr R. M. East a (1936). An kuma sami wasan da ake kira da suna rubutawa shi ne *Wasan Marafa* a 1948. Shi wannan wasa yana fa]akarwa ne a kan muhimmancin tsabta da kiwon lafiya. An samu ha~akar rubutattun wasannin kwaikwayo bayan an gina gidajen rediyo da na talabijin. Haka kuma, kafa kamfanonin buga littattafai shi ma ya da]a samar da littattafan wasan kwaikwayo. A yannzu akwai Misalan littattafan kwaikwayo wa]anda suka hada da:

i. Uwar Gulma na Muhammadu sada
ii. Matar mutum Kabarinsa na Bashari Farouk
iii. Tabarmar Kunya na Dauda Kano da [angogo
iv. Bora Da Mowa na Umar B. Ahmed
v. Zamanin Nan Namu na Shu'aibu Makarfi

Dukkanin wa]annan ka]an ne daga irin misalan rubutattun wasan kwaikwayo.

**AIKI NA I**

1. Yaushe ne aka fara samun rubutaccen adabi?
2. Wane salon rubutu ne aka fara rubuta wa}ar Hausa?

**AIKIN GIDA**

1. Kawo muhimman rabe-raben rubutaccen adabin Hausa
2. Kawo misalai uku-uku na kason rubutaccen adabin Hausa
3. Wane suna ne kuma ake kiran rubutaccen adabi da shi?

**TA{AITAWA**

Tun da farko, a wannan kashi mun }aru da cewar rubutaccen adabi shi ne adabin zamani. Rubutaccen adabi ya tattara abubuwa guda uku: rubutacciyar wa}a; da rubutun zube; da kuma rubutaccen wasan kwaikwayo. Rubutaccen adabi ya wanzu ne a cikin rubutun ajami da kuma na boko. Adabin zamani shi ne sunan da ake kiran rubutaccen adabi.

**MANAZARTA**

]angambo, A (1984) *Rabe-Raben Adabin Hausa Da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa*. Kano: Triumph Publishers Ltd.

Yahaya, et al (1992) *Darussan Hausa 1-3;* Ibadan: University Press Ltd.

Zarruk; et al (1990) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa 1-3",* Ibadan: University Press Ltd.

**KASHI NA 3: {WA{{WARAN NAZARIN LITTAFIN WASAN KWAIKWAYO NA UWAR GULMA**

**GABATARWA**

A kashi na shida a cikin wannan fasalin, an nazarci abin da ake nufi da wasan kwaikwayo. Kuma an san abin da wasan kwaikwayo ya kunsa. A cikin wannan kashin za a nazarci ma}asudin da yakan zaburar da mutum, ya ]auki alkalaminsa da war}o}i domin ya bayyana wani abu da ke cikin ransa ga al'umma. An dai san cewa ruwa ba ya tsami banza. Baya ga haka, za a nazarci yadda marubuci ke isar da sa}onsa ga al'umma a cikin wannan nau'i na adabi wato wasan kwaikwayo.

yana da kyau a tuna cewa, a harsuna da yawa a duniya, akwai kalmomi da suke da ma'anoni dabam-daban, wato kalma ]aya tana iya samun ma'ana fiye da guda. ]angane da wannan batu, zai yi kyau a tuna cewa an sha jin kalmomi kamar su jigo, wanda ake amfani da shi a wajen noman rani ga kuma wata kalma kamar zubi wanda zai iya ]aukar ma' ana ta kamar a zuba wani abu a cikin ko a kan wani abu, ga kuma zubi irin na sa}a da kuma adashi sai kuma wata kalma wai ita tsari, wannan za ta iya ]aukar ma' anar yin abu kamar yaudara ko dubara a wajen tsarance, ko kuma daidaita wani abu ta yadda ake so.

A dai wannan kashin za a nazarci abubuwa ne kamar su jigo da zubi da tsari, amma ba irin yadda aka ]an yi tsokaci a kansu a sama ba. A nan, za a kalle su a adabance ne.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi, ana ganin za a iya:

i. Sanin abin da ake nufi da jigo a cikin adabi, musamman ma a wasan kwaikwayo;
ii. Sanin zubi a cikin wasan kwaikwayo
iii. Sanin tsari a cikin wasan kwaikwayo;
iv. Amsa dukkan tamyoyin da aka yi a }ar}ashin aikace-aikace da ke cikin wannan kashin.

**MATAKAN NAZARI**

1. Za a sake karanta wasan *Uwar Gulma*
2. A yi }o}arin fito da babban jigo da }ananan jigogin wasan *Uwar Gulma*
3. A }o}arta a san yadda zubin wasan *Uwar Gulma* yake
4. A san yadda aka tsara wasan *Uwar Gulma*
5. A karance dukkan wannan kashi

**SABABBIN KALMOMI**

Ga wasu kalmomi da kila ba a san ma'anoninsu a adabance ba:

i. Jigo: sa}on da sha'iri yake son ya isar ma makaranta ko masu saurare ko `yan kallo
ii. Zubi: yadda marubuci ya zuba wasan, wato kamar labarin, ta yadda }ilu ke jawo bau. A iya cewa daga }an}anen abu har a kai }ololuwa, sannan a warware shi.
iii. Tsari: yadda aka kasa wasan zuwa shiga da fitowa ko fitowa da kashi. In kuma a zube ne, akan bayyana shi ta babi-babi ne. In kuma a wa}a ne ta baituka ne.

**AIKI I**

Me aka fahimta da jigo a wasan kwaikwayo?

Ta yaya tsarin wasan kwaikwayo ya sha bamban da na zube?

**JIGO**

Jigo kamar yadda aka bayyana shi a karatun da ya gabata, yana nufin sa}on da marubuci yake }o}arin isarwa ga jama'a. A nazarin jigo, akwai babban jigo, akwai kuma }arami ko }anana, ko da yake wannan ya dangantaka da yadda marubucin ya tsara abin nasa ne.

A wasan *Uwar Gulma*, a iya cewa jigonsa shi ne garga]i irin na nuna illar auren dole. Marubucin ya yi }o}arin nuna wannan muguwar dabi`a ce ta yadda ya warware jigon nasa ne a hankali. Ya dai fara da nuna yadda Hayatu bai damu da matarsa, Halima ba, wato ya bar gida babu abinci, sai da ya dawo kuma ya fara tuhumarta da ta kawo masa abinci, kamar yadda ya bayyana a wasan:

> ***Kar dai ka ce man ka manta da cewa yau ba ka ba da ku]in cefane ba. ……Ana fa cewa auren bana babu ci babu sha, sai ]an karen kashi!***

Haka ]in ma ya da]a tabbata inda abokin shashancinsa ya fa]i cewa, Hayatu ba ya ba matarsa abinci, sai dai shan giya kawai.

> ***--- Ka ji maganar banza....................wai mai barin matarsa gida ba abinci, ya zo nan ya shanye giya da ku]insa har ya kira wani ]an iska!***

A iya cewa, kila saboda Hayatu ya kashe ku]i ne da yawa wajen auren Halima kuma ya tabbatar ba son sa take yi ba, shi ya sa yake wula}anta ta, ya bar ta babu abinci. Ko da yake an san mashaya giya banzaye ne, ai da yawansu an san ba haka suke barin gidajensu babu abinci ba. Wato Hayatu yana fanshe haushin ku]in da ya kashe ke nan kafin ya sami Halima.
Baya ga haka, shi dai wannan auren dole ne ya kai Halima ga halaka. An sha jin cewa yara mata da aka yi musu irin wannan auren sukan kashe kansu ta hanyoyi da yawa ko kuma su yi }o}arin yin hakan. Akwai wa]anda ke fa]awa rijiya, akwai masu }in cin abinci, akwai masu shan guba, akwai ma masu gudu su shiga uwa duniya. Ita dai Halima ba ta yi ko ]aya ba, amma da Al}ali ya tsandara ta ta koma gidan Hayatu, ta yarda ta koma, amma sai ta sha maganin da ba ta san kanshi ha, wanda shi ya halaka ta.
Baya ga babban jigon, akwai }ananan jigogi, wa]anda suke taimaka ma babban jigon.
A wasan *Uwar Gulma*, akwai hannunka mai sanda da aka yi wa masu shashancin irin na shan giya da karuwanci. Kuma irin zaluncin da Al}alai ke yi wajen ]anne gaskiya, idan sun kar~i toshiyar baki kuma irin sa~a wa addinin Musulunci da wasu attajirai ke yi ta bayar da bashi da ruwa irin yadda a sanadiyyar irin gulmace - gulmacen da kan fito daga bakunan wasu jama'a, tun ma ba irin su Uwar gulma ba.

**ZUBI**
Kamar yadda ya gabata, zubi a wasan kwaikwayo ya }unshi yadda marubuci ya fito da `yann wasansa ne da kuma irin }i}i-}a}a ]in da suke shiga a rayuwar yau-da-kullum. Wato, abubuwa kan fara faruwa ne kamar yadda marubuci ya tsara su a hankali, a hankali har su kai ga }ololuwar yadda ake sonsu, sannan, a hankali a warware su ko kuma su warware kansu. A wajen zubi `yann wasa na da matu}ar muhimmanci domin komi ya ta'allaka a kawunansu ne. Marubuci na iya za~ar babban tauraronsa ya nuna shi a matsayin salihi tin daga farko har }arshe, ga shi kuma da magabta wa}anda a }arshe suke shan kunya.

A wasan *Uwar Gulma*, an nuna mana `yann wasan kamar su Hayatu da Halima da Uwar Gulma da sauransu. Shi dai Hayatu, a iya cewa shi ne babban tauraro ya yi abin da ya ga dama kuma babu abin da ya faru da shi. Ai don mutuwar matarsa, ai ba wani abu ba ne balle ma ga mashayi, wanda in abin ya dame shi zai je ya sha ya manta da abin da ya faru. Kuma don mata, ai ana sake wata, sai me kuma? Halima ma tana da muhimmanci amma an }wareta, domin an yi mata auren dole ga ]an iska har ya kai ta ga halaka.
Bugu da }ari, ba a nuna mana irin fitinun da suka faru ga mutane kamar su Uban Ba'u mai bayar da bashi-da-ruwa ba, da Al}ali mai kar~ar rashawa tare da ]an kazaginsa wato yaron Al}ali Ga kuma su Mati da Dujal da Mama mai sayar da giya. Sannan ga Uwar Gulma wadda ta kitsa wa Halima abin da za ta yi. Duk a cikin wannan zubin za a ga cewa masu laifi da yawa, an kyale su, ba a nuna wani mugun abu ]aya ya same su ba. Haka dai marabucin ya za~i irin nasa zubin, ya dai yi ne don ya nuna jigonsa wato illar auren dole da abin da yaka iya haifarwa.

**TSARI**
An nuna tsari a matsayin irin yadda marubuci ka iya za~ar ko dai babi-babi ko shiga da fitowa ko fitowa da kashi kamar yadda suke a zube da wasan kwaikwayo ko kuma baituka ko ]angaye kamar yadda abin yake a rubutacciyar wa}a.
A wasan *Uwar Gulma*, Muhammed Sada ya yi amfani da kashe - kashe ne har guda shida. A cikin kasusuwan nan ne ya ]unke wasan ta hanyar nuna matsaloli dabam-daban da kuma yadda suka kwaranye a }arshe.
A kashi na farko an nuna mana gidan Hayatu da kuma yadda ya dawo aiki a yunwace, ga shi bai bar abin da za a ci a gidan ba. Wato dai matsalar zaman aure, tsakanin miji da mata da irin `yan rigingimun da kan faru.
A kashi na biyu kuwa, an nuna inda Hayatu ya fara saduda ne, ya je neman bashi - da - ruwa a gidan Uban Bau, domin ya wadata gidansa da abinci. Har ila yau, an nuna irin makiricin da kan }ullu a cikin al'umma a sanadiyar gulmace - gulmace.
A kashi na uku kuwa, ai Halima aka nuna a gidan uba da yadda uban ya so ya fafare ta ta koma gidan

mijinta.
A kashi na hu]u kuwa, ai an fito da Hayatu ne a mashaya, da dai kamar ya saduda zai koma gida bayan ya sami bashi-da ruwa. Amma, ai Shai]an ya riga ya same shi, sai ya karkata zuwa gidan giya, wai don kada Halima ta ce yana jin tsoronta. An kuma nuna yadda `yan giya kan kasance idan sun bugu wato, suna maye suna sumbatu.
A kashi na biyar kuwa, an nuna Hayatu da Halima ne a gaban Al}ali, sai dai Al}alin ya kar~i ku]in Hayatu, a saboda haka ya koma masa da matarsa Halima. Wa ya sani ma kila da ya ji sha'awarta da ya bayar da biko ne kawai don ya neme ta; ko kuma ma ya kashe auren gaba ]aya don ya biya wa kansa bu}ata.
A kashi na }arshe kuwa, an nuna yadda Halima ta koma gidan Hayatu ne a cikin ~acin rai. A saboda haka ne ta sha maganin barci da ya zarta }a'ida, wai don ta manta da abubuwan da ke damunta, ai sai kawai rai ya yi halinsa. Hayatu kuma ya nuna 'yar damuwarsa.

**AIKIN GIDA**

1. A sake karanta wasan *Uwar Gulma* tun daga farko har }arshe, Sannan a nemi wasan *Ai Ga irinta Nan* na Umaru [anjuma Katsina, shi ma a karanta shi tun daga farko har }arshe.
2. A Kwatanta jigon wasan *Uwar Gulma* da na *Ai Ga Irinta Nan.*
3. A dangantaka amsar da aka samu a tambaya ta biyu da zamantakewar Hausawa a yau.

**MANAZARTA**

Ahmed, M.M. et al (1999) - *Understanding Literature and Criticism.* Zaria: Supreme Printers

Ɗangambo, A. (1984) - *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Kano: Triumph Publishers Limited

Sada, M. (1968) - *Uwar Gulma.* Zaria: NNPC Ltd

Sani, M. Z. et al (1992) - *Darussan Hausa.* Ibadan: U.P.L Pk

**KASHI NA 4 : FITAR DA JIGON WA{A DA BAYANINTA**

**GABATARWA**

Duk da yake wa}ar yan*r Gagara* ba ta cika wasu }a'idoji na rubutacciyar wa}a ba, kamar rashin amsa-amo, amma jigonta yana da sau}in fahimta, tun da yake muna nazarin jigo ne a nan mun za~i wa}a mai sau}in sarrafawa. A wannan fasalin, za a nazarci jigon wa}ar *'Yar Gagara* ne tare da bayaninta.

Kamar dai yadda masana suka nuna akwai abubuwan da sukan sa mutum ya bayyana abin da ke damunsa a cikin halin rayuwa, komai da]in abin, komai ]acinsa. Irin wannan hali ne ya sanya A}ilu Aliyu ya bayyana ra'ayinsa ]angane da yadda yake kallon matar da ya kira da suna 'Yar Gagara.

]angane da wa}a, kamar yadda Muftah da Keston (1999) suka nuna, kusan babu wani rukunin adabi da ya damu da fayyace tsantsan gaskiyar abin da ya shafi rayuwa kamar wa}a, shi kuma wannan ~angaren, yana amfani da ta}aitattun kalmomi wa]anda aka tsara domin isar da sa}o.

Sau da yawa idan mutum yana sauraren wa}a za a ga yana karka]a kai, har wani lokaci ma yana lumshe idanu domin irin raujin muryar da ke da akwai. Wannan irin da]in da ke cikin raujin muryar nan, tana nisha]antarwa ne. Amma ba nisha]antarwar ce kawai take da muhimmanci ba, sa}on ne da ke ciki ake son lura da shi.

**MANUFA**

A lokacin da ka nazarci wannan kashin, lallai ya kamata ka iya:

1. Sanin jigon wa}ar '*Yar Gagara* ta A}ilu Aliyu;
2. {o}arin fitar da jigon kusan kowace irin rubutacciyar wa}ar Hausa;
3. Bin matakan da marubuci ya yi domin ya warware jigonsa;
4. Jin sha'awar wa}a ta fuskar nisha]antarwa da ta fuskar sa}o;
5. Haddace wasu baitoci na wa}ar *'Yar Gagara* don a nuna muhimmancinta a yau da kuma gwanancewa.

**MATAKAN NAZARI**

1. Wannan kashin, ya }unshi nazari ne kan jigon wa}ar *'Yar Gagara*, a saboda haka dole ne a mallaki littafin da ake kira *Fasaha A}iliya*, wanda a ciki ne wa}ar ta fito.
2. Za a so malami ya karance wa}ar sau da yawa, yana mai dangantaka rayuwar yanr Gagara da irin abin da ke faruwa a yau.
3. [alibi ya yi }o}arin fahimtar kalmomin da bai sani ba, ta yin amfani da }amus irin na P.C. Bargery ko kuma ta tambayar mutane da dama irin wa]annan kalmomin.

**NAZARIN SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Makwalla: | Wuri ne mai }unshe da ]andali |
| La}abi: | Sunan da ake }ara wa mutum kan na yannka |
| Ma-ja-ciki: | Maciji, sago |
| Makana: | Iyaka |
| Kasganya: | Sagarar tunkiya |
| Ruwaito: | Samo daga |
| Wofi: | Banza, mara amfani |
| Gadara: | Ta}ama, izgili |
| Kaushin: | Mugun ko rashin kyawun abu kamar hali |
| Wasan buya: | Aikin banza, aikin assha wanda ba a son wasu su gani |

**JIGON WA{AR *'YAR GAGARA***

Kamar dai yadda aka yi bayani a baya kan ko mene ne jigo, an bayyana shi da cewa, shi ne babban sa}on da marubuci yake son isarwa ga masu sauraro ko makaranta. Jigon wa}ar *'Yar Gagara* dai ba wani abu ba ne da ya wuce GARGADI. An dai nuna illar karuwanci da kuma ita karuwar kanta.

A wa}ar, marubucin ya bu]e wa}arsa ne da *Basmala* kamar dai yadda akasarin mawa}an Hausa suke yi. Daga nan, sai ya fara nuna inda ya sanya gaba wato ya ce:

"*Zan magana bisa jakar birni* " A nan ya nuna mana yadda ya ]auki karuwa, bai ]auke ta a cikakkiyar mutum ba saboda halinta na banza, shi ya sa ma ya kira ta jakar birni.

Daga nan, sai ya ci gaba da warwarar jigonsa yana fa]in halin karuwa irin na sabon Mahalicci da yin }arya da }in yin aure da ha]a fitina idan ta kusanci jama'a.
Marubucin ya ci gaba da nuna yanr gagara a mai neman ta nuna ba ta da laifi, tana }o}arin ta nuna duk halin da ta shiga akan sa ta ne ba wai yin ta ba ne, kamar yadda ya nuna:

Mun rubu sai aka ban wani shi ma, Har ya zarce sa'an tsohona;
**Na gaza ci, ba sha, ba barci, An ki raba mu, gudowa niy yi.**
**Wannan ce ta saka ni a ]andi, Ba jaraba ba, da neman kur]i.**

Har ila yau, ya nuna mana irin kisisinar karuwa ta ladabin }arya don ta cuci jama'a:
**Mai ladabin wofi, 'yar gagara mai sha'awar a yi ba dai-dai ba.**
Marubucin ya ci gaba da muna ta a matsayar wadda ba ta son a yi mata zancen aure, sai a bar ta da wasan banza.
Idan ma sanya tufa ta yi, daga ganinta za ka gane domin zanenta ba ya kai wa can kasa, kamar yadda marubucin ya nuna.

**Zanen da ta ka rufa kai 'yar Gagara, Bai fi kwata uku ma fa]i ba.**
**Kai ko sai ]in ma wata rana, sai ta make shi kamar wani jauje.**

Daga }arshe, marubucin ya nuna ta a matsayar wadda za ta iya ru]in mutum ta aure shi, shi kuma jiki na rawa saboda kisisinarta, bayan ]an lokaci ka]an kuma ta fita abinta ta koma ]andi har kafin a sake samun wani wawan.

**Wato, ni aure a wurina, Ba abu ne mawuyaci can ba;**
**yannzu a yau haka in na ga dama, Gobe i war haka nai wani sabo.**

**AIKI NA I**

1. Yaya ka ga jerin tunanin marubucin wa}ar 'Yar Gagara ]angane da yadda ya bayyana ta?
2. An ce banza ba ta kai zomo kasuwa, yaya ka ga wannan batu ]angane da wa}ar yanr Gagara, ta A}ilu Aliyu?

**TA{AITAWA**

- An nazarci abin da ake nufi da jigo
- An san wasu kalmomi na dabam
- Jigon wa}ar 'Yar Gagara shi ne "gargadi"
- An nuna halin karuwai
- An umurci jama'a da su guje su domin neman tsira

**MANAZARTA**

Aliyu, A. (1976) - *Fasaha Akiliya,* Zaria: NNPC Ltd
Ahmed, M.M. et al (1991) - *Understanding Literature and Criticism,* Zaria: Supreme Printers Ltd.
Yaro, I. Y. etal (1992) - *Darussan Hausa,* Ibadan: University Press Pk.

## KASHI NA 5: {WA{{WARAN NAZARIN LITTAFIN ZUBE

**GABATARWA**
A nan, za mu yi bayani a kan tsarin littafin zube. Wannan yana nufin rubutun da aka tsara shi, ba wa}a ba, ba kuma wasan kwaikwayo ba. Misalin littattafan zube su ne, littafin *Magana Jari Ce*, da littafin *Gandoki*, da kuma littafin *Shaihu Umar*, da dai sauransu.

**MANUFA**
Manufar wannan kashi ita ce, a koyar da ]alibi yadda zai yi nazarin tsarin littafin zube a cikin adabin Hausa. A }arshen wannan nazari, ana sa ran ]alibi zai iya fahimtar ginshi}an abubuwa na nazarin tsarin littafin zube a cikin Hausa.

**MATAKAN WANNAN NAZARI**
Kai ]alibi sai ka samo littafin zube domin a bayyana maka yadda za ka fito da tsarin littafin zube.

**SABABBIN KALMOMI**
Babi - babi - farkon darasi
Bai - ]aya - gaba ]aya

**TSARIN LITTAFIN ZUBE**
Tsarin littafin zube sun kasu kashi biyu:

i. Littafin da aka wallafa shi da kanu masu yawa, watau, babi-babi, kamar *Magana Jari Ce*, na Abubakar Imam.
ii. Littafin da aka yi shi bai ]aya daga farko har }arshe, kamar littafin *Shaihu Umar* na Abubakar Tafawa |alewa.
iii. Wasu marubuta a lokacin da suke rubutunsu sukan yi kwan-gaba- kwan-baya wato, su jinkirta wani muhimmin abu wanda ya kamata su fara fa]arsa tun daga farko. Ko kuma fara fa]ar abin da ya kamata su jinkirta.
iv. Wasu rukunin marubuta kan tsara zaren tunaninsu dalla - dalla ba tare da gabatar da abin da ya kamata su jinkirta ba, ko su jinkirta abin da ya kamata su fara gabatarwa ba.

To, idan littafi mai babi - babi ne, sai ]alibi ya karanta babi ]aya, sai ya tabbatar ya gama shi, sa'an nan ya ci gaba da wani babin.
A lokacin da yake karatunsa zai kula da muhimman abubuwa kamar haka:

i. Wurin da wani abu ya faru, misal in kasuwa, ko gida. ko gona ko ]andali, ko dai wani abu mai kama da wannan.
ii. Wani abu da ya zo a cikin labarin kamar ki]a. ko dariya ko kuka da sauransu.
iii. Kula da duk wani abu da mashahurin mutum ya yi a cikin labarin idan littafin mai bi ]aya ne, to sai ]alibi ya tabbata cewa ya fahimci littafin tun daga farkonsa har }arshensa. Kuma ya bi duk wa]ancan hanyoyi da aka ambata a baya. Wa]annan su ne a ta}aice hanyoyin da ya kamata ]alibi ya bi a nazarinsa na zubi da tsarin littafin zube ]angane da tsarinsa.

**AIKI I**

1. Me ake nufi da littafin zube a cikin adabin Hausa?
2. Ba da ma’anar wa]annan kalmomi kamar yadda ka fahimce su a tsarin littattafan zube.
   i. Babi – babi
   ii. Bi - ]aya

**AIKIN GIDA**

1. Yi bayani a kan kasha-kashen tsarin littattafan zube.
2. Me ka fahimta da kwan-gaba- kwan-baya a cikin tsarin rubutun zube?
3. Kawo muhimman abubuwa biyu a ta}aice wa]anda ya kamata ]alibi ya kula da su a nazarinsa na karatun zube.
4. Rubuta sunayen littattafai biyu na zube; ]aya an rubuta shi ne da tsarin Babi-babi, [Ayann kuma an rubuta shi a tsarin bi - ]aya.

**TA{AITAWA**

Tsarin rubutun zube da aka fi so shi ne, marubuci ya tsara tunaninsa ba tare da ya yi kwan-gaba- kwan-baya ba. Idan ]alibi na son ya fahimci tsarin littafin zube to, sai ya kula da wa]annan abubuwa:

1. A wurin da duk wani abu ya faru ya kula da shi;
2. Wani aiki da aka yi a cikin labarin;
3. Kiyaye duk wani abu da tauraro/taurari suka aikata.

**MANAZARTA**


Yahaya I. Y. da ]angambb .A. (1986) *Jagoran Nazarin Hausa*, Zaria: NNPC.

Zarruk, Rabi`u M, da Wasu, (1990) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa*, Littati Na Uku. Ibadan: UPL Nigeria.

**KASHI NA 6: FITAR DA JIGON LITTAFIN ZUBE TARE DA BAYANIN SALON SARRAFA HARSHE**

**GABATARWA**
A wannan nazari na yau, za mu ba da }arfi ne a kan bayanin jigon littafin zube tare da bayanin salon sarrafa harshe da ake amfani da su a cikin littattafan zube.
Jigo shi ne, sa}on da marubucin littafi yake so ya isar zuwa ga jama'a shi marubucin littafin zube ya bi domin isar da sa}onsa ga Jama'a.

**MANUFA**
Manufar wannan kashi ita ce a sanar da ]alibi yadda zai yi nazarin fitar da jigo da salo a cikin littafin zube na Hausa.

**MATAKAN NAZARI**
[alibi sai ka samo littafin zube wato, littafin da aka shimfida shi ratata wanda rubutunsa ya bambanta da na littafin wa}a ko na wasan kwaikwayo. Misalin littafin zube shi ne littafin ***Magana Jari Ce*** da ***Ruwan Bagaja*** da ***Iliya [an Mai {arfi*** da dai sauransu.
Ka sami ]aya daga cikin wa]annan littattafai ko masu kama da irin su sai ka yi }o}ari ka karanta shi filla - filla ta hanyar kulawa da salon da marubucin littafin ya yi amfani da shi a cikin littafin. Alal misali, irin mutane da ya saka a cikin littafin da ayyukan da ya rarraba musu da wurare na musamman da aka aiwatar da wasu ayyuka na musamman. Hatta ma da kayayyakin da suka yi amfani da su a cikin labarin. Ta haka zai sa ka fahimci bayanin da za a yi maka domin samun damar fitar da jigo da salo a cikin littafin zube.

**SABABB1N 'KALMOMI**
Jigo - sa}on marubuci
Salon sarrafa harshe - dabarun jawo hankali
Tauraro - duk wanda ke cikin littafin

**FITAR DA JIGO**
Idan ]alibi ya karanta littafinsa, sai ya yi tunani ko yana iya fitar da wa]annan abubuwan:
i. Jigon littafin, wato, sa}on da marubucin littafin yake so ya isar zuwa ga jama' a.
ii Salon da yake }unshe a cikin littafin wato, wasu dabaru da mawallafin littafin ya yi amfani da su domin isar da sa}onsa.

To, idan har ]alibi bai gano jigo ba, da salo a lokacin da yake karatun littatinsa, to, ga }arin bayanin fitar da jigo a cikin littafin zube na Hausa:
1. Wani lokaci mai karatu zai fahimci jigon littafin da yake karatu tun daga sunan da marubucin littafin ya bai wa littafinsa. Misali, littafi mai taken: ***l]an So Cuta Ne*** ka ga wannan taken ya yi tsokaci da abin da mai littafin yake so ya fa]awa jama'a.
2. Amma a wani lokacin abin ba ya kasancewa a hakan, sai dai bayan ka }are karatun littafin kaf ]insa sannan ka tsunduma cikin tunanin mene ne jigon littafin? Misali littafin ***Gandoki*** ko na ***Ruwan Bagaja.*** Irin wa]annan littattafai da aka yi wa take da sunayen mutane ko wasu abubuwa daban, yana da wuya tun daga farkon littafin ka iya hasashen jigonsa.
3. Hanya ta uku da mai nazari ke iya fito da jigo ita ce, darasin da aka samu ya fito ta hanyar babban tauraro. Misali littafin ***Ruwan Bagaja*** ta kan Imam ne aka san cewa ba abin da ba ya yiwuwa sai dai a sha wahalar yinsa.

**AIKI I**
1. Bayyana ma'anar wa]annan kalmomi:
2. Taurararo, sa}on marubuci.

**SALO**
Salo yana nufin hanyar da marubucin littafi ya bi har ya kai ga isar da sa}on littafinsa, wato dabarun jawo hankali, da sarrafa harshen Hausa misali, amfani da kalmomi cikin hikima, gina jimloli, da amfani da

azancin zance amfani da kalmomin aro amfani da tsofaffin kalmomi da sauransu.
Haka kuma ]alibi ya kula cewa salo kan }unshi wa]ansu abubuwa da za a }ara ba ka haske a kansu kamar haka:

i. Za~en taurari wato, mutanen da za su fito a cikin littafi.
ii. Wuraren da za a ambata ko kuma aka yi wa]ansu ayyuka a cikinsu kamar dokar daji, gulbi, Sahara, kasuwa, ]andali da dai sauran su.
iii. Ayyukan da za a saka wa wa]annan taurari wa]anda suka aiwatar a cikin littafin.
iv. Kayayyakin da za su yi amfani da su a cikin littafin gwargwadon zamanin da aka shirya littafin, wato idan a da ne a fannin abin hawa za a yi amfani ne da dawaki da ra}uma da alfadarai. Ta fannin makamai kuwa za a yi amfani da makaman gargajiya irinsu takubba, kwari da baka da masu da dai sauransu.

Idan kuwa wannan zamanin ne, za ka ji marubucin na amfani da motoci da jiragen sama da abubuwan hawa. Makamai kuwa zai yi amfani ne da bindigogi da dai sauransu. Wa]annan su ne abubuwan da ya kamata kai ]alibi ka kula da su a nazarinka.

**AIKIN GIDA**

1. Ba da kalma guda da ta dace da dabarun sarrafa harshe.
2. Bayyana kalma ]aya tak da ta dace da sa}on marubuci
3. Kawo sunayen littattafai uku na zube.

**TA{AITAWA**

[alibi sai ka kula da wa]annan abubuwa da za a fa]akar da kai a kansu idan ka tashi fitar da jigo da salo a cikin littafin zube. Su ne:

1. **Jigo:** wato, sa}on mai littafi, wani lokaci za ka iya harsashen jigon littafi tun daga sunansa. Amma a wani lokaci ko ka karance littafin, to, da }yar ne za ka iya hasashensa.
2. **Salo:** hanyoyin da marubuci ya bi don isar da sa}onsa ga jama'a. Za a kula da abubuwa don fito da sato kamar za~en taurari, wuraren da aka yi amfani da su a liftafin, Ayyukan da taurari suka aiwatar. Hatta da kayayyakin da suka yi amfani da su a cikin littafin duk abin kula ne.

**MANAZARTA**

Yahaya, I.Y. and ]angambo A., (1986) *Jagoran Nazarin Hausa*, Zaria: NNPC
Zarruk, R.M (1990) Sabuwar *Hanyar Nazarin Hausa, Littafi na uku*, Ibadan: UPL.

## KASHI NA 7: NAZARIN RUBUTATTUN WA{O{I

### GABATARWA

Wa}a: Ita ce tsararriyar maganar hikima, da ta }unshi sa}o cikin za~a~~un kalmomi da aka auna, domin maganar ta reru, ba fa]uwa kurum ba.

A idon Hausawa, wa}a iri biyu ce, ]angane da tarihinta da zubinta, da kuma yadda ake aiwatar da ita. Wa}a ta farko ita ce wadda ake kira wa}ar ba}a. Ta biyu itace ake kira rubutacciyar wa}a. Amma bayanin da za a yi maka a nan a kan rubutacciyar wa}a ne. Don haka, za mu ta}aita bayani a kanta. A cikin bayanin da za mu yi, za mu ambaci rabe-rabenta da sigoginta da sauran abubuwan da suka bambanta da sauran takwarorinta a cikin adabin zamani, wato, rubutun zube da na wasan kwaikwayo.

### MANUFA

Manufarmu a nan ita ce, mu kawo maka bayanin da zai taimaka maka wajen gane:

- i. ma'anar wa}a;
- ii. yadda sigoginta suke;
- iii. ire - irren wa}ar baka.

### MATAKAN NAZARI

Abin kulawa a nan ga mai karatu shi ne ka kiyaye ma'anar da muka ba ka. Saboda haka saninta shi ne zai taimaka maka wajen bambanta zunzurutun magana da wa}a. Ban da wannan kuma, ka lura da sigogin da ake samu a cikinta. Daga bisani kuma, ka kula da rabe-rabenta, domin tantancewa da abin da kowane kashi ke koyarwa.

### SABABBIN KALMOMI

| | | |
|---|---|---|
| ]ango | - | she]ara ko layin wa}a |
| Baiti | - | jerin ]angogi da ke ha]uwa su yi baiti. |
| Amsa amo ko }afiya | - | sauti ko kalmar }arshe na ]angogin da suka ha]u suka yi baiti |
| Karir | - | tsarin ga~o~in wa}a. |

### SIGOGIN WA{A

Idan ka yi la'akari da ma'anar da aka ba ka ta wa}a a sama a cikin gabatarwa, za ka fahimci wa}a tana da abubuwan da za a iya kira ginshi}an wa}a. Wa]annan ginshi}an su ne magana da kalmomi da tsarinsu da za~en kalmomin da rerawa da sa}o da salo. A ta}aice wa}a tana }unshe ne da abubuwa kamar haka:

1. **Za~en kalmomi:** wato wa}a magana ce mai bu}atar za~i musamman na kalmomi da aka gina ta da su ta hanyar ]ango, baiti da kuma kari.
2. **Rerarawa:** tana nufin furta magana cikin murya mai tafiya mai rausaya
3. **Jigo:** shi ne bayani ko manufar da wa}a ta kunsa
4. **Salo** yana nufin abubuwa da dama da suka shafi mu'amala da harshe da ma'anoninsu. Wato, yadda mawa}i ya sassar}a kalmomi cikin kalmomin. Har ila yau,salo ya ha]a yadda mawa}i ya shimfi]a tunaninsa cikin wa}a. .-
5. **Hikima** wa}a maganar hikima ce. A nan, ana nufin abu biyu. Abu na farko shi ne wanda ya shafi salo. Wato hikima wadda ta shafi saka kalmomi su zama magana. Hikima ita ce fa]ar magana mai fayyace gaskiya ko nuni zuwa ga rayuwa mai nagarta.

### AIKI I

1. Me ya bambanta wa}a da sauran takwarorinta wato wasan kwaikwayo da rubutun zube?

### RABE-RABEN RUBUTACCIYAR WA{A

Sun rabu zuwa rukunoni da yawa. Daga cikin muhimman rabe - raben akwai:

- (i) wa}o}in wa'azi
- (ii) wa}o}in madahu
- (iii) wa}o}in ilimi
- (iv) wa}o}in siyasa
- (v) wa}o}in soyayya

**Bayani: Zuwa gare ka ]alibi sai ka lura:**

1 **Wa}o}in Wa'azi:** wa}o}i ne ke }o}arin hani ko horo ga jama`a. Misali a nan ita ce wa}ar *Tabban Ha}i}an* ta Shehu Usmanu

2. **Wa}o}in Madahu:** su ne wa]anda aka rubuta saboda bege da yabon Annabi Muhammadu S.A.W., kamar wa}ar: *Ma'amare ta Isan Kware.*

3. **Wa}o}in Ilimi: s**u ne wa}o}in da ke ilmantarwa zuwa ga jama'a. Kamar wa}ar Garba Gwandu, *Bulaliya,* wadda ya yabi ilmi.

4. **Wa}o}in Siyasa:** su ne wa]anda aka rubuta domin bayyana siyasar zamani ko yabo siyasa da shugabaninta, ana kuma suka ga abokan hamayya. Kamar *wa}ar N.P.C.* ta Bello Gi]a]awa da *wa}ar P. R. P.* ta Awwalu Bungu]u.

5. **Wa}o}in Soyayya:** wa}o}i ne da suka }unshi bayyana bege da so, galibi daga namiji zuwa ga mace, misali, a nan *wa}ar Mairi* ta Alkali Haliru Wurno.

**AIKI**

1. Me ya bambanta wa}o}in madahu da wa}o}in soyayya?

**AIKIN GIDA**

1. Mene ne ma'anar wa}a a ta}aice?
2. Me ake nufi da za~en kalmomi a cikin rubutacciyar wa}ar Hausa?
3. Me ya bambanta wa}ar ilimi da ta siyasa?
4. Fa]i sigogi biyu da wa}a take da su

**TA{AITAWA**

Wannan darasi ya bayyana wa ]alibi abubuwan da ya kamata ya kula da su a nazarin rubutacciyar wa}a. Wa]annan abubuwa sun ha]a da ma'anar ita kanta wa}a da sigoginta da rabe-rabenta.

**MANAZARTA:**

Yahaya, A. B. (1997) *Jigon Nazarin Wa}a.* Kaduna: FISBAS

Gusau, S. M. (1998) *Jagorar Nazarin Wa}ar Baka.* Kaduna: FISBAS.

**KASHI NA 8: {WA{{WARAN NAZARIN WA{A**

**GABATARWA**
A darussan can baya, mun ga bayani kan adabi da rabe-rabensa. Rubutattun wa}o}i ná daga cikin kashin adabin zamani. Har ila yau, kamar yadda ya gabata an nuna akwai hanyoyi ko abubuwa da ake la'akari da su wajen nazarin rubutattun wa}o}i wa]anda sun ha]a da jigo, da zubi da tsari da kuma salo da sarrafa harshe na marubuci.
A wannan kashi, wa]annan abubuwa guda uku da ke sama, su ne za a fito da su fili, a ga yadda suke in an zo fi]ar wa}a. Littafin *Fasaha A}iliya* na A}ilu Aliyu ne zai zama jagora. To Bisimillah.

**MANUFA:**
Manufar wannan darasi ita ce, ka fahimci wa]annan abubuwa:

1. Muhimman abubuwan lura wajen nazarin wa}a; Yadda ake nazarin wa}ar *Duniya Rawar yanmmata.*

**MATAKAN NAZARI**

i. Bin bayanan da aka yi wajen nazarin wa}ar a hankali.
ii. Kwatanta misalan baitocin da hujjojin da ke tare da su.
iii Yin amfani da samfurin nazarin wa}ar zuwa ga wata wa}ar daban.

**SABABBIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| Fasaha A}iliya | - | fasaha ko hikimar A}ilu |
| {war biyar | - | wa}a mai baiti biyar - biyar |
| {afiya (Amsa-Amo) | - | sautin gabar }arshe a kowane layi |
| Jerin sar}e | - | samun makusanciyar dangantakaka tsakanin kalmomi iri daban-daban a baiti. |
| Kamantawa | - | kwatanta abubuwa biyu ko fiye |

**LITTAFIN *FASAHA A{ILIYA***
*Fasaha A}iliya* ta A}ilu Aliyu, littafi ne da ya }unshi rubutattun wa}o}i da dama masu magana a kan mabambantan manufa don garga]i da wayar da kan jama'a. Daga cikin wa}o}in littafin akwai: *Hausa Mai Ban Haushi*, *Kadaura Babbar Inuwa, Duniya Rawar 'Yammata*, *yanr Gagara. [an gata* da sauransu. A wannan kashi za mu ]auki wa}ar, *Duniya Rawar `yan Mata* ne mu yi sharhi a kai.

**JIGO**
Sa}on mawa}in ga jama'a shi ne, garga]i don a lura da duniya, a kuma yi tattalin lahira.
"Mu mutane ' yan Adam, Sai mu tashi ga]an-ga]an,
Tattalin wancan gida, Duk mu yi shi a nan gidan,
Na fa]a mana gaskiya.

Kar mu je mu sukurkuce, kun ga in muka marmace,
Ba ayyukan an ~ace, Dole za a yi dakace,
An yi banta a duniya

A wurare da dama, ya da]a bayyana jigon nasa ta ba jama'a shawara kan lahira da garga]i a kan duniya wanda ya bayyana siffofinta da halayenta marasa kyau. Za a iya ganinsu a baitoci na 10, 22, 23, 86, 98 da sauransu.

**WARWARAR JIGO**

| | | |
|---|---|---|
| Baiti | 1 -4: | Addu`ar bu]ewa da gabatarwa |
| | 5 - 6: | Jigo |
| | 7 - 9: | Neman gafara wurin Allah |
| | 10 - 21: | Shawarwari don tattalin Lahira |
| | 22 - 59: | Garga]i game da duniya siffofinta, halayenta da makircinta |
| | 60- 65: | Misalai na shugabannin da suka gabata |

66 - 78: {arin bayanin siffofin duniya da shawaran a guje mata
79 - 85: {arin bayanin halayenta na ~atar da jama' a
86 - 90: Yadda duniya kan yi da masoyinta.
91 - 97: {ara bayanin siffofin duniya
98 - 121: Yadda ya kamata a ]auki duniya
122 - 136: Kammalawa - Addu'a da }ara yin tir da duniya

**ZUBI DA TSARI**

Wa}ar *Duniya Rawar `yann Mata* ta }unshi baitoci 136, kuma mai }war biyar ce, sannan kamar ma fi yawan wa}o}in Hausa tana da amsa – amo, don kowane baiti na }arewa da –*ya.* Wa]ansu wa}o}in Hausa suna da amsa - amon - *wa*. Amsa- amo shi ya fi bambanta wa}a rubutacciya da ta baka. A gaba ]aya za a iya kasa wa}ar zuwa gida uku:

a. Gabatarwa - baiti 1 - 4
b. Gundarin wa}ar - baiti 5 - 121
c. Kammalawa - baiti - 122 - 136.

Ɗangane da tsarin ]angogin, mawakin kan yi gangara, inda zai fara magana a ]ango ]aya .bai }arewa sai a na gaba, sai dai babu sa~i - zarce wanda kan faru tsakanin baiti da baiti. Za a iya ganin gangara a baitoci na 52, 94, 116, 125, 133 da saurausu. Misali baiti na 116 ya ce:

"In ya nuna bulaguro shi nufinsa ya gangaro ne, a ]akin daduro ga iyali ya baro, can gida na halaliya".

[angogin wa}ar wa]anda suka gina baitocin duk matsakaita ne. Sannan kamar mafi yawan wa}o}in Hausa, an bu]e da addu'a kuma an rufe da ita.

**AIKI I**

1. Mene sakon wa}ar *Duniya Rawar `yan Mata*?
2. Yi sharhi kan zubi da tsarin *Duniya Rawar `yan mata*.

**AMSA-AMO**

Kamar yadda aka ambata a baya, amsa-amo shi ne mafi muhimmanci daga cikin abubuwan da suka bambanta wa}o}i rubutattu da na baka. Amsa-amo shi ne yadda layukan kowane baiti na wa}a ke }arewa da sauti in ]aya. Idan muka sake duba baiti na 24 kamar haka.

Tsohuwa mai takuna;
Mai baki mai zanzana;
Mai yawan shan majina;
Ga ta nan ba ]anyana;
Ta yi muni duniya.

Za mu ga cewa layuka hu]u na farko duk suna }arewa ne da - *na*. Wannan shi ake kira amsa - amo ko kafiya. Shi amsa - amo in biyu ne. Akwai na ciki akwai kuma na waje. Idan muka dubi baiti na sama layuka hu]u duk suna }arewa ne da ***--na*** amma na biyar yana }arewa da Amsa - amon layuka hu]u ]in nan shi ake kira amsa-amon ciki. Shi kuma na layi na }arshe shi ake kira amsa-amon waje. Amsa-amon ciki yakan canza daga baiti zuwa baiti amma shi amsa-amon waje ba ya canzawa har }arshen wa}a. Don haka a wannan wa}a, amsa-amon waje yana nan - *ya* har baiti na }arshe.

**SALO DA SARRAFA HARSHE**

A gaba ]aya, salon wa}ar mai sau}i ne domin da an karanta za a fahimci sa}on da yake ]auke da shi, Sannan salon na da armashi kasancewar akwai yawan kamance da aka yi don wa}ar ta yi da]i. A mafi yawan wurare, mawa}in na kamanta duniya da wata mace karuwa, wadda wai sunanta Hindu Balaraba, wadda ba ta tausaya wa duk wanda ya so ta. yana cewa:
"Tsohuwa mai takuna, mai baki mai zanzana,
Mai yawan shan majina, Ga ta nan ba ]angana,
sai yawon son zuciya". Baiti 24 "Mai 'ido ba tozali, babu kyau ba kyaun hali, can na ganta a ]andali, Tun da ta rasa hankali, Ta yi muni duniya,
Aure - auren `yan maza, Ba da]ewa, mar maza, sai ta ce musu sun gaza, mai jiki ya kamar guza,

Tai kama da hawainiya".

Wannan irin hikima da mawa}in ya yi, na bayyana siffofi da halayen duniya ya sa wa}ar ta yi armashi sosai.

Mawa}in, ya yi amfani da manya-manyan kalmomi za~a~~u da jerin sar}e, yakan kuma yi ragi ko }ari a kalma da karya }a`idojin nahawu don kawai wa}ar ta hau kan kari kar~a~~e. Har ila yau, a wa}ar ha kamar sauran wa}o}in nasa ba, ba ya yawan tambaya, sannan ba yawan aron kalmomi daga Larabci ko Turanci sai dai `yan wa]anda ba a rasa ba.

Jerin sar}e ya fito a baiti na 38 da 39.

"An sadakin naka]an, an bukin ta je gidan, ya zatar mata Aba]an, za su zauna sarma]an, Kaico, angon Duniya!

Kwanci tashi tana gidan, sai ta toshi ga]an-ga]an, ta gaya mishi mai gidan, ka gani haka yau sa]an, ba na auren, na }iya" Manya, manyan kalmomi za~a~~u na nan baitoci da yawa, misali a baiti na 87:

> "Sal ta hau ta daddaga, Duk cikinsa ta nannaga, sai ta bi shi ta tsattsaga, sun wuce a }ididdigu, cuce-cucen duniya".

**AIKI II**

1. Yi bayanin salon sarrafa harshen wa}ar *Duniya Rawar `yan Mata*. {awata amsarka da misalai
2. Mene ne hikimar amfani da jerin sarke a wa}a?

**AIKIN GIDA:**

1. Wane dalili ya sa A}ilu Aliyu ya kira wannan wa}ar `*Duniya Rawar ' yann Mata*?
2. Me ya bambanta zubi da tsari da sato da sarrafa harshe a wa}a.

**TA{AITAWA**

Wannan kashi, ya yi tsokaci ne a kan wa}ar *Duniya* na A}ilu Aiiyu wadda za ta zama fitila wajen nazarin sauran wa}o}cin da ke cikin littafin. Yayin fe]e wa}ar an kalli muhimman abubuwa guda uku:

a. jigo
b. zubi da tsari
c. salo da sarafa harshe

**MANAZARTA**


Aliyu A. *Fasaha A}iliya* Zaria: NNPC Ltd

Gala]anci M.K.M da wasu (1993) *Hausa Don {ananan Makarantun Sakandire 3.* Longman Nig.

Yahaya I. I da wasu (1992) *Darussanan Hausa Don Manyan Makarantuna Sakandire.* Ibadan: University Press Pk.

## KASHI NA 9: NAZARIN LITTAFIN WASAN KWAIKWAYO

### GABATARWA
A nan kuma, za mu yi wa ]alibi bayani ne a kan yadda zai yi nazarin littafin wasan kwaikwayo. Wasan kwaikwayo shi ne wato aikata wani abu don kwatanta yadda ake yinsa, don a gani a gane kyaunsa da muninsa saboda a }ara fahimtar rayuwa da matsalolinta. To, da jin sunan wannan kashi, ya bambanta da litattafan da aka wallafa a sigar wa}a ko kuma rubutun zube. Misalan littattafan da aka rubuta a cikin wasan kwaikwayo su ne irin su, littafin *Wasan Marafa* na Alhaji Abubakar Tunau, *Zamanin Nan Namu* na A. Shu`aibu Ma}arfi da kuma littafin *Uwar Gulma* na A. Mohd. Sada da dai sauransu.

### MANUFA
Manufar wannan kashi ita ce, a sanar da ]alibi yadda zai yi nazarin littafin wasan kwaikwayo a cikin adabin Hausa. A }arshe ana fatar ]alibi zai sami mabu]an muhimman abubuwa da ake yin nazarin littafin wasan kwaikwayo na zamani da su a Hausa. Ya kuma gane hanyar da zai iya fitowa da jigon wasa da salonsa da kuma zubinsa tare da tsarinsa.

### MATAKAN NAZARI
Tun farko, kai ]alibi sai ka karanta littafin wasan da aka ayyana maka shi saboda wannan karatu. Bayan ka karanta shi tsaf tare da la`akari da salon da marubucin wasan ya yi amfani da shi a wasansa. Da kuma yadda ya shirya `yann wasansa da halayyarsu da suturarsu da wuraren da suka yi amfani da su a cikin wasan da dai sauransu.

### SABABBIN KALMOMI
| | |
|---|---|
| Kashi-kashi: | sashe-sashe |
| Fitowa-fitowa: | sake dawowa kan ]andamali |
| Ɗandamali: | ke~a~~en wuri mai ]an tudu inda za a ri}a aiwatar da wasan kwaikwayo |

### MABU[AN NAZARIN LITTAFIN WASAN KWAIKWAYO
Lallai ne ]alibi ya tsaya a tsanaki ya karanta littafinsa na wasan kwaikwayo domin ya fahimce shi sosai da sosai sannan ya kula da wa]annan abubuwa kamar haka:

1. Jigon littafinsa , wato, manufar mai littafi a kan wannan wasa.
2. Salo. wato, hanyoyi da dabarun da mawallafin ya bi domin ya isar da sa}onsa zuwa ga jama'a
3 Halayen `yann wasan littafin, wato, mutanen da aka yi amfani da su wajen aiwatar da wannan wasan.
4. Zubi da tsarin littafin wasan. A nan, ana nufin yadda aka tsara wasan kashi - kashi ko fitowa-fitowa.

Bayanin da za a }ara maka domin ka sami jagora wajen gano muhimman abubuwan da muka ambata maka a sama su ne:

i. **Jigo:** Ana rubuta wasan kwaikwayo ne da manufofi iri-iri, misali shi ne bayyana wani mugun abu ga jama'a. A nan, a maimakon a ce maka abu kaza ba shi da kyau, sai a sa shi a wasan kwaikwayo a rubuce. Misalin wannan shi ne wasan *Zamanin Nan Namu* na A. Shu`aibu Ma}arfi, wanda yake nuna sharrin tallace-tallacen `yann mata, wanda a }arshe yarinya take zuwa gidan miji ba ta san bihim ba ga addini ko ga ilimin boko. Wannan shi ne ka]an daga cikin misalin fitar da jigo daga littafin wasan kwaikwayo.

ii. **Salo:** Salo shi ne irin hanyar da kowane marubuci yake bi wajen sadar da sa}on da yake nufin sadarwa. Zai yi amfani ne da dabarun sarrafa harshen Hausa da na jawo hankali irin su karin magana, salon magana da dai sauransu. Kuma wajibi ne ka kula da wa]annan abubuwa don }ara samun haske ga nazarin fitar da salo a littafin wasan kwaikwayo. Su ne:

iii. **Taurari:** Taurari su ne mutanen da suka fito a cikin littafin wasan kwaikwayo. A nan ana bu}atar ]alibi ya kula da halayensu da siffofinsu, da sauran abubuwa da suka aikata a cikin littafin ta yadda zai taimaka masa ya gane matsayinsu da muhimmancinsu a cikin wasan.

iv. **Zubi da tsarin wasa:** Haka kuma ana so ka kula da yadda aka tsara wannan wasa, shin ta hanyar fitowa-fitowa ce ko kuwa kashi-kashi ce. Saboda wannan yana da muhimmanci

}warai ga ]alibi ]angane da yadda aka shirya wasan.

**AIKI I**

1. Me ake nufi da fitowa-fitowa a cikin wasan kwaikwayo?
2. Kawo sunayen littattafai biyu na wasan kwaikwayo da ka sani tare da sunayen wa]anda suka wallafa su.

**AIKIN GIDA**

1. Kawo abubuwa uku da ake son a kula da su ga tauraron littafin wasan kwaikwayo.
2. Yi ta}aitaccen bayani ]angane da zubi da tsarin wasan kwaikwayo.
3. Saboda wace irin manufa ce ake rubuta wasan kwaikwayo?
4. Mene ne ma'anar wasan kwaikwayo a cikin adabin Hausa?

**TA{AITAWA**

Akwai abubuwa hu]u da ya kamanta ]alibi ya kula da su a lokacin da ya zo nazarin littafin wasan kwaikwayo:

i. Jigon littafin, wato, manufar mai littafin a wannan wasan.
ii. Salon da marubuci ya bi domin isar da sa}onsa zuwa ga jama'a.
iii. Siffofi da halayyen mutanen da aka yi amfani da su wajen aiwatar da wannan wasa wato taurari.
iv. Zubi da tsarin wannan wasa ya kasance hanyoyin aiwatar da wasan da wuraren da aka yi amfani da su da dai sauransu.

**MANAZARTA**

Zarruk, Rabiu M. da wasu (1990) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa*, Littafi na Uku, Ibadan: University Press Limited, Nigeria.

## KASHI NA 10: BITA

### GABATARWA
A wannan fasalin, an yi bayani ne kan ma'anar rubutaccen adabi, sannan an yi bayanin Rabe - rabensa. Bayan bayanin ma' ana da rabe raben adabin, an yi bayani kan ma' anar Rubutattar wa}a da Rabe rabenta da yadda ake nazarin wa}ar, wato, ta duba jigonta, da zubi da tsarinta, da kuma salon sarrafa harshenta.
Daganan kuma, sai aka yi bayani kan ma' anar rubuttacen zube, da salon nazarinsa, wato jigo da zubin labari da kuma salon sarrafa harshen rubutattan labarai.
Daga karshe an yi bayani ne kan ma'anar wasan kwaikkwayo da nazarin wasu littattafan wasan kwaikwayo. Gabaɗaya a wannan fasalin an yi nazari ne kan Rubutaccen Adabi da ya shafi wa}a rubutatta da rubutun zube da kuma rubutaccen wasan kwaikwayo.

### MANUFA
A wannan bita za a duba Rubutaccen adabi ne gabaɗaya. Kuma ana sa ran in ka gama karanta wannan bitar za ka fahinci abin da ake nufi da rubutacccn Adabi da rabc - rabcnsa da jigogin rabe-rabe da tsari da zubinsu da kuma salon sarrafa harshe na dukkanin rabe raben -harshe na rubutaccen Adabi.

### MATAKAN NAZAR1
Ma so ka karanta wannan Fasali da wannan kashin da kyau. Yin haka ne zai sa ka fahimei fasalin da kyau. Bayan haka, ana so a yi kokari ka amsa aikin da aka bayar a kowane kashi. Idan ka sami matsala a wata tambaya saika tuntubi wani daga cikin `yan' uwanka ]alibai ko kuma ka tambayi wani malami da zai iya yi maka cikakken bayani.

### MATANI
A wannan Fasali an yi cikakken nazari ne kan rubutaccen Adabi gabaɗaya.
An fara ne da ba da ma'anar rubutaccen Adabin da cewa, fasaha cc da take a rubuce. Shi rubutun kuma ya soma zuwa }asarHausa ne bayan zuwan addinin musulunci. Ta yin amfani da alamomin larabci ne aka kagi rubutun ajami wanda da shi ne aka fara yin rubufun Adabi na wa}a tun kafin jihadin Shehu Usman ]an Fodiyo, amma a lokacin jihadin na Usman ]an Fodiyo ne wa}a ta bunkasa, ta sami ranar yin shanya.
Zuwan Rubutun boko bayan Zuwan Turawa }asar Hausa a 1903, ya zo da sauran rabe - raben na Adabi. Su sauran Rabe-raben su ne rubutun Zube, wato rubuta Labarai da tatsunniyoyi da almara da Sauransu, da kuma Rubutun wasan kwaikwayo N,vanda shi ya zo ne bayan da aka sami `yan boko da dama a }asar Hausa.
Bayan gabatar da Adabin Hausa ne, sai aka yi bayani kan jigoginsu. An yi bayani kan jigogin Rubutattun wakoki ne da jigogin Labarun zube da kuma jigogin wasan kwaikwayo.

A karshe, an karkare da takaltaccen bayani kan rassan adabin.

**AIKI I**
1. Mene ne rubutaccen adabi?
2. Da wane salon rubutu ne aka fara rubuta wa}a Hqusa?
3. Yaya kake ganin zubi da tsarin wa}ar Arewa Jumhuriya ko mulukiya ta sa'adu zungur?
4. Me ake nufi da littafin zube a cikin adabin Hausa ?
5. Mene ne ma'anar wasan kwaikwayo?

### AIKIN GIDA
1. Kawo muhimman rabe-raben rubutaccen adabin Hausa.
2. dangantaka fafutukar shari'a da marubucin "wa}ar 'yar gagara" ya yi da abin,da ke faruwa a yau.
3. Me ya sa ake rubuta wasan kwaikwayo?
4. Kawo sunayen littafai uku na zube.
5. Mene ne ma'anar wa}a a takaice?

### MANAZARTA
A duba dukkan littattafan da aka ambata a kashi na ɗaya zuwa kashi na tara na wannan fasalin.

**FASALI NA 7: ZAMAN HAUSAWA**

**KASHI NA 1: TSARIN FASALIN IYALI GABATARWA**

**GABATARWA**

Sanin kowa ne a da babu wani ]an Adam a bayan }asa, aka wayi gari Allah (S.W.T) cikin ikonsa ya halicci mutum na farko, Adamu. Sannan na biyu, Hauwa'u, wa]anda suka hayayyafa suka haifar da al'umma. Daga cikin al'umma ne, ake samun iyali abin da za mu yi nazarinsa a wannan kashi.

**MANUFA**

Manufar wannan kashi ita ce, fahimtar da ]alibi:

i. Ma'anar Iyali;
ii. Tsarin fasalin Iyalin Bahaushe;
iii. Muhimmancin Iyali ga al'umma.

**MATAKAN NAZARI**

Don nazarin wannan kashi, yana da muhimmanci mutum ya:

i. Karanta bayanan a hankali;
ii. Tuna yadda shi kansa ya taso;
iii. Tattauna bayanan da ]alibai;
iv. Amsa ayyuka da tambayoyin da ke biye.

**SABABBIN KALMOMI**

Iyali - Wannan ya }unshi dukkan mutanen da ke zaune a gida a }ar}ashin shugabancin maigida.

Gandu - Zama }ar}ashin maigida.

**MA'ANAR IYALI**

lyali kalma ce da ta }unshi dukkan mutanen da ke zaune a gida, a }ar}ashin shugabancin maigida. Bisa al'ada, iyalin Bahaushe ba kurum sun }unshi matansa da 'ya`yansa ba ne. A'a, sun ha]a, har ma da duk wani wanda yake a }ar}ashin ikonsa, ko sun hada dangantakaka ta jini kamar `yan `uwansa, ko kuma ba su ha]a ba, kamar agola da sauran yaran gida. Don haka, tsarin iyalin Bahaushe tsari ne mai ya]o. Shi mai shugabancin gida shi ne maigida, sauran }ananan masu gida suna }ar}ashinsa watau suna GANDU har kafin su kawo }arfi.

lyali shi ne ginshi}in da aka kafa al' ummar Hausa a kansa. Daga iyali ne jama'a kan faru har su zama ]an rukuni daga nan kuma su ha]u su yi Unguwa. Wa]annan Unguwanni suke ha]uwa su kafa }auye, daga nan, sai gari ya tashi in kuma garuruwa sun ha]u sai a sami }asa.

In aka yi nazari sosai, za a ga tsarin iyali shi ya haifar da ]angi da ma}wabtaka, da `yann`uwantaka, da abokantaka da zumunci. Duk da cinkoson da tsarin iyalin Bahaushe ke da

akwai cikakken tsari na matsayin kowanne da dangantakakarsa da sauran jama'a da hakkinsa a kansu da nasu hakkin a kansa.

**ZAMAN HAUSAWA AIKI I**

1. Lissafta mutanen da suke }aashin maigidan da kake.
2. Mene ne dangantakakarka da mutanen da ka lissafto a sama

**TSARIN FASALIN IYALI**

Tushen samuwar iyali shi ne aure, wanda kan haifar da zuri'a ko ]angi. Daga nan ne akan sami iyaye da yayye, da }anne da `yan`uwa.

i. **Iyaye**: Iyaye sun }unshi kakanni da uba da uwa da yayye da }annen uba da na uwa, kai har ma da abokai ko aminen iyaye.
ii. **Yayye**: Wannan ya }unshi wa]anda suka girmi mutum a gida, ya Allah maza ne ko mata, matu}ar ba su suka haifi mutum ba, kuma ba su a cikin rukunin iyaye.
iii. **{anne**: wannan ya }unshi wa]anda mutum ya girma a gida, ya Allah maza ne ko mata, matu}ar

ba su a cikin rukunin iyaye.

iv. **`Yan`uwa**: Akwai wa]anda saboda wata dangantakaka ta jini ko ta wani abu ya sa suka kasance }ar}ashin maigida.

**MUHIMMANCIN IYALI**

**Tarbiyya:** Hanya ce da Hausawa kan bi wajen koya wa yaransu kyawawan abubuwa don su tashi su girma da halayen kirki.

**Asali**: Kasancewar mutum ya san tushensa, zai sa ya kasance mai alfahari da tin}aho da jin da]i, akasin wanda ba ya da asali misali wato shege.

**Tsaro:** Ta tsarin iyali mutum kan ji yana da kariya ta musamman, don haka zai kwantar da hankalin saya yi abin da zai amfani rayuwarsa.

**Hukuma:** A tsarin iyali kowa hukuma ne a kan na }asansa don haka yana iya horar da shi da sa shi ya yi duk wani abu da yake dai-dai.

**Ha]in kai:** Taimaka wa juna domin samun sau}in rayuwa kamar wajen aikin gayya.

**AIKI II**

1. Lissafto rukunan jama'ar da suka haifar da fasalin iyali
2. Su wane ne ake kira iyayen mutum?

**AIKIN GIDA**

1. Tsarin iyali na Bahaushe, tsari ne mai ya]o. Tattauna.
2. Fa]i tsarin iyalin gidan Bahaushe Yi bayanin biyu daga cikin muhimmancin iyali ga rayuwar Bahaushe.

**TA{AITAWA**

A wannan kashi mun tattauna ne a kan ma'anar iyali da tsarin fasalin iyalin wanda ya }unshi irin mutanen da suka ha]u suka gina iyali. Sannan da muhimmancin iyali a rayuwa.

**MANAZARTA**

Umar, M.B. (1980). *dangantakakar Adabin Baka da Al`adun Hausawa.* Kano: Shonugha Commercial Press.

Yahaya, I. Y. da wasu (1992). *Darussan Hausa Domin Manyan Makarantun Sakandire.* Littafi na 3. Ibadan: University Press Ltd.

**KASHI NA 2: RUKUNAN IYALI DA MATSAYINSU**

**GABATARWA**
Kashi na farko ya yi bayani ne a kan tsarin fasalin iyali, wannan kashin zai ci gaba ne, ya rarraba mana iyalin Bahaushe zuwa wasu rukunai dangane da shekaru, da halin rayuwa, sannan ya nusar da mu matsayi ko gudunmuwar kowannensu.

**MANUFA**
Manufar wannan darasi ita ce, ta fahimfar da ]alibai yadda al'ummar Hausawa ta kasu aji - aji danganeda shekaru da irin ayyuka ko ]abi`u na kowane aji.

**MATAKAN NAZARI**
Wajen nazarin wannan kashi za a:
a) Karanta bayanin a hankali;
b) Yi tunanin ko haka ya faru ga mai karatu ko waninsa;
c) Tattaunawa da sauran ]alibai;
d) Amsa ayyuka da dukkan tambayoyi.

**SABABBIN KALMOMI**
Rukuni: Rarrabuwar abu zuwa kashi-kashi

**RUKUNAN IYAL1 DA MATSAYINSU**
Kamar yadda aka nuna a kashi na farko, iyali shi ne ainihin ginshi}in al'ummar Hausawa, wanda aka nuna ya }unshi iyaye, da yayye da }annai da kuma sauran `yan'uwa.
To, su wa]annan rukunin mutane da aka lissafto za a iya karkasa su gida-gida
(a). danganeda yawan shekarunsu da irin matsayinsu a cikin al'umma
(b). danganeda halin rayuwa. Abin lura shi ne kowane rukuni yana da dangantakaka mai kyau da ]an`uwansu, sannan a kan ba kowanne ha}}insa da ya kamace shi. .

**RUKUNAN SHEKARU**
**Yara -** Wannan lokacin kan fara ne da zaran an haihu, ya zuwa shiga makaranta. Akan kira wannan lokaci, lokacin yarinta. Wanda kan fara tun daga haihuwa har zuwa shekara sha-]aya zuwa sha-biyu.
Danganeda matsayin kuwa, yara kan taimaka wa iyayensu a gida ko gona, ko a wurin sana'a, har ma a wurin aikin gayya.
**Matasa -** Daga ajin yara sai na matasa wanda ya fara tun daga kimanin shekaru sha-uku har ya zuwa talatin da tara. A wannan lokacin ne balaga da }arfi da jarunta kan zo wa mutum**.** Aikace - aikacensu tamkar na yara ne, sai dai nasu ya ]ara nesa ba kusa ba, kuma a wannan lokacin ne akan yi samartaka har a yi aure. Daga baya a fita gandu.
**Dattawa -** Wannan shi ne rukuni na }arshe wanda ya }unshi `yan shekaru kimanin sittin zuwa sama. Mutane na wannan rukuni sun tsufa wasunsu ma sai da taimakon sanda suke tafiya, sannan har akan rasa wasu sassan jiki kamar ha}ora ko ido da sauransu. Tsofaffin nan na taka rawa sosai wajen daidaita lamura a cikin al'umma, sukan ]auki matsayin al}alai da na masu ba da shawara.

**AIKI I**
1. Yi tunanin mahaifinka ko wanda kake hannunsa. A wane rukuni za ka sa shi? Kawo dalili.
2. A wane rukuni za ka sa kanka? Mece ce hujjarka?

**RUKUNAN HALIN RAYUWA**
**1.** **`Yan koli:** Wannan ya }unshi masu }unban susa wa]anda suka ha]a da manyan masu ku]i, manyan sarakuna da manyan ma'aikatan gwamnati. Suna taimakawa wajen kafa kamfanoni da taimaka wa na }asa da su.
**2.** **`Yan tsakiya:** Wannan ~angaren ya }unshi matsakaitan `yan kasuwa da ma'aikata da kuma wa]anda suka yi fice a sana'o'insu, amma kuma ba su shiga rukunin sama ba suna taimaka wa na sama da na }asa don abubuwa su tafi sosai a cikin al'umma.

**3.** **`Yan }asa -** Wannan kashi ya }unshi duk wani wanda ba shi a cikin biyun sama misali: {ananan masu sana'a da }ananan ma'aikata da sauran marasa hali. Talakawa na taimakawa wajen aikace-,aikacen }arfi ga masu ku]i da gwamnati.

**AIKI II**

1. A wane ~angare za ka sanya shugaban {aramar Hukumarku? Mene ne dalilinka?
2. Wane dalilin ne ya sa aka sa masu sarauta cikin ~angaren masu hali?

**AIKIN GIDA**

1. Yi bayanin lokacin samartaka.
2. Wa]anne dalilai za su sa ka kira mutum dattijo?
3. Yi bayanin ]aya daga cikin rukunan halin rayuwa?

**TA{AITAWA**

Wannan kashin ya yi nazarin rukunin iyali ne da kuma matsayinsu a inda ya raba iyali gida biyu:

i. Dangane da shekaru: yara, matasa, manya da tsofaffi.
ii. Dangane da halin rayuwa: `yan koli, yann tsakiya da `yan }asa.

**MANAZARTA**


Umar, M.B. (J980). D*angantakar Adabin Baka da Al'adun Hausawa.* Kano: Shonuga Commercial Press.

Yahaya, I. Y. da wasu (1902). *Darrusan Hausa Don Manyan Makaratun Sakandire. Littafi na 3* Ibadan: University Press Pk.

Zarruk, M, R. da wasu (1990). *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.*Ibadan: University press.

**KASHI NA 3: TSARIN SARAUTA**

**GABATARWA**

A darussan baya, mun tattauna a kan tsarin iyali wanda muka nuna shi ne ginshi}in al`umma. Muka kuma, nuna iyalin nan kan haifar da gida, gidajen kuma su haifar da unguwa,unguwanni su haifar da gari har zuwa ga }asa. A duk wa]annan wurare, akan sami shugabanni wa]anda ke jagorancin al'amurran wuraren da suke. Wannan jagoranci shi ya haifar da kanun nazarinmu a wannan kashi wato tsarin sarauta.

**MANUFA**

A }arshen darasin, ]alibai za su san:

- Wane ne sarki?
- Kashe-kashen sarauta;
- Yadda tsarin sarauta yake.

**MATAKAN NAZARI**

Hanyar nazarin wannan kashi ya ha]a da:

(i) dangantaka darasin kashin da ya gabata (Tsarin Iyali) da wannan darasin.
(ii) Karanta kashin a hankali don fahimtar abin da ya }unsa.
(iii) Danganta bayanin da aka yi da abin da makaranci ya sani.
(iv) Amsa ayyuka da tambayoyin da ke biye.

**SABABBIN KALMOMI**

Sarauta - Mulki ko shugabanci
Masarauta - {asar da sarki ke mulki

**ASALI DA MA'ANAR SARAUTA**

Masana tarihi sun ce, an fara sarauta tun daga zamanin 'ya'yan Adamu na farko, ba don komi ba sai don ha]a kan mutane da kare maras }arfi daga mai }arfi, da kuma, kiyaye martabar ]an Adam.
A da can, akan ba da ikon shugabanci ne ga shugabannin sana'o'in gargajiya ko kuma masu jarumtaka da }warewa ta fuskar ya}i. Daga baya sai shugabancin ya koma hannun wasu mutane na musamman, sannan aka ]aukaka matsayin gado a sha'anin mulki.
Dangane da ma'ana. sarauta na nufin mulki, wanda ya danganci ri}on ragamar al`amuran jama'a wanda ya ha]a da bai wa jama'ar nan umurni da yi musu jagora bisa tafarkin da suka amincewa. da yannke musu hukunci da sulhuntawa tsakaninsu da dai sauransu.

**AIKI I**

1. Wane dalili ya haifar da sarauta?
2. Me ake nufi da sarauta?

**KASHE-KASHEN SARAUTA**

a. Sarautar sarkin yannka: Sarki ne wanda yake da }asa da kuma jama'a a }ar}ashinsa wa]anda yake wa shugabanci. Misali: Sarkin Zazzau, Sarkin Daura da Sarkin Kano.
b. Sarautar masu sana'a - Wannan ya }unshi shugabanci ne na mutane wa]anda suke da sana'a iri ]aya. Misali: Sarkin Magina da Sarkin Aska.

**NA[A SARKI**

Mafi yawan sarautu ana gadon su ne. Wasu kuwa ana samun su saboda `yan `uwantaka da sarki. Wasu ma bayin sarki ne, ya na]a su, kasancewar wata bajinta da suka nuna a fagen ya}i, su kuma `ya`yansu da jikokinsu za su gada daga gare su, a yi ta tafiya a haka.
Galibi, ba a na]a mutum sarki sai wanda ya gada daga mahaifinsa, ko shi ma sai masu za~en sarki sun yi tsokaci a kan cancantarsa bisa sauran `yan`uwansa, ta la'akari da hankalinsa, da iliminsa, da shekarunsa, da adalcinsa da ha}urinsa da sauransu.

**AIKI II**

1. Yi bayanin kashe - kashen sarauta
2. Yaya ake za~en sarki a garinku?

**TSARIN SARAUTA**

Tsarin sarautar gargajiya tsari ne na mataki-mataki ko hawa-hawa. Sarki shi ne ke }oli, gaba da kowa, shi ne shugaba da iko a kan }asa baki ]ayanta. Hakimai wa]anda ke ri}e da wasu garuruwa ko suke ba da shawara, su ne ke biye da Sarki. A }ar}ashin Hakimai akwai Dagatai wa]anda ke jagorancin wasu unguwanni. Daga Dagatai sai masu Unguwanni wa]anda ke jagorancin unguwannin daban-daban. A can }asa }ar}ashin masu Unguwanni akwai masu gida manya da }anana.

Tun daga Sarki har zuwa masu Unguwanni, masu sarauta ne, sauran jama'a kuwa komin ku]in mutum da iliminsa talaka ne, yana }ar}ashin mai sarauta yana bin umurni.

A fada, Sarakuna ke za~ar masu taimaka musu wajen tafiyar da mulkin }asarsu. Wasu mu}aman 'ya`yan Sarki ake ba, kamar Turaki, da Ciroma, wasu kuwa jarumai ake ba, kamar sarkin Ya}i da Jarmai, bayan wasu masu ilimi ake ba, kamar Waziri da Wali, sannan wasu a kan ba mashahuran jama'a ne kamar Madaki da Dallatu.

Wa]ansu Hakiman akan ba su ri}on garuruwa, wasu kuwa `yan majalisar sarki ne masu ba da shawara, sannan akwai masu gudanar da wasu ayyuka na Sarki, bayan wasu suna ri}e da sarautar ne kawai.

**GUDANAR DA MASARAUTA**

Kasancewar }asar Sarki na da fa]i, sai ya na]a Hakimai don su wakilce shi daga cikin `yan`yansa ko wasu aminai nasa. Kowane Hakimi yana da Dagatai. Sannan su kuma suna da rnasu Unguwanni, wa]anda sun san duk jama'a musamman magidanta da ke Unguwannin nasu. Wannan tsari ya sa shugabanci a da yake da tsarki da inganci akasin yanzu.

**AIKI III**

1. Kawo ma'anar wa]annan kalmomi:
   a. Sarki
   b. Sarauta
   c. Masarauta
2. Kawo ayyukan da Sarki ke ma jama'arsa.

**AIKIN GIDA**

1. Ta yaya sarakuna ke tafiyar da mulkinsu?
2. Wa]anne irin ayyuka masu Unguwanni suke yi?
3. Me ya bambanta Sarkin Zazzau da Sarkin Magina?
4. Su wa suke wakiltar Sarki a sauran garuruwan da ba ya nan?

**TA{AITAWA**

dangane da ta}aitawa, wannan kashi ya yi tsokaci ne kan: Asali da ma'ana da kashe - kashen sarauta, yadda tsarin sarauta yake da kuma yadda ake gu]anar da masarauta.

**MANAZARTA**

Alhassan H. da wasu (1982). *Zaman Hausawa.* Ibadan University Press Ltd

Yahaya, I. Y. (1992). *Darussan Hausa Don Makarantun Sakandire.* Littafi na Uku. Ibadan University Press Ltd

**KASHI NA 4: RA'AYIN BAHAUSHE A KAN ISKOKI**

**GABATARWA**

Iskoki wasu halittu ne na ~oye Wa]anda ba cika ganinsu a fili ha. Iskoki na nufin aljannu. A wannan kashi za a yi nazarin irin yadda ra'ayin Bahaushe yake dangane da iskoki. Wannan yana nufin mu ga yadda Bahaushe ya amince da iskoki da kuma yadda yake ta'ammali da su a cikin rayuwarsa ta yau di kullutn.

MANUFA

Manufar wannan kashi ita ce ta nuna yadda zai kasance ka fahimci wa]annan abubuwa dangane da Iskoki bayan kammala wannan darasi. Abubuwan da suka kamata ya kasance su ne:

1.abin da ake kira da iskoki;

2.ire-iren Iskoki a ra'ayin Bahaushe;

3.yadda ra'ayin Bahaushe yake game da ta'ammali da Iskoki. 1.

ne yadda ma'a mala take tsakanin mutane da iskoki a ra'ayin Bahaushe.

sa

da

**SABABBIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| Iskoki | = | aljannu |
| su Buzurwa | | akuya mai gashi tsaitsaye |
| Bale | | ba}ar akuya |

**MATAN I**

**RA'AYIN BAHAUSHE A KAN ISKOK1 KAF1N ZUWAN ADDINI**

1. Tun kafin zuwan addini }asar Hausa Bahaushe ya san da zaman Iskoki (aljannu). A wannan lokacin, Bahaushe ya ]auki Iskoki wasu halittu masu }arfin iya tafiyar da komai yadda suke so. A wannan lokacin Bahaushe ya ]auki Iskoki a matsayin abin bauta. Wannan shi ya sa yake yi masu yanke-yanke da kiyace-kiyace wani na dabbobi kamar buzurwa da ba}ar akuya.

Bahaushe ya yarda cewa Iskoki na da }arfin da za su iya cutar da mutum ko su taimaka masa.

Wannan shi ya sa mabiya ke yin taka-tsantsan wajen aikata abin da ke iya fusata Iskoki kamar yin fitsari a wuraren da ake zaton Iskoki na zama. Haka kuma wannan amincewar da Bahaushe ya yi ta cewa Iskoki na iya cutarwa da taimakawa, shi ya sa suke ha}uri da abubuwan da `yan bori ke aikatawa a lokacin da suke a cikin borin. Wato lokacin da lskansu suka zo gare· su.

Kana iya fahimtar ra'ayin Hausawa a kan Iskoki ka fin zuwan addini kamar haka:

Bahaushe ya amince da wanzuwar Iskoki;

i . Ya amince suna iya taimakawa·suna kuma iya cutarwa

Ya amince suna da }arfin aikata duk wani abu da mutum ba ya iya ko tunanin yin sa;.

iv. Ya ]auke su abin tsoro }warai da gaske;

v. Ya ]auke su har a matsayin abin bauta;

**AIKI I**

1.Idan Bahaushe ya ce lskoki, me yake nufi?

2.Ta wace hanya ce Bahaushe yake bauta wa Iskoki?

**RA'AYIN HAUSAWA A KAN ISKOKI BAYAN ZUWAN ADDINI**

Kamar yadda ka gani, Bahaushe ya ]auki Iskoki a matsayin abin bauta kafin zuwan addini a }asar Hausa. Bayan addini ya zo }asar Hausa kuma Hausawa suka karbe shi sai ra'ayinsu a kan Iskoki ya canza. Da yake addini ma ya yarda da wanzuwar Iskoki, sai ya zama wannan ra'ayi na Bahaushe bai canza ba domin shi kansa addini ya tabbatar da haka. Duk da haka Musulunci ya fitar da Bahaushe daga }angin bauta wa Iskoki da kuma imanin da suke na cewa iskoki sun fi komi karfin iko.

Haka kuma bayan zuwan addini, sai Hausawa suka canza ra'ayin daga amincewar da suka yi ta cewa Iskoki na iya taimakawa ko cutarwa suka koma ga ra'ayin cewa Allah ne kawai yake taimakawa ko cutarwa.

Haka kuma Hausawa sun canza ra'ayinsu daga kasancewar Iskoki abin tsoro fiye da komai, suka koma ga

ra'ayin cewa Allah shi ne abin tsoro fiye da komai, kuma yana da ikon kare mutum daga gare su.
Duk da haka wasu daga cikin Hausawa sun doge bisa ga ra'ayinsu na farko. Wannan ya sa suka ci gaba da tu`ammalli da Iskoki kamar yadda ake yi kafin zuwan addini.
A halin yannzu ra'ayin Bahaushe a kan Iskoki ya kasu kashi biyu akwai masu ra'ayi irin na Maguzanci da kuma masu ra'ayi irin na Musulunci a game da Iskokin.

**AIKI II**

1. Wane kangi ne Musulunci ya kubutar da Bahaushe daga gare shi dangane da Iskoki?
2. Ko Hausawa sun ci gaba da tsoron Iskoki bayan zuwan addini?

**AIKIN GIDA**

1. Ko Bahaushe ya amince da akwai Iskoki?
2. Ko Bahaushe ya yarda da cewa Iskoki na iya cutar da mutum?
3. Yaya Bahaushe ya ]auki Iskoki bayann zuwan addini dangane da taimako?
4. A halin yanzu ra'ayi nawa suke ga Bahaushe dangane da Iskoki?

**TA{AITAWA**

A wannan kashi an dubi yadda ra'ayin Bahaushe yake a kan Iskoki. Tun kafin zuwan addinin da kuma bayan zuwan addini dangane da haka ne za ka fahimci cewa Bahaushe yana da ra'ayinsa a kan Iskoki kafin zuwan addini kamar haka:

• Ya amince da wanzuwar Iskoki da iya taimakawa musamman da }arfin aikatawa da kuma bauta zuwa gare su.

Bayan zuwan addini sai ra'ayin Hausawa ya canza ya koma kamar haka:

i. Bahaushe ya yarda da wanzuwar Iskoki.
ii. Allah yake iya taimakawa ko cutarwa amma ba Iskoki ba.
iii. Allah kawai yake da }arfin aikata komai amma ba Iskoki ba.
iv. Allah ne kawai abin bautawa.
v. Allah ne kawai abin tsoro.

Duk da haka ka lura wasu Hausawan sun tsaya a bisa ra'ayinsu na farko game da aljannu, suka ci gaba da ma'amala da su kamar yadda ake yi kafin zuwan addini.

**MANAZARTA**

Bunza, A. M. (2006) *Gadon Fe]e Al`ada.* Lagos: Tiwal Nigeria Ltd
Kofoworola, Z.O. & Lateef, Y. (1987) *Hausa Performing Arts and Music* Lagos:Dept of Culture, Federal Ministry of Information.

## KASHI NA 5: AL`ADUN HAUSAWA

**GABATARWA**
A wannan kashi za mu yi nazarin al'adun Hausawa. Al'adun kuwa sun ha]a da duk abubuwan da ke tsakanin haihuwa, suna, yaye, kaciya, aure, sana'a, wasanni da mutuwa.
**MANUFA**
A wannan kashi zaka yi wa al'adar Hausawa nazari mai ]an fa]i. Hakan ya zama dole domin yawan abubuwan da za a yi nazarinsu ya }umshi al'adun Hausawa dangane da haihuwa da sauran matakan rayuwa har zuwa mutuwa.
**MATAKAN NAZAR1**
1. Karanta kashin baki ]aya a hankali kana mai lura da muhimman zantukan da ke ciki.
2. Yi }o}arin amsa tamboyoyin da ke ciki da kanka.
3. Duba amsoshin da ke a bayan littafin nan.

**AL'ADUN HAUSAWA**
Al'ada na nufin duk wani abu wanda al'umma ta yarda da shi kuma jama'arta ke amfani da shi wajen harkokin yau da kullum. Wannan ya shafi abubuwa da yawa. Wato, daga haihuwa ne zuwa mutuwa. Idan mutum ya yi nazarin al'adun Hausawa zai ga cewa daga haihuwa zuwa mutuwa akwai abubuwa kamar haka:

- suna
- kaciya
- aure
- sana'o'i
- wasanni
- mutuwa (jana' iza)

Saboda haka al'ada ta }unshi duk rayuwar al'umma. Idan muka yi nazarin wa]annan abubuwa da ke sama za mu ga cewa ana iya rubuta littattafai a kansu. Don haka mu sai dai mu yi tsambare, wato mu ]an tsakura mu yi ta}aitaccen bayani.
Misali, suna shi ne al'adar saka wa ]an da aka haifa suna wanda addinin Musulunci ya kawo. Suna shi ke bambanta mutane wani¸ lokaci. Amma ¸kuma yakan zo ]aya da wani lokaci. Hausawa sukan ba da suna dangane da ranar haihuwa ko lokacin haihuwa ko kuma wani gamon katar a lokacin haihuwar. Shi ya sa za ka ji wani¸ sunansa [antani, wata Laraba, wani kuma Ba}o. Akwai kuma sunayen Musulunci. Suna na da ma'ana ga addinin Musulunci. Wato kamar Al-Amin, amintancce ke nan ko Sabir mai ha}uri da ire-irensu.
Kaciya ita ce yanke lo~a wato fatar da ta rufe kan azzakarin namiji. Wannan shi ma addinin Musulunci ya kawo shi. Akan yi kaciya bayan yaro namiji ya kai shekara bakwai kuma akan bai wa yaron da aka yi wa kaciya (shayi) cikakkiyar lura wajen ba da abinci mai gina jiki kamar nama. Wannan shi ma kamar wani lokaci ne na biki domin akan ha]a yara da yawa da suka kai shekara bakwai a yi musu gaba ]aya. Don haka ga al'adar Bahaushe ana lura da shekaru na shiga wani rukunin rayuwa. Hausawa kan ce kaciya na }ara wa namiji lafiya ta hanyar }arfin gaba da kuma tsaron lafiya daga cuta mai iya tsayawa cikin fatar gaban namiji in ba a yanke ba.
Aure shi ma wani ~angare ne na rayuwar Hausawa. Hausawa na yin aure idan suka kai wasu shekaru. Namiji na aure daga shekara goma-sha-takwas (18) wato lokacin da ya balaga. Balaga ita ce kaiwa munzalin jin da]i idan namiji ya sadu da mace. Ita kuwa mace ta kan yi aure daga shekara goma-sha-uku (13) wato lokacin da nononta ya bayyana. Akan yi ]aurin aure, wato halatta wa mace da namiji junansu. Addinin Musulunci ya kawo nashi tsari.
Abubuwan da ke tabbatar da aure sun ha]a da biyan sadaki, da kammalar shedu, da tabbatar halin ciyarwa, da wurin zama, da halin tufatarwa, da sauransu. Wannan ya nuna cewa ba don son zuciya kawai ake yin aure ba. Dole a bi wasu }a'idoji.

**AIKI I**
Kawo }a'idojin aure guda uku.
Hausawa na da sana'o'i iri-iri. Akwai sana'o'i kamar noma da gini da kasuwanci, aikin fata (dukanci, jima da sauransu) rini, }ira, ginin tukwane, su sa}a, saran icce, da sauransu.
Hausawa sun kasance mutane masu haza}a wajen neman abin da za su ciyar da kansu ta hanayar sana'a.

Ta fuskar wasanni, Hausawa na da ire-iren wasanni da dama. Akwai wa]anda na maza ne, akwai na mata. Misali wasannin kokawa da dambe da langa da sauransu na maza ne. Mata kuma na da wasanni kamar su ga]a da tashe, na mata kamar wasan "Mairama da Daudu". Amfanin wasa shi ne, motsa jiki, idan ya shafi motsa jikin. Ko kuma wasan wasa }wa}walwa kamar kacici-kacici. Duk ire-iren wa]annan abubuwa sun taimaka wajen bun}asar al'adun Hausawa.
Haka kuma wasa na taimakawa wajen bai wa matasa }warin jiki domin aikin ko-ta-kwana. Wato ko da ya}i ya same su suna iya kare kansu da al'ummarsu.
Mutuwa ita ce rasuwa. Wato, mutum da ke raye ya zan babu. Idan mutum ya zan babu ke nan bai iya duk wani abu da yake iyawa yana raye. Wato babu numfashi, babu jin wari ko }anshi, babu gani da ido, babu magana, ba cin abinci, babu motsa jiki kowane iri. Wannan hali shi ake kira mutuwa ko rasuwa ko kuma a ce mutum ya zan babu. Idan wannan hali ya sami mutum sai zancen jana'iza, wato bizne gawar. Addinin Musulunci ya tanadi yadda ake yi wa gawa kafin bizne ta. Na farko mai wankan gawa zai yi mata wasu abubuwa kamar rufe hanci da kunne da auduga da sa turare da rufa likkafani. Bayan wa]annan, sai jana'iza, wato biznewa cikin kabari. Akan yi addu'o'i bayan an bizne gawa, wato gangar jikin mutumin da ya mutu. Bayan wannan sai a watse. Ana yin sadaka bayan kwanaki uku da kuma bakwai. Sai kuma addu'ar arba'in. Wasu kan yi sadaka duk shekara domin mamaci ya sadu da rahamar Ubangijinsa.

**AIKI II**

Yi bayani kan sana'o'i biyu na Hausawa.

**AIKIN GIDA**

1. Me ya sa Hausawa ke ra]a suna ga `ya`yansu?
2. Ko kaciya na da amfani?
3. .Kawo wasannin Hausawa guda biyu da muhimmancinsu.
4. Kawo abubuwa uku da ma}era ke }erawa.
5. Fa]i abubuwa biyu wa]anda ake yi wa gawa ta Musulmi kafin a rufe ta.

**TA{AITAWA**

Wannan kashi yana koyar da al'adun Hausawa. Al'adar al'umma ita ce hotonta na rayuwa. Hausawa na alfahari da al'adunsu domin sukan yi amfani da su wajen bayyana kansu. Wannan ya nuna cewa al'ada abar alfahari ce.

**MANAZARTA**

Daura, B., Isa, Y., and Madauci, I. (1968) *Hausa Customs.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company

## KASHI NA 6: RUKUNAN SHEKARUN YARA DA MATASA DA MANYA DA DATTAWA

### GABATARWA

Al'ummar Hausawa, al'umma ce mai tsari dangane da rayuwar yau da kullum. Al'ummar ta da]e da tsari irin na iyali. Akan sami iyaye da 'ya'ya da jikoki da tatta~a-kunne da dai sauransu. A wannan tsari kowa na da matsayinsa da kuma irin rawar da yake takawa a rayuwar yau da kullun. Shekaru suna da muhimmanci }warai a irin wannan tsari, kuma za a yi nazarinsu a fahimci matsayinsu ]aya bayan ]aya a cikin wannan kashi.

### MANUFA

A wannan darasi za a karkasa jama'ar Hausawa ne dangane da shekaru kuma a yi bayanin ]abi'ar kowane rukuni. Ana sa ran ka karanta darasin ka fahimci yadda Hausawa suka karkasa kansu ta fuskar shekaru da kuma yadda shekarun suke.

### MATAKAN NAZARI

Ana bu}atar ka karanta bayanin cikin natsuwa sannan ka ri}a yi kana tunanin abin da aka karanta ka kwatanta shi da abin da aka sani. Idan an ga wani abu da ba a fahimta ba, to a yi tambaya ga wasu ]aliban ko kuma a tambayi wani malamin da ake ganin ya san abin. Yin haka shi zai sa a fahimta sosai kuma darasin ya zama mai amfani.

### KA DUBA AMSOSHI A BAYAN LITTAFIN NAN
### SABABBIN KALMOMI

| | |
|---|---|
| Rukunai | rabe-rabe |
| Mako | kwana bakwai |
| Kwa~a | hana mutum ya yi abu |

### SHEKARU

Shekara na nufin kwana 360 ko abin da ya kasa haka da ka]an a }irgar Musulunci wadda Hausawa ke amfani da ita domin shekara na da watanni har goma-sha-biyu (12) ne, kuma kowane wata na da kwana talatin (30) idan ya cika cif-cif. Idan ko bai cika ba yana da kwana 29. Akwai kuma mako (kwana 7) har hamsin da biyu (52) a cikin shekarar.

A }irgar Turawa kuwa, shekara na da kwana 365 ne ko 366. Ita ma ta Turawar tana da watanni goma-sha-biyu (12). Wata ]aya wato *Fabarairu* yana da kwana 28 ko 29. Wata hu]u kuma na da kwana 30 sauran suna da kwana 31. A halin da ake ciki a yanzu Hausawa na yin amfani da dukkan wa]annan tsari guda biyu. Ana }irga da]ewar mutum ko dai ta yin amfani da kwanakinsa ko makwanninsa ko watanninsa ko kuma shekarunsa. An dai fi yin amfani da yawan shekaru. Su ne za a duba a wannan darasin.

### YARA

Bayan yin aure, da zarar an sami rabo, kuma an haihu, abin da ake cewa an samu shi ne yaro ko yarinya wato jariri ko jaririya ke nan.

Yaranta a wajen Bahaushe takan fara ne tun daga haihuwa har zuwa wajen shekara goma-sha-biyu kai har ma sha-hu]u.

Yaranta a wajen namiji ta kasu zuwa gida uku. Kashi na farko shi ne zama jariri, wato daga haihuwa har zuwa yaye, wato misalin shekara biyu. Aji na biyu kuma ita ce ta zama yaro, wato daga yaye (shekara biyu) zuwa shekara goma-sha-hu]u. Bayan wannan lokaci, yaro ya zama saurayi.

Ita kuwa 'ya mace tana da aji har biyar. Da farko daga haihuwa zuwa yaye (shekara biyu) tana jaririya. Daga shekara biyu (yaye) zuwa shekara shida ko bakwai tana yarinya. Shekara bakwai zuwa tara kuwa ta zama }waila. Tun daga shekara tara har sha-biyu, tana matakin bera. Daga sha biyu kuma ta zama budurwa. A wannan lokaci ana sa ran ta sami miji ta yi aure. In ta wuce sha-biyar kuwa ta kai sha-bakwai, ko sha-takwas, to ana iya cewa ta da]e ba ta yi aure ba.

**AIKI I**

1. Shekara tana da kwana nawa ne?
2. Da shekara nawa yaro ke zama saurayi?
3. Mataki nawa yarinya ke wucewa kafin ta zama budurwa?

**MATASA**

Zama matashi ko matashiya a Hausa yakan fara ne tun daga shekara ta goma-sha-biyu ga mace, kuma sha-hu]u ga namiji. A lokacin ne shigar balaga ta zo masu. A wannan lokacin ake gane mai ha}uri da mara ha}uri, mai dauriya da marar dauriya da mai }o}ari da marar }o}ari. Ana gane }o}ari ko ha}uri ko dauriyar namiji ta fuskar aikin da ya gada da irin hul]ar shi da jama'a da kuma jure wa wahala. Ita 'ya mace ana gane }o}arinta ne tã yadda take ~ullo wa aikace-aikacen gida da ha}uri da sauran sa'o'inta a wajen wasa ko hul]a da kuma dauriyarta ta fuskar matsatsi na wani aiki ko damuwa.

Mutum na zama matashi ne tun daga shekarar balaga har zuwa wajen shekara arba'in lokacin da }arfinsa da hankalinsa suka gama ha]uwa.

**MANYA**

A al'adar Hausawa mutum kan kai matsayin manyantaka ne tun daga shekara arba'in. A lokacin hankali da }arfi sun kammala. A lokacin an riga an hayayyafa, wani lokacin ma bayan 'ya'ya har da jikoki. Manya a gida su suke ]aukar yawancin ]awainiyar yau da kullun ta 'ya'ya da sauran ]angi. Manyanta na nan tsakanin shekara arba'in (40) zuwa sittin (60).

**DATTAWA (Tsofaffi)**

Dattawa ko tsofaffi su ne wa]anda }arfi ya ragu a gare su da kuma wa]anda }arfin ya }are. Wa]annan suna nan a tsakanin shekara sittin har zuwa ]ari, ko ma fiye.

Saboda shekarunsu, sun koyi abubuwa da yawa na rayuwa su ne suke ba da shawara da kwa~a in bu}atar haka ta taso.

**AIKI II**

1. Wa]anne halaye ake so matashi ko matashiya su kasance suna da su?
2. Daga wane lokaci ake zama matashi ko matashiya?
3. Shekara ta nawa mutum ke shiga dattijantaka?

**AIKIN GIDA**

1. Mataki nawa namiji ke hawa kafin ya zama saurayi, kuma mataki nawa mace ke hawa kafin ta zama budurwa?
2. Daga shekara nawa mutum ke shiga }waryar manya?

**TA{AITAWA**

A bayanin da aka karanta an ga yadda Bahaushe ya raba shekarunsa da kuma matsayin da mutum ke hawa a kowane mataki na shekaru. Tun daga haihuwa wato daga zama jariri zuwa yaranta da zama matashi da manyanta da kuma tsufa. A al'adar Hausawa ana girmama matsayin da kowa yake da shi.

**MANAZARTA**

Yahaya, I. Y. (1992) *Darussan Hausa.* Ibadan: U.P.L. Ltd.

**KASHI NA 7: SIFFOFI DA MATSAYIN KOWANE RUKUNI GA AL`UMMA**

**GABATARWA**

A al'adance, kowane abu akwai irin yadda ake tunani a kansa, kuma akwai kimarsa a idon jama'a wato yadda al`umma ke kallonshi. Irin wannan zance ma haka yake dangane da shekaru da siffa da kuma matsayin da al'umma ta ha kowane mutum. Irin wa]annan siffofi ne za a duba a ga yadda suke dangane da shekarun mutum a cikin kashin nan.

**MANUFA**

Bayan bayanin da za a yi, za ka iya gane, kuma ka rarrabe tsakanin mutane, musamman dangane da shekarunsu. Shekarun za su sa a iya fahimtar ko shekara nawa mutum ya yi a rayuwarsa.

**MATAKIN NAZARI**

Zai yi kyau ka karanta wannan bayani sosai, sannan kuma ka sa ido ka dubi irin mutane, ka kwatanta su da bayanin da aka karanta a ga shin ko bayanin ya dace da siffar. Yin haka zai taimaka sosai wajen samun sau}in fahimtar wannan darasi.

**MATANI**

A kowace al'umma akwai yadda take kallo ko la'akari da yanayi ko siffar mutum don samun shekarunsa wanda shi ne zai sa ta shata masa matsayin da ya dace da shi.
A siffance in an kalli rayuwar Bahaushe za a fahimci bayanan da za su biyo na gaba.

**YARO**

Tun lokacin da aka ]auki cikinsa, an fara ]awainiya ke nan game di rayuwarsa. Bayan haihuwar jariri ba ya da kata~us komi sai an yi masa. Abincinsa bai wuce nonon uwar ba. Ko dai ana ]auke da shi ko yana kwance. In ya kai yaye, ya fara tafiya, ke nan bayan ya yi rarrafe. Haka za a yi ta kula da shi tun ana ba shi abinci har ya fara ci da kansa. Bayan shekara bakwai sai a yi masa kaciya. Daga nan, ya daina tafiya ba wando. Mace kuwa da ma ba ta zama ba sutura komi }ananan shekarunta. A wannan lokaci sun faye wargi da wasanni.
Matsayin yara a wannan lokacin shi ne na mataimaka. Yara kan ba da tasu gudunmuwar ta fuskar kai sa}o, wato a aike su zuwa ma}wabta. Haka kuma, sukan taimaka da yin wasu `yan aikace-aikace na gida, misali renon }annensu, da sharar tsakar gida da wanke-wanke da ]auko ruwa da tanka]e da iza wuta a murhu da dai sauransu.
A wajen ayyukan gona sukan taimaka wajen kai abinci a gona, da kai taki da }one-}one da sauransu. Yara na fara koyon sana'ar gidansu tun da wuri. Misali sukan yi zuga in ma}era ne, ]auko kayan aiki da mayar da shi in masa}a ne ko marina ko majema. Yara ne ke tallar sana'ar da iyayensu ke yi.

**AIKI I**

1. Daga wane lokaci ne yaro zai daina tafiya?
2. Lissafa gudummawa uku da yara ke bayarwa a gida.

**MATASA**

Bayan yarinta wato ga mace ta kai shekara goma-sha-biyu, namiji kuma shekara sha-hu]u, a lokacin suke ga~ar girma. {irar jiki na kammaluwa. A lokacin ne suke yin kyau da ban sha`awa. Matashi zai ci gaba da zama matashi har ya kai shekara arba'in. Daga nan kuma, girma ya zo ke nan.
Matsayin matasa shi ne na masu aiki. Su suka fi jure wa ayyuka na }arfi misali aikin gona, da sana'o'i. Mata matasa su ke haihuwa, da renon `ya`yansu da kula da mazajensu da iyayensu ta hanyar yi masu abinci.
A wannan lokaci ne suke neman arziki duk da yake dai suna nan cikin gandu.

**MANUFA**

A wannan matsayi an riga an girma. Manya na da siffa ta kammalallen mutum. Wasun su har sun aje gemu. Manyantaka kan fara daga shekara arba'in (40).
Matsayin manya a gida su ne masu ]aukar ]awainiyar iyali gaba ]aya. Su ke gudanar da ayyukan gona

da kasuwanci da dai sauran harkokin rayuwa.

**TSOFAFFI**

Tsufa kan soma ne daga shekara sittin (60). A lokacin jiki ya yi taushi, habu isasshen }arfi. Saboda haka ba za su iya yin wasu ayyukan da ke bukatar }arfi ba.

Matsayin tsofaffi a al'umma shi ne na masu lura da yadda al'amura ke tafiya. Su yaba in an yi abin yabo, su kuma kwa~a in an yi ba daidai ba. Suke ba da shawar na gari kan yadda za a gudanar da al'amuran rayuwa saboda kasancewar su na wa]anda suke da sani, wato sun ga abubuwa da dama. Takan yiwu har su kai matsayin da sai an kula da su kamar jarirai.

**AIKI II**

1. Yaya matsayin matasa yake a al'umma?
2. Me ya bambanta tsakanin manya da dattawa.

**AIKIN GIDA**

1. Su wane ne ginshi}an al'umma dangane da matsayinsu?
2. Wace rawa dattawa ke takawa a rayuwar yau da kullum?

**TA{AITAWA**

A darasin da ya gabata an yi magana ne kan irin siffofin da mutum Bahaushe ke da su. wato na shekaru da siffar jiki. Haka kuma an bayyana ire-iren matsayinsa a al'umma. wato tun daga matsayin wanda ake kula da shi, zuwa na wanda ke yawancin ayyuka da wanda ke ]aukar nauyin kowa, sannan kuma ya kai matsayin ba da shawara da kwa~a, kuma in tsufa ya yi tsufa har ta kai ana kulawa da shi.

**MA NAZA RTA**

Ibrahim, M. S. (1983) *Kowa Ya Sha.* Ibadan: Longman Nig. Ltd.
Yahaya, I. Y. et al (1992) *Darussan Hausa.* Ibadan: U.P. Ltd.

## FASALI NA 8: DABARUN KOYAR DA RUBUTU DA KARATU

## KASHI NA: 1 DABARUN KOYAR DA RUBUTU DA KARATU

**Karanci-fa]i:** Wannan ita ce hanya ta biyu. Ita wannan hanya tana sa yaro juriya. Malami na iya }ir}iro dabaru masu yawa daga cikinta. Kayan aiki da ake bu}ata duka-duka ba su wuce allo na bango da alli ba. Wani lokacin akan bu}aci 'yan hotuna na irin abubuwan da kan samu a cikin gari ko a kasuwa. Manufa dai ita ce, yara su iya tsayuwa su dubi kowane ba}i wanda malami yake }o}arin fa]akar da su a kansa. Idan malami ya shigo aji zai fara ne da rubuta ba}a}en da yake so a bambance, yana yi yana karanta su kuma yana tambayar ]alibai. Bu}ata ita ce kowane yaro aka nuna ya yi farat ya ba da amsa.

### AIKI I

1. Zana ba}a}en Hausa, ka kuma jera su a babbar takarda. Lallai ne kowane }aramin ba}i ya zamo yana biye da babban ba}insa.
2. Wa]anne ne manyan hanyoyin koyar da ba}a}en Hausa?
3. Me ya sa ya zamo lallai malami ya yi amfani da ]aya daga cikin wa]annan hanyoyin koyar da ba}a}en Hausa?
4. Wa]anne hanyoyi ne kuma ka ke ganin ya kamata a bi wajen koyar da ba}a}en Hausa? Ba da dalilai

### AIKIN GIDA

Ka yi }o}ari ka bambanta tsakanin wal}ata-kati da karanci-fa]i a matsayin su na muhimman dabarun koyar da ba}a}en Hausa.

### TA{AITAWA

A wannan kashin, ka nazarci bayanin kan ba}a}en Hausa - manya da }anana.
ka kuma nazarci yadda ya kamata a koyar da ba}a}en ta hanyoyin nan biyu:

i) Wal}ata kati (walkiya da kati)
ii) karanci – fa]i ka kuma fahimci wuraren da ake amfani da manyan ba}a}e.

### MANAZARTA

N.E.R.D.0 (1980) *Hausa: A textbook of Methodology* Zaria: Gaskiya Coopefation.
Zarruk, R.M., Kafin Hausa, A.A. & Al-Hassan, B. S. Y. (1987) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.* Ibadan: University Press Ltd

## KASHI NA 2: KOYAR DA HARUFFAN HAUSA (Wasulla) GABATARWA

Jimillar sautukan da ake rubutun Hausa da su, su ake kira haruffa, kamar yadda aka yi bayani a cikin kashi̦ na farko. Mun riga mun ji cewa haruffa sun ha]a da ba}a}e da kuma wasula. Mun kuma fahimta a }arshen kashi na farko cewa lallai ne a koya wa yara yadda za su san haruffan su kuma gane su saboda a sami sau}i wajen rubutu da su. A kashin farko mun tattauna a kan yadda za a koyar da ba}a}e. A wannan kashi kuma za mu duba yadda ya kamata a koyar da wasullan Hausa. Koyar dá wasulla yana da nasa muhimmancin, kamar dai koyar da ba}a}e.

### MANUFA

A }arshen wannan darasi, ya kamata ka kasance ka iya:

i. Kawo ma'anar farfaru, wato wasulla
ii. Bayyana yadda za ka koyar da manya da }ananan wasulla,
iii. Bambanta tsakanin gwauron wasaii da auren wasaii iv.
iv. Fa]i dangantakar ba}i da wasali

### MATAKAN NAZARI

(i) Akwai bu}atar tabbatar ka karanta kashi na farko da ke magana a kan koyar da ba}a}e kafin fara wannan kashin.
(ii) Domin fahimtar wannan kashin sosai ka tabbata ka yi dukkan ayyukan da za a bu}aci ka yi. Kuma ka tabbata ka bayar da amsoshin duk tambayoyin da za a yi maka a cikin wannan kashin.
(iii) Har ila, yau, yana da kyau ka yi }o}arin tunanin cewa ga ka tsaye cikin aji gaban yara kana koyar da su wannan batu na wasulla. Yin hakan zai taimaka maka wajen }ara fahimtar abubuwan da wannan kashin ke koyarwa.

### SABABBIN KALMOMI

Wasulla: Su ne haruffan Hausa in an cire ba}a}en da ke ciki.
Ka rubuta duk wata kalma da ke sabuwa, ko ba}uwa, ko kuma ka rubuta wadda kake ganin ta shige maka duhu. Ka tabbatar ka samo ma'anoninta.

### MATANI

In an cire haruffan da ake kira ba}a}e, kamar yadda ya gabata a kashi na baya, sautukan Hausa da suka rage su ake kira wasula. Wasula sun rabu gida biyu:-

i) Gwauron wasali
ii) Auren wasali

Farfaru taron wasula ke nan su ka]ai ban da ba}a}e. Su kuma farfaru sun }unshi wasula biyar ne.

Wasulla cikakku su ne: A, E, I, 0, U.
a, e, I, o, u.

Gwauron wasali shi ne wanda yake zuwa shi ka]ai kamar a cikin wa]annan jumloli:

E Za ni

I ni ne

A yaushe a ka yi haka, da sauransu.

Auren wasali shi ne, inda wasula biyu suke fitowa tare. Za ta iya yiyuwa irin su ]aya ko kuma su na da bambanci misali shi ne:

Ai, Au, kamar a cikin kai, kau, hau, nai da sauransu.

Akwai bu}atar a jaddada cewa wasali na da ma'ana kamar haka:

Harafi ne wanda yayin rubutu yakan zo ne a bayan ba}i. Wasali shi ne jigon karatu, domin ba a iya fitar da muryar ba}i ba tare da wasali ba. Da farko dai, shi wasali da kansa ana iya karanta shi da sunansa. Muryar wasali ita ce ta ke zama muryar duk ba}in da aka ajiye a gabansa. Misali:

| | | | | |
|---|---|---|---|---|
| a, | e, | i, | o, | u. |
| ba | be | bi | bo | bu |
| ca | ce | ci | co | cu |

da sauransu.

**AIKI I**

1. Zana wasullan Hausa cikakku (gwauron wasali) da kuma auren wasali. Lallai ka zana kowane }aramin wasali ya zamo yana biye da babban wasalinsa.

Wasali, ana iya kallonsa a matsayin gangar jiki a lokacin da ba}i yake a matsayin sutura. Sa'annan shi wasali mai iya zaman kansa ne, ba ya bu}atar wani babu inda ake fara wasali biyu sai a auren wasali ka]ai kamar a "ai" da "au" kamar yadda aka yi bayani a baya ko da an jera su a wani waje to lallai za ka ga an raba su da alamar nan ta katsewa kamar a a'a, o'o da sauransu.
Wannan alama ta katsewa ba a samunta sai a tsakanin wasali da wasali, ko kuma a tsakanin ba}i da wasalin da ba nasa ba.

**AIKI II**

1. Zayyana wasulla a kan }ananan takardu kamar yadda ka yi a kashi na farko inda ka zana ba}a}e a kan wasu guntayen takardu.
   Yi kamar kana koyarwa. Nuna su a aji ka fa]i yadda ake furta su. A nan, za ka nemi yara su furta kamar yadda ka fa]i.
   Yi bayanin muhimmancin wasali wajen ba ba}i sauti. Jaddada bayaninka tare da li}a wasali a jikin wani ba}i domin ya bayar da sauti irin na wannan wasalin. Maimaita yin haka, kana karantawa yara suna bin ka.
   Nemi yara su karanta tare da ba su yabo in sun fa]a dai-dai. Kuma a gyara musu in sun yi kuskure. Samar da wata takarda wadda a jikinta za ka jera duk ba}a}en da aka yi bayani a kashi na farko. Lilli}a wasullan nan a jikin ko wane ba}i. Wannan shi ne zai zama abin kamantawa ga yara.

**AIKIN GIDA**

1. Ta yaya za ka yi amfani da dabarar wal}ata-kati wajen koyar da wasulan Hausa?
2. Bambanta tsakanin gwauron wasali da auren wasali.
3. Fa]i dangantakar ba}i da wasali

**TA{AITAWA**

A wannan kashin an yi nazarin:

- Wasulla cikakku da kuma rabin wasulla
- An fito dangantakar wasali da ba}i
- Daga cikin ayyukan da aka bayar, an yi bayanin yadda za a koyar da wasula.

**MANAZARTA**

Institute of Education, ABU (1979) *Karatu da Rubutu a Harshen Hausa.* Lagos: Thomas Nelson (Nigeria) Limited

Zarruk, R.M., Kafin Hausa, A.A., & Al-Hassan, B.S.Y, (1987), *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.* Ibadan: Ibadan University Press.

**KASHI NA 3: KOYAR DA RUBUTU DA FAYYACE MANYA DA {ANANAN HARUFFA**

**GABATARWA**
Haruffan harshe su ne saututtukan da ake amfani da su a harshe, a Hausa kuma su ne ake kira haruffa. Su wa]annan haruffa akwai manya da }anana, wa]anda kuma suka ha]a da ba}a}e da wasulla. Sanin haruffan, yana,da amfani domin yana share fagen koyon rubutu da karatu. Ta haka ne mai karatu zai iya bambanta manya da }anana, sannan ya na}alci zubi da tsarinsu.

**MANUFA**
Da zarar an kammala nazarin wannan kashi, ya kamata mai karatu ya:
(a) San manya da }ananan haruffan Hausa.
Sanin muhallin da ya kamata a yi amfani da manya da }ananan haruffa.

**MATAKAN NAZARI**
Ga shawarwarin da ya kamata mai karatu ya yi la'akari da su a lokacin da ya fara aiwatar da wannan kashi:
(a) Tanadin haruffa (manya da }anana) a rubuce.
(b) Tunannin rayuwa a zuciya na tsayuwa a gaban aji.
(c) Karanta bayanin yadda za a fuskanci matsala a lokacin nazarin wannan kashi
(d) Yi }o}arin shirya tambayoyi da amsoshinsu.

**YIN AMFANI DA MANYA KO {ANANAN HARUFFA WAJEN RUBUTU**
Gaba ]ayan saututtukan harshen Hausa su ne haruffa. Ga haruffan Hausa manya da }anana kamar haka:
(a) B | C D [ F G H J K { L M N R S T W Y `Y Z
GW, GY, KY, {Y, KW, {W
SH TS
(b) b ~ c d ] f g h j k } l m n r s t w y `y z gy gw h k ky kw k kw }y }w
gy gw ky }y kw }w sh ts,
A zubi da tsarin harshe, rubutu abu ne da ya bambanta da magana, watau shi rubutu wakili ne kawai na maganar da aka yi. Saboda haka akwai bambanci tsakanin rubutu da maganar da aka yi da baki. Wannan shi ya sa rubutun kan tafi da alamomin maganar domin neman dacewa.
Kamar yadda tsarin yake a kowane harshe, haka ma a Hausa cewa rubutu ba haka nan kara zube ake yin sa ba, watau yana da }a'idoji. Amma, tun kafin a fara maganar }a'idoji, abin da ya kamata a fara koyo shi ne sanin haruffa.
Domin a kauce wa `yan matsalolin da yara kan fuskanta wajen sarrafa manya da }ananan haruffa, dole ne a sanar da yara muhallin da ya kamata a yi amfani da manya da }ananan haruffa. Ga misali, na amfani da manyan haruffa a farkon jumla, rubuta sunayen yanka kamar: sunayen mutane, garuruwa, unguwanni, rafuka, tsaunuka da sauransu.
Haka kuma ana amfani da manyan haruffa a bayan kowace aya. Su kuma }ananan haruffa ana amfani da su a sauran wurare da ba na manyan ba. Ta haka ne rubutun kan kasance cikin tsari, ta yadda za a iya karanta duk abin da ka rubuta.

**AIKI NA I**
1. Kawo manyan haruffan Hausa sannan ka jera }ananan ta yadda za su dace.
2. Mene ne ya bambanta rubutu da magana?
3. Ware manyan haruffan Hausa `yan tagwai.
4. Bayyana manyan hanyoyin koyar da haruffan Hausa.
5. Me ya sa ya fi dacewa a yi amfani da ]aya daga cikin hanyoyin.
6. Shin ko akwai wasu hanyoyi kuma da kake ganin za a bi domin koyar da haruffa a Hausa?

Matu}ar dai ana so a sami biyan bukuta, dole ne a bu]e koyar da kowane darasi da annashuwa, raha da nisha]i. Idan wannan ya samu, to sai a shiga koyar da darasi sosai: Shi kuwa darasin, za a iya arnfani da wa]annan hanyoyi guda biyu kamar haka:
(a) Sarrafa kati a matsayin wata dabara ta jawo da tattara hankalin yara wuri ]aya kan abin da ake koyarwa.

(b) Karanci – fa]i domin sanya yara kaimin }ir}iro dabaru masu yawa a cikinta. Hakan yana faruwa da taimakon allo, alli da kuma hotuna.

**AIKIN GIDA**

1. Rubuta ta}aitaceen bayanni mai gamsarwa kan
2. (i) Karanci-fadi
   (ii) Sarrafa kati
3. Ta yaya manyan haruffa suka bambanta da }anana da kuma }ananan haruffa?

**TA{AITAWA**

A }arshen wannan kashi, ka nazarci:

- zubi da tsarin haruffan Hausa (manya da }anana).
- muhallin amfani da manya da }ananan haruffa
- hanyar da ya kamata a bi wajen koyar da haruffa
- haruffan Hausa `yan tagwai

**MANAZARTA**

CNHN (1977) *Sabuwar Hanyar Koyon Harshen Hausa da Al'adun Hausawa.*

NERC (1980) *Hausa: A Textbook of Methodology,* Zaria: Gaskiya Corp.

Zarruk, R.M. Kafin Hausa, A.A. & A.B. Alhassan (1984) *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa.* Ibadan: Ibadan University Press.

## KASHI NA 4: KOYAR DA AWON FAHIMTA

### GABATARWA

Neman abin da aka koyar domin a tabbatar matsayin da aka kai wajen fahimta shi ne auna ita fahimtar kanta. Ta haka ne za a san nasarar da ake samu domin ci gaba, ko kuma matsalolin da ake fuskanta domin a magance su. Saboda haka, malami yana bukatar jagoranci dangane da yadda zai auna fahimtar abin da ya koyawa ]alibai. Idan haka ne (wanda hakan ne), to malami yana bu}atar shawara da za ta zame fitila mai haskaka hanyar da aka shimfi]a aikin a kai. To, da yake auna fahimta na da amfani ashe akwai makama wadda malami zai yi amfani da ita domin ganin cewa kwalliya ta biya ku]in sabulu.

Manufa a nan ita ce, a }arshen wannan kashi, mai karatu ya fahimci wa]annan abubuwa:

iya auna fahimtar abin da aka koya ta na}alta da tanadin muhimmanan abubuwan da za su taimaka.

Sanin hanyar koyarwa mafi dacewa.

bayyana yadda za a koyar da auna fahimta.

### MATAKAN NAZARI

Mai karatu ya nazarci wa]annan shawarwari sannan ya fahimci yadda zai yi amfani da su:

(a) a tanadi matanin da za a yi amfani da shi a lokacin darasi
(b) `yan makaranta a tanadar masu da kwafe daidai na matanin
(c) a bai wa kowane ]alibi damar ya tofa albarkacin bakinsa a lokacin darasi.
(d) malami ya san yadda zai gano ko ya ci nasarar abin da yake koyawa

### SABABBIN KALMOMI

Ka yi amfani da filin da aka bari a }asa domin rubuta duk wata kalma sabuwa ko ba}uwa. Ka tabbata ka samo ma'anarta:

Koyo
Fahimta
Aunawa
Matani
Mataki

### AWON FAHIMTA

Matakan da za a bi wajen koyar da auna fahimta su ne za su jagoranci yadda za a tabbatar da auna fahimtar abin da aka koya.

Da farko dai, akwai bu}atar a samo abin karantawa watau abin da za a ]ora aikin a kansa. Daga nan kuma sai ya tabbata ya yi nazarinsa tun kafin ya shiga aji, domin hakan ne zai ba da damar shiryawa sosai. Haka kuma akwai bu}atar tantance amsoshin tambayoyi kafin zuwa aji, sannan kuma ya za~o sabbabin kalmomi tare da kawo ma'anoninsu domin taimaka wa }arin fahimta. Sai kuma a samo kayan aiki da ka iya taimakawa wajen fahimtar abin karantawa ko kuma sabbabin kalmomi. Daga nan kuma sai gabatarwa a gabatar da darasi kamar yadda aka saba.

### AIKI NA I

1. Bayyana matakan da za a bi wajen koyar da auna fahimta da muhimmancinsu.
2. Kawo misalai 5 na matakan koyarwa a tsarin daga kai sai ni.
3. Shin sai an tanadi matakan koyarwa duka ya kamata a fara darasi ko a'a? A lokacin da aka gabatar da aikin darasin, watau aka yi shimfi]ar abin da za a koyar to sai a fara da karatun farko wanda malami ne zai fara. Hakan ya zama wajibi domin ]alibai su yi koyi da abin da malam ya ce. Wannan shi ne zai kawo mu ga karatun asirce daga ]alibai, sannan kuma, sai karatu tsakanin ]alibai na ]aya bayan ]aya ya biyo baya. Ta haka ne zasu fara fahimtar abin da ake koyarwa.

Abin da zai biyo baya daga wannan shi ne, dasa tambayoyi, watau daga abin da Malami ya koya ne zai gabatar da tambayoyin da ya tanada, wanda su kuma ]alibai za su yi }o}arin amsawa. Daga wannan zango ne kuma, malami zai fara auna fahimtar ]alibai. Sakamakon da ya samu daga auna fahimfar ita ce za ta }ara taimaka masa sanin irin matakin da zai ]auka, watau idan ya gamsu to sai a ci

gaba, amma idan akwai matsaloli, to nan ne za a san yadda za a ~ullo masu.

**AIKI II**

1. Me ya kamata malami ya yi da ya gabatar da darasi?
2. Lallai ne ga malami ya yi amfani da dabarun koyarwa kamar yadda aka yi bayani a sama?
3. Ka na iya kawo wasu hanyoyi gwargwadon fahimtarka tare da dalilai

**AIKIN GIDA**

1. Fa]i dangantakar karatun farko daga malami da karatun asirce daga ]alibi.
2. Ta yaya za ka yi amfani da matakan koyarwa wajen auna fahimta'?
3. Me ake nufi da auna fahimta'? Kawo misali biyar na matakan koyar da auna fahimta.

**TA{AITAWA**

- A wannan kashin, an yi nazarin hanyoyin auna fahimta
- An fito da dangantakar koyarwa da fahimtar abin da aka koya
- Daga cikin irin ayyukan da aka bayar, an yi bayanin yadda za a auna fahimta.

**MANAZARTA**

CNHN (1977) *Sabuwar Hanyar Koyon Harshen Hausa da Al 'adun Hausawa.*

Institute of Education, ABU Zaria (1979) *Karatu da Rubutu a Harshen Hausa.* Lagos: Thomas Nelson (Nigeria).

NERC (1980) *Hausa: A Textbook of Methodology.* Zaria: Gaskiya Corporation:

**KASHI NA 5: KOYAR DA KARATU A LITTAFI**

**GABATARWA**

Dangane da shirin koyar da karatu, a nan dole ne malami ya tanadi muhimman kayayyakin aiki. Da farko, dole ya kasance malami yana da manhaja ta shekarar karatun da zai koyar domin gwada shekarun ]aliban da irin abin da }wa}walwarsu za ta iya ]auka. Bayan haka, yana da matu}ar muhimmanci ga malami ya tabbatar cewa kowane ]alibi ya sami kwafe na littattafin da za a koyar da karatun. Haka kuma shi kansa malami ya karanta labarin da zai koyar tun kafin ya shiga cikin aji, yana da kyau malami har ila yau ya kawo zane-zane cikin aji na abubuwa masu muhimmahci wa]anda za su fito a cikin labarin saboda ya ja hankalin ]aliban su ]okanta da gane abin da labarin ya }unsa.

**MANUFA**

Manufar wannan kashi ita ce, daga }arshe, in an gama hanyar koyarwar a fahimci:

abubuwan da suka wajaba a samar wajen koyar da karatu;
yadda za ka yi wa ]alibanka wajen koya masu karatu;
auna fahimtar ]alibanka wajen gano cewa hanyar koyarwar da ka ]auka ta dace da ]alibanka;
yadda za a yi amfani da sakamakon da ya samu wajen bun}asa koyar da karatu nan gaba.

**MATAKAN NAZARI**

(i) ya kamata ka bi umurnin da aka ba ka wajen matakan koyar da karatu
(ii) ka kasance kana tare da manhaja a tare da kai wajen nazarta wannan kashi don kwatanta abin da aka gaya maka da abin da yake hannunka.
(iii) ka tanadi littafin da za ka koyar domin fahimtar wannan kashi sosai.

**SABBABIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| Manhaja | - | takardar tsarin koyarwa |
| Zane-zane | - | hoto don nunawa a aji |
| kwafe | | nus ha/juzu' i/littafi |
| le~~a | | le~e guda biyu sama da }asa |
| hawa da sauka | | ]aga ko saukar da murya |
| Aya | | alamar tsayawa (.) |
| wakafi | | alamar numfasawa (,) |
| Ayar motsin rai | | alamar karfafawa (!) |

**KOYAR DA KARATU A LITTAFI**

Dole ne malami ya yi la'akari da matsayin ]alibai wajen shirya darasinsa na koyar da karatu domin ya za~a musu karatun da zai dace da matsayinsu. Bayan malami ya karanta labarin da yake so a karanta a aji kafin ya shigo cikin ajin, haka kuma zai yi kyau malami ya shigo ajin da hotuna wa]anda zai nuna wa ]aliban. Wa]annan su ne kayan aikin masu kaifafa fahimta.
Ana so malami ya gabatar da darasi ta hanyar gabatarwa mai kyau sannan gabatarwar ta kasance ta }unshi wani maimai na darasin da ya gabata domin a ]ora a gina sabon darasi a kai. Wajen gabatar da labarin da za a karanta yana da muhimmanci a jawo hankalin yaran tukuna ta hanyar gaya musu wani labari wanda ya shafi wanda za su karanta a aji.
Abu mafi muhimmanci ga malami dole ne ya tsara darasinsa daki-daki a kan mataki-mataki.

**MATAKAN KOYAR DA DARASIN KOYON KARATU A MATAKIN FARKO**

Bayan malami ya samo kayan aiki na koyarwa kamar yadda muka fa]a a sama abu na gaba shi ne gabatar da darasin a matakin farko. Bayan malami ya dasa harsashin darasinsa ta hanyar tisa abin da ]alibai suka sani a da, abu na gaba shi ne shi da kansa ya fara karanta wa ]aliban labarai da yake so su karanta domin su saurare shi; su ji irin yadda ake so su yi karatun. Ta wannan hanyar ce su ma idan sun ji za su iya da]a inganta karatun nasu, tambayoyin da za su yi su kawo mu'amala tsakanin malami da ]alibai.

**AIKI NA I**

1. Me ake nufi da gabatar da darasi?
2. Mene ne amfanin hoto wajen aikin koyarwa?
3. Yaya ake inganta darasi?

**KOYON KARATU A MATAKI NA BIYU**

Bayan gabatar da darasi da malami ya yi ta hanyar dabarun koyarwa, kamar yadda aka zayyana koyar da gundarin darasin shi kansa. A nan, malami zai kawo littattafan da ]aliban za su karanta a cikin aji sannan ya rarraba musu, ko kuma suna da littattafan ya gaya musu sunan littafin da za su ]auko, sannan ya sa su bu]o shafin da yake so su karanta, bayan ya karanta musu labarin da kansa kamar dai yadda aka fa]a a sama wajen gabatarwa. Sannan zai sa su karanta, ko dai ya sa su karanta layi-layi, kamar yadda suke a zaune cikin aji, ko kuma ya ]auki mutum a kowace kwana idan wannan ya karanta an saurare shi, wancan kuma ya karanta shi ma a saurare shi.

**ABUBUWAN DA MALAMI YA KAMATA YA LURA DA SU**

Lokacin da malami ya sa ]alibai su karanta labari a cikin aji, ya kamata ya lura da yadda ]alibi yake ]aukar karatun da inda yake ajiye shi. A nan, ana nufin ya gane farkon jumla da kuma inda ake ajiye jumlar a wajen karatu. A nan, malami zai koya wa ]alibai cewa idan an zo wa}afi akan tsaya a ja numfashi, sannan a ]an tsaya a wajen da aka zo aya.

Sannan dole malami ya saurari yadda ]alibi yake karanta labarin domin ya gyara masa wasu kura-kurai, to, a nan, ka ga dole ne a yi shi wanan karatu a hankali ba cikin sauri ba.

Irin kurakuran da malami zai fi la'akari da su lokacin da ]alibi yake karanta labarin, sun ha]a har da irin yadda yake karanta kalmomi da sirin yadda yake tafiyar da hawa da sauka na murya, lallai su kasance daidai da yadda ake amfani da su wajen aiwatar da harshen yau da kullum. Yana da muhimmanci kuma, malami ya rin}a gyara wa ]alibi yadda yake sarrafa le~~ansa da harshe wajen fa]ar wasu kalmomi. Su kansu kalmomin a fitar da wa]anda ake ganin za su wahalar da ]alibi wajen gane su da fassarar ma'anarsu, a rubuta su a kan allo domin yaran su sake shaida su, su saki jiki da su don kada su sake wahalar da su nan gaba wajen karatu. Sannan a kula da aya da wa}afi, da ayar motsin-rai. Sannan ya kasance ana tantance sakin layi wajen karanta labarin a littafi.

**AIKI NA II**

1. Me ya kamata a yi wa ]alibai, bayan an gabatar da darasi?
2. Wa]anne irin kura-kurai malami ya kamata ya lura da su lokacin da ]alibi yake karatu.
3. Mene ne amfanin yin karatu a hankali a cikin aji?

**AWON NASARAR KOYARWA**

Malami zai iya auna nasarar hanyar da ya bi wajen koyar da darasi domin ya fahimci cewa wannan hanya da ya bi, ko ya sarni nasara ya cimma manufar da ya sa a gaba wajen koyar da ]aliban. Wannan kuwa ba zai yiwu ba sai idan rnalamin ya gudanar da mu'amula tsakaninsa da ]alibai ta hanyar tambayoyi da amsa tsakanin malami da ]alibai. Daga irin amsoshin da suke ba shi, zai gane cewa lallai ]aliban sun gane ko kuwa ba su gane ba. Ta haka zai bun}asa hanyar koyar da karatu a nan gaba.

**AIKIN GIDA**

1. Bayyana yadda ake gabatarwa a darasin koyar da karatu.
2. Yaya ake koyar da karatu a mataki na biyu?
3. Yaya ake gano kura-kuran ]alibi
4. Yaya ake auna nasarar koyarwa?

**TA{AITAWA**

A wannan kashi, ka koyi:

- Shirin koyar da karatu da zayyana manufa.
- Kayan cikin koyarwa, manhaja da littattafai, zane-zane da hotuna.
- Tsara koyarwa, sanin matsayin ]alibi, gane abin da suka sani da gini a kan inda suka tsaya.
- Matakan da za a bi wajen koyarwa, daki-daki.

- Abubuwan la'akari da su kamar karanta kalmomi na musamman, fassarasu, hawa da saukar  murya.
- Kula da aya da wa}afi sarrafa le~~a da harshe.
- Auna nasarar koyarwa don gano hanyar da tá fi dacewa a koya wa ]aliban

**MANAZARTA**

'Cohen, A, and Garner, N (1963) *A student Guide to Teaching Practice.* Hodder and stoughton
Galadanchi M.K.M. Et al (eds) (1978) *UPE Hausa A Textbook of Methodology.* Zaria: N.N.P.C.
Oxford University Press (1963), *Littafin Malamai Kan Litaffin Hausa.* Ibadan: OUP.

**KASHI NA 6: KOYAR DA KARATUN SAURI**

**GABATARWA**

A nan, ya kamata malami ya san irin gogewar da `yan makarantarsa suke da ita kafin ya yi tunanin fara aikin da zai koya musu. Ya kamata yana da manhaja a hannunsa sannan ya tanadi littattafai isassu saboda koya karatun sauri abu ne wanda yake bu}atar da zarar ]alibi ya yi kuskure, nan take a tsai da shi a nuna masa. Koya karatun sauri ba abu ne wanda za a gabatar da shi a }ananan azuzuwa na }asa ba. Don haka, koya karatun sauri a wannan azuzuwa aka fi son a }addamar da shi.

**MANUFA**

Daga }arshen wannan kashi, ana sa ran za ka fahimci:
Yadda za ka tsara aikin da ya fi dacewa ka gabatar wa ]alibai;
gogewar da ]alibanka suka samu ta baya da abin da za ka koyar;
irin kura-kuran da za su bayyana a wajen ]alibansa lokacin koyarwa;
inda zai ajiye darasin, ya kasance matakin da fara koyar da na gaba.

**MATAKIN NAZARI**

(a) Ana bukatar ka tanadi manhajar da za ka koyar domin kwatanta abin da za ka karanta a wannan kashi da kuma abin da yake hannunka.
(b) Ka kasance ka ta~a shiga cikin ajin koyarwa ko kuma an ta~a gudanar da ajin koyarwa a gabanka a matsayinka na mai nazarin aikin koyarwa.
(c) Yana da kyau ka fara nazartar TA{AITAWA ta wannan sashe domin ka ga hoton abin da zai karanta a ta}aice.
(d) Ka nazarci aiki na ]aya da aiki na biyu na wannan sashe domin ka kawo tunanin abin da za ka karanta a cikin ranka kafin ka karanta ]in.
(e) Haka kuma yana kyau ka fara karanta gabatarwa kafin ka tsunduma cikin karatun ka'in da na'in.

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| tanadi | samun abu a ajiye kafin lokaci |
| }addamarwa | gabatar da abu |
| manhaja | takardar tsarin koyarwa |
| ka' in da na' in | gaf da gaf |
| walwala | sakin jiki |
| maimaye | bitar ayyukan da suka gabata |
| karin-kumallo | abincin safe |
| in' ina | cijewar magana |
| tsamin baki | wanda ba ya iya fadar sautuka daidai |

**KARATUN SAURI**

Malamin da zai koya wa ]alibai karatun sauri, dole ne ya tabbatar da wani abu guda a cikin ajinsa kafin ya }addamar da darasi. A nan, ana nufin cewa dole malami ya bu}acl ]alibai su natsu su yi shiru, domin idan da surutu to babu shakka za a ja hankalin ]alibai ga wancan surutu, domin surutu da akan yi a aji yawanci tsegumi ne, wanda yake ya fi da]in ji fiye da karatun da ake aiwatarwa.
Sannan yana da muhimmanci ga malami ya dasa darasinsa a kan irin gogewar da ]alibai suka samu a azuzuwan baya. A nan, ba wai ana bu}atar malami ya sake karanto darussan da suka gabata ba ne, abin nufi kusan hakan ne to amma ana so ya kasance jirwaye ne kamar wanka, wato ana so ya rairayosu ya tuna wa ]aliban ta hanyar dabarun koyarwa yadda ]aliban za su tuna da ayyukan da. A sanadiyyar waiwayo ayyukan baya ]alibai za su saki jiki da sabon darasin da malami zai kawo musu a cikin aji a halin yannzu.
Dangane da shi wannan karatu cikin sauri, abin da ake nufi ba wai mutum ya yi ta karatu ratata ba har a kasa fahimtar abin da yake cewa ba, ana nufin mutum ya yi shi wannan karatu a cikin siga irin yadda yake maganarsa ta yau da kullum, cikin walwala da natsuwa

Ga~o~in da aka fi amfani da su wajen gudanar da karatun sauri su ne, kunne da ido da kuma baki, dole ne shi mai karatu ya kasance yana sauraron abin da shi kasan yake fa]a domin ya ji cewa kalmomin da ya ambata ya fa]e su daidai kamar yadda ake fa]arsu a zance na yau da kullum. Sannan su ma masu sauraro wato ]alibai `yan`uwansa. Sannan shi uban tafiya jagora wato malami.
Sai ga~a ta gaba wato idanu, shi idanu ana so ya dinga bin she]ara da she]ara inda mai karatu yake karantawa domin ya dubo inda mai karatu ya yi kuskure, saboda haka sai malami ya saurari inda zai ji an fa]i wata kalma ba daidai ba wajen hawa da sauka na muryar mai karatu, ko ya tsallake ta bai fa]e ta ba. Haka kuma, dole malami ya bi ]alibai da yake karatu da kallo sannu sannu ya gano inda ya tsallake, watau layi ko ma sakin layin baki ]aya. Malami ya lura cewa wasu ]aliban suna da sauri wasu suna da la}a}i.

**AIKI NA I**

1. Me ya kamata malami ya yi a matakin farko na koyar da karatun sauri?
2. Wa]anne ga~o~i aka fi amfani da su wajen yin karatun sauri?
3. Mene ne abin da malami zai fi kula da shi idan ]alibai suna karatu?

**MATSALOLIN KARATU**

Malami ya kamata ya gano inda matsalaloli suke, domin ya gyara su, wanda gyara wa]annan matsaloli sai ya nuna }warewarsa ta malanta. Wasu matsalolin da za su zo cikin aji tun daga gidajen su kansu ]aliban suka samo asaii, wasu matsalolin kuwa a ji kin shi kansa ]alibin suke sannan wasu matsalolin a cikin aji suka samu. Saboda haka su wa]annan matsaloli su ne za su faru su yi tasiri wajen kawo cikas ga saurin karatun ]alibi. A nan, ana bu}atar malami ya yi }o}arin warware wa ]alibi wa]annan masaloli. Sannan su kansu matsalolin ba iri ]aya ba ne a jikin ]alibai kowane ]alibi yana da irin tasa matsalar, a inda ake da matsalolin iri ]aya, to, tarihin matsalar wannan ]alibi ta sha bamban da ta wancan wajen girman matsalar ko inda matsalar ta sa gaba, wato kowane allazi da nasa amanu.
Daga cikin matsalolin da masana suka fi gano wa Wa]anda suka fi damun ]alibi wajen hana shi karatu ita ce, wadda ta samo asaii daga gida. Misali, watakila lokacin da yaro ya taho daga gida ya baro uwarsa da ubansa suna fa]a, ko mahaifiyarsa da ma ba ta gidan saboda haka kishiyar uwarsa tana matsa masa, ko ya taho cikin aji bai sami karin kumallo ba. Idan malami ya gano wannan sai ya yi }o}arin tunanin matakan da zai ]auka domin ya rage wa ]alibi tunani a zuciyarsa, wadda za ta hana masa karatu.
Wata matsalar kamar yadda aka ambata tana jikin ]alibi shi kansa, wato yana da matsala ta gani sosai saboda haka da }yar yake gane rubutun dake cikin littafin, nan sai malami ya lura ya san matakin da zai ]auka a kan ]alibi wajen bai wa iyaye shawara a yi masa gilas ya sa shi a gaba, wato layin gaba a cikin aji.
Wata matsalar ta ji ce ]alibi yake da ita. A nan, malami zai gano wannan matsala a jikin ]alibi ta wajen ma'amula a aji lokacin yin tambayoyi, ko amsa kira idan ana kiran suna nan ma an so malami ya ]au mataki don taimaka wa ]alibi.
Wata matsalar kuma ta karatu ita ce, wani ]alibin yana da in'ina wani yana da tsamin baki, wani yana da saurin baki, wani }wa}walwarsa ba ta iya ri}e abu da sauri, wani kuma }wa}walwar tasa mai kaifi Allah ya ba shi yana da saurin gane abu a cikin haka shi yakan sha gaban kowa a cikin aji. Dole malami ya yi la'akari da duk wa]annan abubuwa ya shiga tsakani ya san irin gyare-gyaren da zai kawo wa]anda za su taimaka wa ]alibai wajen gudanar da karatunsu.

**AIKI NA II**

1. Mene ne matsalolin karatu?
2. Yaya malami zai iya gano matsalar ]alibi?
3. Ko matsalar ]alibai iri ]aya ce?

**AIKIN GIDA**

1. , Bayyana dabarun da malami zai bi ya jawo hankalin ]alibai a kan darasi
2. Ya ya malami ya kan taimaka wa ]alibi mai matsala ta musamman?
3. Yaya malami zai taimaki ]alibi mai matsala a gida?
4. Yaya sigar karatu cikin sauri take?

**TA{AITAWA**

- gabatar da darasi
- magana game da darasin baya
- gane matsalolin karatu, a jikin ]alibi da gidansu
- fa]a tsakanin uwa da uba a gida
  rashin cin abinci kan a zo makaranta,
  rashin gani sosai,
  in'ina,
  saurin baki,
  kaifin }wa}walwa.

**MANAZARTA**


Cohen, A. and Garner, N. (1963). *A Student Guide to Teaching Practice*. Hodder and stoughton.

Galadanci, M.K.M Et al (eds) (1978). *U.P.E. Hausa A Textbook of Methodology*, Zaria: N.N.RC.

Grant, M. (1960) *School Methods with Younger Children. A Handbook For Teacher in Africa.* Evans Brother Nigeria

Oxford University Press (1963). *Malamai a kan Littafin Hausa*. lbadan: OUP.

## KASHI NA 7: BITA

### GABATA RWA

Masana dabarun koyar da harshe sun ha]u a kan cewa }o}arin koyar da yadda za a yi magana da harshe shi ne farko kafin koyar da rubutu. Su `yan makaranta da za a koya wa wannan FASALI, na karatu da rubutu, ana tunanin cewa sun ]an san yadda za su yi mu'amula ta amfani da harshen Hausa. A kan wannan tunanin aka gina wannan FASALI na koyar da karatu da rubutu.

Koyon karatu da rubutu ba ya yiwuwa sai an bi wasu matakai daki-daki. Shi wannan FASALI an yi bayanin wa]annan matakan dalla- dalla, Wa]anda suka ha]a da:

– {a'idojin rubutu da amfaninsu;
– Rabe-raben kalmomi;
Haruffa (Ba}a}e da wasula);
– Awon fahimta da kuma;
– Karatun Sauri.

A cikin wannan kashin, za mu yi bita ne kan wa]annan da ma sauran abubuwan da suka shafi koyar da karatu da rubutu. Daga }arshe za a bayar da wasu ayyuka da kuma wata ta musamman wadda za ta ha]e duk sassan wanda ke cikin wannan FASALI.

### MANUFA

A }arshen wannan kashi, ana sa ran za ka:

(i) Zamato ka yi bitar duk muhimman abubuwan da wannan FASALI ya koyar; .
(ii) Iya kawo wasu daga cikin }a'idojin rubutu tare da bayanin yadda za ka koyar da su;
(iii) Iya kawo haruffan Hausa gaba ]ayansu (ba}a}e da wasula) tare da bayanin yadda za ka koyar da su;
(iv) Za ka iya fa]ar ma'anar awon fahimta tare da kawo bayanin yadda za ka koyar da ita.

### MATAKAN NAZARI

Nazari kan wannan kashin ba zai yiwu ba cikin sau}i in ba ka riga ka gama nazarin sauran kasusuwan da ke cikin wannan FASALI. Ba kuma yin nazarin ne kawai muhimmi ba, ana bu}atar ka aiwatar da duk ayyukan da aka ba ka da kuma amsa duk tambayoyin da aka yi maka a }arshen kowane kashi da ke cikin wannan FASALI.

Wannan FASALI ya shafi koyarwa da dabarun ta. Idan kana neman hanya mai sau}i ta nazarin wannan kashi, tare ma da duk sauran kasusuwa irin sa, to sai ka yi abu guda. Wannan abu guda kuwa shi ne ka }addara tsaye kake gaban yara ka na koyar da su domin ta haka ne kawai za ka iya tunanin ita kanta koyarwar da matsalolinta.

### SABABBIN KALMOMI

**Dabarun** koyarwa: Hanyoyi na koyarwa da aka samo su ta hanyar gwaje-gwaje da na nazarce-nazarce, kuma aka tabbatar da ingancinsu wajen inganta koyarwa ga malami da sau}a}a fahimta ga ]alibai.

**{a'idojin Rubutu:** Wasu sharu]]a ne da masana suka zayyana su a matsayin matakan bi wajen gabatar da wani abu a rubuce a cikin harshen Hausa. Sau da yawa in ba a kula da wa]annan sharu]]a wa]anda ake kira }a'idojin rubutu ba, sai ka ga rubutu bai ba da ma'anar da aka yi nufi ba.

### MATANI

Daga kashi na ]aya zuwa na tara an ambaci dabarun koyarwa da suka ha]a da:

– shifta
wal}ata-kati da kuma
– karanci-fa]i

Bayan an yi bayanin su dalla-dalla an kuma yi }o}arin gwada yadda za ka yi amfani da kowace hanya daga cikinsu wajen koyarwa, musamman wajen koyar da rabe-raben kalmomi, da koyar da haruffa, koyar da yadda fayyace manya da }ananan haruffan Hausa, da kuma koyar da awon fahimta da karatun sauri.

**AIKI I**
Kawo ma'anar wa]annan a matsayinsu na dabarun koyarwa:
1. Shifta
2. Wal}ata-kati
3. Karanci-fa]i
Yi bayanin yadda za ka yi amfani da shifta wajen koyar da awon fahinta.
{alailaicewa tsakanin haruffa, watau ba}a}e da wasula, da kuma tsakanin manya da }ananan ba}i na daga abubuwan dubawa na farko. Da zarar an nusasshe da yaro wa]annan abubuwa, mataki na gaba shi ne a ]ora a kan hakan ta hanyar koyar da karatun sauri, da awon fahimta da kuma bambancin da ke tsakanin su.
An ambata a kasusuwan da suka gabata cewa, koyar da rarraba kalmomi ma na da nasa muhimmancin. Daga ciki, a fannin akwai gyaran ma'ana a cikin rubutu da kuma sau}a}a karatun shi kansa. An kawo misalin da wa]annan:
yaga mata
ya gama ta
ya ga mata
Abin da aka ankarar da kai shi ne in aka ha]a kalmomi biyu ko fiye aka mayar da su abu ]aya to lallai sai ka ga ma'anarsu ma ta canza.

**AIKIN GIDA**
1. Kawo ma'anar wa]annan a matsayinsu na dabarun koyarwa
   shifta
   wal}ata-kati
   karanci-fa]i
2. Ta ya ya za ka yi amfani da kowace ]aya daga cikin wa]annan hanyoyin wajen koyar da haruffa da awon fahimta da kuma karatun sauri?

**TA{AITAWA**
- A wannan kashin, ka yi bita abubuwan da aka gabatar tun daga kashi na ]aya zuwa na tara da ke cikin wannan FASALIN.
- Bayan wannan ka sake }alailaice manya-manyan dabarun koyarwa guda uku da aka sake gabatarwa a wannan FASALIN. Dabarun koyarwar su ne:
  – shifta
    wal}ata-kati
  .- karanci-fa]i

**MANAZARTA**
Garba, A. (1991) *Sabuwar Hanyar Koyar da Hausa:* Kano, Triumph.
Institute of Education, ABU, Zaria (1979) *Karatu da Rubutu a Harshen Hausa.* Lagos: Thomas Nelson (Nig) Limited

## KASHI NA 8: DABARUN KOYAR DA HAUSA TARE DA KAYAN AIKI

### GABATARWA
A wannan kashi, za mu tattauna dabarun koyar da Hausa ta hanyar yin amfani da kayan aiki. Koyorwa ta hanyar yin amfani da kayan aiki ta fi kawo sau}in fahimta. Za a duba manyan rassan nazarin Hausa guda uku, a ga yadda dabarun amfani da kayan aiki ke taimakawa wajen sau}a}a fahimta.

### MANUFA
Manufar wannan darasi ita ce a nuna wa ]alibi wa]annan abubuwa dangane da koyar da Hausa ta hanyar yin amfani da kayan aiki:

a) akwai dabarun koyar da Hausa ta hanyar yin amfani da kayan aiki.

b) dabarun koyarwa da kayan aiki sun fi a koyar haka ba tare da wani taimako ba.

### MATAKAN NAZARI
Za a gabatar da kayan aiki, a kuma nuna maka yadda ake amfani da su wajen koyarwa.

i. Za ka yi dukkan ayyukan da aka ce a yi a wannan kashi.

### SABABBIN KALMOMI
[alibi zai san ma'anar wa]annan sababbin kalmomi kamar yadda ake amfani da su a fannonin nazarin Hausa daban-daban. Kalmomi su ne: fannin furuci; harda; hoto; kwali; murya; sauti (sautuka); tufafi; zahiri.

### RASSAN NAZARIN HAUSA
Hausa tana da manyan rassa na nazari guda uku. Rassan su ne, nahawu da adabi da al'adu. Kowanne daga cikin wa]annan manyan rassa, akwai dabarun yin nazarinsa ta hanyar yin amfani da wasu kayan aiki na koyarwa. Kayan aikin suna taimakawa wajen koyarwa don samun sau}i da kuma saurin fahimta. Abin lura a nan shi ne, kowane reshe yana da irin nasa kayan koyarwa Wa]anda suka fi dacewa da shi. Za mu ]auki wa]annan rassa ]aya bayan ]aya mu ga irin kayan koyarwar da kowane reshe yake amfani da su da kuma yadda ake amfani da su wajen koyarwar.

### KOYAR DA NAHAWU
Nahawu yana da nasa fannonin amma a nan za mu ]auki fannin furta sautuka mu ga yadda za a koyar da shi ta hanyar yin amfani da kayan aikin koyarwa na musamman. Za a yi amfani da kayan aiki iri biyu, wato rakoda da kwalaye }anana. Amfanin rakodar shi ne a ]auki muryar furucin dukkan sautukan Hausa, wato ba}a}e da wasulla. Amfanin kwalayen }anana shi ne a zana hoton dukkan sautukan Hausa a kan kwalayen. Kowane kwali zai ]auki hoton sauti guda ]aya kawai. Malami zai ba da muryar sauti guda don ]alibai su yi, sannan ya nuna musu kwali wanda yake ]auke da wannan sauti. Haka malami zai ci gaba da yi sai ya tattabar an yi muryar kowane sauti, an kuma ga hotansa a kwali. Babu shakka wannan hanya ta fi kowace hanya wajen sau}a}a fahimtar furucin sautukan Hausa da kuma gane yadda suke a rubuce.

### AIKI I
1. Rubuta sautuka guda 10 na Hausa wa]anda za a zana su a kan }ananan kwalaye don koyarwa.

### KOYAR DA ADABI
Adabi shi ma yana da nasa fannoni, amma a nan za mu ]auki fannin rubutattun wa}o}i mu ga yadda za a koyar da su ta hanyar yin amfani da kayan aikin koyarwa. Za a yi amfani da kayan aiki iri biyu, wato rakoda da takarda. Amfanin rakoda shi ne a sa mata kaset na wa}ar da ake so a koyar don ]alibai su yi ta. Amfanin rakoda shi ne a rubuta wa}ar a kan takarda don ]alibai su gan ta a rubuce. Malami zai sa wa ]alibai wa}ar su yi ta a rakoda a kalla sau uku. Daga nan, sai ya ba su wa}ar a rubuce a takarda. Wannan zai ba ]alibai damar hardace wa}ar, kuma yin nazarinta zai yi sauki ainun . Wannan hanya ta fi kowace hanya wajen sau}a}a fahimtar wa}a da hardace ta.

**KOYAR DA AL`ADU**

Al'ada ita ma tana da nata farnoni, amma a nan za mu ]auki al'adar da ta shafi tufafin Hausawa mu ga yadda za a koyar da ita ta hanyar yin amfani da kayan aikin koyarwa. Za a yi amfani da hotuna wajen gabatar da wannan darasi. Amfanin hoto shi ne ya taimaki ]alibi wajen fahimtar kowace tufa, ya kuma ba shi damar gane ta, ii wata rana ya ganta a zahiri. Malami zai nuna wa ]alibai hotunan tufafi in daban-daban, yana yi, yana yin bayani game da kowannensu.

Wannan zai ba ]alibai damar ri}e hotunan tufafin a zukatansu, ya kuma sa su shaida a duk inda suka gan su. Wannan hanya ta fi kowace hanya wajen sau}a}a fahimtar ire-iren tufafi musamman ma in tufafin ba za a iya kawo su ]alibai su gansu a zahiri ba.

**AIKI II**

Lissafa tufafin Hausawa guda 5 wa]anda ka ta~a ganin hotunansu

**AIKI III**

1. Rubuta sautuka guda 10 na Hausa Wa]anda za a zana su a kan }ananan kwalaye don koyarwa.

**AIKIN GIDA**

1. Tattauna amfanin hoto wajen koyar da fannin al'ada da ya shafi tufafin Hausawa.
2. Ta yaya arnfani da rakoda zai taimaka wajen koyar da rubutattun wa}o}in Hausa ga ]alibai?
3. Wa]anne ne manya-manyan rassa na nazarin Hausa?
4. Me ya sa hanyar yin arnfani da kayan aiki ta fi dacewa wajen koyar da ]alibai darussan Hausa'?
5. Mene ne amfanin rakoda wajen koyar da sautukan Hausa ga ]alibai?

**TA{AITAWA**

A wannan kashi ka koyi wa]annan abubuwa:

- manyan rassa na nazarin Hausa.
- fifikon yin amfani da kayan aiki wajen koyar da darussan

**MANAZARTA**


Gusau, S.M. ***Dabarun Nazarin Adabin Hausa.*** Kaduna: Fisbas Media Services.

Ningi, H. 1985. ***Jagorar Malaman Makarantun Firamare.*** Kano: Triumph Publishing Company.

Salim, B.A. 1985. ***Koyar Da Hausa A Makarantun Firamare.*** Kano: Triumph Publishing Company.

Zarruk, R.M. 1980 ***Siffofin Aikin Koyarwa*** lbadan. Oxford University Press.

**KASHI NA 9: AUNA FAHIMTA**

**GABATARWA**

Wannan abin da za ka karanta yanzu, wani sharhi ne a kan noma. Kila ma duk abin da aka fa]a an riga an san shi. Ma}asudin nazarin sharhin shi ne a tabbatar ]alibi na iya karanta wani jawabi kuma ya fahimci bayanin da ke cikinsa.

A yi nazarinsa a tsanake. Duk inda ake jin wata kalma ko jumla na da baki biyu, a sake bitar wurin a tsanake. Akwai tambayoyin da ake so a amsa daga }arshe.

**MANUFA**

A lokacin da ]alibi ya karanta wannan sharhi ya kamata a ce:

Ya fahimci abin da marubucin yake so ya sanar;

ii) Ya gane ma'anar kalmomin da suka fito a sharhin;

iii) Ya }ara da wasu sababbin kalmomi;

iv) Ya ga wani sabon salon da marubucin ya yi amfani da shi domin ya }awata rubutunsa

**MATAKAN NAZARI**

Ka karanta sharhin a tsanake.

Ka yi amfani da }amus ka gane ma'anar duk wata ba}uwar kalma.

Kada ka }addara cewa an fahimci abin da ake nufi don kawai an son yadda ake yin noma.

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Zaunanne | dahir |
| Mangala - | abin ]aukar kaya na jaki |
| Sassabe- | sare }armo |
| Birne - | bizne "shuka tun kafin ruwa |
| Bazara- | lokacin zafi |

**MATANI**

Karanta labarin nan ka amsa tambayoyin da ke bayansa.

**NOMA**

Na du}e tsohon ciniki,
Kowa ya zo duniya,
Kai ya tarar.

Galibin Hausawa manoma ne, ko suna zaune a birni ko kuma a }auye. Zuwa gona abu ne zaunanne ko da rani balle kuma da damuna.

Da rani ana kai taki gona shi takin nan shara ce daga gida ta }azanta, misali toka daga murhu da kuma kashin dabbobi wa]anda suke a gida. Wa]annan dabbobi su ne kamar su dawaki da jakai da tumaki da awaki. Manomi Zai labta wa jakinsa mangala cike da taki wani lokaci har shi kansa ya ]auka a ka, ya kai gonarsa. Idan kuma mai yara ne zai sa yaran nasa su raka shi, ko kuma su su je, shi kuma ya tsaya a gida ya yi wani aikin.

An tsakuro wannan darasi ne daga littafin Mu Fara Karatu, littafi na biyar, na Liman Muhammad daga shafi na I zuwa na 2.

Ana zuba taki daga gefen gona a kwari, ba a game gona duka. Duk lokacin da aka zo gona, ba za a a zubar da takin a kwari ba. A'a za a ]an baza da kara a gona a yi ‘yan gyarc-gyare wasu masu garka wani abu daban da za su je garkar su gyare shinge, da sauran abubuwan da suka kamata. Banda yan gyare-gyare na yau da kullum, manoma suna gyara wanda ya shafi gona baki ]aya. Wannan gyara shi ne shara da sassabe wanda ya shafi kowa idan lokaci ya yi.

Wannan lokaci shi ne watan bakwai. A cikin wannan wata ne na bazara, ake ganin alamun damuna. Za a cika zafin rana, kuma a fara ganin giza-gizai. To, idan manoma sun yi lissafi sun ga damina ta }arato, sai su tara shin i dominta.

Manoma suna tanadi kafin damana ta fadi. Tun daga kakar bara, za a fitar da gero, da dawa da wake da gyada da masara Wa]anda suka dace, a adana don biyan wannan bukata. Wani lokaci ma'aikatar gona za ta raba wani takin wanda ita kanta ta tanada. Banda in kuma masu zarafi za su nemi takin zamani irin wanda gwamnati take saidawa a buhuna.
Idan (damina ta fadi, wato an yi ruwan sama kamar biyu ko sau uku, kuma ana ganin alamu, watakila za a ci gaba da ruwa, sai manoma duka su fita gona domin shuka. Ana yin shuka ko da ruwa bai samu ba amma ana ganin lokacin samuwarsa ya yi. Wannan in shuka cikin rani ita ake kira birne.
Da zarar ruwa ya samu, kuma shuka ta zauna sai manomi ya ci gaba da tattaka gonarsa. A galibin }asar Hausa an fi shuka gero, da dawa da masara da gya]a da wake da auduga.
Gero da dawa suna bukatar shuka mai kyau, kuma mai tsafta. Wato, a yi sari mai kyau, kuma mai zurfi wajen-shuka kuma a rufe da kyau. Idan shuka ta fito ta rabu da }asa sai a shiga noman farko,wato noman cira. A wannan noman ne za a bugi gindin shukar ya saki. Daga nan kuma sai a za~i tsiro kamar hu]u ko biyar daga cikin shukar ta rami guda, a cire sauran a zubar. A ci gaba ana nome haki ana yi wa shuka ta kowane rani haka, har sai an gama gona.
Ana kuma cikin noma ne irin haka ake baje takin da aka kawo da rani, da zuba na zamani, takin buhu Da an gama wannan a gona, babu sauran wani muhimmin aiki kuma sai maimai.
Ana fara maimai lokacin da in manomi ya du}a zai ~ace a cikin gona wato shuka ta yi 'gaban doki ke nan . A Maimai kuma, ana nome hakin gona, a sassauta kewayen shuka, kuma a tara }asa a }ar}ashin shuka

## AIKI NA I

1. Mene ne ya sa ake yi wa noma kirari da cewa "tsohon ciniki?"
2. Su wane ne ke kai taki gona?
3. Mene ne ake yi idan an kai taki gona?
4. Daga ma manomi ke samun in?
5. Saboda me ake yin birne?

## AIKIN GIDA

1. Me ake nufi da bazara a labarin nan?
2. Zayyanna yadda manomi ke kula da gonarsa daga zuba taki zuwa maimai.

## TA{AITAWA

Galibin dukkan Hausawa suna noma, suna kuma amfani da taki iri biyu. Idan har watan bakwai ya yi ba a fara ruwa ba manoma kan yi birne. Gero da dawa da masara da gya]a da auduga su ne abin da Hausawa suka fi shukawa.
Ma yi wa shuka noma iri biyu.

## MANAZARTA

Muhammed, L.(1985) ***Mu fara Karatu, Littafi na biyar:*** Lagos; Longman, Nig.

**KASHI NA 10: KOYON MAGANA DA KARATU**

**GABATARWA**

Magana da karatu abokan juna ne. Magana ce ake rubutawa ta zama karatu. Idan aka karanta karatu ya zama magana. Koyon magana da karatu suna da matakai kamar haka:

(a) gaisuwa;
(b) sunayen sassan jiki;
(c) sunayen abubuwan kusa;
(d) Sunayen abubuwan nesa;

Ta fuskar karatu kuwa, dole sai an kiyaye abubuwa kamar haka:

(a) Ba}a}e da wasulla
(b) tafiyar ba}a}e da wasulla
(c) ha]uwar kalmomi
(d) tayar da jumla mai ma'ana.

Idan ka kula, magana da karatu abu ]aya ne, abin da ya bambanta su rubutu. Zai fi kyau a ce, sai an iya magana kana a iya karatu.

Yadda tsarin wannan kashin yake shi ne, abubuwa uku su tafi bi da bi kamar haka:

(i) koyon magana.
(ii) koyon rubutu.
(iii) koyon karatu.

Bi a hankali ka ga yadda abubuwan ke tafiya a karatun Hausa. Ka tuna kowanenmu sai ya fara magana kana ya koyi rubutu idan yana son ya }ware a karatu.

**MANUFA**

Kashin ya shafi yadda ake koyon magana da karatu, don haka manufa ita ce:

(i) A kiyaye muhallin kowace irin magana.
(ii) Fahimtar tsarin gaisuwa da yadda ake yin ta.
(iii) Fayyace sunayen abubuwa da Hausa.
(iv) Sanin yadda za a ha]a sunaye a yi magana.
(v) Tsara magana a rubuce a karanta ta.
(iv) Yadda za a yi karatu mai ma'ana sosai.

**MATAKAN NAZARI**

(i) Koyar da magana ta hanyar farawa da gaisuwa.
(ii) Koyar da sunayen abubuwa da saninsu a ido.
(iii) Tsara jumloli da sunaye domin magana.
(iv) Fito da wasu sautuka masu matsala da yadda ake karanta su.
(v) Koyon rubutun abin da aka sani da karanta shi.

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Rubutu: | hanyar sadarwa ta amfani da alkalami da takarda. |
| Karatu: | fa]ar abin da aka rubuta da fahimtarsa |
| Sautuka: | ba}a}en Hausa kamar \b\ \t\ \d\ \n\ |
| Wasula: | sautukan da ba ba}a}e ba irin \a\ \u\ \i\ /e\ |
| Tagwaye: | ha]a]]un ba}a}e ko wasula kamar \kw\ \an\ |
| Magana: | sadarwa ta hanyar furuci |
| Koyo: | }o}arin fahimtar abu da yin sa. |
| Kwai kwayo: | yin abu ta kallon mai yin sa. |
| Alkalami: | abin da ake rubutu da shi a kan takarda. |

Sauran kalmomi da za ka ci karo da su ka nemi }amus don }arin bayanni.

**GAISUWA**

Gaisuwa ta kasu daban-daban. Akwai ta asuba da rana da wuni da kuma ta dare. Akwai ta aiki da ta godiya da ta ta'aziyya da ta jaje. Ga yadda tsarinsu yake.

yanayi; Barka da Asuba Barka da Rana Barka da Yamma
**AIKI**: Sannu da aiki! Ina gajiya?
Allah Ya taimaka!
**GODIYA**: Sannu da }o}ari!
A gaishe ka da ]awainiya! Na gode }warai da gaske! Sannu da fama!
**TA'AZIYYA**: Yaya aka ji da rashi?
Allah ya gafarta masa. Allah ya ba ku ladar jinya. Allah ya kar~i ba}uncinsa. Allah ya sa ya huta.
**JAJE**: Allah ya tsayar nan.
Allah ya ba da sabon arziki. Allah ya sa ya zama kaffara. Allah ya da]a arziki.
**MARAS LAFIYA**: Yaya jiki?
Allah ya kawo sau}i. Allah ya ]auke wahala Allah ya tada kafada.

**AIKI NA I**

1. Rubuta gaisuwa uku na yannayi.
2. Ambaci gaisuwa uku na ta'aziyya.
3. Rubuta gaisuwa uku na jaje.

**DA KAI DA JIKINKA**
yanzu sa natsuwa ka dubi sunayen wa]annan abubuwa na jikinka ]aya bayan ]aya ka gani.
Gashi/suma Furfura
Saje
Gemu
RUKUNI NA [AYA
(GASHI)
Gashin baki;
Hana }arya;
Gira
Kai
Goshi
Ha~a
RUKUNI NA BIYU (GABBAI)
Le~e
Kunne
Baki
Ido
Ha}ora
Harshe
Hanci
Hannu
{afa
Yatsa
RUKUNI NA UKU (GA||AI)
Dubura
Zakari
Farji
RUKUNI NA HU[U
(GA||AI)
Cibi
Maraina
Cinya
RUKUNI NA BIYAR
(AL' AURA) Duwawu

**AIKI NA II**

1. Rubuta sunayen gashi uku na mutum
2. Rubuta sunayen ga~~ai uku naka.
3. Rubuta sunayen al'aura uku.

yanzu sai ka kiyaye da sunayen abubuwan da ke cikin gida duka. Dubi wa]annan ka gani.
[aki

Zaure
Soro
Gado
matashi
shinfi]a
murhu
faifai
kwarya
tukunya

adda
gatari
fartanya
lauje
wu}a

doki
ra}umi

akuya
jaki

RUKUNI NA [AYA
(WURIN SHIGA)

RUKUNI NA BIYU
(WURIN KWANCIYA)

RUKUNI NA UKU
(ABUBUWAN GIRKI)

RUKUNI NA HU[U
(MAKAMI)

RUKUNI N BIYAR
(dabbobi)

AIKI NA III

1. Rubuta sunayen dabbobi uku
2. Rubuta sunayen kayan girki biyu
3. Rubuta sunayen makamai uku.

KOYON KARATU

yanzu sai ka kula da zubin ba}a}e da wasula yadda suke tafiya kamar haka: Ba}a}e:
B C D F G H J K L M N R
S T W Y Z.
Wasula: A I E O U
Tagwayen Ba}a}e: gw, kw, ky, }y, fy, gy
Ba}a}e masu }ugiya: }, ], ~
Tagwayen Wasula: ai, au

Ha]a wasali da ba}a}e:
da bi bo bu be Ca ci co cu Ce da di do du de fa fi fo fu fe
ga gi go gu ge.
Rubuta kalma:
Baba Caca Delu Musa Mari
Rubuta kalmomi da tagwayen ba}a}e:
Gwari Gyacia Kyaw, Kwano, Fyata, {yashi
Rubuta kalmomi da tagwayen wasula: Audu
Aiki
Rubuta kalmomi da ba}a}e masu }ugiya
~arawo
]ari
}yaure

Rubutun jumla:

Baba ya zo
Mama ta tashi
Malam ya rubuta
Mun karanta da Malam.

**AIKIN GIDA**

1. Rubuta ba}a}e masu }ugiya
2. Rubuta tagwayen wasula
3. Rubuta tagwayen ba}a}e uku
4. Rubuta jumlori uku

**TA{AITAWA**

Mun fahimci sunayen sassan jiki
Mun ga sunayen kayan aikin gida
Kwaikwayon rubutu da ba}a}e da wasula kwaikwayon karatun jumloli

**MANAZARTA.**

Ahned, M.B.M. (1972) *Sabuwar Hanyar Koyon Harshen Hausa da Al'adun Hausawa*, CSNL. Kano

Bunza , A.M. (1998) *Hausa a Saukake don Makarantun firamare*, Books 1-6, Hudahuda, Zaria.

Bunza, A.M. (1999) *Nahawun Rubutu. Jagoran Ka'idojin Rubutun Hausa*, ANLAT (Sokoto, Kebbi & Zamfara Branch) Sokoto.

SAIIM, B.A. *(1985) Koyar Da karatu A Makarantun Firamare*, Triumph, Kano

## KASHI NA 11: KOYAR DA BA DA LABARI DA KACICI-KACICI

**GABATARWA**

Natsuwa da kwantar da hankali tagwaye ne. Kowane lokaci aka sami natsuwa hankali kwance yake. A duk lokacin da hankali ya tashi babu natsuwa. Hausawa sun ce" aiki da hankali ya fi aiki da agogo." Don haka ne, masu karin magana suka ce "ido mudu ne ko bai ci ba ya san abin da ke cika masa tumbi". A koyaushe ka kiyaye da fa]ar tsofaffi cewa, "hankali ke gani ba ido ha." Idan ka ji wani na magana ka saurare shi ka ban i sai ya kare kayi bambaya ga abin da ba ka gane ba. Ka kiyaye sosai, ba a tambaya cikin tambaya, kuma ba a ba da amsa ga abin da ba a tambaya ba.

Idan za ka ba da labari ko za ka yi tatsuniya, ka bar za}ewa. Ka dinga fa]ar kamar yadda aka ce, ko kamar yadda na ji.." Babu tabbas ga abin da ba ka da ha}i}aninsa. Haka kuma yawan surutu na sa a yi }arya. Yawan kawaici wata alama ce ta ta~uwar hankali. Dariya da murmushi kwalliya ce ga mutum, idan suka yi yawa sukan wautar da mai su.

Mai ba da labari ba ya gaggawa, mai saurare kuma ba ya magana. Idan ba ka kiyaye da hakalinka samun natsuwa hankalin ka kuwa ya kwanta.

**MANUFA.**

Manufar wannan kashi ita ce, fito maka da̩wasu manyan rassan ababen rayuwa biyu: Magana da fahimta mai yin magana kuma ka fahimci magana ka iya zaman duniya ke nan.

(i) ka iya bayar da labari da kanka.
(ii) ka san yadda ake ba da labari.
(iii) ka fahimci yadda ake sauraron labari.
(iv) ka bambanta labari da tatsuniya da kacici-kacici.
(v) ka lura da kashe-kashen kacici-kacici.

**MATAKAN NAZAARI**

(i) ka sa natsuwa idan kana sauraren labari.
(ii) ka dinga rubuta kalmomi da ba ka fahimta ba.
(iii) ka dinga lura da darussan da ke cikin labari.
(iv) ka kiyaye sunayen da ke cikin labari.
(v) ka fahimci gaskiyar labari da }aryarsa.
(vi) ka ri}a kula a kan wa ake ba da labari.
(vii) ka dinga lura da tambayoyin kacici-kacici.

**SABABBIN KALMOMI**

| | |
|---|---|
| Natsuwa: | rashin rigima |
| Hankali: | lura da ganewa da aiki da su |
| Labari: | bayanin wani abu ]aya |
| Tatsuniya: | }ir}irarrun labaran gargajiya. |
| Kacici-kacici: | tambayoyin cikin tatsuniya da raha. |

| | |
|---|---|
| Fahimta: | ganewa |
| Ta~uwar hankali: | hauka |
| Surutu: | yawan magana a kai a kai. |
| Dariya: | nuna fara'a da washe baki da ha}ora tare da sauti |
| Murmushi: | da]i da gyara baki na shirin dariya ba a kuma yi dariyar ba. |

**BAKI MAI [AURE WUYA**

Wani maigadin gidan Bature ne, mai yawan surutun wofi da neman a san shi, ga shi ba turanci yake ji ba, amma a koyaushe sai ya cika bature da surutun banza.

Wata rana, tun da asuba ya je gidan Bature da Bature ya fito suna labari sai ya ce. jiya na yi mafarkin an }ara maka girma" kai tsaye Bature ya shiga gida ya rubuta takardar sallaman aiki ya ba maigadi. Maigadin na ganin shi da ya cancanci a ba shi kyauta kan albishir da ya yi wa Bature kuma sai a kore shi. Ya tafi gida, ya kai }ara ga manya domin a shiga ciki a agyara abin.

Da aka nemi bayani daga Bature ya ce: "wanda aka ]auka aikin gadi wane lokaci gare shi na yin barci har

da mafarkai? " Ai wannan ya nuna barcinsa kawai yake yi. Don haka dole a kore shi. Da jama'a suka ji haka, suka dinga fa]ar cewa, lallai haka yake; Hausawa sun ce; baki mai ]aure wuya.

**A**IKI

1. Wa ake yi wa gadi?
2. Mene ne maigadi ya yi mafarki?
3. - Wane sakamako aka yi wa labarinsa?

**DA TSOHON ZUMA AKE MAGANI**

Wata rana na tafi wani }auye ziyarar `yan'uwa. Bayan da aka ci abinci da dare sai muka tattara a kofar dakin wata tsohuwa tukuf. Tsohuwar nan ta dinga yi mana tatsuniya wai mu ba da amsa; Daga cikinsu nakan tuna irin su.

(a) Icce gidanmu inuwa gidan wasu?
Amsa-

(b) Ga fili babu yan kokuwa
amsa-

(c) `yan matan gidanmu kullum wanka?
Amsa ...................................

(d) cinkiskis! A cikin cikis!
Amsa-

(e) Ma saye abin da ba shi da riba?
Amsa ...............................

(f) yan matan gidanmu farfarun baki gare su?

Amsa. ................................

(g) kamar mutum daga nesa?
Amsa .................................

(h) Na la~e ba ka shigowa?
amsa..............................

**AIKI II**

1. Me sunan irin wannan tatsuniyar?
2. Da wane lokaci ne aka yi tatsuniyar?
3. Ba da amsoshin tatsuniyar.

**IN KAI NE MENE ZA KA Yl?**

Karanci wa]annan abubuwa ka nuna ra'ayinka.

Ka hau icen goruba sai zaninka ya fa]o }asa ka zama tsirara. A }asa ka hango surikinka,' a sama ga }aton kumurci ya doshe ka. Idan kai ne yaya za ka yi?

**WA YA Fl RU[EWA?**

Wasu mutane hu]u ne fatake, yunwa ta koro su suka je wani gida aka yi masu masauki suna fara salla, sai aka turo yaro da abinci. Da yaron ya zo ya tarar suna salla ba zancen magana sai ladan ya ce aje nan". Mamu ]aya ya ce: idan ana salla ba a magana. ]aya ya ce: Liman ka]ai ne bai ce uffan ba. Liman ya ce . In yi magana sakarai ne ni? Wa ya fi wauta a cikinsu?

**AIKIN GIDA**

1. Mene ne ya sa baki ke ]aure wuya?
2. Wane ne surukin mutum?

**TA{AITAWA**

- Yawan surutu ba ya da amfani ga yaro.
- Azar~a~in fadar magana na kai ga da-na-sani.
- tsofaffi ke yi wa yaro tatsuniya da dare
- Wajibi ne matafiyi ya tanadi guzurin abinci

**MANAZARTA:**

Alhassan H. Musa 1(1980) *Koyon Magana do Fahimta: Zariya.*
Bunza, A.M. (1999) *Baki Abin Magana, ANLAT (Sokoto, Kebbi & Zamfara Branch), Sokoto govt. Press.*

## KASHI NA 12: RARRABA KALMOMI AJI-AJI TA HANYAR AMFANI DA KATUTTUKA

### GABATARWA
Muhimmancin rarraba kalmomi na da yawa. Daga ciki, mun ji cewa akwai gyara ma'ana da kuma sau}a}a karatu. Su kansu kalmomin sun rabu aji-aji. Dalili shi ne ita kalma lafazi ce da ake ba dun}ulalliyar ma'ana. Idan kuwa kamar a rubuce take to dole a nuna ta ta hanyar barin fili a tsakankanin kalma da kalma. Misali:-

| Bello | ya | sa | tabarau | fuska |
|---|---|---|---|---|
| | 2 | 3 | 4 | |

A wannan jumla, akwai kalmomi mabambanta kamar guda shida. Idan an lura an bar fili a tsakanin kowace ]aya daga cikin kalmomi. Wa]annan kalmomi ana iya rarraba su zuwa aji-aji. Ma'ana, kowace kalma da aji nata na kanta. Wa]annan ajujuwa su ne:

Suna
Aikatau
Wakilin suna
Bayanau da sauransu

A wannan kashin, za mu yi nazarin yadda za a iya rarraba kalmomi domin zuzzuba su zuwa aji-aji. Azuzuwa hu]u kawai za mu tattauna.

### MANUFA
A }arshen wannan darasin, ana sa ran za ka iya:

i) Fa]ar azuzuwan kalmomi guda hu]u;
ii) Fa]in ma'anar kowane aji na kalmomi;
iii) fayyace bambancin da ke akwai tsakanin azuzuwan kalmomi;.
iv) kawo jumla tare da fa]in ajin da kowace kalma take a cikin jumlar.

### MATAKAN NAZARI
Kafin ka tsunduma cikin wannan kashin akwai bu}atar ka tanadi takardu guda hu]u. A kan kowace takarda, sai ka rubuta ]aya daga cikin wa]annan azuzuwa

Suna
Aikatau
Wakilin suna
Bayannau

Wa]annan takardu za su yi maka amfani ne wajen gabatar da ayyukan da za a nemi ka yi a nan gaba.

### SABABBIN KALMOMI
**Suna:** Lafazin da ake kiran ko ambaton mutum, ko abu ko wuri, ko wani abu wanda za a iya gani da wanda ba za a iya gani ba, mai rai da kuma maras rai.

**Aikatau:** kalma ce mai nuna aiki a cikin jumla.

Wakilin suna: Kalma ce mai zama a maimakon suna. Wato tana wakiltar suna.

**Bayanau:** Kalma ce a cikin jumla mai }ara haske a kan aikatau. Watau tana }ara bayanni a kan irin aikin da a ka ambata a cikin jumlar.

### AZUZUWAN MALMOMI
Kodayake akwai azuzuwan kalmomi masu yawa a Hausa. A wannan kashin za mu duba guda hu]u ne kawai, saboda su ne muhimmai, kamar yadda aka yi bayanni a baya. Kowace kalma akwai aji na ta da za ta iyà fa]awa a ciki. Ga bayanni nan a kan kowane ]aya cikin azuzuwan hu]u:

i) Suna: kamar yadda aka yi bayani a baya, 'suna ' kalma ce mai nuna yadda ake ambaton abu, ko mutum, ko wani abu watau ko ma mene ne. Misali, Kabiru, bishiya, kaza da sauransu, shi kansa 'suna' ya kasu kashi-kashi.

   Daga cikinsu akwai sunan yanka, da suna gama-gari.

   Sunan yankai shi ne kamar su Usman da Bilki da Kaduna da Jamus da sauransu. Suna gama-gari shi ne kamar ire-iren abubuwa na yau da kullum kamar agogo da gida, jaka da sauransu.

ii) Wakilin suna: A matsayinsa na aji na musamman, wakilin suna na wakiltar suna ne domin

gujewa mai-mai da rashin ma'ana. Abin nufi shi ne, ana yin amfani da'shi a mai makon suna.

Ga ire-iren misalansu:

'Shi a mai makon Bashir "Ita" a maimakon Binta

'Su" a maimakon `yan makaraata "Ni" a maimakon ni kai na "Mu" a maimakon ni da wasu "ku" a maimakon kai da wasu "kai" a maimakon kai kanka da sauransu.

iii) Aikatau: Duk wani abu da aka aikata ko za a aikata, ko kuma ake aikatawa a cikin jumla ana nuna shi ne a cikin aikatau:

Kabiru ya cinye tuwo.

Garu ya fa]i kasa.

Audu ya tayawo.

Ire-iren kalmomi da aka ja layi a }ar}ashinsu su ne aikatau.

Bayannau: kalma ce mai nuna }ara haske a kan aikatau. Misali -

Bello ya sa tabarau a fuska

Garu ya fadi a }asa

Bala ya dawo jiya

Ire-iren kalmomin da aka ja layi a }ar}ashinsu su ne bayanau

A duk lokacin da mutum zai koyar da rarraba kalmomi ta hanyar amfani da kati, to ya kamata ya ware kalmomi zuwa aji-aji kafin ya tantance azuzuwan da zai koyar.

b) ya kamata mutum ya rubuta kalma ya kuma rubuta sunan ajinta a ta}aice a kan kati.

Yin haka zai sa a sami misalai kwatankwacin haka

| shiga | Karaga | Kusa | }an}ane |
|---|---|---|---|
| AK | SN | Byn | sf |

| | | | |
|---|---|---|---|
| Shi / ita | Ak | = | Aikatau |
| Ws | Sn | = | Suna |
| | Byn | = | bayanau |
| | Sf | | sifa |
| | Ws | | wakilin suna |

bin wannan bayani da alamtawa, zai taimaka wa ]alibi wajen ri}e abin da ya koya a zuci

**AIKI I**

Wata}ila a yannzu ka riga ka tanadi katuttukan da aka bu}aci ka tanada.

i) Yi amfani da katuttukan wajen ware kalmomin da za su iya shiga }ar}ashin kowane aji. Misali, kowane kati sai ka ba shi lamba kamar haka:

| | |
|---|---|
| suna | 1 |
| wakilin suna | 2 |
| aikatau | 3 |
| bayannau | 4 |

ii) Rubuta jumloli masu yawa kamar guda goma. Yi amfani da katuttukan da ka tanada domin ka ware kalmomin da ke cikin kowace jumla zuwa azuzuwan da suka dace.

**AIKI II**

Yi ko}ari rubuta da kuma fahimtar rna'anomin wa]annan kalmomi:

Suna

Wakilin suna

Aikatau

Bayannau

Ka tabbatar ka duba manazarta da aka ambata domin la}antar ma'anoninsu . Ka sake bitar darussan da wannan kashin ya kawo dalla-dalla

**AIKIN GIDA**

1. Ina dangantakar Suna da Wakilin Suna
2. Mene ne ka fahimta da Aikatau?
3. Mene ne aikin Bayanau?
4. Ta yaya ake tantance ma'anar kalma a rubuce?

**TA{AITAWA**

- A wannan kashin, ya kamata a ce ka fahimci azuzuwa hu]u na kalmomi
- ka san ma'anar kowane aji;
- Za ka iya fayyace bambancin da ke tsakanin azuzuwa na kalmomi
- Za ka iya kawo jumla tare da fayyace matsayin kowace kalma da ajinta.

**MANAZARTA**

Yahaya, I.Y., Zariya, M.S., Gusau, S.M. Yar'aduwa, I.M. (1992)Darussan *Hausa 2: Don Manyan Makarantun Sakandare* Ibadan: University Press PK.

## FASALI NA 9: AIKIN FASSARA

## KASHI NA 1: AIKIN FASSARA

### GABATARWA
Aikin fassara wani babban aiki ne a fannin nazarin harshe. Hausa na daga cikin manyan harsunan Afirka da ke da wadatattun kalmomin da ke isar da sa}o wajen fassara wani matani zuwa harshen Hausa. Abin da ake nufi da fassara shi ne juya ma'anar abu daga wani harshe zuwa wani.
Ya kyautu a Kula da cewa, Ba haka kawai a ke fassara babu dabaru Ba. Masana fassara sun karkasa fassara zuwa gida uku : dole ne mai fassara ya kiyaye su kamar haka:
(1) fassara mai `yanci;
(2) fassara nan take;
(3) fassara ba}i da ba}i.
Domin kai ga burin bayyana wa]annan abubuwa, za mu kasa matanonin gida-gida. Na farko, za mu ba da }arfi ga yadda za a yi aikin fassaran kansa, kana mu yi }o}arin gwada aikin a bayyanne.

### MANUFA
(i) Fito da ma'anar fassara daki-daki.
(ii) Bayyanna rabe-raben fassara.
(iii) Gabatar da yadda ake fassara.
(v) Fito da ratsin al'ada cikin fassara.

### MATAKAN NAZARI
(i) ka rika kula da kalmomin da ake fassarawa.
(ii) ka lura da yadda aka fassara su.
(iii) ka kula da yadda tsarin matanonin fassara yake.
(iv) ka lura da }a'idojin fassara da aikin fassara

### SABABBIN KALMOMI
Fassara: Juya ma'ana daga wani harshe zuwa wani.
Matani: Ainihin abin da za a fassara.
Al'ada: ]abi'an mutane na rayuwarsu.
`yanci: damar yin walwala da sakewa.
Take: zama ]aya
Asaii: tushen abu
Harshe: yaren da ake magna da shi

### FASSARA DA RABE-RABENTA
Fassara ita ce juya ma'anar wani harshe zuwa wani harshe. Dabarun da ake bi wajen aiwatar da aikin fassara su ne kashe-kashen ta. Ga dabarun kamar haka:
(a) fassara mai `yannci
(b) fassara ba}i da ba}i
(c) fassara nan take.

### FASSARA MAI `YANCI
Wannan ita ce fassara da za ta ba mai fassara `yancin yin duk wata dabara da yake da ita domin isar da sako. Ita ce fassara da ta fi kar~uwa kuma ta fi dacewa a yi. Fassara mai ‘yannci za ta bai wa mai fassara dammar sadar da sa}onsa cikin wani salo na daban. Ga misali kamar haka:

English:

1. I saw your father (Na ha]ui da babanka)
2. Too late to cry when the head is cut. (Ihu bayan hari)
3. It rained cats and dogs. (An yi ruwa kamar da bakin }warya)

Arabic:

4. Lassai kabaru kal iyanni (gani ya kori ji)

Izaa jaa'a ma labudda minhu famarhaba (kibiyar da ba ta kure gaba ake ba ta)

**FASSARAR BA{I DA BA{I**

Ita ce fassarar da za a bi ba}i da ba}i ana fassara. Bin wannan fassarar ba ta da burgewa da isar da sa}o kai tsaye.

Tana cike da matsaloli da cikas ga mai fassara da masu karatu. Ga ka]an daga cikin misalanta:

English 1. Black market Hausa: ba}ar kasuwa
2. Stomach trouble jidalin ciki
3. Father's father uban uba
4. My wife's father uban matata.

Idan an lura an yi fassara kai tsaye ta fuskar bin ba}i da ba}i. Da ba a bi ba}i da ba}i ba, da sai a ce:

1. kasuwar bayan fage
2. ciwon ciki
3. kakana
4. surukina.

**FASSARAR NAN TAKE**

Wannan fassarar ita ce irin ta `yan gidan rediyo da ake yi kai tsaye ana jawabi suna fassarar. Haka kuma, takan kasance irin fassarar malaman zaure idan ana karantun sani ko tafsiri. Fassara ce da za ka ji ana yi ana }ir}ire jumloli ba ma'ana cikakkiya. Irin wannan fassarar ita ce:

English

1. I thank all of you: na godewa kowanenku
2. On the job well done: ga aikin }warai da aka yi

Arabic:

1. wa in kuntum: kun kasance.
2. fi rai bin: cikin shakka.

**AIKI I**

1. Mene ne fassara?
2. Rabe-raben fassara nawa ka sani?
3. Fassara wa]annan kalmomi:

English

a. in totality -
b. far above -

Arabic:

c. kunfayakunu -
d. raujarribun -

**DABARUN FASSARA**

Baya ga matakai uku da muka ambata na fassara akwai wasu abubuwan da ake son mai fassara ya yi. Mai fassara yana da damar ya Hausantar da kalma kai tsaye ko ya al'adantar da ita ta buwaya.

A nan yana iya ya kushe duk abin da ke ga matani ya fa]i abin da ya ga cewa zai ba da ma'ana wadatacciya. Haka ba za ta kasance ba, dole sai mai fassara ya }oshi da harsunan biyu. Abin nufi shi ne, ya }ware a harshen fassara da wanda ake fassarawa, Dubi wa]anan misalan ka gani:

English

1. United Nations: Majalisar [inkin Duniya
2. Speaker of the house: kakakin majalisa
3. Ghost: fatalwa

Arabic:

Majus· Bamaguje
Mushrik: Arne
Fasik: Shawaraki

Idan kuwa za a Hausantar ne kai tsaye ga yadda abin ke kasancewa:

English
1. Fan: fanka
2. motor: Mota
Arabic:
1. Zakat: zakka
2. Hajj: Hajji.

**AIKI II**
1. Mene ne ake bukata ga mai fassara?.
2. Fa]i dabaru biyu na fassara.
3. Fassara wa]annan kalmomi
Telephone, master

**AIKIN GIDA**
1. Fassara wannan zuwa Hausa:
I am sorry for not being able to help you over the issue. However, you must be very careful and honest in all your dealings. I advice you to be very obedient to your parents and respect your teachers.
2. Fassara wannan zuwa Turanci:
KoyaushE:. ka shirya wa abin da kake da niyyar yi gobe. Bari aiki ya yi ma girshi rikis! Shi ke hana aiki kyau. Yawan alfahari da nuna iyawa na ~ata aikin ma 'aikaci.
3. Fassara wannan zuwa Hausa: . Bismillahir rahamanir rahim. A'uzu billahi minash shaidanir rajim. Alhamdu lillahi Rabbil alamin.

**TA{AITAWA**
A bayannan da suka gabata an yi zancen:
- ma'anar fassara
- rabe-raben fassara
- ayyukan fassara
- dabarun fassara
- Yadda ake fassara.

**MANAZARTA:**

Ahmed, U.B. (1978) *A. School Certificate Hausa Course,* NNPC Zaria.
*Hanyoyinta da Matsaiolinta* BUK, Kano.
Rufa'I A. (1983) *Some Aspects of Translating CSNL.* B.U.K.
Yakasai, A&Malunfashi (1996) *Translations: Introductory guide,* FISBAS, Kaduna. CSNL. *Fassara:*

**KASHI NA 2: KOYAR DA YADDA [ALIBAI ZA SU GABATAR DA JAWABI A RUBUCE DA KA**

**GABATARWA**

An dai san cewa ]an Adam baya rayuwa shi ka]ai, dole sai da wani ]an Adam a tare da shi . A sanadiyyar haka ne ake samun cu]anya da ma'arnaloli dabam-dabam a tsakanin al'umma.

Tun da yake al'umma ta kafu ai dole ne a samu wasu su zama shugabanni wasu kuma su zama mabiya.

Dangane da jawabi, a duk lokacin da wani ya tashi zai yi jawabi a lokacin da ake saurarensa, to shi ne shugaba a wannan lokacin. Shi jawabi wani abu ne da ya samo asali tun zamanin da can.

Jawabi zai iya kasuwa kashi biyu, da wanda za a iya aiwatarwa a magance da kuma wanda za a aiwatar a rubuce. Za a ga wannan a wajen matani a nan gaba. Sai dai kada a manta, jawabi a magance shi ne ya fi asali.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashin za a iya:

1. gane jawabai iri biyu da na baka da na rubuce.
2. gane rukunan da akan bi wajen rubuta jawabi
3. gane amfanin alamomin rubutu a wajen rubuta jawabi
4. rubuta jawabi ba tare da matsala ba

**MATAKAN NAZARI**

1. Za a nemo wani jawabi da aka rubuta a nazarce shi da kyau
2. A yi la'akari da alamomin rubutu idan an zo rubuta jawabi
3. A kwatanta rubuta jawabi kan wani abu da ya gabata.
4. A rubuta jawabi a natse kan wani batu na abin da ake tunanin zai zo nan gaba.

**SABABBIN KALMOMI**

1 Alamomin rubutu wasu alamomi ne da ake amfani da su a wajen rubutu kamar su aya alamar motsin rai, wakafi da sauransu.
2. Jawabi wani nau'i ne na magana da ake yi ko a magance ko a rubuce. A kowane su amfana da shi.

**MATANI**

Kamar yadda Sani et al (1992) suka nuna, jawabi wani nau'i ne na rubutun insha'i. Kowane rubutun jawabi yana da manyan rukunai guda uku kamar haka:

Gabatarwa.
Ma}asudi.
Kammalawa.

Duk wa]annan rukunan suna da ]imbin muhimmanci domm idan ba ]aya daga ciki jawabi ba ya yin armashi.

**GABATARWA**

A wajen gabatarwa, za a so marubuci da ya }ayatar da ita domin mai sauraro ya ji da]in 'sautaro, kuma ya natsu tsaf. Gabatarwa tana da muhimmanci, domin ita ke sa jawabi ya yi armashi.

A gabatarwa, za a so a yi amfani da kyakkyawar salo da kuma harshe mai sau}i yadda za a iya fahinitar abin da ake nufi. Ya kamata gabatarwar ta kasance 'yar madaidaiciya. kuma ta fito da abin da jawabin ya }unsa.

**MAKASUDIN JAWABI**

A nan marubuci zai bayyana duk abin da jawabinsa ya }unsa ba tare da ya bar komi ba.

Manufa. Ya kamata, kowace jumla ta kasance tana cin gashin kanta, wato, a sanya mata aya bayan an }are ta.

Sakin layi ma yana da muhimmanci domin shi ke nuna zantuka daban-daban wato kowane abu yana cin gashin kansa, ba tare da an ha]a wuri guda ba. Ya kamata a yi am fani da gajerun jumloli ba masu tsawo ba.

**AIKI I**

1. Rubuta jawabi matsakaici kan irin yadda za ka kawo wa jama'ar unguwarku ]auki game da irin matsanancin rashin ruwan da suke fama da shi.
2. bayyana alamomin rubutu guda biyar.

**KAMMALAWA**

A nan, marubuci zai kammala jawabinsa tare da na]ewa yana mai amfani da kyakkyawar Hausa wajen rubutunsa.

Ya kuma kamata ya dunga yi yana waiwayen kadan daga cikin abin da ya rubuta, domin kada lokaci ya }are ba-zato-ba-tsammani.

**AIKI II**

Rubuta jawabi mai matsakaicin tsawo a matsayinka na shugaban ]alibai don gabatarwa ranar saukar karatunku na firamare.

**TA{AITAWA**

- An nazarci gabatarwa a wajen rubutun jawabi. An nazarci ma}asudin rubutun jawabi
- An nazarci yadda za a kammala rubutun jawabi.

**MANAZARTA**

INST. OF EDUCATION, A.B.U. ZARIA- *Sabuwar Hanyar Rubutun Hausa:* 'Nelson Publishers(1980**)**
Sani M.Z. etal (1992) - *Darussan Hausa Vol* I Ibadan: UPL. PK

**KASHI NA 3: KOYAR DA SHIFTA DA JAWABI DA TA{AITAWA TA HANYAR SAURAREN ZANCE A KASET**

**GABATARWA**

Wannan darasin ya bambamta da sauran da aka yi. Ba daga littafi ne za a yi wannan aikin ba. A'a, wani jawabi ne da aka ]auka a kaset za a saurara. Daga nan ne za a samo }ashin bayan wannan darasin.

**MANUFA**

A lokacin da ]alibi ya gama sauraron wannan kaset zai iya:

i) Rubuta dukkan abin da ya saurara;
ii) zai iya yin rubutu ba tare da sa~a ka'idojin rubutu ba;
iii) zai raba insha'insa daki -daki yana mai la'akari da inda ya kamata ya fara sakin layi da dai sauran ka'idoji;

**MATAKAN NAZARI**

i) Ka saurari kaset da kyau, ka gano bakin zare.
ii) ka rarraba insha'in nan daki-daki, a fitar da sakin layi sanka sanka kada ka yi watsi da }ananan ka'idojin rubutu irin su wa}afi da wa}afi mai ruwa da alamun motsin rai da saunransu.

**SABABBIN KALMOMI**

Tun da malami ne zai bayar da batun da ]alibi zai yi magana a kai malami na iya neman lallai jawabin da za ayi ya ha]a da wasu kalmomin da yake ganin lallai a bambace su Misali idan ya ce a yi jawabi kan siyasa to ana iya cewa lallai a yamutsa da kalmomi irin su jam'iyya da `yan adawa da kakakin majalisa da shugaban kwamitin ku]i da 'yar takara da `yan banga da sauransu. Idan kuwa alal misali ya ce a yi bayani ne a kan rance da Nijerya za ta karbo, to a nemi ]alibi ya sa}ala kalmomi irinsu, Asusun Lamuni na Duniya, da {ungiyar Paris da ministan ku]i da lamuni ·da hage da riba da sauransu.

**MATANI**

]alibi ya zabi ]aya daga cikin batutuwan nan 3 ya yi jawabi a kansa;

i) Bashin da Nigeriya za ta ciwo daga asusun lamuni
ii) Bada}ala tsakanin shugaban }asa da `yan majalisar dattawa.
iii) Bai dace ba a bambamta tsakanin albashin ma'aikatan Tarayya da na jiha.

**AIKI I**

1. Su wane ne ma'aikatan tarayya?
2. Su wane ma'aikatan jiha?
3. Mene ne ya bambanta su?
4. Ya kamata a kashe jihohi, Nijeriya ta zama }asa mai gwamnatin }ananan hukumomi da ta tarayya. Ka yarda?
5. Mene ne ake nufi da mulkin soja?
6. Su wane ne `yan siyasa?

**AIKIN GIDA**

Ka saurari labari daga Rediyon Tarayya na Kaduna ka rubuta shi. Ka yi la'akari da ka'idojin rubutu.

**TA{AITAWA**

[alibi ya ]auki ]aya daga cikin sharhin da aka yi ya ta}aita shi. Ga misali a kan sharhi (insha'i) na 4.

Idan aka kashe tsarin jihohi ya zama daga }ananan Hukumomi sai Tarayya, wannan yana nufi an rage ku]in da ake kashewa a kan masu mulki a jihohi irin su gwamna da kwamishinoni. Haka ma gwanmnati za ta samu ragin ma'aikata tunda su ma ma'aikatan su koma }ananan Hukurrnmi ko Tarayya. Ba }aramin raran ku]i za a samu ba idan aka yi haka. Kwararrun ma'aikata na jiha da dama za su koma {ananan Hukumoni. Wannan zai bun}asa karkara.

**MANAZARTA**

Alhassan, H. & Musa, 'CM., *Koyon Magana da Fahnnta* , New Nigerian Newspapers, Kaduna,

1989.

**KASHI NA 4: KOYAR DA MAGANA TA HANYAR MUHAWARA**

**GABATA RWA**

Harshe ya kasance wata babbar hanyar da ]an Adam ke amfani da shi wajen sadarwa, tun da yake haka ne, ashe ko wanda ya iya bakinsa shi ne zai fi cin galaba a lokacin da aka ha]u wurin hira musamman ma hirar da ta }unshi fadin ra'ayi da kare kai kan wata matsaya da aka cimma, da ma shi lokacin da ake neman jawo ra'ayin wasu zuwa ga
wani ra'ayi.

Muhawara ta kasance wata takamammiyar hanyar hira wadda a ake amfani da ita domin }ara wa juna ilmi. Muhawara ba aiki ne na mutum ]aya ba, tamkar aikin gayya ce da sai mutum ya samu `yan uwan da za su taimaka masa. Wannan ne ya sa ta zama wata muhimmiyar dabarar koyarwa wadda ke }ara }arfafa hul]a da dan}on zumunci tsakanin malami da dalibansa, da kuma tsakanin ]alibai a junansu. Irin wannan halayyar muhawara ta zama a tattauna kowa ya fa]i albarkacin bakinsa, ya kawo }wararan hujjojin da za su kare masa ra'ayin da yake kai kuma ya samu damar sukar ra'ayin da ya bambanta da nasa, su ne suka tabbatar da shaidar cewa sun kuma }ware ga yin tunani da amfani da harshe don sadarwa tsakaninsu da sauran mutane.

**MANUFA**

A wannan kashi, ana sa ran ]alibi ya gane wa]annan batutuwan:

(i) ma'anar muhawara da sharuddanta;
(ii) iri-iren muhawara;
(iii) yadda ake yin muhawara;
**(iv)** amfaninta;

**MATAKAN NAZARI**

Ka lura sosai domin ka gane ba muhawara tsakanin malami da dalibansa, kuma za a fahimci cewa muhawara tana da wa]annan matakan:

Ajin zai kasu kashi biyu; kowane da nasa ra’ayi kan batu;

(i) Za a tsayar da batun da za ayi muhawara a kansa;
(ii) Kowane kashin ]alibi zai gabatar da hujjojin kare nasa ra'ayi;
(iii) kowane kashi zai fito da sukarsa ga hujjojin da ]aya ~angaren suka gabatar.
(iv) Malami zai yi amfani da matsayinsa na shugaba ya rufe muhawara.

**SABABBIN KALMOMI**

Kalmomi da ke da bu}atar a sanin ma'anarsu domin fahimtar batutuwan da ke cikin kashin sun ha]a da:

| | | |
|---|---|---|
| sadarwa | | Isar da sako |
| cin galaba | - | Samun nasara |
| gayya | - | Ha]uwar Jama'a |
| goyon baya | | Nuna amincewa |

**MUHAWARA DA SHARU[[ANTA**

Muhawara ita ce hirar da aka girka da manufar neman }ara wa juna ilmi ta hanyar musayar ra'ayi. Wannan ne ya sa ta bambanta da hirar da za a yi haka kawai, saboda manufar da take da ita ne na }ara wa juna ilmi. Akan haka ne za mu yi amfani da ita a matsayin hanya ko dabara da za ta koya wá ]alibai iya magana.

Irin sharu]]an da sai sun samu ne za a shimfi]a muhawara sun ha]a da:

Dacewarta; wato sai an tabbatar da cewa ita ka]ai ce hanyar da ta dace a yi amfani da ita a matsayin dabarar koyarwa.

(i) Yawan masu yinta; da yake aiki ne na gayya, sai an samu isassun ]aliban da za iya raba su }ungiya -}ungiya. Za a shirya su yadda }ungiyoyi za su fuskanci juna ne, wato kowa na ganin kowa.
(ii) Bai wa kowa damar yin magana; lallai ne a ba kowane ]alibi damar yin magana daidai da kowa.
(iii) Kiyaye ladubban muhawara; za a tabbata cewa ana bin irin ladubban yin muhawara kamar (a)

sauraren abin da mai magana ke fa]i ba tare da yi masa dariya ko katse masa hanzari ko cin gyararsa ba.

(iv) Wanda duk ke neman ya yi magana zai ]aga hannunsa shi kuma shugaba zai ba da fifiko ga wanda ya fara ]aga hannu don tabbatar da adalci.

(v) Kowa zai yi amfani da }arfin hujjojinsa ta hanyar ba da dalilai masu }wari domin neman rinjaye ba wai ya tsananta ra'ayi ba.

(vi) Ba za a yarda maganar ta kauce wa manufar muhawara ba koda maganar tana da ma'ana ko farin jini ga ]alibai ko malami.

**AIKI I**

1. Mene ne ma'anar muhawara?
2. Kawo sharu]]an muhawara.
3. Fito da ladubban yin muhawara.

**IRE-IREN MUHAWARA MUHAWARA TA KA SU KASHI UKU**

Muhawarar fa]in ra'ayi: A cikin irin wannan muhawara ]alibai na samun damar fa]in ra'ayinsu ne kan wata magana. Idan aka za~i batun da za a yi muhawara a kansa, duk wanda aka bai wa damar yin magana zai yi }o}arin amfani da }wa}walwarsa ya tsara irin dalilai da hujjojin da ya tabbatar da za su fito da ra'ayinsa yadda kowa zai gane ga irin matsayar da yake kanta game da batun.

Ire-iren batutuwan da za a iya tattaunawa a irin wannan muhawara ta fa]in ra'ayi sun ha]a da:

a) Ra'ayina a kan aikin `yan sanda:

b) Maganin yawan ha]arin mota;

c) Abubuwan da ke kawo tawayen `yan makaranta.

Muhawarar goyon baya ko sukar wani ra'ayi: A irin wannan kuwa an samu dama ne ta ]aukar matsaya a kan batu. Batun da za A tattauna kansa yana da manufa biyu ne, wato ko dai ka goyi bayan ra'ayin ko kuma ka yi }o}arin kawo hujjoj inda za su karfafa ~angaren da ka ]auka .

Ga irin batutuwan da za a yi wa irin wannan muhawara:

a) Radiyo ya fi amfani ga jama'a fiye da Talabijin.

b) Iska ya fi ruwa amfani ga dan Adam.

c) Mulkin soja ya fi mulkin farar hula kawo ci gaba ga al'umma.

iii) Muhawarar ba da haske: A irin wannan muhawara, ana bu}atar mai yin ta ya ba da haske ta hanyar tattauna wani batu, ya fito da abin da ke haddasa abin idan na haddasawa ne da kuma irin abin da zai iya haifarwa. Idan kuma batun da ake muhawara kansa matsala ce, to ta hanyar ba da haske ne za a iya yin maganinta ko kuma a zartar da shawara a kanta irin batutuwan da za ayi muharawar ba da haske a kansu sun ha]a da:

a) Abin da ke kawo matsaiar rashin ruwan sha.

b) Yadda gwamnati za ta taimaki gajiyayyu.

**AIKI II**

i) Mene ne ake son mai magana ya yi }o}arin yi a muhawarar fa]in ra'ayi?

ii) Kawo nau'in muhawara da ka sani.

iii) Rubuta batutuwa biyu da aza a iya tattaunawa a muhawarar goyon baya ko sukar wani ra'ayi.

**YADDA AKE YIN MUHAWARA**

Kamar sauran dabarun koyarwa ita ma muhawara tana da sashe uku ne, wato tana da farko ko mabu]in da za bu]e ta da shi, tana da gangar jiki kuma tana da }arshe ko marufai da za rufe ta da shi.

Bu]e muhawara: Farkon muhawara ita ce, inda malami ko shugaban da aka za~a zai gabatar da batun da ake son a tattauna. Akwai hanyoyi hu]u ko fiye da ake iya bu]e muhawara da su, wato, ko da bayani ko da in -kai-ne, ko da tambaya, ko wasan kwaikwayo.

Bu]e muhawara da bayani shi ne, inda za a gabatar da wani bayani a kan batun, da ake son a tattauna, sannan a nemi masu muhawara su kawo dalilai da abin ya kasance yadda yake. Misali, malami ya yi wa ]alibai bayanin lamarin gurgusowar hamada cikin }asashen Arewa kafin ya a umurci ]alibin ya shiga muhawarar tattauna, da irin dalilan da suke haddasa wannan matsalar. A salon in-da-kai-ne kuwa, shi ne

inda za a gabatar da wata matsala sai a za~i wani kowasu a saka su cikin matsalar don neman su fito da irin dabarun da za su yi don su tsame kansu daga cikin matsalar. Misali, a ce a unguwa ce ake zaman mama}wabtaka tsakanin mutane uku sai ga shi a lokaci guda gidan makwabci ]aya ya kama da wuta yana neman taimako, shi kuwa ]aya ~arawo ne ya shigo masa, ya fara ihun neman taimako , sai ]aya abokin zamansu ne kawai ke kusa, kuma ga shi ya ji kururuwar kowane daga cikin biyu. To sai a za~i wani ko wasu a sa su cikin matsalar ana neman su za~i wanda za su fara kai wa agaji tsakanin mai gobara da mai ihun ~arawo. Idan kuma da tambaya ne za a bu]e muhawara, to za a sa}o tambaya mai yawan amsoshi ne kuma wadda za ta }ara haifar da wasu tambayoyin. Misali, a gabatar da matsalar ~arnar iska a farkon kowace damina cikin garuruwanmu, sannan a nemi, shin da me da me ke haddasa ~arnar iskan nan? Kuma wa]anne hanyoyi ne za a bi a magance irin wannan ~arnar ta shekara-shekara. Ta hanyar wasan kwaikwayo kuma ana bu]e muhawara ne da wasan sai bayann an gama ko an yi nisa kowa ya tsima, hankali ya nutsu ga abin da ke faruwa cikin wasan kwaikwayo sai a tsayar da wasan a nemi ]alibai su kawo hanyoyi iri-iri da za a iya }arasa wasan. Ko kuma sai an kammala wasan gaba ]aya sai malami ya nemi ]alibai su ba da ma'anar wasu abubuwa da suka abku cikin wasan ko halayen wasu `yan wasa da ma'anonin da za a iya fitarwa daga wasan.

~angarorin jikin muhawara: Aiki biyu ne suka rataya ga malami a lokacin da yake gudanar da muhawara, wato yana kiwon almajiran don tabbatar da kafuwar hankalinsu, a kan aikin da ake yi da kuma neman sa}on ko }o}arin tabbatar da cewa ba a fita daga sa}on aka gangara zuwa wani abu ba. Muhimman abubuwan da zai kiyaye sun ha]a da }ir}iro hanyoyin da zai rika tuntubar ]alibai don jin ra'ayinsu kan batun da ake muhawara kansa. Haka ma malami zai shirya yadda zai ri}a tayar da wanda ya ru]e ko ya sa wani ya tayar da shi . Lallai sai ya kula da tabbatar da an bi ladubban yin muhawara yadda ya kamata. Neman }arin bayani lokacin da ake bu}atar haka daga mai magana ko masu saurare da kuma kange shigar son kai da zai sa a saki tafarkin manufar muhawara suna daga cikin abubuwan da malami zai lura da su.

**AMFANIN MUHAWARA**

Baya ga }ara karfafa hul]a tsakanin malami da ]alibai, da kuma tsakanin ]alibai a junansu akwai tabbacin cewa tana amfani kamar haka:

a) Ba dallibi damar yin tunani na kansa, har ya samu damar fassara abubuwa da }ago wa kansa dabarun warware matsala idan ta samu.

b) Tana horar da ]alibi ya tsaya kan gaskiya da fa]arta a kowane hali , ba wai don kawai ya }aryata ra'ayin wani don kare nasa ra'ayi ba .

c) Tana wayar da kan ]alibi ya gane arnfanin sanin ra'ayoyi da yawa da gane martabar ra'ayin wa]ansu da koyon abubuwa ta hanyar wasu ra'ayoyi.

d) Tana ba ]alibin hasken gane cewa irin ladubban da ake koya na muhawara sun yi daidai da ladubban sauran ma'amala da ake yi da mutane.

**AIKI III**

1. Sashe nawa ne za a iya kasa muhawara?
2. Kawo ire-iren hanyoyin da za a iya bu]e muhawara da su?.
3. Kawo ayyuka biyu da ke rataye ga malami a yayin muhawara.

**AIKIN GIDA**

Kawo muhawara da ka sani tare da misalai irin batun da za a tattauna cikkinsu wadanne irin sharu]]a ne ke ga muhawara?

3. Kawo ma'anar wa]annan kalmomin:

(a) Muhawara

(b) Ladubba

(c) Gayya

(d) Wayar da kai

4. Wane irin amfani muhawara ke yi wa ]alibai?

**TA{AITAWA**

Abubuwan da aka koya a wannan kashin sun ha]a da:

- Ma'anar muhawara
- Sharu]]an muhawara
- Ire-iren muhawara da amfaninta.

**MANAZARTA**

Ahmed, U.B. (1975) *A School Certificate Hausa Course* Zaria NNPC Zarruk, R.M. (1979) *Sififofin Aikin Koyarwa* Oxford U.P..

Zarruk, R. M., Kafin Hausa, a. Ada Alhasan, B.S.Y. (1990) ***Sabuwar hanyar Nazarin Hausa Don Kananan Makarantun Sakandare.*** Ibadan University Press.

**KASHI NA 5: BITA**

**GABATARWA**

A cikin wannan fasalai za mu tattauna bitar dabarun koyar da harshen Hausa. A fannonin koyar da harshe da Adabi da kuma al'ada ta hanyar amfani da kayan aiki don samun sau}in fahimta.

**MANUFA**

Manufar wannan fasali ita ce auna wa ]alibi wa]annan abubuwa dangane da koyar da manyan sassan nazarin Hausa guda uku wato harshe da adabi da kuma al'ada. Domin ba da misalin wa]ann anabubuwa za mu bayyanna wa ]alibi misalan dabarun koyarwa kamar haka:

Koyar da ]alibi dabarun koyar da harshe kamar haka:

(a) amfani da katuttuka wajen koyar da Hausa;
(b) koyar da magana ta hanyar muhawara;
( c) koyar da amfani da kayann koyarwa irin su kwalaye, rikoda da kaset da takardu;
(d) koyar da magana da karatu ta hanyar kwaikwayo a fill.

**MATAKAN NAZARI**

(a) Za a gabatar da kayan aiki a kuma nuna wa ]alibi yadda ake amfani da su wajen koyarwa.
(b) Kai ]alibi za ka yi dukkan ayyukan da aka cc kayi.
(c) Koyar da magana ta hanyar farawa da gaisuwa.
(d) Koyar da sunayen abubuwa da sanin su a ido.
(e) Fito da wasu saututtuka masu matsaia da yadda ake karanta su.

**SABABBIN KALMOMI**

Sautuka: Ba}a}en Hausa kamar /b/ /k/, /m/ da sauransu.
Wasulla; Sautuka da ba ba}a}e ba irin /a/, /u/ /o/ i/k/e/
Kwaikwayo: Yin abu ta kallon mai yinsa.

**RASSAN NAZARIN HAUSA**

Hausa tana da manyann rassan nazari guda uku. Rassan su ne nahawu da adabi da al'adu. Kowane daga cikin wa]annan rassa akwai dabarun yin nazarinsa ta hanyar yin amfani da wasu kayan aiki na koyarwa. Kayan aiki suna taimaka wa ]alibi wajen koyo kuma su taimaka wa malami wajen koyarwa don samun sau}i da kuma saurin fahimta. Abin lura a nan shi ne kowane reshe yana da irin nasa kayan koyarwa wa]anda suka fi dacewa da shi. Za mu dauki wa]annan rassa ]aya bayan ]aya mu ga irin kayan koyarwa da kowane reshe yake amfani da su wajen koyarwa.

**KOYAR DA NAHAWU**

Nahawu yana da nasa fannoni, amma a nan za mu ]auki fannin saututtuka don mu ga yadda za a koyar da shi ta hanyar amfani da aikin koyarwa na musamman. Ana iya amfani da kayan aiki iri biyu, wato rakoda shi ne a ]auki sautukan Hausa. Amfani da kwalaye }anana shi ne a zana hoton dukkan sautukan Hausa a kan kwalaye. Kowane kwali zai ]auki hoton sauti guda ]aya. Malami zai bu]e muryar sauti guda don ]alibai su ji sa'an nan ya nuna musa kwali wanda yake ]auke da wannan sauti.

**AIKI I**

Rubuta ba}a}en Hausa (5) Wa]anda za a zana su wajen koyarwa.

**KOYAR DA AL'ADU**

Al'ada ita ma tana da nata fannoni da yawa, amma a nan za mu ]auki al'adar da ta shafi tufafin Hausawa mu ga yadda za a koyar da ita ta hanyar yin amfani da kaya da hotuna wajen gabatar da wannan darasi. Amfanin hoto shi ne ya taimaki ]alibi wajen fahimtar kowane tufa ya kuma ba shi damar gane shi, in wata rana ya ga irinsa. Malami zai nuna wa ]alibi tufafi iri-iri na hotuna daban-daban.

**KOYAR DA ADABI**

Adabi shi ma yanna da nasa fannonin amma nan za mu ]auki fannin rubutattun wa}o}i mu ga yadda za a koyar da su. Ta hanyar yin amfani da kayan aikin koyarwa. Za a yi amfani da kayan aiki iri biyu wato, rikoda da takarda. Amfanin rikoda shi ne a sa mata kasset in da ake so a koyar da ]alibai su ji. Amfanin takarda shi ne a rubuta wa}ar a kan takarda don ]alibai su gan ta a rubuce.
Malami zai sa wa ]alibai wa}ar su ji ta a rikoda a }alla sau uku . Daga nan sai ya ba su wa}ar a rubuce a takarda.

**AIKI**
Lissafa tufafin Hausawa guda biyar da ka-sani.

**AIKIN GIDA**

1) Tattauna hanya mafi sau}i wajen koyar da fannin alada.
2) Kawo manyan rassa na nazarin Hausa.
3) Rubuta yadda ya kamata a bu]e darasin koyar da Hausa ta hanyar gaisuwa a lokuta guda uku wato, da safe, da rana da kuma yamma.

**TA{AITAWA**
A wannan kashi mun yi bitar yadda za a koyar da ]alibai manyan rassan nazarin Hausa guda uku:

- Nahawu ta hayar yin amfani da kayan aikin koyarwa na musamman wato rikoda da kwalaye }anana.
- Mun yi bitar yadda za a koyar da ]alibi adabin Hausa ta hanyar amfani da kayan koyarwa irin su takarda da ridoda.
- Mun yi bitar yadda za a koyar da al'adun Hausawa ta hanyar amfani da hotuna daban-daban wajen gabatar da darasi ga ]alibai.

**MANAZARTA**

Alhassan, Musa. (1989) *Koran Algona da Pithina.* Nigerian News papers Limited. Kaduna.

BUNZA. A.M. (1999) *Nahawun Ruhunt .higomn KoVaiin Ruhutun Hausa.* ANLA1. (Sokoto. Kebbi and Zamlara branch)

Ningi L. L., (1985) *Jugamr Alalantan Alakarantun Firamare.* Kano: Ii mph Publishing. Company.

Zarruk. R.M.. (1980) *Si.1101in Aikin* Kovarwa. lbadan : Oxford Press.

## FASALI NA 10: DABARUN KOYAR DA ADABI DA [ABI`U

### KASHI NA 1: HANYOYIN KOYARWA

**GABATARWA**

Aikin koyarwa kamar yadda kowane aikin }warewa yake, yana bu}atar horarwa ainun. A yayin horarwar akwai abubuwa da dama da ake koya wa malamin. Daga ciki akwai ilmin sanin halayya da ]abi`u da kuma hanyoyin da za a bi a tarairayi mai koyo. Amma mafi muhimmanci daga ire-iren abubuwan da ake koya wa malamin yayin horar da shi, shi ne hanyoyi da dabarun koyarwa.

Mutane da dama sun ha]u sun yarda cewa tsire-tsire iri-iri ne. A yayin da mutum ya shuka wani iri to lallai yana bu}atar sanin abubuwan da za su sa irin nan ya fito ya zama mai amfani. Ke nan akwai bu}atar tantancewa ko irin yadda bukatar ban ruwa mai yawa ko ka]an; akwai bukatar a tantance irin takin da irin yake so, akwai bukatar a sani cewa yana son rana ko ba ya son rana da sauran abubuwa da dama. A bisa wa]annan da ma wasu dalilai ne ake ta }o}arin ganin cewa malami ya sami horo ko }a}a kafin ya fara koyarwa. Manufa sai an fahimtar da mlami yadda zai fahimci ]alibansa da irin yanayinsu domin a samu madafar koya musu yadda za su fahimta.

Haka kuma ana son ]alibai su lura da hikimar abin da ake koya musu da muhimmancinsa a rayuwar duniya da tarbiyarsu ba wani zunzurutun karatu ba.

A wannan kashin za mu duba wasu hanyoyi ne ko dabaru na koyarwa domin malami ya samu makama a yayin da ya zo koyarwa a aji. Kuma a san abin da aka koyar a aji amfaninsa ya fi a wajen aji.

**MANUFA**

A }arshen wannan darasi ana sa ran za ka iya:

1. Fa]in manya-manyan hanyoyin koyarwa akalla guda uku;
2. Yin bayani a rubuce kan ]aya daga cikin hanyoyin koyarwa da ka koya
3. Amfani da kowace hanya domin koyar da wani fanni na Hausa.
4. Nuna muhimmancin darasi a rayuwar wajen aji

**MATAKAN NAZARI**

1. Wannan fannin ne mai bukatar aikace-aikace. Sai ka natsu ne kawai za ka iya aiwatar da abubuwan da za a bukaci ka yi.
2. Akwai bukatar ka tabbatar ka gudanar za ayyukan wannan kashin domin yin hakan zai }ara maka fahimtar abin da ake so ka koya.

**SABABBIN KALMOMI**

Hanyoyin koyarwa: Dabaru ne da malami kan yi amfani da su wajen koyarwa domin }ara wa yara himmar koyon abubuwan da ake koya musu.

**MATANI**

Wani masani ya ta~a kawo misali da cewa idan kana da ruwa a cikin }warya sai wai ya zo da kwalba yana bukatar ka ba shi daga ruwan nan naka, abin yi na farko shi ne a samo bututu, in kuwa ba haka ba ruwan nan zai zube ne a banza a yayin da aka zo ]ura shi a kwalbar. Ba samo bututun ne abin dubawa ba. Ya zama dole a samo bututun da ya yi daidai da bakin kwalbar. In kuwa ba haka ba a nan ma sai ruwan ya zube a banza.

Abin yi shi ne a yayin da mutum ya zo koyarwa yana bukatar ya za~i dabara ko hanyar koyarwa daidai da daliban. In ba haka ba kuwa zai ~ata lokacinsa ne a banza kuma ya ~ata wa yara lokaci.

A dalilin haka ne masana suka tace dabarun koyarwa masu yawa. Daga cikinsu ne za mu duba guda hu]u a nan kamar haka;

**1. Hanyar koyarwa ta lacca**

Lacca ko hu]uba ko kuma bayani, wata hanya ce daga cikin hanyoyin koyarwa. A cikinta malami zai bi duk hanyoyin fara koyarwa na al'ada kamar yana tambayoyi wajen gabatar da sabon darasi da kuma ankarar da su a kan sabon darasin. Daga nan ne sai malami ya shiga zuba bayani kan fannonin sabon darasin. A yayin bayanin babu wani lokaci na tambaya daga ]alibai. Shi ma

malamin ba kasafai yake tambaya ba. Babban abin kulawa kawai shi ne a yayin da malami ke gabatar da laccar yana yi ne yana amfani da kayayyakin koyarwa wa]anda ya riga ya tanada tun kafin ya shigo aji. Ire-iren kayayyakin sun ha]a da botuna da alamomi da sauran abubuwa kamar rediyo da talabijin.

Malami zai yi ta yin haka har sai ya kammala lacca a duk fannonin darasin da ya shirya. Daga }arshe sai ya ba wa yara dammar su yi tambayoyi. Shi ma malami zai yi nasa tambayoyin don gani abubuwan da ya koya.

**2. Hanyar koyarwa ta wasanni**

Wasa na da muhimamanci wajen yara. Shi ya sa ma aka yarda cewa samun kulawa ga abin da ake koyarwa a aji ta}aitaccen abu ne. Wasa ya fi komai muhimmanci a wajen yara. A sakamakon haka ne masana suka ce to tun da haka ne ya kamata a yi amfani da abin da yaran suka fi so don koya musu aikin aji. Ita dabarar yin wasanni yayin koyarwa ta }unshi abubuwa guda uku. Na farko a lura da ire-iren wasannin da yara suka fi sani ko suka fi sha'awa. Na biyu a danganta shi wannan wasan da aka za~a da shi sabon darasin da ake so a koyar. A nan in an ga cewa a ire-iren wasannin da yara suka sani ko suka fl sha'awa babu wanda zai dace da gabatar da sabon darasi, a iya samo wani da zai dace da su yaran.

Mataki na uku shi ne fasalta matakan da za a bi wajen yin amfani da wasan wajen gudannar da sabon darasin. Ana bukatar malami ya yi taka-tsan tsan wajen gudanar da wasan. Lallai malami ya sani cewa wasan ba shi ne manufa ba. Manufar ita ce a yi amfani da wasan don shigar da sabon ilmi a kwakwalwar yara.

**3. Hanyar koyarwa ta gani-da-ido**

Akwai wasu fannoni na ilmi da su ke da matsala. Ko kuma a ce in an gan su da ido koyo zai fi fa'ida da inganci. Shi ya sa masana suka yarda cewa babu laifi a kawo irin wa]annan abubuwan cikin aji kowa ya gan su. Amma akwai wasu abubuwan da ba za su zo cikin aji ba, ko dai don saboda nisa ko saboda girmansu.

A irin wa]annan wurare sai a kwashi ]alibai a ]unguma da su wajen da abin yake domin su gani da idanuwansu. Ita wannan dabara a matsayinta ta hanyar koyarwa ta }ara wa ]alibi saurin fahimta.

Har ila yau tana }arawa malami sau}in koyarwa. A yayin da malami ya kawo gundarin darasin cikin aji ko kuma ya ]auki yaran ya kai su inda za su gani da idanuwansu sai ya gifta sharu]]a kamar haka:

kona sai ya rubuta tsawon shafi ko layi kaza a kan abin da ya gani;
cewa sai ya amsa tambayoyi da malami ya riga ya bayar tun kafin a ga abin;
sannan kuma sai kowa ya tashi a aji ya yi bayani a kan wani abu da malami zai tambaye shi.

**Hanyar koyarwa ta yi-da-jiki**

Wani lokacin koyarwa ta fi fa'ida idan masu koyon suka shiga cikin tsarin koyarwar ka'in da na'in. Wani lokacin duk yadda malami ya kai da bayani, ko kuma ya kai da iya yin wasanni a aji domin koyarwa, babu yadda za su yi da wasu yaran wajen fahimta.

Wasu yaran ma ko da sun gani da idanuwansu ba kasafai suke koyo ba yadda ya kamata. Hanyar kawai da ake gamsar da ire-iren wadanan ]alibai ita ce ta ba su dama su yi da jikinsu.

Abin dubawa a nan shi ne malami ya samar da dama a cikin hoyarwarsa wacce a cikinta ]alibai ba kawai zama za su yi su saurara ba. Su ma yara za su fito su wada da kansu tare da bin umurnin malamin.

Muhimmin abu dai a nan shi ne a fahimtar da yaro cewa duk abin da aka koya a aji, amfaninsa a rayuwar yau da kullum ne wato tarbiyyar rayuwa ba don boko ba. Wannan shi ne ma}asudin wannan fasali.

**AIKI I**

Yi }o}arin bambantawa tsakanin hanyoyin koyarwa na lacca da na wasanin; na gani-da-ido da na yi-da-jiki.

**AIKI II**

[auki hanya guda ]aya daga ayyuka guda hu]un da aka ba da bayanni a baya. Yi kamar kana aji, ka dinga tunanin ga ka kana koyar wa yara wani fanni na Hausa ta hanyar amfani da ita wannan hanyar ta koyarwa.

**AIKIN GIDA**

(i) Fa]i ma'anar kowace ]aya daga cikin wa]annan hanyoyi/dabarun koyarwa

lacca

wasanni

– gani - da - ido

yi - do - jiki

(ii) Zayyanna a rubuce, yadda kake jin za ka iya amfani da kowace ]aya wajen koyar da kowane irin fanni na Hausa.

**TA{AITAWA**

A wannan kashin ka nazarci:

- manya manyan hanyoyin koyarwa guda hudu;
- yadda za ka iya ba da bayani a kan a}alla ]aya daga cikin dabarun koyarwa guda hu]u;
- yadda za ka yi amfani da hanyoyin wajen koyar da darussan Hausa.

**MANAZARTA**

Garba A (1999) *Sabbin Hanyoyin Koyar Da Hausa.* Kano; Triumph Publishing Company

**KASHI NA 2: LABARU DA AKE DANGANTAWA DA FATALWA**

**GABATARWA**

Kowace irin al'umma tana da al'adu irin nata da tunani irin nata da kuma yadda take tafiyar da rayuwarta. Al'ummar Hausawa su ma suna da irin nasu al'adu daidai gwargwado. A cikin irin wannan al'adu har da zancen fatalwa. Fatalwa ita ce gawar wani mutum wanda ya mutu sannan aka yi masa butuki, sai ya dawo da wata siga mai ban tsoro yana }wazzabar jama'a. A cikin wannan darasi za a fa]akar da yadda ita irin wannan fatalwa take da kuma yadda ake danganta labarai da ita.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi ana sa ran cewa za ka }ara fahimtar:

1. abin da ake nufi da fatalwa;
2. yadda fatalwa take samuwa;
3. dalilan da sukan sa fatalwa ta zo.

**MATAKAN NAZARI**

1. Ya kamata ka shirya jin labari mai ban tsoro da mamaki.
2. Ka karanta gabatarwa kafin ka tsunduma cikin karanta darasin.
3. Ya kamata kuma ka karanta sashen TA{AITAWA domin fahimtar darasin.

**SABABB1N KALMOM1**

| | | |
|---|---|---|
| Fatalwa | • | matacciyar gawa mai yawo |
| Butuki | • | mutum ya kyautata ma ka cuce shi |
| Hakki | • | a nan yana nufi ba tare da laifi ba |
| Mamaci | | wanda ya mutu |
| Bakin wuta | | }onannen ice mai gawayi |
| Siga | | kama |
| Gagaruma | | mai yawa |

**LABARUN FATALWA 1**

Ita dai fatalwa kamar yadda aka bayyanna a gabatarwa gawa ce ta wani mutum ko kuma gawar ]an jariri wanda bai gama shan nono ba. Irin wannan kila an yi masa laifi wato musamman butuki, kafin ya rasu ko bayann ya rasu ]in. Zafin irin wannan butuki da aka yi masa shi ne yakan sa gawarsa ta dawo duniya ta yi wa mutane fatalwa su ma ta dame su. A wani ~angaren ma ita fatalwa ta sa a kai ga kisan kai, domin ta rama abin da aka yi mata. Wani lokaci kuma }o}arin amma buri ke mayar da fatalwa duniya kamar kwa]ayin ku]i ko sarauta ko kuma soyayya.

Irin butukin da yakan sa a kai ga samun fatalwa, shi ne idan mutum ba tare da hakkinka ba ya kashe ka, musamman ma idan matar ta san da shirin kisan ta }i bayyanna wa mai gidan nata. To idan sun je sun yi auren takan kai ga mamacin ya yi musu fatalwa. Haka shi ma jariri idan ba da hakkinsa aka kashe shi ba ko don, ba a son ya rayu don kada uwarsa ta ji kunya, ko don gudun kada shi jaririn ya girma ya zama sarki, ko ya gaji wata gagarumar dukiya da dai sauransu, ya kan dawo shan fasa. Fatalwa na iya dawowa da siffar mutum sak.

Akasari dai yadda ake siffata fatalwa ana ganin kan mutumin da ya rasu ]in da fuskarsa da komai amma wani lokaci a kan jikin doki ko jikin dai wata dabbar daban. Wasu kuwa sun ce ba a ganinta sai dai idan ta zo za a ji tana tsi tsi. Ko dai a wace Siffa ta zo yadda ake rabuwa da ita shi ne ana bin ta aguje ne da bakin wuta, sai ta gudu ta ~ace. Wasu kuma sai an hada da siddabaru na a-zo-a-gani.

**AIKI I**

1. Yaya ake samun fatalwa?
2. Mene ne fatalwa takan yi?
3. Yaya sigar fatalwa take?

**LABARUN FATALWA II**

Idan mutum ya yi dare sosai yana tafiya zai ji kamar ana bin sa a baya amma ko ya waiga ba zai ga kowa

ba, ko kuma mutum yana zaune a ]aki cikin duhu ya ji an yi masa tsaki to duk wannan take-take ne na fatalwa.
Wani lokaci kuma fatalwa takan dami dukkan gari gaba ]aya ta yi ta fito musu a wurare daban-daban ta ba su tsoro.

**AIKI II**

1. Yaya fatalwa take damun mutum?
2. Wane irin mutum ne yakan zama fatalwa?
3. Ko fatalwa gaskiya ce?

A Wannan ~angare abin da ake so shi ne kada ka }arfafa }aryata samuwar fatalwa. Ka nuna kowace al'umma tana da nata camfi. Su kuma Hausawa ga nasu. Daga }arshe ana so ka lurar da yara cewa dogon buri abu a ne mai kyau domin yana iya fataki in ba da kiyayewar Allah ba. Haka kuma ka lurar da yara cewa fatalwa ta mutane masu cin amana da kuma masu butuki. Ka lura da yara kuma cewa yawon tsakar dare ba dalili yakan sa wata rana a yi gamo. Don haka kowa ya yi }o}arin gyara halayensa.

**AIKIN GIDA**

(1) Bayyanna yadda fatalwa take kasancewa tsakaninta da mutum.
(2) Ko fatalwa takan kashe mutum?
(3) Wane kin butuki ne yakan sa fatalwa ta fito?
(4) Kawo ta}aitaccen sharhi a kan fatalwa.

**TA{AITAWA**

- Fatalwa itace rnatacciyar gawa wadda ta sake dawowa duniya ta wata siga daban.
- Takan faru ne a dalilin butuki ko cin amana da aka yi wa mani mamaci.
- Fatalwa takan fito ta gallabi jama'a ta gari ko mutum shi kadai.
- Akan rabu da fatalwa idan an kore ta da bakin muta.

**MANAZARTA**


CNHN (1977) *Sabuwar Hanyar Koyon Harshen Hausa da Al 'adun Hausawa* CNHN (1981) *Rayuwar Hausawa* Thomas Nelson Nig. Limited

Dangambo, A (1984) *Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga rayuwar Hausawa.* Kano; Triumph Publishing Company Zaria.

Madauci, I, da saura (1968) *Hausa Customs* Zaria; Northern Nigeria Publishing Company

**KASHI NA 3: HIKIMOMIN SANA'OIN GARGAJIYA A ALUMMAR HAUSAWA**

**GABATARWA**
A wannan kashi za a tattauna hikimomin sana'o'in gargajiya na Bahaushe. Don haka za a za~i wa]ansu sana'o'i na gargajiya a nuna irin hikimominsu ga al'ummar Hausawa.

**MANUFA**
Manufar wannan darasi ita ce ka:
1. san hikimar da ke tattare da kowace sana'a ta gargajiya ta Hausawa;
2. }ara fahimtar al'ummar Hausawa ta idon sana'o'insu na gargajiya.

**MATAKAN NAZARI**
(a) Za ka yi }o}ari ka fito da hikimar da ke tattare da sana'o'in da aka za~a ta yadda za ka ga hikimar.
(b) Za ka yi dukan ayyukan da aka ce a yi a wannan kashi.

**MATANI**
Hausawa suna da sana'o'i na gargajiya da yawa. Alal misali, Hausawa suna da sana'ar aski da ta fawa da ta }ira. Wa]annan sana'o'i ne wa]anda tun fil-azal Bahaushe yake yinsu. Hasali ma dai Hausawa ba su iya rayuwa sai ana gudanar da wa]annan sana'o'i da muka ambata da wasu masu kama da su. To, tunda abin haka yake, wato ke nan sana'o'in gargajiya na Hausawa sun }unshi wa]ansu hikimomi na musamman wa]anda suke rayar da al'ummar Hausawa, su kuma ci da ita gaba. Idan aka yi maganar hikimar sana'ar gargajiya ga al'umma, ana nufin irin tasirin da wannan sana'a kan yi a kan al' ummar Hausawa. Sana'ar na iya zama mai muhimmanci }warai ga al'ummar ta yadda dole a gudanar da ita don ci gaban al'ummar.
Akwai wa]anu sana'o'in gargajiya guda uku da muka za~a wa]anda muke so mu nuna irin hikimomin da suka }unsa. Sana'o'in su ne aski da fawa da }ira.

**AIKI I**
Lissafa abubuwan guda 5 wa]anda ma}era ke }erawa don amfani da su a cikin gida.

**SANA'O'IN GARGAJIYA**
Sana'ar aski ko wanzanci sana'a ce mai muhimmanci ga Bahaushe. Wanzamai tankar likitoci suke a al'ummar Hausawa. Su suke yin aski su cire belu, su yi kaciya, su yi tsaga su kuma fitar da hakin wuya da gurya.Wa]annan ayyuka muhimmai ne ga al'ummar Hausawa kuma rayuwa ba ta yiwuwa sai da su. Ashe ke nan hikimar samun wanzanci cikin al'umma ba 'yar ka]an ba ce. Al'ummar Hausawa ba ta yi sai da wanzami. Wani abin lura kuma shi ne wanzamai na ba da magani. Al'umma na amfana }warai da gaske daga irin magungunan da wanzamai kan bayar.
Sana'ar fawa ita ma muhimmiya ce ga al'ummar Hausawa. Mahauta ko wan]a sukan yanka dabbobi irin su shanu da ra}uma da raguna da awaki don amfanin jama'a. Hikimar mahauta tana da yawa. Mahauta su ke yanka rago, suna su fe]e shi su karkasa nama.
Haka kuma su ne suke yanka ragon layya da sallah, su fe]e shi, su gyara shi. Kowace safiya, a birane ko a }auyuka, mahauta ne ke yanka dabbobi don amfanin jama'a. Al'adun suna da layya suna da muhimmanci }warai a rayuwar Hausawa. Haka ma al' adar yin miya da nama kullum idan da akwai hali. Da babu mahauci a cikin al'umar Hausawa da duk wa]annan al'adu ba su wanzu yadda ake son su ha. Don haka hikimar sana'ar fawa a al'ummar Hausawa a bayyane take.
Sana'ar }ira muhimmiyar sana'a ce a wurin Hausawa. {ira sana'a ce wadda take sarrafa }arfe, a yi abubuwan amfani iri daban daban. Ma}era su ke }era fartanya da garma da bindiga da kibiya da baka da takobi da ruwan gatari da }yaure (gambu) da guga da kwanoni da lauje da sauran kayayyakin amfani a cikin gida. Don haka rayuwar Bahaushe ba ta tafiya sai akwai ma}era a kusa. Idan haka ne, ashe ke nan hikimar sana'ar }ira a al'urnmar Hausawa a bayyane take. Sarakunan Hausawa ma sun san muhimmancin ma}era domin kuwa ma}era ne ke }era masu kayayyakin ya}i da na adon mata da na dawaki.

**AIKI II**

Fa]i dabbobi uku da mahauta kan yanka don sayarwa ga jama'a.

**AIKIN GIDA**

1. Me ka fahimta da cewa akwai hikima tattare da sana'o'in gargajiya na Hausawa?
2. Wa]anne sana'o'in gargajiya na Hausawa aka za~a aka yi bayaninsu a wannan kashin?
3. Wace hikima ce ko hikimomi aka ce sana'ar aski (wanzanci) ta }unsa?
4. Wa]anne al'adun Hausawa ne aka ce sana'ar fawa na da muhimmanci }warai wajen gudanar da su?
5. Me ya sa fawa ta fi su hikima a wajen Hausawa?

**TA{AITAWA**

A wannan kashi an tattauna wa]annan abubuwa:

- ire iren sana' o' in gargajiya na Hausawa;
- ma'anar hikimomin sana'o'in gargajiya;
- hikimar da ke cikin wasu za~a~~un sana'o'in gargajiya na Hausawa.

**MANAZARTA**


Madauci, et al. (1968). *Hausa Customs*. Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Nadabo, M.H. (1980) *Ciniki Da Rum 'o'i A kavar Hativa.* lbadan; Nelson

NNPC. (1971). *Labant Na Da Da Na yannzu* Zaria; Northern Nigerian Publishing Company (NNPC)

NNPC (1980) *Zaman Aaron Da Sana'arsa.* Zaria: Northern Nigerian Publishing Company (NNPC).

Zan-uk, R.M. et al. (1982.) *Zaman Hausawa.* Zaria: Institute of Education, Ahmadu Bello University.

**KASHI NA 4: MU{AMAI DA AYYUKANSU**

**GABATA RWA**

A darussan baya mun ]an tattauna kan tsarin iyali da tsarin sarauta wa]anda ]aya ba ya inganta sosai sai da ]ayan don abu ne da ya danganci jama'a da shugabanci. Kowane mutum a cikin al'umma yana da wani matsayi da kuma aikin da yake gudanarwa a cikinta, wannan kashi zai yi bayani ne a kan irin wa]annan matsayi da kuma aikace aikacen da ke tattare da matsayin.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashi, za ka fahimci;

1. ma'anar mu}ami;
2. yadda tsarin mu}aman al adun gargajiya yake.

**MATAKAN NAZARI**

Flanyar nazarin wannan kashi ya ha]a da:

- karanta bayanin dalla-dalla;
- danganta bayanin da abin da ke faruwa a inda mutum yake zaune;
- amsa tambayoyin da suka biyo baya.

**SABABBIN KALMOMI**

| | | |
|---|---|---|
| Mu}ami | - | ]aukakar matsayi |
| Sarki - | - | mai mulki |
| Talaka | - | wanda ba sarki ba |

**MA'ANAR MU{AMI**

[aukakar matsayi ita ce mu}ami. Matsayi kuwa abu ne da jama'a suke iya gani a tare da mutum dangane da halayensa na zama da mutane, da ilminsa ko wadatarsa ta abubuwa, da kuma yadda yake gudanar da wa]ansu al'amura. Matsayi shi ne ma'aunin mu}ami, domin shi ne ke nuna inda wani ya fi ¸wani ]aukaka.
Dukiya da tufafi da yawan mabiya ko barori ko bayi ko ma 'aikata, su ne manyan alamu na mu}ami, ya Allah ga sarki ne ko ga talaka. Mu}ami na da dangantaka da tsarin cudanya, wanda tsari ne na abubuwan da ake ba mutum, ko Wa]anda ake yi masa, da shi kuma irin abubuwan da yake saka wa jama'a da su. Misali bisa al'ada, sarki shi ne jagora, shi ne ke wakiltar talaka, shi ke bayar da kyautar girma na dawakai da tufafi da sauransu. Komin mu}amin talaka kuwa yana yi wa saraki hidima ne, yana ba }asa abinci, yana kai gaisuwa ga sarki, da fadanci da bin umurni da sauransu.
Wannan tsari, shi ne babban ginshiki na rayuwar sarauta a }asar Hausa. Shi yake kawo zaman cu]e-ni-in-cu]e-ka tsakanin sarakuna da talakawansu. Duk inda wani abu ya ]an toge daga cikin tsari, misali rashin adalci ko }wace wajen sarki, ko kuma rashin biyayya wajen talaka, to sai dangantakar to raunana.

**c)** **Dagaci-Dagaci** shi ne shugaba ko sarkiin }auye. Dukkan matsala da ta shafi wannan }auyen tana hannunsa ne, sai in ta fi }arfinsa, sannan a wurin hakimi.

**d)** **Mai unguwa-**Dagaci da mai unguwa wa da }ane ne. Mai unguwa ¸shi ne }ani, sai in matsala ta fi }arfinsa sannan zai kai wa dagaci. Mai unguwa ya fi isa da jama'ar gari don haka shi ke kar~ar haraji, shi ke sulhu, shi ke kawo wa jama'a sa}on Sarki, ya kuma kai wa Sarkin labaran jama'a.

2. **TALAKA**

a) Malami: In ka ]ebe saraki, mutum na sama ne }asar Hausa shi malami wanda akan ]orawa ha}}in tarbiyyar almajirai, su nuna musu hanyoyin yi wa na gaba ladabi da biyayya da yadda za su zamo mutanen }warai.

b) Attajirai: Wannan ya }unshi mutane ne masu }unban-susa watau masu hali Wa]anda kan taimaka wa sauran jama'a ta hanyoyi daban daban.

c) ‘yan kasuwa: Wa]annan nau'in jama'a ne da ke taimakawa wajen bun}asar tattalin arzikin }asa ta hanyar saye da sayarwa.

d) Masu sana'a: Masu sana'a ba }aramar gudummuwa suke bayarwa ba ga rayuwar Bahaushe, domin ba domin su ba, da al'ummar ta tsaya cik.

e) Sauran jama'a: Wannan ya }unshi dukkan Wa]anda ba a ambace su a sama ba, manya da yara,

maza da mata. Bambancin mu}ami ba ya hana hul]a ko cudanya tsakanin al'ummar Hausawa, sai dai ]an abin da ba a rasawa a fagen auratayya, da kiran gaskiya da sauransu.

**AIKI I**

1) A naka ra'ayi me ka fahimta shi ne ma'anar mu}ami?
2) Yi bayanin dangantakar da ke akwai tsakanin mu}ami da tsarin cu]anya.

**TSARIN MU{AMAI DA AYYUKANSU**

Tsarin mu}ami bayani ne na yadda mu}amin mutane yake hauhawa, wani gaba da wani, sai dai lura tsarin mu}anamin ba bayani ne na amfanin mutum ko gudumuwarsa ga jama'a ba, domin yana yiwuwa mutum ya fi ka mu}ami, kai kuma ka fi shi amfani ga jama'a.

Hanyoyin bayyanna tsarin mu}ami iri-iri ne. Daga ciki akwai:

a) shekaru babba shi ke gaba da yaro;
b) gado musamman wajen sarauta ko sana'a;
c) jinsi tsakanin maza da mata;
d) tarihi a tsarin bauta ]a ya fi bawa;
e) al’adun gargajiya tsakanin saraki da talaka.

**TSARIN MU{AMAN AL’ADUN GARGAJIYA**

Daga cikin hanyoyin bayyana tsarin mu}ami, tsarin na al'adun gargajiya (watau) shi ya fi bayyana rayuwar Bahaushe a fili wanda ya bambanta shi da sauran al'ummomi akasin sauran Wa]anda ana iya ganin su a kowace al'umma.

A ta}aice idan aka duba tsarin mu}aman gargajiya na Hausa, Sarakuna su suke gaba da kowa. Daga sua sai malamai, sai kuma attajirai da yan kasuwa da masu sana’a Wa]anda ake fifita su akan sauran talakawa. Dangane da wannan nazari za a iya kasa tsarin zuwa gida biyu.

**SARKI**

a) Sarki: Sarki Shugaba ne mai cikakken iko, shi ke zartar da kowane irin hukunci a }asarsa, kodayake wani lokaci yakan saurari mashawartansa. A da sarki yana da ikon ya sa a kashe mai laifi ko a ladabtar da shi ko a kore shi daga }asar sa'anan yana da ikon na]a mutum ko tu~e shi daga kowace irin sarauta a }asarsa.
b) A Fada, akan sami wa]ansu mutane masu wa sarki hidima a gidansa, wa]anda ake kira fadawa. Wasu daga cikin fadawan su ne; Shamaki ko Sallama da Shantali da Sarkin Gida, Sarkin Zagi, Jakadiya, Sarkin Fada da saur ansu.
c) **Hakimi:** Hakimi kan kasance ]an sarki, ko wani mai ilmi ko jarumi wanda ya yi fice a wani fanni na rayuwa. Daga Sarki sai Hakimi, shi ke taimaka wa Sarki wajen shugabancin jama'a. Wa]ansu daga cikin hakimai akan ba su rikon garuruwa, wasu kuwa yan majalisa ne masu ba da shawara da gudanar da wasu ayyuka da Sarki yakan ke~e musu. Ayyukan nasu sun bambanta daga wuri zuwa wuri. Daga cikin mu}aman hakimai akwai Waziri da Madaki da Makama da Wali da Iya da Magajin Gari da Ciroma da Dallatu da sauransu.

**AIKI II**

1) Ka tsaro sunayen sarautun gargajiya guda goma. Biyar na fadawa, biyar na hakimai. (Kada ka kawo Wa]anda ke wannan darasi)
2) Wane dalili ya sa aka kira attajiri talaka?

**AIKIN GIDA**

1) Kawo sarautu uku - uku da ake ba wa]annan mutane; (a) 'yayan sarki (1) jarumai
2) Yi bayanin irin ayyukan da mai unguwa yake yi.
3) Wa]anne irin gudummawa ‘yan kasuwa suke bayar wa ga al'ummar Hausawa'?
4) Mene ne aikin malami a }asar Hausa?

**TA{AITAWA**

A wannan kashi mun ga ma'anar mu}ami, da kuma tsarin mu}amai da ayyukansu, sannan da tsokaci na musamman a kan mu}amin al'adun gargajiya.

**MANAZARTA**

Yahaya, 1. Y. et. al. (1993) Darussa[n] Hattsci *Om; Maltarnairtir Nalaillifill! Ha* 3 Univ, Press Pk.

## KASHI NA 5: BAYAR DA MISALAI NA ADABI DA RABE-RABENSA DA RUKUNANSA

**GABATARWA**

Saboda muhimmancin da adabi ke da shi a rayuwar ]an Adam da kuma ]imbin tasirin da yake da shi a tsarin zamantakewar jama'a, ya sa ake cin karo da shi a kai a kai, adabi wani abu ne mai }ara nuna irin martabar da yake da ita. Masana da dama sun ha]u a kan cewa za a iya kallon adabi ta fuskoki biyu. Fuska ta farko ita ce a matsayinsa na sarrafaffen harshe sarrafaffe wanda a cikinsa akwai basira da balaga masu bayyana hikimomi da tsarin zaman jama'a. Fuska ta biyu ita ce a matsayin adabi na wata hanya mai ha]a bayani dalla dalla a kan yadda wata al'umma ke gudanar da tsarin rayuwarta.

Haka kuma masana sun lamunta a kan cewa, ana iya amfani da adabi wajen tarbiyyar al'umma. Wannan kuma ita ce manufar wannan fasali baki ]aya. Da wannan manufar ce za mu yi }o}arin duba rabe-raben adabi guda biyu da kuma rukunan da suke cikin kowane rabo; watau adabin gargajiya (nab aka ko na ka) da na zamani (rubutacce).

**MANUFA**

A }arshen wannan darasi ana sa ran za ka:

(1) iya fadar ma'anar adabi;

(2) kawo rabe-raben adabi guda biyu;

(3) bayani a kan wasu rukunoni na kowane ~angaren adabi;

(4) kawo misalai daga kowane rukuni na adabin gargajiya da na zamani.

**MATAKAN NAZARI**

Ka karanta wannan kashi sosai kuma ka tabbatar ka yi duk aikin da a ka ba ka. Ka tabbatar ka bayar da amsa ga duk tambayoyin da za a bukaci ka amsa.

**SABABBIN KALMOMI**

Adabi: kalma ce wadda Hausawa suka aro ta daga harshen larabci suka bayyana nau'o'in azancinsu da fasahohinsu da sauran hanyoyin zaman rayuwa.

Rabe-raben adabi; Manya manyan azuzuwan adabi guda biyu su ne adabin baka (adabin gargajiya); da rubutaccen adabi (adabin zamani).

**MATANI**

Kamar dai yadda shehin malami Abdulkadir [angambo ya nuna a littaffinsa mai suna Rabe-Raben Adabin Hausawa cewa rabe-raben adabin Hausa guda biyu ne:

i) Adabin Gargajiya wanda akan kira adabin baka.

ii) Adabin Zamani wanda akan kira rubutaccen adabi.

A kowane daga cikin wa]annan manya manyan rabe - rabe akwai rukunoni masu dama. Za mu ]auki wasu sassa mu yi la'akari da rukunonin da ke cikinsu da gudummawarsu a tarbiyya da dabi'u.

**Misalai Daga Adabin Gargajiya da na Zamani**

Adabin gargajiya: A nan za mu ]auki guda uku domin ba da misali a cikinsu.

i) Tatsuniya da labari: Tatsuniya iri biyu ce. Akwai tatsuniya mai labari da kuma tatsuniya ta kacici-kacici. Tatsuniya mai labari ita ce wadda sai dai kawai a saurara. Ita ce wadda ta }unshi Gizo, da {oki da Dodo da sauransu. Tatsuniya ta kacici - kacici kuwa ita ce wadda ta }unshi tambaya da amsa. Misali, }ulin kulifita gauta da sauransu.

Wasa kwakwalwa: Shi wannan wani labari ne }ir}irarre wanda a cikinsa za a kawo wata cukurku]a]]iyar matsala kuma a nemi ka warware ta. Misali labarin akuya, da kura da hatsi Wa]anda ake so a }etare da su kogi da dai sauransu.

Maka]a da mawa}an baka: wa}o}in maka]a sun kasu kashi daban daban kan rabe-raben wa}o}i ya danganta daga dalilai da ya sa ake yin wa}ar. Misali daga cikin rabe raben akwai:

Maka]an fada kamar su Musa dan {wairo da Naramba]a. Maka]an jama'a akwai su Shata da [an maraya Jos. Maka]an maza akwai [an Anace da Hamisu mai ganga. Maka]an ban-dariya akwai 'yan kama da 'yan gambara. Maka]an sana'a akwai maka]an noma da na fawa.

**ADABIN ZAMANI**

,

i) Zube**:** Wani rubutu ne wanda akan yi a kan }agaggun labarai ko wani Sharhi kan fannoni daban-daban misali a nan shi ne kamar littafin Ruwan Bagaja da su Iliya [an Mai {arfi

Wasan Kwaikwayo: Rubutu ne wanda ke nuna wasa da ake gina shi kan kwaikwayon wani labari, ko matsala da sauransu. Misalai a nan sun ha]a da Uwar Gulma da Matar Mutum Kabarinsa.

Rubutattun Wa}o}i: Ba kamar ˙yadda wa}a take a adabin gargajiya ba, wa}a a adabin zamani a rubuce take. Misali a nan shi ne kamar su wa}o}in su Sa'adu Zungur da Wa}o}in Mu 'azu Ha]eja.

**AIKI I**

Duba ragowar rukunonin adabin gargajiya ka yi }o}arin samo misalai daga cikinsu

**AIKI II**

1) Kawo misali a kan magaganmu da akan kira gagawr Gwari fa]i.
2) Kawo misalai guda goma na sana'oin gargajiya.
3) [auki biyu daga cikin misalai na sana'o'in gargajiya ka bayar a tambaya ta biyu ka kuma ba da ]an gajaren bayani a rubuce a kan kowane.

**AIKIN GIDA**

1) Mene ne adabi?
2) Kawo rabe- raben adabi guda biyu.
3) Jera rukunonin adabin gargajiya ka kuma kawo misali a kan kowane rukuni.
4) Jera rukunonin adabin zamani kuma ka kawo misalai a kan kowane rukuni.

**TA{AITAWA**

A wannan kashin ka nazarci:

i ma'anar adabi
ii) rabe-raben adabi guda biyu;
iii) rukunonin adabin zamani da na gargajiya

**MANAZARTA**

[angambo, A (1984) *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa* Triumph Publishing Compnay, Kano

Yahaya, I. Y. Zariya M. S., Gusau, S. M. and Yar'aduwa, T, M. (1992) *Darussan Hausa . Don Manyann Makarantun Sakandare* Ibadan. Unversity Press Plc.

**KASHI̩ NA 6: JAGORA ZUWA GA LITTATTAFAN DUBAWA A KAN KOWANE FANNI**

**GABATARWA**

Nazarin adabi koyaushe yana tafiya tare da nazarin littattafan karatu. A kowace fanni na adabi ana da ]umbin littafan nazari da za ka yi anfani da su. Yawan karance-karance na littafai zai }ara maka fahimtar abin da ka riga ka sani. [alibi koyaushe a cikin karatu aka san shi. A wannan kashi za a kawo sunayen littafan karatu da za ka iya samu domin karantawa.

**MANUFA**

Bayan wannan darasi ana fatar za ka:

}ara ilmi da wa]annan littafai da aka jera maka daga kowane fanni na Hausa. Abin lura a nan shi ne mutum ya san adabi bayan Nisha]antarwa ana iya amfani da shi wajen inganta tarbiyyar yara. Don haka littafan da za a za~a za su kasance sun cancanci manufarmu a nan.

**MATAKAN NAZARI**

Karanta wannan kashi sosai sannan ka nemi littafan da aka bayyana maka a ]akin karatu

**MATANI**

Kowane fanni na adabi ka ]auka akwai littafan da za ka }ara sani a kansu. Ba bugaggun littafai ba. Mujallu da ma}alu, kai har ma da jaridu idan ka karanta su za su taimaka maka wajen fahimtar adabin Hausa. Ga jerin sunayen littattafai nan da za ka duba domin }arin ilmi, an raba littafan zuwa gida biyar domin su dace da darasin da ka koya na adabi.

**KASHI NA [AYA**

Wannan kashi ya }unshi littafan da za ka samu bayanin ma 'anar adabi da rabe-rabensa. Ga jerinsu nan.

(i) [angambo, A. (1984) Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa Kano; Trumph Publishing Company

(ii) Gusau, S. M. (1996) Dabarun Nazarin Adabin Hausa. Kaduna; Fisbas Media, in) Yahaya, I. Y. et al (1992) Darussan Hausa 1 - 3 Ibadan: University Press

(iii) Zarruk et al (1990) Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa 1 - 3 Ibadan: University Press.

**KASHI NA BIYU**

Wannan kaso ya }unshi littafan da aka wallafa a kan adabin baka na Hausa. Haka nan wannan kashi ya }unshi rubuce- rubuce a kan ]ai]aikun sassan adabin baka na Hausa. Ga jerin wasu nan.

(i) Alhassan, et al (1982) Zaman Hausawa Lagos, Islamic Publications

(ii) Bichi, A. Y. (1980) Wa}o}in Bikin Aure Lagos: Nelson

(iii) Dembo, U. (1982) Wasanni da Wa}o}in Yara Zaria; Ganuwa.

(iv) Ibrahim, M. S. (1982) Kowa Ya Sha Kida lbadan: Lagos Longman.

(v) Umar, M. B. (1987) dangantakar Adabin Baka da Al'adun Gargajiya,Kano Triurnp Publishing Company.

(vi) Yahaya, I, Y. (1977) Tatsuniyoyi Da Wasanni 1 - 6 Ibadan University Press.

(vii) Yunusa, Y. (1978 Hausa a Dun}ule. Zaria NNPC.

**KASHI NA UKU**

Kashi na uku ya }unshi littafan da aka rubuta a kan fannin adabin zamani. A nan za mu fara ne da rubutattan wa}o}i.

(i) Aliyu, A. (1977) Fasaha A}iliyya. Zaria NNPC.

(ii) Junaidu, 1 (1080) Ciza Ka Busa lbadan Longman

(iii) Muhammad, 1. Y. (1979) Wa}o}in Hikimomin Hausa. Zaria: NNPC.

(iv) Sipikin, M. (1971) Tsofaffin Wa}o}i da Sababbin Wa}o}i. Zaria NNPC

(v) Zungur, S. (1957) Wa}o}in Sa'adu Zungur Zaria NNPC.

**KASHI NA HU[U**
Wannan kashi ya }unshi misalan rubutun zube na Hausa.
(i) Gwarzo, M. (1978) Idon Matambayi Zaria NNPC
(ii) Imam, A. (.1931) Magana Jari Ce 1 - 3 Zaria Gaskiya
(iii) Imam, A. (1978) Ruwan Bagaja Zaria; NNPC
(iv) Kagara, (1968) Gan]oki Zaria NNPC
(v) Tafida, J..(1977) Jiki Magayi Zaria: NNPC.

**KASHI NA BIYAR**
A wannan kashin na biyar za mu ga misalai ne a kan rubutaccen wasan kwaikwayo.
(i) Balewa, A. T. et al (1974) Shehu Umar; Zaria NNPC
(ii) Ma}arfi, S. (1970) Zamanin Nan Namu. Zaria. NNPC.
(iii) Roukbah, B. F. (1981) Matar Mutum kabarinsa.
(iv) Sada M. (1971) Uwar Gulma. Zaria NNPC
(v) Ahmed, U. B. (1999) Turbar Turabulus, A. B. U. Press, Zaria.

**AIKI**
Kawo misalai guda biyu daga rubutaccen wasan kwakwayo Wa]anda ke koyar da tarbiyya ga al'umma.

**AIKI GIDA**
1. Shiga ]akin karatu ka nemo wasu daga cikin littafan da aka lissafa.
2. Ka rubuta misali guda a kan kowane rukunin littattalan da ka koya.

**TA{AITAWA.**
A wannan kashi mun ga misalan ayyuka ne dangane da rubutaccen adabin baka na Hausa. Amma wa]annan misalai ka]an ne aka tsamo domin ka }ara fa]a]a saninka dangane da adabin Hausa. Idan ka shiga dakin karatu ya kamata ka nemi wa]anan littafan domin za su }ara maka fahimtar abin da ake }o}arin tunashe ka.

**MANAZARTA**

Yahaye, et al (1986) Jagoran Nazarin Hausa. Zaria NNPC
Yahaya, I. Y. (1988) Hausa a Rubuce: Tarihin Rubuce - rubuce cikin Hausa Zaria: NNPC
Yahaya et al (1992) Darussan Hausa 1 - 3 Ibadan: University Press.
Zarruk et al (1990) Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa 1 -3 Ibadan University Press.

**KASHI NA 7: KACICI - KACICI DA HIKIMOMIN DA KE CIKINSA**

**GABATARWA**

Manufar wannan aiki shi ne ya ba da haske a kan ma'anar kacici-kacici da irin rabe - rabensa tare kuma da za}ulo hikimomin da ke tattare a cikinsa. Wannan batu (kacici-kacici) wani ]an yanki ne na daga cikin ~angaren adabin Hausa wanda aka tsara.

**MANUFA**

Manufar wannan aiki shi ne ana son ka san ma'anar kacici-kacici da irin hikimonin da ke }unshe a cikinsa, wanda a }arshe kuma ana sa ran ya iya koyar da kai gabatar yadda za a gabatar wa ]alibai a cikin sassaukar Hausa ta yadda za su fahimta

**MATAKAN NAZARI**

1) Ana son ka lura da hikimar kacici-kacici da mahimmancinsa wajen kaifafa basira da zurfin tunani.
2) Ka san tubalan gina wasan da kuma tsarin sa.
3) Ka san ma'anar kacici-kacici.
4) Ka san muhimmancinsa.

**SABABBIN KALMOMI**

kacici-kacici: daga kalmar cici, watau ambatar sunan wani abu, ko adadi na wani abu da tun asali ba a sani ba ko kuma an sani amma ba a nuna a zahiri ba.
Zahiri : a bayyanne, a fai ba a goye ba
{alubale: gasa
Gajeru: mara tsayi, guntaye
Sauti : amo ko }ara na wani abu
Na ~oye: suna ne da ake bai wa mai fa]in tambaya da amsar wasan kacici-kacici basira
La}abawa: sanyawa wani abu suna
Rumbun kalmomi = tarin kalmomin da mutum ya iya (ma'ajiyar kalmomi)
Jimloli: Akasari Cu]anya = Kwarewa = Zurfafa
cikakkar magana/zance.
mafi yawa (daga abu)
saduwa ta hanyar mu'amala ko hul]a. iya abu ko gwaninta
}ara yawaita abu.

**MATANI (I)**

Mafi yawa daga cikin alummar Hausawa wa]anda suka fi yin wasan kacici- kacici ko cinci - kacici mata ne da kuma yara da daddare ko kuma wani lokaci na daban.
Ana gina wasan ne a bisa irin wasu tubalai kamar haka: amfani da cikakkiyar magana (jumla),
amfani da guntaye ko gajerun magana (zance) na kacici-kacici ta yin amfani da abubuwan da ke tare da su ko cudanya na yau da kullum.

**AIKI I**

(1) Su wa da wa suka fi yin wasan kacici - kacici?
(2) A wa]anne lokuta ne ake yin wasan?
(3) A kan wa]anne abubuwa ne akan gina wasan kacici - kacici?

**MATAN I (II)**

Ma'anar Kacici - Kacici: Kacici- Kacici ko cinci - kacici hanya ce da al'ummar Hausawa kan shirya wasu ‘yan gajerun tambayoyi a cikin hikima Wa]anda suke bukatar a bayar da ma'ana ko amsa nan take.
Kacici-kacici ya rabu zuwa gida uku.

(a) Kacici-kacici mai }alubale (gasa)
Misali, shirin ba ci ba = baba
Takanda ba kashi, ba = kanwa

Tunda daga nesa na ji muryar }anwata = ganga

(b) Kacici - kacici mai sauti/amo;

A nan, akan jero kalmomi ne masu amo ko sauti in ]aya a kuma bu}aci mai sauraro ya fa]a ta bin yanayin sautin misali:

[illin bari ]illin, ]illin na kalloki ma'ana = kaza bari tono shaho na kallanki.Yadda ]illin takan yi ]illin haka ma ]illin takan yi ]illin.

Ma'ana = Yadda kaza takan yi }wannan haka ma }wannan yaka yi kaza

(c) Kacici - Kacici mai malam na ~oye.

A nan, akan sa yaro ne ya ~uya a wani wuri da za a sanya wa suna malam na ~oye. Yara kan taru a wani gefe su yi layi daga cikinsu wani zai dinga zuwa wajen Malam na ~oye yana gaya masa tambaya da amsarta, sai ya dawo ya rika tambayar sauran yara.

Kacici-kacici na da muhimmanci domin yana;

sanya wa yara jimirin hakuri;
ilmantar da yara sanin abubuwa iri daban - daban;
}ara wa yara dabaru da hikimomi;
suna }aruwa da hanyoyin }warewa da harshe;
zurfafa tunaninsu wajen iya rabe abu mai kyau da mara kyau;
}ara yawaita rumbun kalmominsu.
yana baiwa yara nisha]i.

**AIKI**

(1) Kawo ma'anar kacici - kacici.
(2) Kacici - kacici iri nawa ka sani?
(3) Kawo yadda ake yin wasan kacici - kacici mai }alubale.

**AIKIN GIDA**

1. Su wa da wa ne suka fi yin wasan kacici - kacici? Kuma a wasu lokuta ne aka fi yin wasan?
2. Wasu tubalai ne ko ginshikai ake gina wasan kacici - kacici?
3. Mene ne ake nufi da kacici - kacici? Iri nawa ne ka sani na wasan kacici - kacici?
4. Jero guda 4 daga cikin muhimman kacici - kacici?

**TA{AITAWA**

A wannan kashi, gaba ]aya an yi }o}arin gabatar muku da matsayin kacici - kacici a cikin adabin gargagiya da ma gurbin da Hausa take da shi a cikin tsarin karatu na 6-3-3-4. Daga nan ne aka kawo matakan nazari wa]anda daga bisani aka sanya su a cikin matani na ]aya da matani na biyu. Kowane matani a }arshensa akwai ayyuka wa]anda ake bukatar ]alibi ya amsa su.

**MANAZARTA**

Abdulkadir Dangambo, Sa'adu Zungur (1984). *Rabe-Raben Adabin Hausa da Muhimmansa go na yawan Rayuwar Hausawa*. Triumph (gidan) Sa'adu Zungur Kano

IbrahimYaro Yahaya da wasu, (1992). *Darussan Hausa Don Manyam Makarantun Sakandare suka amin* (littafi na I) University Press PK, Ibadan

Mamusu Aminu. Kano Nigeria *Kacici - Kacicin* Hausa Zurinriya Recording and wannan Publishing Company dabi 'a

## KASHI NA 8: MATSAYIN CAMFE-CAMFE GA ALU'MMAR HAUSAWA

### GABATARWA
Bayan mun yi nazari kan camfi. A wannan kashi za ka yi nazari kan matsayinsa ga ummar Hausawa. Wato sanin yadda Hausawa suka ]auki camfi a al'adarsu.

### MANUFA
Manufar wannan kashi ita ce ka san cewa duk irin munin da ake gani a camfi za a iya mfani da shi a koyar da ]abi'a tagari.

### MATAKAN NAZARI
Za ka tabbatar cewa wannan kashi an koyar da shi sosai domin fahimta. Dole ka yi bayani gamsasshe domin duk abin da ka koyar ya sa mu fahimta. Don haka dole ka tabbata an gane.

### MATSAYIN CAMFE-CAMFE GA HAUSAWA
Camfi, kamar a bayanin da ya gabata, wata hanya ce ta yarda da abu cewa idan kaza ya faru shi zai yi sanadiyyar kaza. Wannan dabi'a ga al'ummar Hausawa ta zamo kamar ciwo a wani lokaci, amma an samu sau}i kadan wajen maza. Mata kuwa har yannzu akwai wannan dabi'a. Camfi kamar matsayin addini yake ga jahilin mutum. Wato, wannan dabi' a wadda ba an koya wa mutane ba ne, sun tashi sun ga iyaye da kakanni da abin da suka amince da shi ne. Saboda haka su ma sun hau sun zauna ya zamo kamar sun gada. Wannan shi yasa yake da }arfin gaske wajen aminta. Mace ce za ta ga cewa ]anta yana yawan rashin lafiya. Sai mahaifiyarta ko mahaifi ya cc ta kai yaron wajen malam wane ko boka. Bayan ta je ya ba ta magani, }ila a dace yaro ya sami sau}i. Bayan wani lokaci rashin lafiya ya dawo. Idan ta koma ya ce ga laya ta daura masa a wuya ko }ar}ashin wajen kwantar da shi, haka din za ta yi.
Matsayin camfi ya samo asali ne daga dace da samun sa'a wajen biyan bukata. Wannan  na iya }arfafa su wajen al'umma musamman mata. Don haka al'ummar Hausawa dole su nemi ilmi domin ya}ar bokaye.

### AIKI
Wane matsayi ne camfi ke da shi ga Hausawa?
Hausawa masu biyayya ne ga manya. Shugabannin addini su ya kamata su }ara zage dantse su yi wa'azi. Sannan a makaranta da masallatai da mujalisu a }ara tilasta iyaye su kai yaransu makaranta sannan kuma su daina zuwa wurin bokaye. Muddin ba haka aka yi ba muna nan gidan jiya. Ya kuma kamata mata tsofaffi masu zuwa gidajen `yan mata da aka yi wa aure suna koya masu karatu shi ma a shawo kansa. Domin suna cikin masu ba su irin wa]annan shawarwari na zuwa gun boka da kuma camfe-camfe kamar yadda aka fada can baya. Kasancewar manya (tsofaffi) ke ri}e da wannan dabi'a shi ya taimaka wajen ha~akarsa. Saboda haka
wannan shi zai shawo kan al'amarin.
Haka kuma ya zama wajibi a }arfafa ilmin addini domin sanin matsayin camfi ga al'umma. Alal misali, Addinin Musulinci ya yi bayani mai }arfi cewa camfi haramun ne. Imani da camfi fita ne daga Addinin Musulunci. Duk musulmin da ya ji haka ba ya da wani za~i sai guda biyu. Ko dai ya bari ya tabbata Musulmi ko ya ri}e ya fi ta cikin Musulunci.
Saboda haka duk da cewa camfi na da matsayi mai }arfi, wato ri}onsa da tsofaffi w]anda ba su da ilmi suka yi, yana bazuwa ga 'ya'ya da jikoki. Dole malaman addini da masu ilmi cikin al'umma su tashi tsaye su ya}e shi.

Duk da rashin kyawonsa, akwai wasu abubuwa kyawawa da camfi kan tilasta jama'a su yi ko su bari. Alal misali, akwai inda camfi ya nuna cewa duk mai zama kan dokin kofa aljannu za su banka]e shi. Idan aka yi la'akari za a ga cewa wannan ana yi wa yara tarbiyya ne domin su yi aiki da hankali.

### AIKI (II)
Ta wace hanya za a rage yarda da camfi?

**AIKIN GIDA**

1. Wane lokaci Hausawa suka fi amfani da camfi?
2. Wane ra'ayi bokaye da tsofaffi ke da shi game da camfi?
3. Wane wuri camfi ya fi yawa? Maraya ko }auye?
4. Ko malaman addini na iya taimakawa su rage bazuwar camfe- camfe?
5. Rubuta wani camfi ]aya da ka sani.

**TA{AITAWA**

Wannan kashi na koyar da abubuwa masu bu}atar Hausawa su fahimta domin in bai dace da addininsu ba su bari. A darasin an gane cewa camfi yana da tasiri a al'adar Hausawa, amma an kuma fahimci cewa ya yi karo da addinin musulinci wanda ya hana shi.

**MANAZARTA**

Daura, B. Isa Y, and Madauci, I. (1968) *Hausa Customs.*, Zaria: Northern Nigerian Company.
Madabo, M. H. (1979) *Ciniki da Sana'o'i a {asar Hausa*, U. K.: Thomas Nelson (Nigeria) Limited.

**KASHI NA 9: JIGOGIN LITTAFAN ZUBE DA MUHIMMANCINSU A TARBIYYA**

**GABATARWA**

Littafan zube na Hausa su ne littafan da aka rubuta labarai a cikinsu. Labaran da ake nufi kuwa su ne labarai masu tsawo wa]anda kan }unshi mutane da abubuwan da sukan yi na yau da kullum iri-iri. Tsawon irin wa]annan labarai ba abin da za a iya iyakan cewa ba ne. Gajartarsu kuma ba ta hana a sami cikakken bayani akan sa}on da marubuci ke son ya wanzar ba.

A wannan sa}o za a yi amfani ne da mutane daban - daban da halayensu iri daban daban da abubuwan da suka yi ko aka yi musu su ma daban - daban. Daga bisani irin wa]annan labaru sukan kammalla yadda za a iya cewa sun isar da sa}on da suka so bayarwa. Wa]anda aka yaba da su a irin wa]annan labarai, har aka buga su a matsayin littafai don mutane su karanta su sami nisha]i, kuma su }ara wayewa da rayuwa, su ake kira littafan zube.

**MANUFA**

Manufar wannan kashi ita ce a yi bayani a kan jigogin littafan zube. Ana fatar cewa }arshen wannan darasi za ka fahimci abin da ake nufe da littafan zube ka kuma san abin da ake nufi da jigo. Daga nan ne ake sa ran ka san ire-iren jigogin littafan zube ta yadda za a iya tantance su. Har wa yau ana son ka kasance idan ka karanta labari kana iya cewa ga jigonsa, watau ba sai wani ya bayyanna maka ba. Ana fatar abin da za ka koya a karance ya yi maka amfani a rayuwarka.

**MATAKAN NAZARI**

Mataki na farko don nazarin jigogin littafan zube shi ne ka kasance ka ta~a karanta wasu littafai na Hausa masu shigen labari irin wanda aka bayyana a sama. Wannan kamar sharar fage ne.

Daga nan sai ka yi }o}arin tuna abubuwan da ka karanta a wa]annan littafan kana daganta su da abubuwan da ake magana a kansu a nan. Ya kamata ka san littafai na zube a }alla uku da kyau da kyau domin ka mori wannan darasi sosai.

**MA'ANAR JIGOGI**

Littafan zube Wa]anda ake magana a kansu a nan }agaggun labarai ne. {aggaggun labarai su ne labarun da mutum ya }ir}ira a zuciyarsa ya rubuta su ba tare da abin ya ta~a faruwa ba. Irin wa]annan labaru kamar yadda aka ambata can baya ba su da kayyadadden tsawo. Gajartarsu kuma ba ta cuta wa ingancin labari ba.

A yayin da masana ilmin adabi suka karanta littafi sukan tantance ma}asudin abin da littafin ke magana a kansa. Watau idan da za a ]auki ~angarorin rayuwa iri-iri ko wane ~angare ne na rayuwar ]an Adam za a ce wannan littafi ya fi }o}arin bayyannawa. Wannan ~angare na rayuwar ]an Adam da littafi ya yi }o}arin bayyannawa shi ake kira jigo. Jigogi sun bambanta daga littafi .zuwa littafi. Kowane littafi kuma dole ne a yi nazarinsa a tsanaki kamin a iya tantance jigonsa.

**AIKI I**

1. Me ake nufi da littafan zube?
2. Me ake nufi da jigon littafi?

ldan aka ]auki soyayya za a ga cewa wannan jigo ya fito a *So Aljannar Duniya* da *Mallakin Zuciyata* .

Idan kuma aka ]auki jaruntaka za a same ta a littafin *Iliya [an Mai {arfi* da kuma littafin *Gan]oki* na Bello Kagara. Idan ana so a ci karo da raha a matsayinta na jigo sai a duba littafin *Ruwan Bagaja* na Abubakar Imam. Haka za a sami tarbiyya a matsayin jigo a littafin *Nagari Na Kowa*.

Wani lokaci za a iya tararwa cewa tantance jigon littafi ba abu ba ne mai sau}i. Idan mutum ya ]auki littafin *Jiki Magayi* zai iya cewa jigonsa soyayya ne, idan an yi la' akari da wasu abubuwa da suka faru a littafin. Amma kuma idan aka }ara dubawa sai a ga nema ma kan iya zamowa jigon wannan littafi. Har wa yau kuma ana iya cewa fansa ma tana iya zama jigon wannan littafi. Don haka a galibin littafai akan samu jigo ]aya muhimmi wanda ya bazu a littafin gaba ]aya. Idan aka ]auki littafin *So Aljannar Duniya* ana iya cewa }addara ce jigonsa ta wani fannin, watau matar mutum kabarinsa. Haka kuma sai a ga kamar halin rayuwar Fulani, wato fulako shi ne jigon. Idan aka dubi littafin *Shaihu Umar* na Abubakar Tafawa Balewa sai a ga nan ma }addara ce jigonsa amma kuma nema ma tana da nata rabon. To, a haka shi ma littafin *Jiki Magayi* za a iya cewa }addara ce jigonsa.

Sha'anin gane jigon littafi ba abin wasa ba ne a fannin nazarin littafan zube. Sanin jigo yakan taimaka }warai wajen mutum ya fahimci labari da irin salon da aka bayar da shi a ciki. Jigon littafi na da dangantaka ta }u}ut da irin taurarin da aka za~a da sauran gogayen littafin. Haka kuma yana da tasiri a kan irin harshen da marubuci zai yi amfani da shi da kuma yadda za a yi warwarar labarin.
Idan jigon littafi soyyaya ne za a ga ana amfani da harshe mai da]in lafazi, za a ga wasu gogayen halayyarsu ta dace da a so su wasu kuma a }i su. Za a ga gogaye na shiga halin farin ciki da na ba}in ciki da kewa da tausayi da zautuwa.
Idan alal misali jigon littafi jaruntaka ne, za a ga ana amfani da harshe mai tsauri. Za a ga gogaye suna shiga ha]ari da abubuwa masu sa tsigar jikin mutum ta tashi. Wata kila a shiga halin da ma sai an zubar da jini. Irin wa]annan abubuwa za a same su a *So Aljannar Duniya* (na soyayya) da kuma *Gandoki* (na jaruntaka) alal misali.

**AIKIN GIDA**

1. Wa]anne abubuwa ne za su iya zama jigogin littafan zube na Hausa?
2. Mene ne ya sa jigo yake da wahalar tantancewa idan ba an karance littafi duka ba, kuma a tsanake?
3. Wa]anne abubuwa ne jigon littafin zube ke da dangantaka da su ta kukut?

**MANAZARTA**

Zarruk Rabiu Mohd. et. al. (1987) *Sabuwar Hanyar Nazarin* Hausa. University Press Limited, Ibadan.

**KASHI NA 10: BITA**

**GABATARWA**

Adabi, kamar yadda aka yi bayani a kasusuwan da suka gabata fanni ne na Hausa mai fa]in gaske. Masana da dama sun kawo misalai masu yawa a kan ~angarorin adabi da aka riga aka nazarta a wannan kashin. To ba sani adabin ne kawai muhimmi ba a nan. Sanin yadda za a koyar da shi ma yana da nasa muhimmancin.

Aikin koyarwa ba kamar sauran ayyaukan yau da kullum ba, aiki ne mai bukatar dole sai an nusar da kai yadda za ka gudanar da shi. Saboda yana da hikimomi da dabaru irin nasa Wa]anda sai an bi su sannan koyarwa ta sau}a}a, kuma koyo ya inganta. Daga kashi na ]aya zuwa na tara a cikin wannan fasali an ta~o ~angarori daban daban. Mafi yawan ~angarorin sun yi magana ne a kan yadda za a koyar da wani nau'i na adabi.

A wannan kashin za mu yi bita ne a kan fasalin gaba ]aya tare da fito da muhimman abubuwan da kowane kashi ya gabatar.

**MANUFA**

A }arshen wannan kashin ana sa ran za ka iya:

1) fa]in muhimman hanyoyin koyarwa tare da kawo bayani a kan kowane;
2) amfani da wasu daga cikin hanyoyin koyarwa wajen koyar da:
    a) Adabi,
    b) [ab'ia kyakkyawa
3) yi wa ]alibai jagora wajen za~in littattafan da za su karanta domin neman }arin bayanni a kan abubuwan da wannan fasali ya gabatar.

**MATAKAN NAZARI**

Kafin ka nazarci wannan kashin sai ka tabbatar da cewa ka nazarci kasusuwan da ke cikin wannan fasali. Ba kuma nazarin kasusuwan ne kawai muhimmi ba. Ana bukatar sai ka aiwatar da duk ayyukan da aka ba ka a cikinsu da kuma bayar da duk amsoshin tambayoyin da aka yi maka.

A yayin da ka fara nazarin wannan kashi ana so ka yi ta tunanin cewa ga ka tsaye a gaban ]alibai kana koyar da su.Yin hakan zai taimaka maka wajen }ara fahimtar koyarwa da matsalolinta.

**SABABBIN KALMONI**

**Bita:** sake nazarin wasu fannoni na ilmi da ka riga ka koya. A yayin da ka kammala nazarin wani kashin, sai kuma ka dawo kana }ara karantawa, watau za a iya cewa kana yin bita.

**MATANI**

An yi bayani a kan hanyoyin koyarwa guda hu]u. Idan ba ka manta ba wa]annan hanyoyin sun ha]a da:
hanyoyin koyarwa ta wasanni;
hanyoyin koyarwa ta gani da ido;
hanyoyyin koyarwa ta yi-da jiki;
hanyoyin koyarwa ta lacca.

Bayan kawo bayanin kowannensu an ci gaba da }alailaice yadda za a yi amfani da kowace daga cikin hanyoyin wajen koyar da wasu ~angarori na adabi da ]abi`un Hausawa.

**AIKI I**

1) Ta yaya za ka yi amfani da ]aya daga cikin hanyokin koyarwa guda hu]u wajen koyar da:
    a) salon magana
    b) ]abi`u
2) Kawo ma'anonin wa]annan;
    a) gani da ido
    b) yi da jiki

Shi kansa adabin da aka yi ta yin maganganu a kansa a cikin wannan fasalin da sauran fasalolin, an yi }o}arin a kawo misalai a kansa.

A cikin adabin gargajiya, misali; an ta~o bangarorin da suka ha]a da;
Wa}o}i da maka]an Hausa
bukukuwa
wasanni na yara da wa}o}insu
aure da mutuwa
azanci da hikima da kuma fasaha
tumasanci da ro}o da zambo da sauransu.

Daga irin misalan da aka bayar an tabbatar da cewa kowane rukuni na adabin da aka ambata an kawo aka misali guda ]aya.
Da aka tabo adabin zamani a nan ma an kawo misalai daga littattafai daga kowane rukunin. An kawo misalai daga rubutun zube da rubutattun wa}o}i da kuma wasan kwaikwayo.

**AIKI II**

1) Rubutaccen adabi shi ne ake kiran sa adabin zamani. Kawo rabe- rabensa da kuma misalai daga kowane kashi.
2) Adabin baka shi ne ake kiran sa adabin gargajiya. Kawo hu]u daga rabe-raben kuma ka ba da misalai daga kowane.

**AIKIN GIDA**

Yi bayanni dalla-dalla akan yadda za ka yi amfani da kowace ]aya daga cikin wa]annan hanyoyin na koyarwa wajen koyar da gabatar da jawabi a rubuce. Hanyoyin Su ne:

Ta gani-da-ido
Ta yi-da-jiki
Ta lacca
Ta wasanni

**TA{AITAWA**

Wannan kashin an yi bitar kashi na ]aya zuwa na tara da ke cikin wannan fasali. Ka yi nazarin hanyoyin koyarwa da kuma yadda za a yi amfani da su wajen koyar da adabi da kuma ]abi`u.

**MANAZARTA**

Garba. A. (1998) *Sabuwar Hanyar Koyar da Hausa.* Kano: Triumph Publishing Company.
Institute of Educ. ABU, Zaria (1979) *Karatu da Rubutu cikin Harshen Hausa:* Lagos: Thomas Nelson (Nig) Limited

## FASALI NA 11: DABARUN KOYAR DA HARSHE

### KASHI NA 1: DABARUN KOYAR DA HARSHE

**GABATARWA**
A wannan kashi, za mu tattauna dabarun koyar da Hausa ta hanyar yin amfani da kayan aiki. Koyarwa ta hanyar yin amfani da kayan aiki ta fi sau}a}a fahimta. Za a duba manyan rassan nazarin Hausa guda uku, a ga yadda dabarun koyarwa kan taimaka a fahinci darasi yadda ya kamata.

**MANUFA**
Manufar wannan darasi ita ce a nuna wa ]alibi wa]annan abubuwa dangane da koyar da Hausa ta hanyar yin amfani da kayan aiki:

(a) akwai dabarun koyar da Hausa ta hanyar yin amfani da kayan aiki.
(b) dabarun koyarwa da kayan aiki sun fi a koya haka nan ba wani taimako.

**MATAKAN NAZARI**
(i) Za a gabatar da kayan aiki, a kuma nuna maka yadda ake amfani da su wajen koyarwa.
(ii) Za ka yi dukkan ayyukan da aka ce a yi a wannan kashi.

**SABABBIN KALMOMI**
]alibi zai san ma'anar wa]annan sababbin kalmomi kamar yadda ake amfani da su a fannonin nazarin Hausa daban-daban. Kalmomi su ne: fannin furuci; har da; hoto; kwali; murya; sauti (saituka); tufafi; zahiri.

**RASSAN NAZARIN HAUSA**
Hausa tana da manyan rassa na nazari guda uku. Rassan su ne, nahawu da adabi da al'adu. Kowane daga cikin wa]annan manyan rassa, akwai dabarun yin nazarinsa ta hanyar yin amfani da wasu kayan aiki na koyarwa. Kayan aikin suna taimakawa wajen koyarwa don samun sau}i da kuma saurin fahimta. Abin lura a nan shi ne, kowane reshe yana da irin nasa kayan koyarwa wa]anda suka fi dacewa da shi. Za mu ]auki wa]annan rassa ]aya bayan ]aya mu ga irin kayan koyarwar da kowane reshe yake amfani da su da kuma yadda ake amfani da su wajen koyarwar.

**KOYAR DA NAHAWU**
Nahawu yana da nasa fannonin amma a nan za mu ]auki fannin furta sautuka mu ga yadda za a koyar da shi ta hanyar yin amfani da kayan aikin koyarwaa na musamman. Za a yi amfani da kayan aiki iri biyu, wato rakoda da kwalaye }anana. Amfanin rakodar shi ne a ]auki muryar furucin dukan sautukan Hausa, wato ba}a}e da wasulla. Amfanin kwalayen }anana shi ne a zana hoton dukan sautukan Hausa a kan kwalayen. Kowane kwali zai ]auki hoton sauti guda ]aya kawai. Malami zai ba da muryar sauti guda don ]alibai su yi, sa'annan ya nuna musu kwali wanda yake ]auke da wannan sauti. Haka malami zai ci gaba da yi sai ya tabbatar an yi muryar kowane sauti, an kuma ga hotansa a kwali. Babu shakka wannan hanya ta fi kowace hanya wajen sau}a}a fahimtar furucin sautukan Hausa da kuma gane yadda suke a rubuce.

**MANAZARTA**

Gusau, S.M. *Dabarun Nazarin Adabin Hausa Kaduna:* Fisbas Media Services.
Ningi, H. 1985. *Jagorar Malaman Makarantun Firamare.* Kano: Triumph Publishing Company.
Salim, B.A. 1985. *Koyar Da Hausa A Makarantun Firamare.* Kano: Triumph Publishing Company.
Zarruk, R.M. 1980 *Siffofin Aikin Koyarwa* lbadan. Oxford University Press.

## DAGA SHAFI NA GABA ZUWA {ARSHE SUN {UNSHI

# AMSOSHIN AYYUKA

**KASHI NA {A`IDOJIN RUBUTU**

AIKI I
Haruffa guda biyar masii ba}a}e bibbiyu su ne: gw,`y, gy; kw, ky, ts

**AIKI II**

**Harafi** shi ne ba}i ko wasali wanda ake amfani da shi don rubuta harshe.

1. Hausa tana da haruffa 33
2. Jadawalin haruffan Hausa

**kalma**

**Daidaita**
Rashin Daidaita

Ba}a}e: b, ~, c, d, ], f, g, gw, gy, h, j, k, kw, ky, }, }w, }y, l, m, n, r, s, sh, ts, t, w, y, ‘y, z
Wasulla: a, i, e, o, u, ai, au,

4. (a) Dokar rubuta haruffa masu ba}a}e biyu
   (b) Duk cikakkiyar kalma ana rubuta ta ita ka]ai.
5. {a'idar kyautata rubutu.. .

**KASHI NA 2: ALAMONIN KYAUTATA RUBUTU**

1. Alama ce kamar haka(,) (fa take nuna dakatawa ta dan gajeren lokaci. .Abdu ya „ . gutsiri burodi, ya sa a baki.
2. Sunayensu da ka
   Ayar Motsin rai
   Aya mai ruwa

1. [ansandan ya ce, 'wa]anne kaya naka ka ba ni?.Abdu ya ce, kai dada wasanni.'

**INSHA'I**
2. Wa]anne kayayyaki aka ba wa Abdu? An ba Abdu kayayyaki kamar haka: wando da riga da takalmi da kuma hula.
3. A wurin da ke da itatuwa da ciyayi, ruwa ba ya iya gudu sosai balle ya zaizayi }asa.

**AIKIN GIDA**
1. Wa}afi yana zuwa a cikin jumla ko sassanta, yayin da aya ke zuwa a }arshen jumla ko cikar magana.
2. Maza-maza ka tafi gida.
   - Ma}eri yana hura wuta da zuga-zugi
   Abdu yana zane-zane a kan allo.
3. Wayyo Allah! Ku taimake ni.
4. Kash! Na manta shi a gida:
   Kaico! Labarin Bai mana da]i ba.
5. Aya alama ce ta tsayawa, a inda aka samu cikar magana. Ayar tambaya kuwa alama ce da take nuna cewa jumlar da ta gabata tambaya ce.

**K A S H I - 1 1  N A  3 :  M A ' A N A R  I N S H A ` I**

**AIKI 1**

Rubutun muhawara ya bambanta da na labari ta wa]annan fuskoki:

1. dogewa kan ra`ayi
ii.kariya ta hujjojinka
iii rashin amfani da karya
iv rashin yin kari.

Rubutun labari kuma, ga yadda zai zama:
i.Sanar da wani abu da ba a sani ba (kan labarin)
ii babu bukatar kariya daga wannan ra`ayi
iii. Ana iya kari (karya cikinsa).

**AIKI 11**

Rubutun siffantawa:
1: sanin abu ko ganinsa shi ke sa siffanta shi
2. babu rubuta adireshi a hannun hagu
3. babu rubuta zuwa ga
4. babu kammalawa da 'wasalam' ko (ka huta lafiya).
5. kan bu}aci amsar wasi}a,
6. siffanta ba ya bu}atar amsa

**RUBUTUN WASI{A**

1. ana bu}atar adireshi a hannun hagu
2. **ana rubuta `zuwa ga' ko** kuma 'mai girma' idan ta kamfani ce.

**INSHAI**

3. kammalawa da 'wasalam' ga ta aboki da kuma 'ka huta lafiya' ga ta kamfani.
4. ana bu}atar amsa ko ga ta aboki ko kuma ta kamfani.
5. Bu}atar jigo ko ma}asudi; ko na gaisuwa ko a neman aiki.

**AIKIN GIDA**

1) Matsayin insha`i a adabin Hausa shi ne rarraba rubutu kashi-kashi. Akwai na muhawara da na labari, da na siffanfawa da kuma rubutun wasi}a.
2) Muhawara shi ne rubutun gardama wato kariya ga ra`ayi
3) ta hanyar labari.
4. I, ana iyawa ta hanyar kawo surorinsa ta yadda mai karatu zai iya ganewa.
5. i) rubuta adireshin mai rubutu a saman hannun hagu
   ii) rubuta gaisuwa da kuma 'zuwa ga'
   iii) rubuta sa}o ko ma}asudin wasi}a.
   iv) }arewa ko kammalawa sai an jima' ko `sai a ji daga gare ka.
   v) rubuta suna na farko kawai.

**KASHI NA 4: INSHA'I (LABARI, SIFFANTAWA, MUHAWARA, WASI{A)**

**AIKI 1**

i) Ginannu ne masu soraye da kalankuwa, an kuma shafe su da zarta da makuba. Kowane gida yana da dakali.
ii) Ana sako dabbobi, ana kuma gana yin, shuka da damina.
iii) Fara jin yunwa.
i) Masallacin Juma'a.
ii) marina.
iii) kasuwa .
iv) 'yar dole.

**KASHI NA 5: SHIFTA DA INSHA`I**

a. Wanda bai bari ba ya ji hoho
b. Waddaren gulya'e .

ii) Ya dau da sauri.
iii) Sannu a hankali ko yau da gobe.
iv) Ya umurce su, ya ba su umurni.

**KASHI NA 6: RUBUTUN JAWABI MAI LINZAMI**

**AIKI 1**

1. Abin da ake nufi shi ne rubutu mai }ayyadadden lokaci ko kalmomi da sauransu.
2. Rubutu mara walwala.

**AIKI II**

Ta hanyar ba da umarni cewa a goyi baya ko kada a goyi baya wajen rubutu kan wani abu.

**AIKIN GIDA**

1. Magana ko rubutu wanda ya }unshi bayani kan wani abu.
2. Idan an }ayyade wa mai rubutu yawan kalmomin da zai yi amfani da su.
3. Rubutu mai linzami yana da amfani ta wani ~angare yana kuma da rashin amfani ta wani ~angaren
4. Takura.

**KASHI NA 7: RUBUTUN SHIFTA DA INSHA'l**

**AIKI 1**

1. Insha'i shi ne tsara rubutu mai kyau a kan wani batu.

**AIKI II**

1. Da akwai Insha'i na labari
Insha'i na wasika
Insha'i na bayani da kuma
Insha'i na muhawara.

**AIKIN GIDA**

1. a. Insha'i na labari.
b. Insha'i na jawabi.
c. Insha'i na muhawara.
d. Insha'i na wasi}a.

2. Gabatarwa - gajeren bayani da aka yi game da batu da

3. Za a yi insha'i a kansa. Ma}asudi, Ainihin zantukan da suka shafi batun da za a yi insha'i a kansa.
Kammalawa - Gajeren bayani na ta}aitawa da ake yi a kan batu da aka yi insha'i.

**KASHI NA 8: DABARUN RUBUTA JAWABI**
**AIKI I**

1) Sakin layi shi ne rubuta bayani daki-daki wato wani na bin wani
2) Alamomin tsai da magana (su ake kira alamomin rubutu) wasu alamomi ne da ake amfani da su wajen kyautata rubutu da sakin karatu da kurna fitar da ma'ana.

**AIKI II**

1) A rubutun jawabi mai linzami ana bin duk dabarun rubuta jawabi, a rubutun jawabi sake-ba- }a'ida

ba a cika sharu]]an rubuta jawabi.
2) Gabatarwa,
Gundarin jawabi
Kammalawa

**AIKIN GIDA**
1) Amfani da gajerun jumloli sakin layi
Alamomin tsai da magana za~en kalmomin da suka dace
bin }a'idojin rubutun Hausa
2) Insha'i
3) {afiya
4) Shi ne mai jawabi ya bayyana tunaninsa kani na bin wani, kada ya ri}a maimaita bayanan da ya yi a baya.

**KASHI NA 9: {IR{IRO JAWABI**

**AIKI I**
A wajen gabatar da jawabi ana bu}atar a fa]i muhimman abubuwan da jawabi ya }unsa. Wato dai a yi magana daidai misali.

**AIKI II**
Mu, Muke, Mun.

**AIKIN GIDA**
Mai girma Gwamna da sauran 'Yan Majalisar Sarki, Manyan ba}i da sauran jama'a, assalamu alaikum. Mun taru ne a nan yau domin mu }addamar da bukin hana shan }waya da sauran miyagun magunguna. Mun lura cewar a wannan gari namu kullum ita wannan matsala ci gaba take yi. Mun samu bayani cewar samari da 'yan mata su ne suke aikata wannan mummunar ]abi'a. Saboda haka muna umartar iyayen yara musamman matasa su lura da tarbiyyarsu. Dukkan wanda aka kama zai ]an]ana ku]arsa. Ba za mu samu ci gaba ba har sai yaranmu sun daina wa]annan mumunan ]abi'u.
Daga }arshe muna sanar da iyaye cewar tarbiyar 'ya'yansu a kansu take. Allah ya mayar da kowa gidansa lafiya, amin.
1. Mu, mun, muke, muna
2. Rubuta jawabi yana da }a'idoji, kamar haka:
3. Bu]ewa
Sa}o
Za~en kalmomi
4. Gabatarwa, Ma}asudi, Kammalawa.

**KASHI NA 10: BITA**
1. {a'idoji uku na jawabi su ne:
   (a) Bu]ewa
   (b) Gundarin sa}o
   (c) Za~en kalmomi.
2. {afiya
3. Jadawalin haruffan Hausa:
Ba}a}e: b, ~, c, d, ], f, g, gw, gy, h, j, k, kw, ky, }, }w, }y, l, m, n, r, s, sh, ts, t, w, y, ‘y, z
Wasulla: a, i u,o,e,ai,u
4. Aya alama ce mai nuna cikar Magana. Ita kuwa ayar tambaya, alama ce mai nuna cewa zancen da aka yi tambaya ne.
5. Jeranta tunani a tsarin rubuta jawabi shi ne mai jawabi ya bayyana a tunaninsa baya ]ayan ]aya ba tare da ri}a maimaita bayanan da suka gabata ba.

**KASHI NA 1: BA{A{E**

**AIKI I**
A Hausa akwai gwaurayen ba}a}e guda ashirin da uku, kuma ana kiransu gwauraye ne saboda ba}a}e ne }waya ]ai-]ai wa]anda ko a magance ko a rubuce za a tarar ]ai-]ai ]in suke.

**AIKI II**

A Hausa akwai ba}a}e guda talatin da daya, su ne: j,
w, ts, y da hamza da kuma fy gy ky gy ky ky gw kw kw da.'y.

**AIKIN GIDA**

(1) Za a iya karkasa ba}a}e zuwa gida biyu watau gwaurayen ba}a}e wa]anda suke }wara dai-dai irin su: b, , c, d, , f, g, h, j, k, l, m, n, r, s, sh, ts, t, w, y, z da hamza. Kana kuma akwai kuma ba}a}e masu goyo wa]anda aka yi musu karin wasu ba}a}e inda sukan ha]a su zama ba}i guda mai sauti guda misali: gy, fy, ky, gw, kw, kw, 'y.

(2) Babban abin da ya bambanta nau'o'in ba}a}e shi ne kashi na farko furuci guda-guda ne tun asali kuma a gudan ake furta su. Su kuwa tagwayen ba}a}e ko masu goyon furucin ba}i bibbiyu ne aka gwama su aka tayar da furuci guda.

(3) Kalmoni biyar masu nuna ba}a}e masu goyo su ne:
Gya]a, }wallo, }yaure, gwauro, `yanci.

(4) Akwai ba}a}e ashirin da hu]u a wannan jumla.
"Rashin sani ya ]arar ma rashin tsaba ~arna ko da ta gya]a ce."

**KASHI NA 2: WASULAN HAUSA**

**AIKI I**
Gwauron wasali shi ne wasali }wara guda da ake furta shi shi ka]ai ba tare da an ha]a shi da wani ba. Sa'annan kuma gwauron wasali ya kasu zuwa nau'i biyu dogaye: aa, ee, ii, oo, uu da gajeru: a e, I,o,u.

**AIKI II**
Tagwan wasali shi ne wasalin da wasulla biyu gwauraye masu cin gashin kansu suka ha]u suka tsirar da shi ta hanyar furta su a fasali guda. A Hausa muna da guda biyu: 'au' da `ai'.

**AIKIN GIDA**

1. A Hausa akwai wasula guda goma-sha-biyu su ne: a, e, i, o, u, e, aa, ee, ii, oo, uu kuma au da ai.
2. Gwauron wasulla su falen ]aya ne watau }waya dai-dai ne yayin da aka zo furta su, kana kuma akwai rnasu nuna tsawo watau wa]anda akan dan ja su yayin furuci misali aa oo, amma su kuwa tagwayen wasulla ne nau'i biyu masu zaman kansu kan ha]u su tayar da su, misali au da ai.
3. Kalmomi 5 masu nuna auren wasulla su ne:
(a) aure (b) Hausa (c) Daura (a) taiki (e) aiki
4. Kalmoni biyar masu gwauron wasulla su ne: kaadaa, daka baa saa sana' a.

**KASHI NA 3: MANAR KALMA**

**AIKI I**
Kalma ita ce furuci guda mai dun}ulalliyar ma'ana da za a iya tantancewa walau a magance ko a rubuce. Kalmomi watau jam'in kalma sun rarrabu da dama a tsarin nahawu, akwai suna, aikatau da bayanau da sifa da sauransu.

**AIKI II**

Abubuwa 3 ne ke da matu}ar muhimmanci wajen gane kalma, wa]annan abu uku su ne.

a. Tsawon wasali
b. Tsarin ga~a
c. Karin sauti

**AIKIN GIDA**

1. Kalmomi uku masu kama da juna da tsawon wasali ke bambanata su su ne.

| | | |
|---|---|---|
| Dooka | - | sunan gari |
| dookaa | - | umurni da aka aje a kan wani abu |
| gaaraa | | kaya da ake rako amarya da su |
| garaa | | }waro da ke taushe itatuwa ko katako kuma yana zama a suri |

1 234
tun/fa/filya BWB BW BW
1234
al/ma/ji/ra WB BW BW BW
1
ja BW
1
Y[i] BW
12
ja/ki BW BW
12
sar/lci BWB BW

3. kalmomi 5 tare da karin sautinsu

| | |
|---|---|
| fara | ks (kwaro mai ~arna) |
| kazanta | k sk s |
| kafinta | s s k |
| ayaba | k k k |
| masinja | s S |

4. 1
Ga/daa - BW BWW kadarkon da mota ko abin hawa kan bi
12
Gaa/daa BWW BWW mutum ya gaji abu
12
ru/ga BW BWW bukkar fulani
12
ruu/gaa BW BWW gudu
12
Ga/doo BW BWW - makwanci
1 2
Gaa/doo BWW BWW- mallakar abu daga mahaiti ko 'yan uwa

**KASHI NA 4: RABE –RABEN KALMOMI**

**AIKIN GIDA**

(1) a. Sunan yanka - Idi, Tani, Ingila, Katsina, Giwa.
b. Suna gama-gari - MaIlam, Allo, Jaka, Alkalami.
c. Suna tattarau - Kungiya, garke, Tawaga.
d. Gagara-kirga - Kasa, nono, madara.

(2) a. Ailcatau so - karba - Bala ya bugi jaki. Kare ya ciji yaro. Kaza ta ja zalcara. b. Aikatau Id-karba. Gari ya kafu. Dalibi ya kintsu. Shugaba ya kidime.

(3) Bayanau - Kare ya fita a guje. Sanyi ya kama sosai. Aji ya cika ainun.

(4) Sifa - Yarinya baka ta mutu. Musa ya auri mata gajera.

**KASHI NA 5: GA|AR KALMA A HAUSA**

**AIKI I**

1. a) kashi 2) gan)
kashi I) ga ) ganga
kashi 2) kan)
kashi 1) ge ) kange
c) kashi 1) ko )
kashi 2) gin) xc'gin
d) kashi 1) go )
kashi 2) gan) gogan

2. a) kashi na daya kuku, kaka, keke. koko, sisi, soso b) kashi ma biyu:
kankan_ (sQsol c-ar c-an (kamar

**AIKI II**

1. Sa (bajimi, namijin saniya) Wa (na gaba da mutum wajen haihuwa) shi (wakilin suna na mutum na uku) ki (nuna rashin yarda) ci (sa a baka zuwa ciki) shaa (sa abu mai ruwa a baka zuwa ciki ) kai (mutumin da ake ma' ana da shi)kwai (kokon da kaza kan harfi danta a ciki) sawu (takon kafa) yau (ranar da ake ciki)
2. Nan (ba nesa ba) can (ba kusa ba) war (kamar; duba war haka ) san (sani) kar (kada) kash (alamar jin kataici) bar (daina).

**AIKI III**

1. Kai mutum ya iya nazarin ga~a ya kamata ya san sigogin sautukan .Hausa, *ya* san wasula da ba}a}e da ire-irensu.
Ta~aragaza - aikin rashin kimtsi/hankali; katankatana - yin abu ba kan gado; tanta}washi - ~argo; kwatankwaci - misalin; amisuwa - amai
2 Ga~a iri biyu ce dangane da wasalin }arshe, da gajeriya da doguwa.
3 Rufaffiyar ga~a ke nan.
4. A'a, idan aka ga ga~a wadda ta fara da wasali akan ]auka ta fara ne da ba}in hamza. Shi kuma ba}in hamza ba a jin sautinsa.

**KASHI NA 6: SAIWA DA [AFE-[AFENTA AMSOSHI**

**AIKI I**

1. Saiwar kalma ita ce sashen kalma wanda ba ya sauyawa.
2. Ta hanyar lura da abin da ya }are a }arshen kalma, in akwai wasali sai a share wasalin }arshe.
3. Saiwar kalma ba ta jirkita. .

**AIKIN GIDA**

1. damfara
2. maratayi
3. aik aiki .
4. cut macuci
5. bud abudi
6. madubi
7. huda - mahuda
8. jim Jima
9. suya
10. zag.

**KASHI NA 07: [AFA GOSHI AMSOSHIN TAMBAYOYI**

1. Ba
2. Ba
3. Ba
4. Ba
5. Ma
6. Ma
7. Ma
8. Ma
9. Ma
10. Ma.

**AIKIN GIDA**

1. [afa-goshi shi ne abin da ake fara li}awa a farkon saiwar kalma.
2. Ta hanyar gano saiwar kalma.
3. Ire-iren ]afa-goshi sun ha]a da:
   (i) Bature
   (ii) Bafade
   (iii) Baduku
   (iv) Mawanki Manomi
   (v) Mabu]i
   (vi) Maburgi

[afa-goshi na nuna sana'a da mai yin aiki da abin da ake yin aiki da shi da asali da sauransu.

**KASHI NA 8: [AFA -CIKI**

**AIKI I**

1. Saiwar kalma ita ce sashen da ba ya sauyawa a jikin kalma.
2. Ta hayar shafe wasalin }arshe.
3. Ba ta jirkita.
4. [afa-goshi shi ne abin da yake li}e wa saiwa a farkonta.
5. [afa-keya shi ne abin da ya ke li}e wa saiwar kalma a }arshenta.
6. Wannan na zuwa a farko wannan a }arshe.

**AIKIN GIDA**

1. [afa-ciki shi ne abin da yake like wa saiwar kalma a cikinta.
2. Murahu, asake, guragu da sauransu.

3. [afa-ciki na fitowa saiwar kalma a cikinta ne.
4. (a) C
   (b) D
   (c) D
   **(d)** B
   **(e) A**
   **(f) B**
   **(g)** C

   (h) C
   (i) C
   (j) B

**KASHI NA 9: [AFA {EYA AMSOSHI**
**AIKI I**
1. [afa-}eya shi ne ake li}a wa saiwar kalma a }arshenta.
2. [afa-goshi na zuwa ne a farkon saiwar kalma.
3. , a) -ci b) -i-nci c) -nci d) -o
   f) -rta g) -iciya h) -iya

**AIKI II**

Dangantakar da ke akwai guda biyu ne. Na farko shi ]afa-}eya koyaushe yana li}e ne a }arshen saiwar kalma. Na biyu idan an }yale ]afa-}eya shi ka]ai ba kasafai zai ba da ma`ana ba.

**AIKIN GIDA**
1. [afa-}eya shi ne ake li}a wa saiwar kalma a }arshenta.
2. [afa-}eya sai ya kasance yana tare da saiwar kalma yake da kuzari.
3. Ba a samun ]afa-}eya a farkon saiwar kalma.
4. Baka, yarinya, tsohuwa da sauransu.
5. Yana nuna jinsi, }abila, halin mutum da sauransu.

**KASH1 NA 10: B1TA**

**AIKI I**
(1) Kalma ita ce furuci guda mai dun}ulalliyar ma'ana da za a iya tantancewa walau a magance ko a rubuce. Kalmomi watau jam'in kalma sun rarrabu da dama a tsarin Nahawu, akwai suna da aikatau bayanau da sifa da sauransu.
(2) Abubuwa 3 ne ke da matu}ar muhimmanci wajen gane kalma, wa]annan abu uku su ne;
   a – Tsawon wasali

   b - Tsarin gaba

   c - Karin sauti

**AIKI II**

1. Rabe-raben suna
   (a) Sunan yanka - Idi, Tani, Ingila, Katsina, Giwa
   (b) Suna gama-gari - mallam; allo, jaka, alkalami

(c) Suna tattarau - }ungiya, garke, tawaga
(d) Suna gagara-}irga - }asa, nono, madara.

2. Aikatau so-kar~a
   - Bala ya bugi jaki.
   - kare ya ciji yaro.
   - Kaza ta ja zakara.

**AIKIN GIDA**

(1) [afa-}eya shi ne ake li}a wa saiwar kalma a }arshenta.
(2) Misalan ]afa-}eya: Baka, yarinya, tsohuwa.
(3) Ta hanyar gano saiwar kalma
(4) Kalmomi masu ]afa-goshi.

Bature, Bafade, Baduku, Balarabe. Manomi, Mabu]i.

## KASHI NA 1: JUMLAR HAUSA

### AIKI NA I

1. Ha]a kalmomi a kan tsari su ne ke inganta jumloli masu ma'ana da za su dace da yadda masu harshen ke magana.
   Aikatau - ainihin aiki.
   Ma'aikaci - mai aiwatar da aiki
   Kar~au - wanda aiki ya fa]a kansa Lamiri- wakilin mai aiki
2. Audu ya zo - Kande ta dafa abinci Ali ya karanta littafi

### AIKI NA II

1. Za a iya kasa jumlolin Hausa zuwa gida biyu, watau jumla mai zaman kanta da kuma maras zaman kanta.
2. i) jumla sassau}a ita ce mai sau}in fahinta ta fuskar ma'ana ba tare da wahala ba.
   ii) Jumla har]a]]iya ha]aka ce ta jumloli biyu, watau guda cikin guda ta yadda za su harhade wajen ma'ana.
   iii) Jumla sar}a}}iya jumla ce wadda ake samun ma'ana fiye da guda a cikin jumlar:
3. i) Ali ya ci abinci
   ii) Kande ta tafi
   iii) Sani ya zo
   iv) Audu ya mutu
   v) Ladi ta yi aure

**AIKIN GIDA**

1. a. dangin dangantau
   b. dangin bayanau
   c. dangin siffatau
2. Nahawun harshe shi ne yadda tsarin harshe yake, yadda kalmomi suke ha]uwa da juna cikin tsari
3. Jumla ita ce yadda aka tsara kalmomi cikin wata kira mai ma'ana jumla mai zaman kanta da kuma jumla maras zaman kanta. Ita ce kuma mai dangantawa. e) Kawo ire-iren jumlar Hausa, sannan ka ]auki kashi ]aya ka yi bayaninsa

**KASH1 NA 2: SASHEN  SUNA DA RABE-RABENSA**

**AMSOSHI**

**AIKI NA I**

1) Jumlar Hausa ya kamata ta }unshi sashen suna da kuma sashen aikatau.
2) Sashen nahawu zai kasance cewa sassan kalmomi sun taru sun gina jumla mai ma'ana
3) **i)** Mairo ta dafa abinci
   ii) Wani yaro ya shiga gida
   iii) Audu ya wanke hannunsa
   iv) Motar mai ta sauke fetur
   v) [an kasuwa mai nagarta ya ci riba.

**AIKI NA II**

1) Wata yarinya mai jan zani ta ci jarrabawa.
2) Idan an raba jumla gida biyu a nan ne ake samun ~angaren ma'aikaci wato
3) aikau da kuma ~angaren lamari misali: masu azumi/sun sha ruwa
4) Talen hula/fara ya shiga shagona
5) (Aikatu) (Lamiri)
6) Ba za a iya samun jumlar marar yankin suna ba sai dai ganga.

**AIKIN GIDA**

1) Tsarin jumlar Hausa ya }unshi yankin suna da yankin aikatau, a inda yankin suna ya }unshi siffatau da suna da wani siffatau ]in, sannan yankin aikatau ya }unshi aikatau da gurbin aikatau ]in
2) A ~angaren ma'aikaci na jumlar Hausa ana samun yankin suna ne.
3) Bambancin lamiri da yankin aikatau shi ne, a nahawun gargajiya ne ake kiransa lamiri amma a nahawun zamani yankin aikatau ake kiransa.
4) Babu shakka yankin suna za iya ]aukar siffatau kamar **ba}a:**
   i) sarki
   ii) wani sarki -
   iii) wani sarki mai fara'a
   iv) wani irin sarki mai fara'a.

**KASHI NA: 3 SASHEN AIKATAU**

**AIKI NA I**

1. Aikatau shi ne wasu suke kira fi'il i wato aikin da aka yi a cikin jumla wadda ke ]auke da aikatau
2. Kar~au shi ne suna wanda ya wanzu a cikin yankin aikatu wato ma'aikaci na jumla
3. Misalan yankin aikatau guda biyar su ne kamar haka:
   suka sayi mota

   ya fita waje

**AIKI NA II**

1) Gurbin aikatau shi ne yanki a cikin yankin aikatau wanda ya }unshi wakilin suna da aikatau
2) Gurbin aikatau iri biyar su ne kamar haka:
   **i)** **ta** ]auko
   **ii)** ya fito
   **iii)** sun mayar
   **iv)** ta zauna
   **v)** ya saka
3) Misalan gurbin aikatau a cikin yankin aikatau guda biyar su ne kamar haka:
   **i)** **ya fasa** kwai

ii) **ta daka** tsawa
iii) **suka taya** muma
iv) ta **dafa** wake
v) **ya ha]a** kai

**AIKIN GIDA**

1) Jumloli masu aikatau guda biyar su ne kamar haka:
   i) Musa ya **ha]a** wanki
   ii) Sa'adiya ta sauka daga mota
   iii) Shanu suna hu]a da garma
   iv) Audu ya **kunna** Rediyo
   v) **Halima ta bugo waya.**

2) Bayanin yankin aikatau a cikin jumla shi ne, shi dai yzzzu Wan aka raba jimlar Hausa zuwa manyan sassa guda biyu, idan ka cire yankiri suna, ragowar abinda ya rage shi ne yankin aikatau:

3) Jimloli gudo hudu masu gurbin aikatau su ne kamar haka:
   i) **Amadu ya tafi** kasuwa
   ii) Hassan ya **kasa** dankali
   iii) Haibibu y**a fara** hakori
   iv) Zainabu tana **wanke** kaya

4) Ai katau guda goma su ne kamar haka:
   i) sara
   ii) sayi
   iii) yank a

**FASAL1 NA 3: Nahawu Da Milani Da Shi**

(i) saka
(ii) kama
(iii) gaya
(iv) caka
(v) daga
(vi) ha]a.

**KASHI NA 3: JUMLOLI MASU HARSHEN DAMO**

**AIKI I**

1. Jumlar Hausa mai harshen damo tana da tsari na kalmomin mnusamman cikin wata }ira mai bin }a'idar harshe domin fitar da wani furuci mai ma'ana fiye da guda. Ga misali:

   "Yaran Halima da Fati sun makara"

2. i. Audu ya sari Bala
   ii. Musa ya san mota
   iii. Ya kama hannunta\
   iv. Maganar kande ta dami Audu
   v. Farautar Zaki na da dadin kallo

3. Abin da ya banbanta jumla mai harshen damo da kuma wadda ba ita ba shi ne, ita wadda ba mai harshen darno ba tana da sau}in fahimtar ma'anar sa}on da ke cikin jumlar. Ita kuwa mai harshen damo tana da ma'ana ta sarari da kuma ta ~oye, saboda haka sai an nazarci jumlar sosai.

4. Dangane dá sigar jumla mai harshen damo, galibi akwai abubuwan da ke sa a ce jumla kaza tana da harshen damo, ba kamar wadda ba ta da shi ba. Saboda haka ita wannan jumla tana }unsar ma'ana guda biyu ko fiye, wato ma'ana guda biyu ko fiye, wato ma'ana ta ~oye a kuma ma'ana ta sarari.

5. (i) Ma'ana ta sarari ita ce wadda ake fahimta ba tare da wahala ba. Nan take ma'ana ke bayyana
   (ii) Ma'ina ta ~oye ita ake wahala kafin a fahinci ma'ana gaba ]aya

6. Yadda jumla mai harshen damo ke faruwa shi ne, da farko idan kana da jumla kamar "Musa ya san mota" to abin da zai fara zuwa shi ne ma'ana ta sarari. Bayan wannan kuwa wata ma'anar ta ~oye tana samuwa daga gareta. Daga misalin sai mu ce ko dai Musa ya iya mota a matsayinsa na direba ko kuma yana da ilmin sanin komai game da mota.

**AIKIN G1DA**

1. A nahawun harshe, kalmomi ne ake tsarawa cikin wata kira mai ma' ana tare de bin }a'ida domin samar da zance mai ma'ana. Wannan mataki shi ne na jumla. Saboda haka jumla mai harshen damo tana daga cikin jumlolin Hausa wadda ta }unshi tsarin kalmomi na musamman domin fitar furuci mai ma'ana fiye da ]aya. Galibi, ita tana da ma'ana ta sarari da kuma ta ~oye.
2. Jumla mai harshen damo tana da na'anoni iri biyu kamar haka:
   i. Ma'ana ta sarari.
   ii. Ma'ana ta boye.
3. Jumla mai harshen damo tana faruwa a lokacin da aka fahimci ma'ana fiye da guda, Idan haka ya faru, to ma'ana guda ta saranri ce, guda kuma ta ~oye. Ga misali; "Audu ya sari Bala" na iya zama Audu ya yi amfani da makami ya cuta ma Bala, ko kuma ya yi amfarn da baki ya fa]i wani abu da bai kamata ya fada ba game da Bala.
4. i. Nahawun harshe shi ne yadda tsarin wannan harshe yake, watau yadda kalmominsa suke, a yadda suke ha]uwa da juna cikin tsari domin su ba da ingantattun jumla
   ii Kalma ha]aka pe ta ]ai]aikun Saututtukan harshe cikin tsari domin samar da kalmomi daban daban. Ga misali:
   Noma
   Gona
   Tufafi
   Ruwa
   Tuwo
   Jumla ita ce jerin kalma cikin magana ma i ma'ana. Ga misali;
   Audu ya tafi gona
   Kande ta dafa tuwo.

**KASHI NA 5: RARRABA SUNAYE, TSAMO SUNAYE DA GANO SASSAN JUMLA**

**AIKI**

1. a. Aliyu, Rakiya, Ahmad, Asma'u, Hauwa
   b. Kafancan, Turai, Jamus, Maiduguri, Ma}arfi
2. Muhammadu sunan yanka ne, Auwalu la}abi ne da yake nufin na farko
3. Mangwaro, ka]anya, durumi, }irya, giginya, rimi
4. a) Danladi - Wanda aka haifa ranar
   b) Wadata- Idan an haifi yaro a lokacin da aka samu wadata ko yalwar wani abu.
   c) Tanko; Yaron da aka haifa bayan an haifi 'ya'ya mata
   Ciwake: Idan an haifi yaro lokacin roron wake.

**AIKI NA II**

1. Labbo, Birnin Magaji
2. Jumu'a Shinkafa
   Mutum Wake
   {auye Nama
   Hannu Ku]i
   Yunwa Ha}uri

**AIKIN GIDA**

1. Sunan yanka shi ne sunan mutane wanda aka ra]a musu tun suna jarirai. Misali. Hadiza, Sa'adatu.

Umaru ko kuma sunan wani kafaffe ko tabataccen wuri misali. Kazaure, Rijiyar Zaki,.Damaturu

2. a. "Dabbobi, Tsuntsaye da }wari; Ra}umi, Bushiya
   b. Fitattun abubuwa; Tsintsiya, Murhu
   c. |oyayyun abubuwa; Mugunta, Yunwa
   d. Dun}ulallen suna; Bishiya. Dabba
   a. i. [an farin yaro
      ii. Halima mai tuwon 'yan gayu
      iii. Wata sabuwar mota fara
      iv. Wani ba}on malami
      v. [an gurgu -mai gemu
      vi. Aliyu mai doki ya wuce gida
      vii. Fatima 'yar masu masa ta sayi fura
      viii. Miko dogo ¸ya huge All I3akura
      ix. Farar akuya gurguwa ta cinye gari
      x. Mai barci ya farka

3. Wata rana Aliyu ya tashi da safe ke nan sai Alhaji Musa ya aiko yarsa Halima ta kawo masa makullin motar da zai tu}a ya kai 'yan matan amarya Kano'. wajen, bukin sa lalle.

Da ya fito da motar daga gareji sai ya lura tana bukatar a }ara iska a tayoyin gaba. Sai ya aika a fa]a wa matan cewa su jira shi, har ya tafi shagon Sambo mai faci don a cika tayoyin. Bayan ya dawo ne sai suka shiga mota, ba su tsaya ko'ina ba tun tashinsu daga Kaduna sai Zariya, inda suka tsaya don yin sallar. La'asar.

## KASHI NA 6: NAZARIN GININ KALMA

### AIKI I

1. Ga~a
2. kalma
3. i) ma-ga-na
   ii) ma-gan-ga-nu
   iii) Al-mu-baz-za-ran-ci
   iv) gi-d
   v) SO

### AIKIN GIDA

1. kalma lafazi ce mai dun}ulalliyar ma'ana da ake rarrabewa wajen rubutu,
2. Ta hanyar lura da filaye da Aka bari a cikin rubutu.
3. a) suna kalma ce mai nuna la}abi da ake yi wa abu
   b) kalma ce da ke nuna aikin da aka yi cikin jum1a
   c) sifa kalma ce da ake amfani da ita don }arin haske game da suna.

## KASHI NA 7: IRE-IREN ADON HARSHE

### AIKI NA FARKO

1. **Adon Mahe_ na** nufin irin kwalliyar magana da aka yi amfani da ita a cikin magana tun ma ba adabi ba. Misalansa su ne:

   Kamantawa
   Mutuntarwa
   Karin magana
   Habaici
   Ba}ar magana
   Siffantawa
   {arangiya

**AIKI NA BIYU**

1: karin magana wata magana ce dun}ulalliya wadda ta }unshi hikima da ma'anoni a cikinta.

2. }arfafawa ha nnfitt maimaita wata kalma a cikin zance don a nuna fa'idar abin Ake magana a kai. Wani lokacin ma maganar ake maimaitawa gaba ]ayanta.

3. mutuntarwa na nufin a ba wani abu mara rai ]abi'a irin na ]an adam domin a Mutunta shi.

**AIKIN GIDA**

1. Habaici na nufin yi da muturn a fakaice ba tare da an ambaci sunansa ba

2. Kamantawa na nufin yadda ake kamanta abubuwa biyu, wa]anda ba ]aya suke ba. Yana amfani da wasu kalmomi kamar su kamar, I, tamkar da sauransu.

**KASHI NA 8: AMFAN1 DA ADON HARSHE**

**AIKI I**

1. [aukan abu rnaras kyau ba tare da mutum ya sani ba.
   Dauka sosai.
   wawa.

**AIKI II**

1. a. shakulatin ~angrgo
   b. karya guiwa,
2. a. [aurin batar makafi
   b. dutse hannun riga.
   c. Baki ba farsa.

**AIKIN GIDA**

1. Adon harshe
2. A. ranka ya da]e, ai ya amshi mabu]i gun zakara'(Gan]oki shafi na 17)
   c. `kaito! Yaro man kaza. sai na ji Gagarau ya }ara (Gan]oki shafi na 17)

**KASHI NA 9: NAHAWU A TA{AICE**

1. Nahawu shi ne sanin }aidojin harshe
2. Nahawu ya kasu kashi biyu
3. Bayyanannan nahawu shi ne wanda malamai masu koyar da harshe suke da shi. Suke fe]e duk wata kalma ko jumla domin su san }a'idoji harshe.

**AIKI II**

1. Sunaye su ne kalmomin ambato
2. (i) sifa kalma ce mai }arin bayani game da sunaye
   (ii) wakilan suna kalmomi ne masu tsayawa a madadin suna.
   (iii) bayanau su ne kalmomi masu karin bayani ga aikin da aikatau yake nunawa.
   (iv) mafayyaci kalma ce da ke bayani a kan nisa ko kusancin mai magana.

**AIKIN GIDA**

1. Nahawu shi ne sanin }a'idojin harshe
2. (i) Abubakar, malam, Binta, Yaro
   (ii) akuya, kura, kare
   (iii) Kano, kasuwa, tasha
3. Bayyananuan Nahawu ' kamar yadda bayaninsa yake a cikin littafin ' *Sabuwar Hanyar Nazarin Hausa Don {ananan Makarantun Sakandare* na su zarruk, R.M. shi ne salo da }a' idoji da hanyoyin da ake bi ana warware kalmomi da ake fe]e su kamar yadda bakanike ya ke yiwa }arfe.

Wannan kuwa sai wanda ya je wajen malarni ya zauna a }arkashinsa ya sami wannan ilmi ke iya yin wannan bayyanannan nahawu.

4. (i) siffa kalma ce mai }arin bayani game da sunaye
   (ii) Wakilin suna kalma ce da ake amfani da ita a 'madadin suna. Watau kalmomi da ake amfani da su a maimakon-suna misali, **shi** da **ni** da **ita** da **kai** da **mu** da sauransu,
   (iii) Bayanau su ne rukunin kalmomi masu }arin bayani a kan aikin da aikatau yake nunawa.

**KASHI NA 1: AMFANIN ADABIN BAKA GA AL`UMMA**

Adabin baka wani nau'i ne na adabi da ke }unshe da maganganu ko zantuka na hikima da suka fito daga bakin Bahaushe. Adabin baka kan sa nisha]i da annashuwa.
Adabin baka kan taimaka wajen ilmantar da al`umma
Kowa ya ga na gida, ya ~ata ahu, (na nuna zumunci).
Bawan damina attajirin rani, (ke bayyanna sana'ar noma).
Maganganun kakkarya harshe. Kacici-kacici
Wasannin yara

**AIKIN GIDA**

(1) - Zaurance
Habaici
- Karin-magana ;

(2) Da kwa]o da }ato suka je yawon }oto
– }ato yai }oto, kwa]o yai }oto..
– suka yi katako-katako.

Wa zai }wace wa wani }oto?
{ato ne zai }wace wa kwa]o }oto?
Ko kuwa kwa]o ne zai }wace wa }ato }oto?

(3) Adabin baka kan taimaka wajen koyar da tarbiyya ga yara.
Adabin baka kan zama abokin hira.

(4) - Abdu: Kututture uku gagara ]auri.

Musa: Kwai.
Abdu : Abu ]il ya saukar da mai gari daga kan doki.
Amsa: Fitsari
Abdu: Matana guda uku: [aya raguwa ce.
Amsa: Toka.

**AIKI I**

(a) Tatsuniya iri biyu ce, tatsuniyar kacici-kacici da tatsuniyar labari.
(b) Ana aiwatar da tatsuniya ne da dare.
(c). Wannan jumla ana amfani da ita a lokacina aka zo }arshen tatsuniya.

**AIKI II**

Abin da ya bambanta almara da sauran labarai,shi ne, ita almara bayan an kare ta sai an yi tambaya, sauran kuwa ba su da tambaya.

**AIKIN GIDA**

(a) Tatsuniya wani labari ne }agagge da Hausawa suka tsara tun kaka da kakani domin koya wa 'ya'yansu dabarun zaman duniya.
(b) Dagacikin labarun zube akwai almara wadda ita ke }arewa da tambaya da kuma hikaya wadda ita an fi yin ta a wuraren malamai.
(c) Tatsuniya tana da mabu]i wato "gatan-gatanku" da marufi wato "}urungus kan kusu" da kuma taurarin da suka ha]a da halittu da babu su, kamar batorami.
(d) Batorami na fitowa ne a matsayin tauraro a cikin tatsuniya.

(e) Samari su ne suka fi aiwatar da almara.

**KASHI NA 3: MA'ANAR KACICI-KACICI DA RABE-RABENSA**

**AIKI I**

(i) Kacici-kacici tatsuniya ce mai tambaya da-amsa.... .

(ii) Ta rabu gida biyu. Ta wasan cinke da ta wasa }wa}walwa.

(iii) Ana yin ta da dare bayan cin abinci.

(iv) Yana cewa, na ba ka gari. •

(v) Yana koya mana sarrafa harshe da dabarun sadarwa da tunani da kuma al'adun Hausawa.

**AIKI II**

(i) Za Su Fatauci

(ii) A Cikin Kogi -

(iii) [an Sarkin Gani

**AIKIN GIDA**

(i) Tambaya: uku-uku ta gama gari Amsa: murhu

(ii) Tambaya: 'yar ba}a jakar mata

Amsa kujera

**KASHI NA 4: KARIN-MAGANA**

**AIKI I**

1. Karin magana wani ta}aitaccen zance ne mai }unshe da hikima irin ta Hausawa.

2. a) - Da muguwar haihuwa gara kyakkyawar tusa.

Abin da ake nufi da wannan karin magana shi ne da mutum ya haifi ]a lalatacce gara ma ba a haife shi ba. Kai tusa mai wari ma ta fi shi. Idan gemun ]an`uwanka ya kama wuta sai ka yayyafa wa naka ruwa. Abin da ake nufi da wannan karin magana shi ne saboda shi Waziri ya ga yadda ]an sarki ya lalace shi ya sa ya ]au matakai kar shi ma ]ansa ya lalace.

**AIKI II**

1. Sigogi uku na karin magana su ne:

karin maganar da ba sai mai kawo ta ya cike sauran sashin }arshe ba;

– wadda mai sauraro ne zai kawo sauran sassanta;

– wadda ta }unshi labari.

2. Wani yaro ne aka ba shi aikin gida. Da zuwan babansa sai ya fara murna yana zaton zai yi masa aikin ne. Sai kuwa uban ya ce 'kai kuma da zuwan sarkin fawa sai miya ta yi za}i"?

3. Karin magana mai }unshe da mutum su ne:

– abin wani bai ta~a yi wa wani magani.

– abin na yi ne an biya wa bazawara Hajji.

a ]aga sama an yi wa wada }wace

**DABBA**

Ature ba shi raba kare da kura.

A lokacin da mage na nan ~era ba ya wasa

Ba hali bera ya je kasuwa.

**SANDARARREN ABU**

– Annurin fuska kaurin hanji.

- A dingi zuwa rafi, wata rana a fasa tulu.

– Idan jifa ya wuce kanka ko kan wa ya fa]a.

**KASHI NA 5: MANUF0F1 DA MUHIMMANCIN WA{AR BAKA GA HAUSAWA**

**AIKI I**

(a) Manufar wa}o}in tatsuniya ita ce tabbatar da abin da ake koya wa yaro a cikin tunaninsa.

**(b)** Mata kan yi wa}o}insu ne da manufar furta abin da ke damun su a cikin rayuwarsu.

**AIKI II**

(a) Wa}ar baka rumbu ce ga Bahaushe domin adana harshe, saboda cikinta ne ake samun duk wata tsohuwar kalma wadda ta shafi al'adu.

(b) Hukuma na amfani da wa}ar baka a cikin al'ummar Hausawa ta hanyar sadarwa da kuma wayar da kai.

**AIKIN GIDA**

(a) Manufafofin da ke da dangantaka da wa}ar yara su ne:

i. tabbatar da wani abu a cikin tunanin yaro;

jawo hankalin yaro ga wani abu da ake koya masa.

(b) Manufofin wa}ar reno ita ce nuna }auna ga jariri da kuma fitar da wata damuwa da ke cikin zuciyar uwa.

(c) Manufar wa}ar fada ita ce fito da martabar wanda ake yi wa wa}ar.

(d) Wa}a ga Bahaushe tana da muhimmanci kamar haka:

i. koyarwa;

ii. adana harshe;

iii. garga]i; da

iv. sadarwa.

**KASHI NA 7: RABE-RABEN MAKA[AN HAUSA**

**AIKI 1**

| Sunayen Maka]an Fada | Sunayen Maka]an Jama`a |
|---|---|
| 3. a. Musa [an}wairo | Alhaji Mamman Shata Katsina |
| 4. Naramba]a | Amadu Doka |
| 5. Sa`idu Faru | Garba Liyo |
| 6. Salihu Jan-ki]i | [an-Maraya Jos |
| 7. Mamman Sarkin Taushin Katsina | Babba Mai Goge |
| | Garba Sufa |
| | Muhammadu Ganga-ganga |

**AIKI II**

1. `yan kama. Dalili kumwa shi ne sun }ware wajen iya kwaikwayo. Misalin wajen da suke koyon malamai suna cewa:

"wa atsokakum tsoka zalla malam
wa wajiyakum da wajiya

Idan kuwa `Yan gambara ka ]auka. Dalili shi ne sun }ware wajen wajen iya ba'a.

**AIKIN GIDA**

1. Kamar yadda Zurruk ya bayyana ki]a yana nufin wanzar da dada]an amo daga abubuwan bugawa ko gogawa ko busawa ko kuma girgizawa.

2. Maka]an Fada. Saboda su ba sa yi wa kowa ki]a sai uban-gidansu ko kuma idan shi uban-gidan ya ba su izini na su yi wa wani. Za kuma a ce rashin cikakken `yancin ya faru ne saboda masarautar da suke yi wa ki]a ta ]auke nauyin cinsu da shansu da tufafinsu da sauransu.

**KASHI NA 8: NAU'O'IN WA{O{IN MAKA[AN HAUSA**

**AIKI I**

1. (a) Mamman Sarkin Taushin Katsina wa}ar Sarkin Zazzau.
(b) Alh. Musa [an}wairo wa}ar *Sarki Kano Ado*.

**AIKI II**

1. ]alibi ya fa]i sunan mawa}i ya kuma rubuta wa}o}in da suka fi burge shi ko da ]iya daidai ya kawo.
2. (a) [an-anace wa}ar *Ado [ankure* da wa}ar *Shago*.
(b) Hamisu mai ganga wa}ar *Sabo Wakilin Tauri*.

Idan ka rubuta ire-iren wa}o}i da ka ji to ka ci ~angare guda na tambayar. Haka kuma idan ]aya na wa}ar jama'a da ta sana'a da ta sarakuna, to, ka ci.

**KASHI NA 9: DARUSSAN DA WA{O{IN MAKA[AN HAUSA KE KOYARWA**

**AIKI I**

1. Tana koyar da ri}o ga al'adun gargajiya.
2. Hakkin maigida guda shi ne kai ruwan wanka. Hakkin uwargida kuwa shi ne maigida ya ba ta tufar sawa.

**AIKI II**

1. Tsare-tsara da tsattsame da tsattsara da tsantsame da tsari da tsaf da tsamiya.
2. " Tunku]a tunku cikin tukar rukubu tuku]in Sambo yai tu~us"

**AIKIN II**

1. A'a, ban yarda ba .
Suna koyar da darussa masu amfani ga jama'a. Misali wa}ar
[an-Maraya Jos ta aure tana ]auke da nasiha ga miji da matarsa. Haka wa}ar Haruna Oji na wayar wa jama' a kai don su fahimci sabon ku]i.
2. Ri}e al'adun gargajiya muhimmin abu ne ga kowace irin al'umma domin ta haka ne za ta ri}e tarihinta kam-kam. Da zarar al`umma ta yi watsi da al`adunta na gargajiya to sai ka samu cewar ba}in al'adu sun yi katutu. To, irin wannan ci gaba shi Hausawa ke ba la}abi da "ci gaban mai hakan rijiya".
Misalin wa}a mai nuni da a ri}e al'adun gargajiya ita ce wa}ar [an}wairo.
3. Wa}ar Haruna Oji tana wayar da kai ne. A cikinta ya bayyana alamomin da suke jikin sababbin ku]i saboda mutane su ri}a tantance matsayin kowane.

**AIKI I**

Adabin baka ma'adanar hikimomin Hausa ne a cikin tatsuniya, labari, almara, wa}e-wa}e da karin magana, kacici-kacici, salon magana duk domin ilmantar da yara al'adunsu, harshensu, na nisha]i da tarbiyyar yara baki ]aya, da tarihin kakaninsu.

**AIKI II**

1. Tatsuniya dai }agaggen labari ne kawai ]auke hikimar koyar da wani abin amfanin rayuwa. Labarin zube ko in biyu ne - na almara don a wasa }wa}walwa a gano ]aya abin da da ya fi wani ]ayan ko fiye da ]aya na hikaya kuma na malamai don a koyar da martabar wani ko wani abu na tarihi:
2. Almara dal labari ne tsantsa mai tambaya a }arshe don a gano ]ayan da ya fi: kacici-kacici kuma tana neman a wasa }wa}walwa ne, ita ma hanya biyu ce: ta cinke ko ta tsagwaron wasa }wa}walwar.

**AIKI III**

Kacici-Kacici bayani ne da ake neman mai sararo ya gano ma'ana. Salon magana kuwa akan so mutum ya yi }o}arin fa]in wata sar}a}iyar magana ce, idan ya kasa a yi dariya ko kuma ya fa]i magana mi}a}}iya amma komai ya gama maimaitawa ya ~ata zance da zagi ko kuma batsa ba tare da ya sani ba a ba da misaiai da kanka.

**AIKI IV**

Ana son ka lissafa duk mawa}ini da ka tuna da shi amma kuma ka fa]i ko wane irin maka]i ne kamar Sani Aliyu [andawo – Maka]in Fada.

**AlKIN GIDA**

1. Ana son ka fa]i cewa tatsuniya ma labara ce sai dai ko yaushe }agagge. Ana zube, ba lallai ne ya zama }agagge ba. Kana iya maganar bu~e tatsuniya da rufe ta a nan.
2. A nan ma ana son ka kawo misalai da kanka. Misali, Ibrahim Nahabu, wa}ar Murtala Muhammad a kan Ta'aziyya.

**KASHI NA .1: RUBUTAC'CEN ADABI (MA'ANA)**

**AI KI I**

1. Rubutaceen adabi shi ne adabin Hausawa da ya wanzu a rubuce.
2. Hanyoyin su ne ajami da boko
3. Adabin Hausa ya kasu zuwa gida biyu muhimmai: adabin gargayiya da kuma adabin zamani

Adabin Zamani shi ne adabin da ya tara bayanin rayuwar Hausawa amma a rubuce. Adabin zamani ya zo ne a cikin Ajami da Boko.

**AIKIN GIDA**

1. Ajami tsarin rubutun Hausa ne ta hanyar amfani da haruffan Larabci.
2. Boko tsarin rubutun Hausa ne ta hanyar amfani da haruffan Turanci.
3. Dalilai su ne: ciniki, addini, binciken yanayin }asa da gudanar da mulki.

**KASHI NA 2: RABE-RABEN RUBUTACCEN ADABI**

**AI KI I**

1. An fara samun rubutaceen adabi ne bayan zuwan Larabawa da kuma Turawa.
2. An fara samun rubutaceen adabi da salon rubutun ajami.

i. Muhimman kaso su ne:

a. Rubutacciyar wa}a

b. Rubutun zube

c. Rubutaccen wasan kwaikwayo

2. Misalan ayyuka na kaso:

a. Rubutacciyar wa}a

i. Wa}ar *{i]aya* ta Akilu Aliyu Wa}ar *Infiraji* ta Aliyu Namangi

*Tabban Ha}i}an* ta Shehu Usmanu.

b. Rubutun zube

i. *Ruwan Bagaja na Abubakar Imam*

ii. *Gan]oki* na Bello Kagara

3. Ana kiran rubutaccen adabi da adabin Zamani

**KASHI NA 3: {WA{{WARAN NAZARIN LITTAFIN WASAN KWAIKWAY0 NA *UWAR GULMA***

**AIKI I**

1. Jigo a wasan kwaikwayo:

Kamar dai yadda Hausawa kan ce "banza ba ta kai zomo kasuwa". To, lallai haka wannan maganar take. A rayuwa, duk abin da mutum ya yi, ai tabbas akwai dalilin da ya sanya shi yin wannan abin. A Wasan kwaikwayo ko ma a adabi, su sha'irai ]in sukan yi sha'ircinsu ne tare da wata manufa, wato wani irin sa}o ne da suke son su fayyatar ga jama'a. Wannan shi ne jigo.

3. Tsarin wasan kwaikwayo ya sha bamban da na zube domin shi dai zube ana tsara shi ne ta hanyar babi-babi, shi kuwa wasan kwaikwayo ta fitowa da kashi ne aka tsara shi. Ana dai amfani da tsarin dukkansu a warware jigo a hankali wato daga abu mai sau}i zuwa babba.

**AIKIN GIDA**

1. A karanci wasannin kwaikwayon *Uwar Gulma* da *Al Ga Irinta Nan.*
2. A wajen kwatanta jigon wasan *Uwar Gulma* da wasan *Ai Ga Irinta Nan*, za a yarda cewa dukkansu garga]i suke yi. Musamman ma kan auren dole. A cikin wasannin duka an wanke yara mata ne wato Halima da Baturiya aka kai su gidajen mazajen da ba su so, kuma ga mazajen mashaya giya, wa]anda ba su san darajar aure ba. Duk wa]annan mashayan ba su barin iyalansu da abinci, giyar dai ita ce ke cinye albashin nasu. Har gwamma Baturiya ma da yake an sake ta bayan ta sha ]an karen wahala da yuwa da ba}in ciki. Ita kuwa Halima mutuwa ta yi a }o}arin ta samu ta yi barci.
3. Idan aka danganta amsar da abin da ke faruwa a yau, za a ga cewa cin hanci dai ya yi katatu a cikin al'ummar yau. Wannan abin ba lalai sai a ma'aikatu ba, har a gidaje ana samu. A cikin wasan *Uwar Gulma* iyayen Halima ai sun kar~i toshiya ne suka bai wa Hayatu auren Halima. A *Ai Ga Irinta Nan,* Gimbiya ce ta ci ku]in yaron a saboda haka dole ta aurar masa da Baturiya.

Baya ga wa]annan, an nuna mana inda Alkali ke nuna zalunci ta hanyar sayar da gaskiya ga mai ku]i, wannan ya bayyana a *Uwar Gulma*:

Ga kuma garga]i kan auren dole, wannan dai shi ya haifar da dukkan matsalolin da suka faru a wa]annan wasannin.

**KASHI 4: FITAR DA JIGON WA{A DA BAYANIINTA**

**AIKI NA I**

1. Marabucin ya jero tunaninsa ne daki-daki yana warware jigonsa. Ya yi ta nuna, halayen `Yargagara tun daga farko har }arshe daidai da abin da ya sau}a}a.
2. {warai banza ba ta kat zmo kasuwa, dole sai da dalili, irin wannan dalilin ne ya sa A}ilu Aliyu ya ]auki al}alami da warka ya rubuta wannan wa}a ta '*Yar Gagara* domin ya farkar da jama'a kan wannan ba}ar ashana }ona gari don ya yi garga]i ma'ishi tare da nuna halayenta na banza, tun da babu abin sha'awa, a cikinta balle har a kusance ta.

**AIKIN GIDA**

Dama shari'ar Musulunci ta hana zinace-zinace, balle har a ce ga wani gida na musamman an ke~e shi ne don matan banza masu yin zina da a ciki.

Marubucin ya nuna wa]annan matan, a matsayin matsiyata duniya da lahira sai fa in sun tuba. To, dama abin da sharia take tabbatarwa ke nan. Idan za a farga a guje musu, da su da kawunansu za su tuba su bar wannan muguwar hanyar.

**AIKI I**

1. Littafin da aka tsara ba a sigar wa}a ba ko wasan kwaikwayo.
2. Tsarin Babi - Babi shi ne littafin da aka kasa kashi-kashi. Shi kuwa ]aya na nufin littafin da aka rubuta shi har }arshe ba a raba shi

**AIKIN GIDA:**

1. Tsarin rubutun zube ya kasu kashi biyu wasu marubuta na rubuta littattafansu ta hanyar babi - babi. Wasu kuma na rubutawa ta hanyar bai-]aya
2. Shi ne rashin tsara tunani ya tafi bisa tsari a cikin rubutun zube.
3. Ya kamata ]alibi a lokacin nazarinsa ya kula da wuri ko wuraren da duk wani abu ya faru. Ya kuma kula da duk wani aiki da wani mutum ya yi a cikin littafin.
4. Littafin *Magana Jari Ce,* an rubuta shi a tsarin Babi - Babi. Littafin *Shaihu Umar* an rubuta shi ne a bi-]aya.

**KASHI 6: F1TAR DA J1GON LITTAFIN ZUBE TARE DA BAYANIN SALON SARRAFA HARSHE**

**AIKI I**

1. Tauraro: shi ne mutumin da ya fito cikin littafin zube. Sa}on marubuci shi ne jigo.

**AIKIN GIDA**

1. Salo
2. Jigo
3. *Magana Jari Ce, Iliya [an Mai}arfi* da *Ruwan Bagaja.*

**KASHI NA 7: NAZAR1N RUBUTATTUN WA{O{1**

**AIKI I**

1. Abin da ya bambanta wa}a da sauran labarai saboda sigoginta, irinsu tsarin baiti da ]ango da rerawa.

**AIKI II**

1. Wa}o}in Madahu su ne na yabon Annabi, su kuma na Soyayya sun }unshi bayyana bege da so.

**AIKIN GIDA**

1. A ta}aice, wa}a na nufin tsararriyar maganar hikima da ta }unshi sa}o cikin za~a~~un kalmomi da ake rerawa.
2. Za~en kalmomi na musamman don wa}a.
3. Wa}ar Ilmi ita ce wadda aka tsara don ilmantar da jama'a. Ita kuwa ta siyasa an shirya ta ne saboda yabon siyasa da mutanenta.
4. Sigogi biyu na wa}a su ne baiti da ]ango.

**KASHI NA 8: {WA{{WARAN NAZARIN WA{A**

**AIKI I**

1. Garga]i da fa]akarwa kan duniya da lahira. Baiti na ,5-6. 10. 22. 23 da sauransu.
2. {war biyar da amsa-amon *-ya*

Akwai Gabatarwa, gundarin wa}ar da kammalawa
Akwai gangara a tsarin ]angogin
[angogin matsakaita ne.
Akwai addu`ar bu]ewa da rufewa.

**AIKI 11**

1. Salon mai sau}i ne, kuma da armashi akwai kamance da }a}ale

Akwai jerin sar}e - baiti 38 ko 39
Akwai manya-manya kalmomi za~a~~u - Baiti 87

Ba yawan tambaya a wa}ar, ba aron kalmomi
Akwai ragi, ko }ari ga kalma da karya }a'idojin nahawu
2. Nuna }warewa wajen iya sarrafa harshe.

**AIKIN GIDA**

1. Duniya ba dindindin take ba, wata rana za ta na]e.
2. Zubi da tsarin wa}a ya }unshi yadda aka tsara ta zuwa baiti - baiti, da yawan layuka, da amsa - amo da yadda aka shimfi]a wa}ar tun daga farko har zuwa }arshe. ,
3. Salo da sarrafa harshe kuwa ya }unshi irin dabarun da marubuci ya yi amfani da su domin jawo hankalin makaranci ga wa}ar tasa da irin gwanintar da ya nuna wajen na}altar harshen Hausa.

**KASHI NA 9: NAZARIN LITTAFIN WASAN KWAIKWAYO**

**AIKI I**

1. Shi ne yadda aka tsara shirye-shiryen `yan wasa a cikin wasan kwaikwayo
2. *Uwar Gulma* na Alh. Moh. Sada da littalm *Wasan Marafa* na Alhaji Abubakar Tunau.

**AIKIN GIDA**

1. ‘Yaw wasa wato taurari su ne mutanen da suka fito a littafin wasan kwaikwayo, ana so ne a kula da
i. halayensu siffofinsu da ayyukan su.
2. Ana tsara littafin wasan kwaikwayo ne kashi - kashi ko fitowa-fitowa.
3. Ana rubuta wasan kwaikwayo da manufofi iri-iri don wayar da kan jama' a
4. Ma'anar wasan kwaikwayo ita ce: aikata wani abu don kwatanta yadda ake yinsa.

**KASHI NA 10: BITA**

**AIKI I**

1. Rubutaccen adabi shi ne, adabin Hausa da ya wanzu a rubuce.
2. An fara da salon rubutun ajami
3. Zubi da tsarin wa}ar *Arewa Jumhuriya ko Mulukiya* shi ne tana da layuka biyu. Wato }war biyu ce ko tagwai.
4. Littafin da aka tsara ba a sigar wa}a ba ko wasan kwaikwayo.
5. Ma'anar wasan kwaikwayo ita ce aikata wani abu don kwatanta yadda ake yinsa.

**AIKIN GIDA**

1. Muhimman rabe-raben rubutuccen adabin Hausa su ne:
   a. Rubutacciyar wa}a
   b. Rubutun zube
   c. Rubutaccen wasan kwaikwayo
2. A Musulunci, shari`a ta hana zinace-zinace balle a ce ga wani gida na musamman an ke~e shi don matan banza masu yin zina da lasisi'. Marubucin ya nuna wa]annan matan a matsayin matsiyata duniya da lahira, sai fa in sun tuba. To, dama abin da shari'a take tabbatar wa ke nan. Idan da za a farga, a guje musu, to da su da kansu za su tuba, su bar wannan muguwar hanyar.
3. Ana rubuta wasan kwaikwayo ne da manufofi iri-iri. Misali, wasan kwaikwayo, ta hanyarsa, ana bayyana wani mugun abu ga jama'a. A nan, a maimakon a ce wa jama'a abu kaza ba shi da kyau, to, sai a sa shi a wasan kwaikwayo a rubuce.
4. Littafi uku na zube:
   *Magana Jari Ce*
   *Iliya [an Mai}arfi*
   *Ruwan Bagaja*
5. A ta}aice, wa}a na nufin tsararriyar maganar hikima da ta }unshi sa}o cikin za~a~~uan kalmomi da ake rerawa.

**KASHI NA 1: TSARIN FASALIN IYAL1**

**AIKI I**

I. Uwa, `ya' ya (yayye da }anne). Sauran `yan `wa da yaran gida.
2. Mahaifiya, wa da }ani, da Uwa.

**AIKI II**

1. Iyaye, yayye, }anne, `yan `uwa
2. Kakanni maza da mata, lyaye rnaza da mata da `yan `uwa maza da mata.

**AIKIN GIDA**

1. Daga miji da mata, a sama akwai iyayensu da kakanni, a }asa akwai `yan`yansu da jikokinsu da Tatta~a kunne da sauransu, a tsakiya ga `yan `uwansu maza da mata.
2. Kakanni, iyaye, yayye, }anne, yan `uwa da yaran gida.
3. Tarbiyya - Koyar da kyawawan ]abi`u
4. Asali - tushe
   Tsaro - kariya
   Hukuma – Al}alanci
   Ha]in Kai - Taimako

**KASHI NA 2: RUKUNAN IYALI DA MATSAYINSU**

**AIKI 1**

1. Manya ko dattawa - Saboda shekaru da siffar jiki.
2. Yara ko matasa - saboda shekaru da siffar jiki.

**AIKI II**

1. Masu hali - saboda yana da ku]i, sannan ga mulki
2. Mafi yawansu suna da ku]i sannan kuma ga mulki

**AIKIN GIDA**

1. Lokacin da mutum ya soma kawo }arfi, ga dai girman jiki ga na murya sannan ya balaga. Kimanin shekarun mutum kan kasance tun daga shekara sha-biyu har zuwa ishirin da biyar ko fiye.
2. Shekarunsa, siffar jiki
3. Masu hali, matsakaita. Talakawa.

**KASHI NA 3: TSARIN SARAUTA**

**AIKI I**

1. Ha]in kan mutane, kare mara }arfi daga masu }arfi, kiyaye martabar dan Adam.
2. Mulki –ri}on ragamar al` amuran jama'a.

**AIKI**

1. Sarkin yanka - sarkin da yake da }asa. Sarautar masu sana'a - mulkinsu ya ta'alla}a ne ga wa]anda ke da sana' a irin tasu.
2. Gado, halayen kirki, za~e

**AIKI III**

1. Sarki - uban }asa, shugaban kowa da kowa, sarauta - mulki ko shugabanci masarauta - }asar da sarki ke mulki to shugabanta

2. Ba da umurni, yin sulhu, yin hukunci, kar~ar haraji, taimakon talakawa, ha]a kan jama'a, nema ma jama'a hakkinsu da sauransu.

**AIKIN GIDA**

1. Daga sarki zuwa Hakimi, zuwa Dagaci, zuwa mai Unguwa, Sannan zuwa sauran jama'ar }asa. Kar~o da ba da umurni, yin sulhu, yin hukunci, kar~ar haraji, hada kan jama'a da sauransu
2. Sarkin Zazzau na da }asa bayan jama'ar da yake mulka
   - Sarkin Zazzau na da ayyuka ayyanannu wa]anda gwamnati ta amince da su.
   - Sarkin Zazzau na aiki a }ar}ashin gwamnati ne, akasin Sarki Magina.
3. Hakimai.

**KASHI NA 4: LABARIN ZUWAN BAYAJIDA**

**AIKI**

1. Saboda ya kashe maciji da ke hana su }ibar ruwa a rijiya.
2. Ranar Juma'a

**AIKIN GIDA**

1. Ayyana
2. Bawo
3. Kano da Katsina da Daura da Zazzau da Gobir da Rano da kuma Biram (Garun Gabas)
4. Zamfara da Kwararrafa da kuma Yawuri

**KASHI NA 5: GADO**

**AIKI I**

1. Gado na nufin mallakar ku]i ko }adarori Wa]anda mamaci ya bari.
2. Lokacin jahiliyya shi ne lokacin da addinin Musulinci bai zo wa Hausawa ba.
3. Magada suna iya gadon duk abin da wanda ga rasu ya mallaka ban da mutane.

**AIKIN GIDA**

1. Gado shi ne mallakar duk abin da mamaci ya bari ban da mutane.
2. Masu gado na iya gadon

i. gona, gida ko mota da sauransu

3. Hausawa na yin addu'o' i ga mamaci bayan wa]annan kwanaki.
4. 'Ya`ya da iyaye da m 'aura da dangi `yan'uwa

**KASHI NA 6: IRE-IREN LAIFUFFUKA A AL`UMMAR HAUSAWA**

**AIKI I**

1. Laifi, shi ne aikata wani abu da ya sa~a wa }a'idar da al`umma ta ajiye domin kiyaye rayuwar jama'a da kuma samun zaman lafiya da kwanciyar hankali da lumana. Ire-iren laifuffuka sun ha]a da sata da lalata da ha`inci.
2. (a) Manyan laifuka biyu na manya sun ha]a da ha'inci ko alguishu ko zamba- cikin-aminci watau bayan an amince wa mutu an ba shi ajiya sai ya ci amanar, walau ta dukiya ko ta magana. Ana kuma ha'inci a sana'a domin a }wari abokin sana'a ta hanyar ba shi abu marasa kyau ko daraja a bisa farashin mai daraja.

   (b) Munafunci ko algungumanci ko annamimanci laifi ne da manya kan yi watau a ]auki maganar wannan a kai wa wancan domin a yi gaba da hatsaniya da husuma.

**AIKIN GIDA**

1. Laifuffuka biyu da manya suka yi tarayya da yara sun ha]a da }arya - watau }ir}iran zancen abin da bai faru ba a ce ya faru a ri}a ya]awa domin neman fice da tagomashi. Yara na yi manya na yi. Haka nan, sata, watau, ]aukar kayan wani ba da izinin shi ba a je a more shi ko a sayar. Sata kuma iri-iri ce akwai yankan aljihu, akwai bin gida, akwai fashi, sai dai yara da manya sun fi tarayya a yankan aljihu.
2. {yuya laifi ne da yara kan yi, watau imma dai babba ya sa su aiki su }i yi ko su sa ganda watau su yi sama - sama, ko kuma yaro ya ki zuwa ko ya ma}e. Hausawa kan ce:
   Laifin yaro }yuya laifin babba rowa.
3. Yara sun fi aikata laifin }arya da yawon banza
4. Tsiwa ita ce a yi wa yaro magana ya mayar da ba}ar magana ko kurna babba yana magana yaro yana amsawa.

## KASHI NA 7: IRE-IREN HORO A AL`UMMAR HAUSAWA

**AIKI I**

1. Ana horo ko ladabtarwa ne domin a hana mai laifi ci gaba da laifin ko don a tsawatar da shi, a gaba da laifi ko dan a tsawatar da shi, a kuma kwa~i mai niyyar aikatawa, saboda a samu al'umma mai nagarta rnai walwala da ha]in kai da zaman lafiya da lumana da }aruwar arziki.
2. Hausawa na amfani da tsari uku wajen horo da ladabtarwa. Watau akwai tsarin - gargajiya wanda yake tun da. Akwai tsarin Musulunci wanda ya sami gindin zama bayan kafa Daular Usumaniyya a }asar Hausa da kuma tsarin Bature Nasara wanda ya kafu tun zamanin mulkin mallaka.

**AIKIN GIDA**

1. Hausawa ida suka kama ~arawo a al`adance sarki kan sa a yi masa waso. A raba shi da iyalinsa a kuma kore shi daga }asa. A zamanin Daular Islama kuma akan yanke hannu zuwa tsintsiyar hannu. Da Nasara ya zo sai aka ri}a ]auri ko tara.
2. A Al'ummar Hausawa idan yaro ya yi laifin akan fara yi masa zuru ko a harare shi, kana a yi masa fa]a a }an}ane shi, idan tura ta kai bango akan yi masa duka da tsumangiya, domin a kwa~e shi ya girma mutum sak.
3. lyayen yaron sukan gode wa mutumin
4. Ana tsoratar da yara har yanzu domin horo.

## KASHI NA 8: DANGANTAKA TSAKANIN LAIFI DA HORO

**AIKI I**

1. Laifi na nufin fandare wa tarbiyya ta gari wadda al'umma ta ke ganin ya sa~a wa tsarinta.
2. Horo a ta}aice hanya ce ta tarbiyya.
3. {arya
4. Laifuka

**AIKIN GIDA**

1. Horo hanya ce ta kyautata rayuwar mutum da shiryar da shi ya zuwa halaye masu kyau da nagarta.
2. A' a
3. Laifukan da yara kan aikata }in zuwa makaranta

## KASHI NA 9: YADDA LAIFI DA HORO SUKA SHAFI YARA DA MANYA A AL`UMMA

**AIKI I**

1. Tsawatarwa da harara da zare idanu, tsare su a gida da hana su abin da ake ganin suna so

da kwa]aita musu abin da ake ganin suna so da dukansu da bulala da tsoratar da yara maza da kaciya ko dodo.

2. Bai dace ba. Saboda shekarunsu ba ]aya suke ba.

3. I, na yarda. Laifi ya kan jawo horo haka kuma horon da aka yi ba daidai ba a maimakon ya kyautata tarbiyyar mutum, to sai ka samu cewar tarbiyyar na }ara ta~ar~arewa.

**AKIN GIDA**

1. Bambanta
2. Halaye da ayyuka
3. Manyann
4. Shawarwari da garga]i da tsawatarwa da gurfanar da su gaban shugabanni.

**KASH1 NA 10: B1TA**

**AIKI I**

1. Shugabanci shi ne zama babba ta hanyar wakiltar al'umma. Kalmar ta samo asali ne daga shugaba.
2. Daga sarki sai Hakimai sai Dagatai sannan sai al'umma.
3. Hausa bakwai: Kano, Zazzau Daura, Katsina, Rano, Biram da Gobir.

Banza Bakwai: Nupe, Kwararrafa, Yarbawa, Gwari, Zamfara, Kebbi da Yawuri.

**AIKI II**

1. Gado yana nufin mallakar duk abubuwan da mamaci ya bari dag dukiya ta ku]i zuwa }addara.
2. Iyaye, `Ya`ya, mata, miji }anni da yayye
3. Ana mallakar abu ta hanyar kyauta da saye da musaya da gado.

**Al KI III**

1. A, Al'ummar Hausawa idan yaro ya yi laifi akan fara yi masa zuru ko a harare shi, kana a yi masa fada a }an}ace shi, idan tura ta kai bango akan yi masa duka da tsumangiya, domin a kwa~e shi.
2. Akwai, karya da ha'inci da sata da karuwanci da shaye-shaye.
3. Akwai tara da ]auri da duka da kwa~o da kuma kora daga gari.

**AIKIN GIDA**

1. Daga Sarki zuwa Hakimi zuwa Dagaci zuwa Mai unguwa, sannan zuwa sauran jama'ar }asa.
2. Asalin sunan Bayajida Abu Yazid baban shi sarki ne a Bagadaza. Da suka yi want tashin hankali sai ya baro }asarsu ya zo Barno, daga nan ya iso Daura har ya auri sarauniyar Daura. Sarauniya ta ba shi }war}wara. Sarauniya ta haifar ma shi `y`aya guda shida da suka yi mulki a gararuwan Hausa bakwai. {war}wara ta haifar ma shi `ya`ya bakwai da suka yi mulki a gararuwan banza bakwai.
3. Mallaka ta na nufin ikon amfani da abu a matsayin na mutum halak - malak. Tana kuma iya zama ta samun abu ya zama }ar}ashin ikonsa.

**KASHI NA1:AL'ADUN HAUSAWA**

**AIKI I**

1. { a' idoj in aure guda uku su ne:

(i) Sadaki,

(ii) waliyi

(iii) Shedu.

**AIKI II**

Sana'o'i na Hausawa guda biyu su ne:

(i) Noma

(ii) {ira

Noma shi ne gyaran gona da yin mata shuka. Bayan shuka ta fito ana nome amfanin gona. Ruwan sama shi ne abin da ke taimakawa shuka ta fito. Hausawa kan dogora kan amfanin gonar da suka samu domin abinci.

ii) Kira ita ce saka }arfe a wuta in ya yi ja sannan a sarrafa shi. Sarrafa }arfe shi ne a }era wani abu da shi. Ana }era takobi da wu}a da lauje. Dukkansu da }arfe ake yinsu

**AIKIN GIDA**

1. Hausawa na ra]a suna ga `ya`yansu domin addininsu ya umurci haka, kuma domin tantancewa.
2. I, Kaciya na da amfani. Amfaninta shi ne }arfin gaba da kuma tsabta. Wato, yin na kara lafiya.
3. (i) Dambe
   (ii) Kokawa, Muhimmancinsu shi ne motsa jiki da kuma }arin }arfi ko da ya}i zai same su.
4. Ma}era na }ero
   (i) takobi
   (ii) wu}a
   (iii) garma.
5. Ana wa gawar musulmi wanka da sailah.

**KASH1 NA 2: AL'ADUN GARGAJ1YA**

**AIKI I**

1. Kwana 360 ko 365 ko 366
2. Shekara 14
3. Mataki hu]u, da jinjira da yarinya, da }wai1a da bera sannan budurwa.

**AIKIN GIDA**

1. Namiji mataki uku daga jariri da yaro da kuma saurayi.
2. Mace kuma mataki hudu, daga jinjira, sai yarinya, sai kwaila, sai bera daga nan sai budurwa
3. Mutum kan shiga }waryar manya daga shekara arba'in.
4. Dattijantaka ba ta }arewa sai in an mutu.

**KASHI NA 3: SIFFOF1 DA MATSAYIN KOWANE RUKUNI GA AL'UMMA**

**AIKI I**

1. Shekara bakwai (7), bayan kaciya
2. Gudumawar da yara ke bayarwa sun ha]a da reno, da shara, da aike, da wanke-wanke, da kuma ]auko ruwa.

**AIKI II**

Suke yawaicin ayyukan }arfi, suke haihuwa.

Shekarun manya sun fara daga arba'in har zuwa shekara sittin na dattawa daga sittin zuwa sama, wato har kwana su }are.

**AIKIN GIDA**

1. Matasa da manya su ne ginshi}in al'umma saboda su ke yin aikin' }arfi, suke haihuwa kuma su ke kula da yadda ake gudanar da ayyukan yau da kullum.
2. Dattawa su ke tabbatar da an yi abin da aya kamata ta hanyar ba da shawarwari da kwa~o in bukutar kwa~on ta taso.

**KASHI NA 04: RUKUNONIN JAMA'A (WASANNI DA, BUKUKUWA DA {UNGIYOYI)**

**AIKI I**

1. Wasanni irin su 'yartsana da lilo da guje-guje da raye-raye a dandali
2. Na aure da suna da kamun kifi da farauta. Ha]a kai da sau}a}a tafiyar da al'umma a gari.

**AIKI II**

1. Wasanni irin na gado misali cin wuta da tauri da dabo
2. Suke shugabantar bukukuwa
3. A'a sukan dai ba da shawara in an bukata.

**AIKIN GIDA**

1. Sukan yi girke-girke da wanke-wanke da talla da ]ebo ruwa.
2. Matasa
3. Ba da shawarwari.

**KASHI NA 5: AMFANIN KOWANE RUKUNI NA ADABI**

**AIKI I**

1. An kasa Adabin Baka gida uku
2. Muhimmin abu da wa}a ke da shi ga al`umma shi ne nisha]antarwa.
3. Ta fuskar tarihi amfanin zube shi ne koyon darasi.
4. Amfanin wasan kwaikwayo a aikace a al'ummar Hausawa shi ne }arfafa zumunci.

**AIKI II**

1. Bayan zuwan Musulunci, masamman kuma bayyanar Shehu [anfodiyo.
2. Don yin garga]i ga jama'a
3. Sun yi bayanai kan tsarin Mulki
4. Wasan kwaikwayo ya yi bayani kan harkar aure da al'amuran rayuwa irin ta yau.

**AIKIN GIDA**

1. Muhimmancin adabi a dun}ule shi ne samun nisha]i ga jama'a da taimaka wa matasa da manya samun sau}in ayyuka. Adabi yana taimakawa wajen }arfafa gwiwar maya}a a fagen fama, da adana tarihi, da }arfafa zumunci da garga]i game da rayuwa na yau da kullum da dai sauran abubuwan da suka shafi rayuwa.
2. Zuwan Turawa }asar Hausa ya kawo rubutun boko. Da rubutun bokon ne aka yi rubuce-rubuce irin na zube, da wasan kwaikwayo wa]anda suka yi garga]I da adana wa Hausawa wasu abuwa da suka shafi tarihinsu da kuma fito da abubuwan da suka shafi tsarin mulki.

**KASHI NA 6: WASA TSAKANIN HAUSAWA DA KUMA WASU KABILU**

**AIKI I**

1. Barkwanci

**AIKI II**

2. a. Bagobiri da Fulani
b. Katsinawa da Nufawa

**AIKIN GIDA**

1. Barkwanci wasa ne da ake yi na magana tsakanin Hausawa da wasu {abilu.

2. a. Ya}e-ya}e
b. Aurattayya
c. Ciniki wato zaman tare.
3. a. Katsinawa da Nufawa
b. Kanawa da Zage-zagi.

**KASHI NA 7: SANA'O'IN GARAGAJIYA**

**AIKI I**

Sana'o' in gargajiya 10 na Hausawa:

(i) Aski
(ii) Dukanci
(iii) Farauta
(iv) Fawa
(v) Jima
(vi) Kiwo
(vii) Noma
(viii) Rini
(ix) Sa}a
(x) Sassa}a.

**AIKI II**

| Sana'a | Kayan Aiki |
|---|---|
| (a) Aski | Aska |
| (b) Fawa | Wu}a, Janta]i |
| (6) Jima | Bagaruwa, majema |
| (d) **Sa}a** | Zare; allura |
| (e) Sassa}a | Gatari, gizago. |

**AIKIN G1DA**

1. Sana'a, wata aba ce wadda mutum yake yoya ya iya, wadda kuma sai da ita ne, mutum yake iya zaman duniya. Sana'a tana da matu}ar amfani ga al`umma kuma akwai sana'o'i in daban-daban. Misali, akwai sana'ar }ira da fawa da rini da dillanci da su da sauransu.
2. Sana'o'in da ake ganin cewa nan gaba za su mutu su ne farauta da rini.
3. Kayan Aiki

**Sana'a**

(a) Aska
(b) Bindiga
(c) Gatari
(d) Wu}a
(e) Zare

Aski
Farauta
Sassa}a, Fawa, Farauta Fawa, Farauta, Dukanci Sa}a, [inki

4. Amfanin Sana'a

(i) Rayuwar mutane ta dogara ne kan sana'o'i. Al'umma ba ta rayuwa sai da sana'o'i
(ii) ]an Adam ba ya rayuwa sosai sai yana da sana'ar yi. Daga sana'ar ne yake samun abin da zai ci na yau da kullum.

5. Ci-gaban zamani na iya kashe sana'ar gargajiya idan kayan da zamani ya kawo sun ]ara wa]anda

ake samu ta hanyar sana'ar gargajiya. Alal misali, zamani ya kawo tufafi masu aminci wa]anda ba su bu}atar a rina su. Idan aka ci gaba da yin amfani da ire-iren wa]annan kaya, to, ka ga ke nan sana'ar rini za ta mutu.

## ACKNOWLEDGEMENT

The National Teachers' Institute is grateful to the following resource persons who at various times contributed to the 2013 revised edition of our course books on the Pivotal Teacher Training Programme (PTTP).

**HAUSA**

**Dr. Balarabe Abdullahi** — **ABU, Zaria**
**Mal. Ahmed H. Malabu** — **FCE, Yola**

The above built on the initial foundation laid by the following writers of the 2000 edition.

1. Adamu Ibrahim Malumfashi
2. Magaji Tsoho Yakawada
3. Abubakar Zakari
4. Muhammad Abbas Aliyu
5. M.A. Dantumbishi
6. Muhammad Lawal Amin
7. Hamza A. Ainu
8. A.A. Dunfawa
9. Balarabe Abdullahi
10. Dr. A.H. Amfani
11. Bello Bala Usman
12. Dr. A.M. Bunza
13. Dr. S.A. Yakasai
14. Dr. Isa Mukhtar
15. Hafizu Miko Yakasai
16. I.G. Satatima
17. Abdulrashid Garba
18. Basher Mansur
19. Dr. B.S.Y. Alhassan
20. Aliyu Musa
21. Dr. Rabi'u Zarruk
22. Ramlatu Jibir Daura
23. Ibrahim Bala Daura
24. Ibrahim A. Liman
25. Prof. Thomas K. Adeyanju

I would like to express my appreciation for the purposeful leadership and guidance provided by Prince S.A. Kolawale, Director, Academic Services, Mr. I.S. Mbaya, Coordinator PTTP, and Emeritus Professor Thomas K. Adeyanju, Principal Consultant to the Institute who coordinated the writing.
Finally, I wish to record the indebtedness of the NTI to the Federal Ministry of Education for its initial support and motivation for getting the programme started.
We also wish to acknowledge the tireless efforts of the staff of Tee Kay Educational Consultancy Services, notably Mr. Ike M. Iromu, Mrs Lisa Shade Mosugu, Miss Jock Ruth, and Mr. Festus Mahmud who handled the heavy computerization, formatting, and draft production.

**Dr. Aminu Ladan Sharehu**

Director General & Chief Executive,
**National Teachers' Institute, Kaduna**